**KIRARIN SARAKI A BAKIN  MATA: NAZARIN ZABIYANCI A {ASAR HAUSA**

**NA**

**HALIMA KABIR DAURA**

**PhD/ARTS/12534/2011-2012**

**September, 2016**

**KIRARIN SARAKI A BAKIN MATA: NAZARIN ZABIYANCI A {ASAR HAUSA**

**NA**

**HALIMA KABIR DAURA**

**B.A (1993), PGDE (2004), M.A ( 2008), ABU.**

**PhD/ARTS/12534/2011-2012**

**A Thesis submitted to the School of Postgraduate Studies, Ahmadu Bello University, Zaria, in Partial Fulfillment of the Requirements for the Award of Doctor of Philosophy in African Literature (Hausa), Department of African Languages and Cultures, Faculty of Arts, Ahmadu Bello University, Zaria.**

**September, 2016**

## Declaration

I hereby declare that the work in this thesis titled "*Kirarin Saraki a Bakin Mata: Nazarin Zabiyanci a {asar Hausa*'' was performed by me, in the Department of African Languages and Cultures, under the supervision of Professor Muhammad Lawal Amin, Dr Balarabe Abdullahi and Dr Magaji Yakawada Tsoho. The information derived from the literature has been duly acknowledged in the text and a list of reference provided. No part of this work has been presented for another degree or diploma at any institution.

-----------------------------------------------------

Halima Kabir Daura,
Department of African Languages and Cultures,
Faculty of Arts,
Ahmadu Bello University, Zaria.
September, 2016.

## Certification

The thesis titled "*Kirarin Saraki a Bakin Mata: Nazarin Zabiyanci a {asar Hausa*" meets the regulations governing the award of the degree of Doctor of Philosophy of the Ahmadu Bello University, and is approved for its contribution to knowledge and literary presentation.

-------------------------------------------------- ------------------------ -----------------
Professor Muhammad Lawal Amin (Signature) (Date)
(Chairman, Supervisory Committee)

-------------------------------------------------- ------------------------ -------------
Dr Balarabe Abdullahi (Signature) (Date)
Member, Supervisory Committee

-------------------------------------------------- ------------------------ -----------------
Dr Magaji Yakawada Tsoho (Signature) (Date)
Member, Supervisory Committee

-------------------------------------------------- ------------------------ -----------------
Dr Salisu Garba (Signature) (Date)
(Head of Department)

-------------------------------------------------- ------------------------ -----------------
Professor Kabir Bala (Signature) (Date)
Dean, School of Post Graduate Studies

## **Sadaukarwa**

Sadaukarwa

ta

Musamman

ga

Fatima Muhammad Sadauki.

## Godiya

Godiya ta tabbata ga Allah (swa), mai kowa mai komai, wanda cikin ikonsa wannan aiki ya zo }arshe. Tsira da amincin Allah su }ara tabbata ga Manzon tsira, Annabi Muhammad (saw), da alayensa da sahabbansa.

Godiya ta farkon fari da jinjina ga jagoran wannan aiki, Farfesa Muhammad Lawal Amin, wanda ya yi namijin }o}ari wajen duba wannan aiki filla-filla, har ya kai matsayin da yake a yau. Allah Ya yi masa sakayya da mafificin alheri.

Ina kuma mi}a godiya ga jagororin wannan aiki, na biyu da na uku, Dr Balarabe Abdullahi da Dr Magaji Yakawada Tsoho saboda gyara da shawarwarin da suka bayar. Na gode matu}a, Allah Ya saka da alheri.

Godiya ta musamman ga malaman da suka jagoranci zaman gabatar da wannan aiki na farko da na biyu, da kuma na uku, Farfesa Munir Mamman da kuma Farfesa Abubakar Aliyu Liman. Na gode, Allah Ya saka da alheri.

Har ila yau, ina mi}a godiyata ga irin shawarwarin da na samu daga malamai irin su Farfesa [alhatu Muhammad da Farfesa Sani Abba Aliyu da Farfesa Tanimu Abubakar da Farfesa Mustapha Gwadabe da Dr Hadiza Ahmad Tukur da Farfesa Aisha Zakari Muhammad (Jami'ar Ahmadu Bello) da Farfesa Aliyu Muhammad Gusau da Dr Ahamad Magaji (Jami'ar Bayero) da Farfesa Ibrahim Aliyu Malumfashi (Jami'ar Jihar Kaduna) da Farfesa Haruna Abdullahi Birniwa da Farfesa Aliyu Muhammad Bunza da Farfesa Atiku Ahamad Dunfawa da Farfesa Salisu Ahamad Yakasai da Dr Bello Bala Usman da Dr Ibrahim S.S. Kontagora da kuma Dr Yakubu Gobir (Jami'ar Usmanu [anfodiyo,Sakkwato).

Ba zan manta da abokan karatuna na digiri na farko ba, kuma abokan aikina a yanzu, Dr Salisu Garba Kargi da Dr Shu'aibu Hassan, domin sun ba da gagarumar gudunmuwa na shawarwari, wa]anda suka taimaka ga cim ma gaci. Allah Ya saka, Ya kuma bar zumunci.

Godiya ga malamaina da sauran abokan aiki a wannan jami'a, irin su Malam Adamu Ibrahim Malumfashi da Dr B.S.Y Alhassan da Dr Haruna Aminu da Dr Isa Sulaiman da Dr Yahuza M. Imam da Malam Ibrahim Khalil da Malam Muhammad S. Usman da Malam Abubakar M. Sarki da Malam Shu'aibu A. Alhassan Dr Hauwa Muhammad Bugaje da Malam Rabi'u Muhammad Tahir da Malam Abubakar Ayuba da Malam Adamu Shede da Malam Abdulmalik Aminu da Malam Aminu Abubakar da Malam Jibrin Dambo da kuma Malam Halliru Abubakar.

Ba zan manta da addu'ar fatan alheri da gudunmuwar iyaye da 'yanuwana ba, domin haka nake isar da godiya mai ]imbin yawa ga iyayena, Alhaji Muhammad Kabir Daura da Hajiya Bintu. Sannan da yayyena, Zainab Ali Kotoko da Fatima Shettima. Sai kuma }annena, Arch Musa K. Daura da Hafsat K. Daura da Asma'u K. Daura da Abdulrazak K. Daura da

Rabi K. Daura da Fatima K. Daura da  Mustapha K. Daura da kuma Aisha Kabir Daura. Allah Ya bar zumunci da }auna.

Haka kuma, ina godiya ga sauran iyaye da ‘yan’uwa irin su Sarkin Sudan Daura, Alhaji Nalado Yusuf da Engineer Muhammad Abdulfatah da Hajiya Murjanatu Muhammad da Alhaji Umaru Sanda da Farfesa Sulaiman Dangana Abdul da Babana Alhaji Shu’aibu Ba}o ([anmasanin Suleja) da Alhaji Yunusa Katamba da Alhaji Haruna Ahmad (Madakin Toto) da Hajiya A’isha Ahmad Hussaini da Dr Ramlatu Jibir Daura da Farfesa Sadiyya Sani Daura da Dr Salamatu Idris Isa da Dr A’isha Ahmad Umar da Dr Maryam Dewu da Pharm Maryam Abdullahi da Hajiya Bassama Bello Alhassan da Hajiya Fa’iza Tukur Bello da kuma Malam Isma’il Sanda.

Ina mi}a godiya ta musamman ga maigidana, Alhaji Muhammad Sadauki (Majida]in Madakin Toto),wanda ya bayar da gudunmuwarsa ta fuskoki da dama da suka ha]a da ha}urinsa da juriyarsa da goyon bayansa da agajinsa, domin ganin aikin nan ya cim ma gaci.

Ba zan yi tuya in manta da albasa ba, godiya zuwa ga ‘ya’yana: Fatima (Ummi) da Zainab da Muhammad Kabir (Amir) da Muhammad Rabi’u (Abba) da Fatima (Iman) da Halimatul Sadiya da kuma Muhammad Kabir (Khalifa). Allah Ya yi masu albarka.

A  }arshe,  ina mi}a godiya ga dukkan al’ummomin fadar da na ziyarta, irin su fadar Kabin Argungu da Daura da Ha]eja da Kano da Katsina da Kazaure da Mara]i da Sakkwato da kuma Zazzau. Babu shakka na sami ha]in kai da goyon bayansu matu}a. Allah Ya saka masu da alheri.Ina kuma godiya ga Malam Yahaya da ya buga wannan aiki tare da dukkan ]alibaina a wannan jami’a, musamman Malam Rabi’u Bashir da Aliyu Rilwanu da Falama Bello da Najiyullah A. Tijjani da ]an’auta Mubarak Idris.

## Abstract

The study, entitled 'Praise Epithet: An Analysis of Female Royal Praise Singers' like numerous others, aims at examining the folk culture of the Hausa people from a literary perspective, through the application of ethnographic theory for analysis. As a systematic theory that notes cultural practices in any given society. The study draws its data from six Hausa Emirate Councils: Kabin Argungu, Daura, Kazaure, Kano, Hadeja and Zazzau. The study therefore discusses the theme, style and structure of the text to analyses the import of the praise epithets. The theme, which is largely panegyric, eulogizes the Royal Lords with five variable; genealogical pedigree, bravery and capacity to face up challenges, ability to guide his subjects and protect their religion, administrative qualities and generosity towards the needy. In effect; the research further affirms that literature is a mirror that reflects the socio-political as well as the history and life of a community. Similarly, the work documents that women are also a factor to be reckoned within a Hausa Court.

# Tsakure

Wannan nazari, mai taken ‘Kirarin Saraki a Bakin Mata: Nazarin Zabiyanci a {asar Hausa”, ya yi amfani da kirarin da Zabiyoyin Fada ke yi wa saraki domin fito da tunanin Bahaushe game da saraki da sarauta a {asar Hausa. Binciken ya yi amfani da ra’in tarihin al’umma, ya zagaya fada shida na Kasar Hausa: Kabin Argungu da Daura da Kazaure da Kano da Hadeja da kuma Zazzau, domin samo kirarin da Zabiyoyin Fada kan aiwatar, aka nazarci jigo da salo da kuma zubinsa. Daga jigon kirarin, kamar yadda aikin ya gano cewa yabo ne, Zabiyoyin Fada suna yabon Saraki da abubuwa biyar :tarihin asali, da iya rikon jama’a da jaruntaka, da tabbatar da addinin al’ummarsu, da kuma kyauta. Wa]annan duka, sun bayyana a kirarin, wanda ya }ara tabbatar da cewa idan ana neman al’adun al’umma da ma tarihinsu da zamantakewa da siyasa, adabi ne taskar da ke adana su. Kamar yadda aka gani daga jigon kirarin da aka nazarta.To, haka kuma aikin ya gano cewa hatta a Fadar Hausa, an san da zaman mata saboda irin gudunmuwar da suke bayarwa

## Qumshiya

Cover Page……………………………………………………………………………i

Declaration ............................................................................................................ ii

Certification........................................................................................................ iii

Sadaukarwa .......................................................................................................... iv

Godiya ................................................................................................................... v

Abstract ............................................................................................................... vii

Tsakure ............................................................................................................... viii

Qumshiya.............................................................................................................. ix

BABI NA [AYA...................................................................................................... 1

SHIMFI[A ............................................................................................................... 1

1.1 Gabatarwa.......................................................................................................... 1

1.2 Manufar Bincike ................................................................................................ 2

1.3 Hujjar Ci Gaba da Bincike ................................................................................ 3

1.4 Dalilan Bincike .................................................................................................. 4

1.5 Muhimmancin Bincike ...................................................................................... 5

1.6 Farfajiyar Bincike .............................................................................................. 6

1.7 Hasashen Bincike .............................................................................................. 7

1.8 Kammalawa........................................................................................................ 8

BABI NA BIYU ....................................................................................................... 9

BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA ............................................................ 9

2.1 Gabatarwa........................................................................................................... 9

2.2 {asar Hausa Hausa da Hausawa ........................................................................ 9

2.3 Saraki a {asar Hausa......................................................................................... 14

2.4 Mata a {asar Hausa........................................................................................... 20

2.5 Fada ... 25
2.5.1 Tarihin Fada ... 26
2.5.2 Al’adun Fada ... 32
2.5.3 Adabin Fada ... 46
2.5.1 Kirari ... 54
2.5.3.2 Take ... 60
2.5.3.3 Wa}a ... 63
2.6 Zabiyanci ... 69
2.7 Jigo ... 77
2.7.1 Yabo ... 79
2.7.2 Zuga ... 84
2.8 Salo ... 90
2.8.1 Salon Sarrafa Harshe ... 92
2.8.2 Adon Harshe ... 93
2.9 Zubi da Tsari. ... 95
2.10 Kammalawa ... 97
BABI NA UKU ... 98
HANYOYIN GUDANAR DA BINCIKE ... 98
3.1 Gabatarwa ... 98
3.2 Dalilan Za~en Fada ... 98
3.3 Hanyoyin Tattara Bayanai ... 100
3.3.1 {wa}}warar Hanya ... 100
3.3.2 Sauran Hanyoyi ... 100
3.4 Ra’in Bincike ... 101
3.5 Hanyoyin Tace Bayanai ... 103

3.6 Tarihin Zabiyoyin da aka Nazarta ........ 104
3.6.1 Zabiyar Daura, Hajia Zulai (Dakamar Sarkin Daura) ........ 104
3.6.2 Zabiyar Ha]eja, Malama Hajara Alhassan ........ 106
3.6.3 Zabiyar Kano, Hajiya Ajuji Maitazargade ........ 107
3.6.4 Zabiyar Kazaure, Hajiya Indo ‘Yarsukola. ........ 108
3.6.5 Hajiya A’i (Dogariyar Zazzau) ........ 109
3.6.6 Rabi Bazamfara ........ 109
3.6.7 Zabiyar Kabin Argungu (magu]iya) Fati Manukwai ........ 110
3.6.8 Zabiya {arangiya (Zabiyar Kazaure ta biyu). ........ 111
3.7.1. Tambayoyin da aka yi wa Zabiyoyin Fadojin da aka Nazarta. ........ 112
3.7.2 Tambayoyin da aka yi wa Sauran Jama’ar da ke Fada. ........ 115
**3.8 Kammalawa** ........ 116
BABI NA HU[U ........ 117
TARKEN ZABIYANCI A FADAR {ASAR HAUSA ........ 117
4.1 Gabatarwa ........ 117
4.2 Jigo a Zabiyancin Fada ........ 118
4.2.1 Yabo ........ 118
4.2.1.1 Tarihin Asali ........ 120
4.2.1.2 Addini ........ 166
4.2.1.3 Jaruntaka ........ 172
4.2.1.4 Iya Mulki da Ri}on Jama’a ........ 185
4.2.1.5 Kyauta ........ 193
4.2.2 Habaici ........ 202
4.2.3 Zuga ........ 208
4.3 Tasirin Addinin Musulunci A Kan Zabiyanci ........ 220

4.3.1 Tasirin Addinin Musulunci ta Fuskar Jigo ............ 220
4.3.2 Tasirin Wayewar Addinin Musulunci A Kan Zabiyanci ............ 231
4.4 Tasirin Zamani A Kan Zabiyanci ............ 233
4.5 Kammlawa ............ 235
BABI NA BIYAR ............ 236
SALO DA ZUBI A ZABIYANCIN FADA ............ 236
5.1 Gabatarwa ............ 236
5.2 Salo a Zabiyancin Fada ............ 236
5.2.1 Adon Harshe. ............ 237
5.2.1.1 Jinsintarwa ............ 237
5.2.1.2 Alamci ............ 251
5.2.1.3 Hotoncin Zuci ............ 256
5.2.1.4 Tamka ............ 261
5.2.1.5 Kwalliya ............ 262
5.2.1.6 Karin Magana ............ 273
5.2.1.7 Amsa kama ............ 275
5.2.1.8 Kambamawa ............ 278
5.2.2 Salon Aiwatar da Harshe a Zabiyancin Fada ............ 281
5.2.2.1 Tsofaffin Kalmomi ............ 281
5.2.2.2 Kalmomin Aro ............ 299
5.3 Zubi a Zabiyancin Fada ............ 304
5.3.1 Tsarin Ga~o~i a Kirarin Zabiyoyin Fada ............ 306
5.3.2. Amsa -Amo a Kirarin Zabiyoyin Fada ............ 310
5.3.3 Kirarin Zabiyoyin Fada a Matsayinsa na Adabin Baka ............ 313
5.3.4 Sigar Tambaya a Kirarin Zabiyoyin Fada ............ 313

5.3.5 Amshi da Kar~i a Kirarin Zabiyoyin Fada ........................................................... 317
5.3.6 Numfasawa a Kirarin Zabiyoyin Fada ................................................................. 319
5.3. Maimai a Kirarin Zabiyoyin Fada ......................................................................... 320
5.3.8 Mabu]i da Marufi a Kirarin Zabiyoyin Fada ......................................................... 322
5.3.9 Tasirin Addinin Musulunci Dangane da Sigar Kirarin Zabiyoyin Fada ................ 325
5.4 Kammalawa ........................................................................................................ 329
BABI NA SHIDDA ...................................................................................................... 330
NA[EWA ..................................................................................................................... 330
6.1 Gabatarwa ........................................................................................................... 330
6.2 Ta}aitawa ............................................................................................................ 330
6.3 Kammalawa ........................................................................................................ 332
6.4 Shawarwari ......................................................................................................... 345
Manazarta .................................................................................................................. 346
Rataye na [aya ........................................................................................................... 358
Rataye na Biyu (mutanen da aka gana da su) ............................................................ 391

## BABI NA [AYA

## SHIMFI[A

### 1.1 Gabatarwa

Fada kusan ita ce idon jama'a a {asar Hausa tun kafin jihadin Shehu Usman [anfodiyo (1804), har ma bayansa, idan ka ]ebe sauyin zamani da zuwan Nasara da guzurin mulkin da suka zo da shi, wanda a iya cewa ya rage }imar fada ko kuma darajarta a idon jama'a. A iya fa]in haka, ganin cewa da can a baya idan ana neman tarihi da adabi da al'adun al'umma, fada ce wurin da ake fara zuwa. Masana da manzarta sun yi ayyuka da dama da suka shafi fada a {asar Hausa, kama tun daga tarihin kafuwarta zuwa al'adunta da kuma adabinta. Ta fuskar adabi za a iske cewa an nazarci kusan mawa}an fada a duk fadar {asar Hausa, da ya ji~anci tarihinsu, da yadda suke shirya wa}o}insu, tare da jigonsu da salonsu da kayan ka]e-ka]e da na bushe-bushen da suke amfani da su. To sai dai kash! Wani abin mamaki shi ne, wa]annan ayyuka da aka yi, kusan duk sun tattaru ko ta}aita ne ga ayyukan da maza suke yi, wato gudunmuwar maza, alhali kuwa mata ma akwai babbar rawar da suke takawa a adabin fada da al'adunta a {asar Hausa. [aya daga cikin wannan rukuni na mata ita ce 'Zabiyar Fada' wadda ta fa]o cikin rukunin 'yan ma'abba/bamba]o ko kuma 'kwando', masu yin kirarin baki. Zabiyar Fada kuwa ba }ashin yardawa ba ce a fada, domin tana ]aya daga cikin wa]anda ke }ara wa Sarki kwarjini da }ima a idon talakawansa da sauran jama'a baki ]aya. Baya ga zuga shi, ya }ara ji babu kamarsu cikin jama'arsa, ta hanyar amfani da sigogin nan na cim ma yabo, wato: asali da ri}o da addini da jaruntaka da kyauta da kuma }warewa ga ri}on jama'a (iya mulki), wa]anda za a iya cewa mizani ne da talaka ke auna saraki a {asar Hausa. Babban aikin Zabiya a fada shi ne fito da Sarki daga cikin gida zuwa majalisa duk safiya, ta kuma mayar da shi bayan an kammala zaman fada. Idan kuma tafiya

ta kama shi, takan raka shi ya hau doki ko ya shiga mota. A lokacin da ya dawo gida, ita za ta tarbe shi zuwa gida, sannan ta mi}a shi hannun Jakadiya. A ta}aice, ita ke sanar da sauran jama'a, musamman fadawa fitowar Sarki zuwa majalisa, ko wani wuri da komowarsa, ta hanyar amfani da kirarinta.

Akwai Zabiyoyi biyu a Hausa. Ta farko ita ce wadda take jagoranci wa}a, ta biyu kuma ita ce matar da a bisa al'ada, a kan ajiye a fada, domin yi wa saraki ka]ai kirari. Wannan bincike idan ya ambaci 'Zabiya', yana nufin ta biyun. Binciken, mai kanun, 'Kirarin Saraki a Bakin Mata: Nazarin Zabiyanci a {asar Hausa', ya yi amfani da wata al'adar fada, wato 'zabiyanci', a matsayin 'madubi', aka nazarci adabin da ke ciki (kirarin saraki), domin fito da rayuwar al'umma, kasancewa adabi shi ke bayyana rayuwar al'umma da ma tarihinsu.

**1.2 Manufar Bincike**

Masana da manazarta sun yi ayyuka da dama da suka shafi adabin fada, to sai dai a ce galibi ayyukan da aka yi ba su ta~o wa]anda mata suke yi ba, musamman ma Zabiyar Fada, domin haka wannan bincike na da manufofi kamar haka:

i. jaddada cewa baya ga maka]a da mawa}an fada maza a {asar Hausa, akwai wani kaso na takwarorinsu da kan yi kusan irin aikinsu, watau Zabiyoyin Fada.

ii. fito da irin gudunmuwar da Zabiyoyi suke bayarwa a Fadar {asar Hausa.

iii. gwada tunanin Bahaushe game da saraki da sarauta a {asar Hausa.

iv. za}ulo nau'o'in adon harshen da ke cikin kirarin da Zabiyar Fada ke yi wa saraki da irin zubinsa.

## 1.3 Hujjar Ci Gaba da Bincike

Al'adu da dama a doron }asa, musamman na nahiyar Afirkas a kullum suna }ara ~acewa a sanadiyyar barazanar da zamani ya haifar, wanda ya sa galibi masu aiwatar da wasu al'adu da ma `yan kallo, suka yi watsi da su. 'Al'adar Zabiyanci a Fadar {asar Hausa' ma ba ta tsira ba, domin a sume take, saboda haka tana neman agaji. Babban agajin da za a kawo mata a nan, shi ne sassauta mata wannan hali na 'ni-`ya-su', a taskace kirarin ta fuskar nazari a fagen ilimi, watau a nazarce shi, a fito da irin fasahar da ke cikinsa. Wannan hujja ita ta haifar da matsalar wannan bincike, aka ga ya zama tilas a gudanar da wannan nazari saboda muhimmancinsa. Agaji irin wannan ya zama wajibi, domin haka, za a taskace kirarin Zabiyar Fada, a kuma nazarce shi filla-filla. Wannan hujja ta tabbatar a zahiri, wannan al'ada ta Zabiyanci ta sami na}asu, saboda wa]annan dalilai:

i. zabiyanci ya zama tsohon yayi a Fadojin {asar Hausa da dama. Misali, babu Zabiyar Fada a Fadar Katsina da Gobir da ta Rano. Haka ma a Fadar Kano, in ban da wani faifan Sidi (CD) guda ]aya rak, na Zabiya Ajuji Maitazargade, wadda ta rasu shekara ashirin da hu]u, wato a 1992.

ii. a ce har gara-gara a Fadar Gobir (Sabon Birni) da Zazzau, kodayake an sami sauyi ko 'juyin mulki' a wa]annan fadoji.Yanzu babu Zabiyoyin Fada a Gobir da Zazzau, amma wasu sun ]auki nauyin maye gurbinsu. Alalmisali, a Fadar Zazzau, akwai masu aiwatar da wannan al'ada ta 'Zabiyanci', duk kuwa da cewa ba a na]a su ba, a Gobir kuwa, an na]a 'Zabayi' ne (namiji), domin ya maye gurbin 'Zabiya'. Saboda haka, a iya cewa wa]annan fadoji biyu, Gobir da Zazzau, al'adar zabiyanci tana }o}ari ne ta rayu, kada a ce babu ita ko kuma ta mutu gaba ]aya. Sai dai a ce ta zama bara – gur~i, ana }o}arin sama mata tushe. Masu iya magana dai sun ce, "Da babu gara ba da]i".

### 1.4 Dalilan Bincike

Kusan a ce Zabiyar Fada jaruma ce, saboda a da can da ita ake zuwa fagen fama, domin kwarzanta maza da kirarinta, idan kuwa ba ta je ba, tana rakiya bayan gari, tana gaba, saraki da maya}a na baya. Tana tafe kuwa tana harzu}a maza, ta hanyar jaddada asalinsu ( da ke nuni da cewa su ba mutanen banza ba ne), da tunatar da su irin jarunta da bajintarsu da ta magabatansu da kirarin nata. Bayan kuma an dawo ta tarbi maya}a. To, amma masana da manazarta ba su lura da wannan muhimmanci nata ba. Domin haka, dalilan aiwatar da binciken su ne:

(i) cike gi~in da masana da manazarta suka bari na kasa gudanar da nazari a kan Zabiyoyin Fada.

(ii) bu}atar nuna wa jama'a cewa kirarin Zabiya a Fadar {asar Hausa, babban kaso ne na adabin fada da ke bayyana al'adun al'umma.

(iii) bu}atar taskace kirarin Zabiyar Fada, a same shi a rubuce, domin a adana shi saboda duk fadar da aka ziyarta, an iske ba a ta~a tunanin taskace wannan adabi ba, ga shi kuwa yana neman salwanta. Wata fadar ma yanzu babu Zabiyar Fada, babu kuma kirarin nata a rubuce, domin haka babu abin da za a nuna wa yara masu tasowa ko manazarta. Barazanar shirin game-duniya, wanda babbar manufarsa ita ce ya lan}wame al'adun jama'a, yana yi wa al'adunmu, musamman na Afirka bazarana, saboda haka akwai bu}atar taskace wannan kirari na Zabiyar Fada. Har ila yau, wayewar zamani da sanadiyyar ilimin boko ya haifar, ya sa 'ya'yan Zabiyoyin Fada ba sa sha'awar gadonsu, suna ganin }auyanci ne 'Zabiyanci', wanda haka ya sa al'adar take hanyar gushewa. Tasirin addinin Musulunci ma, wanda ya yi hani ga ro}o,

musamman tsakanin mata da maza (kasancewa kuma Zabiyar Fada mace ce), ya sa yanzu ba kowace mace za ta yarda ta yi zabiyanci ba. Al'adu da dama yanzu sun zama tarihi a sanadiyyar haka.

vi. kirarin Zabiyar Fada cike yake da adon harshe da muhimman turakun wa}o}in fada da suka kasance mizanin da talaka ke auna saraki. Saboda haka, akwai bu}atar a nazarce shi, domin a tabbatar da wannan hasashe da binciken ya yi.

## 1.5 Muhimmancin Bincike

Ana sa ran wannan bincike ya bayar da gudunmuwa ta fuskoki da dama, kamar haka:

i. taskace wani muhimmin batu na tarihi da al'ada da adabin fada da ke neman ~acewa, a sanadiyyar barazanar zamani, da wayewar addini (addinin Musulunci), domin 'yan baya su sami abin waiwaye.

ii. masana da manazarta tarihi za su sami wani fagen tarihin wata al'ada ta fada, musamman sunayen Ssarakunan da suka gabata da ake ambato su a kirarin.

iii. masana da manazarta al'ada za su }aru da wannan kirari na Zabiyar Fada, saboda an fito masu da wata tsohuwar al'ada wadda take neman ~acewa.

iv. masana da manazarta adabi ma ba za a bar su a baya ba, domin binciken zai ba su damar samun cikakken nazari a kan adabin Zabiya a Fadar {asar Hausa, musamman ta fuskar zubi da salo da kuma jigonsa.

v. masana da manazarta ilimin zamantakewar ]an Adam ma za su }aru da wannan bincike ta hanyar sanin ]abi'un Zabiya a Fadar {asar Hausa.

vi. masana ilimin harshe, musamman a fagen ilimin walwalar harshe ba za a bar su a baya ba, saboda za su }aru da wannan bincike, su nazarci kirarin Zabiya ta sigar harshe, domin an sama masu kayan aiki.

vii. a fagen ilimi, Hukumar Tsara Manhaja ta {asa, (NERDC), za ta }aru da wannan bincike, ta hanya sa al’adar Zabiyancin Fada a manhaja.

viii. binciken zai kore shakku game da zargin danniya da ake ikirarin al’adun Hausawa na yi ga mata. Domin haka masu cewa al’adun Hausa na danne ha}}in mata, za su fahimci cewa hatta a fada , sai da aka sama masu ‘yancin bayar da gudunmawarsu.

ix. wannan bincike zai taimaka wa al’ummar Hausa baki ]aya, su san Zabiyancin Fada, musamman matasa wadanda galibi ba su san al’adunmu ba.

x. ma’aikatar ilimi ta tarayya da na jihohi ma za su amfana da wannan aiki, ta fuskar sa Zabiyancin Fada cikin darasin ‘Al’adun Alumma da Fasaharsu, watau, *Community Cultural Arts* (CCA).

xi. sassan Nazarin Harsuna da Al’adun Afirka a jami’o’i ma ba a bar su a baya ba, domin an sama masu kayan aiki.

xii. ana sa ran hukumomin taskace tarihi da al’adu na gwamantin tarayya da na jihohi su amfani da wannan aiki.

xiii. gidajen sadarwa, musamman rediyo za su amfana da wannan aiki, ta hanyar sanar da al’umma wannan al’ada.

**1.6 Farfajiyar Bincike**

Wannan bincike ya ta’alla}a ne ga fito da gudunmuwar Zabiyoyin Fadar {asar Hausa. {asar Hausa tana da fa]i, saboda haka ba za a iya game ta da wannan bincike ba, amma an yi }okarin za~en wasu fadoji na {asar Hausa da ke ~anganen Arewacin Nijeriya, wa]anda suka yi fice bayan jihadin Shehu Usman [anfodiyo, da suka ha]a da Fadar Kabin Argungu da Daura da ta Ha]eja da Kano da Kazaure da kuma Fadar Zazzau. Wani hanzari ba gudu ba, a Fadar Kano an iske yanzu babu Zabiyar Fada, babu kuma taskatattcen kirarin da take

yi wa saraki a rubuce, amma an sami faifan sidi (CD) da aka yi amfani da shi. Ana sa ran wa]annan fada sun wakilci {asar Hausa.

i. Kodayake aikin yana da ala}a da al'ada, amma ba al'adar tsantsa aka nazarta kai tsaye ba. Adabin da ke cikin a'adar aka sarrafa, domin a fito da tunanin Bahaushe game da saraki da sarauta.

ii. A adabin, abin da ya shafi kirari ne aka nazarta.

iii. Kirarin ma wanda mata suke yi wa saraki a fada, na wasu fada shida da ke arewacin Nijeriya da suka ha]a da Kabin Argungu da Daura da Ha]eja da Kano da Kazaure da Kuma Fadar Zazzau.

iv. A nazarin kirarin ma, an nazarci jigonsa da salonsa da kuma irin zubinsa ne kawai. Wato, ba a nazarci yadda ake aiwatar da kirarin ba, ko kuma ta fuskar sigar ilimin harshe ba.

v. An kuwa za~i nazarin jigon kirarin ne saboda, nazarin jigo shi ke fito da sa}on adabi, adabi kuma shi ke fito da rayuwar al'umma.

vi. An nazarci ire-iren nau'o'in adon harshen kirari domin }ara fito da sa}on da aka yi bayani a kai.

vii. Kasancewa aikin sabo ne, aka ga akwai bu}atar a nazarci irin nau'in zubinsa .

viii. Ta fuskar lokaci, aikin ya nazarci kirarin Zabiyoyin wa]annan fada da aka ambato, daga bayan jihadin Shehu Usman [anfodiyo, zuwa yau. Wato, daga 1907 -2015. Kodayake bincike ya gano cewa kirarin da ake aiwatarwa a Fadar Kabin Argungu da Daura, sun fi shekara ]ari biyu (200) ana aiwatar da su. Za a iya ganin haka daga kalmomin dauri da ke cikin kirarin.

**1.7 Hasashen Bincike**

Binciken ya yi wasu hasashe kamar haka:

i. kirarin Zabiya gamagari ne a Fadar {asar Hausa
ii. su ma mata suna bayar da gudunmuwa a adabin fada.
iii. kirarin Zabiya Fada yana taskace tarihin fada.
iv. Zabiyar Fada tana nisha]antarwa.
v. kirarin Zabiyar Fada cike yake da jigon yabo da adon harshe tare da sau}a}}an zubi .

vi. kirarin Zabiyar Fada mizani ne da talaka ke auna saraki.

**1.8 Kammalawa**

Kamar yadda sunan babin ya nuna, an yi shimfi]a ne a kan aikin da aka gabatar kan kirarin da Zabiyoyin Fada ke yi wa saraki a {asar Hausa. A iya cewa babin shi ne al}ibla ga nazarin. Da farko, an gabatar da aikin a ta}aice, an kawo manufarsa da hujjar da ta haifar da binciken da dalilan da suka sa aka gudanar da shi da hasashen bincike da kuma muhimmancin da ake sa ran zai bayar ga masana da manazarta da al'umma baki ]aya. Hausawa ko masu iya magana na cewa, "Sanin wurin bugu shi ne }ira". Saboda haka a babi na biyu, an yi bitar ayyukan masana da ke da ala}a ta kusa da wannan bincike, sannan aka yi sharhi daidai gwargwado.

# BABI NA BIYU

# BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA

## 2.1 Gabatarwa

Masu iya magana sun ce, “Waiwaye Adon Tafiya”. Aiki irin wannan, musamman na nazari ba zai kammalu ba, sai ya ta~o abin da ke da dangantaka da shi (na nesa da na kusa), domin samun madogara ko madafar ci gaba da bincike. Wannan bincike, aiki ne da ya shafi wani nau’i daga adabin fada, saboda haka ba zai cika ba sai an yi bitar adabi da wasu nau’o’insa, musamman wa}a da take, saboda kusancinsu da kirarin da Zabiyar Fada ke aiwatarwa. Aikin ya kuma yi bitar ayyukan masana a kan ma’anar al’ada, kasancewa Zabiyanci al’ada ce ta fada da ake ajiye mace Musamman domin yi wa saraki kirari, wanda a wannan nazari aka yi amfani da kirarin domin fito da tunanin Bahaushe game da sarauta da saraki. An kuma yi bita a kan ma’anar jigo da manyan jigogin adabin fada, wato yabo da zuga, sannan aka waiwayi ra’ayoyin masana a kan Hausa, {asar Hausa da Hausawa. Har ila yau, an yi bitar ayyukan da masana da manazarta suka gudanar da ya ji~anci fada da matsayin saraki da ma mata a {asar Hausa. Babu ko shakka, bitar wa]annan ya haskaka wannan aiki da aka aiwatar.

## 2.2 {asar Hausa Hausa da Hausawa

Masana ilimin al’ada da adabi da harsuna da tarihi irin su Palmer (1928) da Greenberg (1946) da Johnson (1967) da Smith (1960, 1978) da Smith (1970) da Niven (1971) da Bagari (1972) da Adamu (1976, 1978) da Tsiga (1978) da Lavers (1980) da Ibrahim (1982) da Schuh (1983) da Augi (1984) da Jinju (1985) da Magaji (1985) da saura da dama sun yi

nazarce – nazarce da rubuce-rubuce a kan {asar Hausa, musamman abin da ya shafi asalin Hausa da Hausawa.

Adamu (1978:1), ya bayyana ‘ Hausa’ a matsayin sunan wata al’umma ko }abila, sunan harshen wannan al’umma, kuma sunan muhallin da wannan al’umma take zaune. Watau, ‘Harshen Hausa’, Hausawa’ da ‘{asar Hausa’. A yayin da Amfani (2011:2), yake cewa, Hausa harshe ne, kuma yana ]aya daga cikin harsunan ]an Adam wa]anda ake samu a nahiyar Afirka. Masanin ya kuma bayyana cewa a lissafi irin na masana ilimin kimiyyar harshe (linguists), harshen Hausa yana cikin wani babban rukuni na kason harsunan duniya wanda ake kira ‘Afroasiatic’. Shi ma wannan babban rukuni yana da ‘ya’ya kuma kowane ]a, shi ma }aramin rukuni ne mai ]auke da harsuna. {aramin rukunin da Hausa ke cikinsa shi ake kira ‘ Gidan Harsunan Chadi’. Wasu harsuna ‘yan gidan Chadi, wa]anda ‘yanuwan Hausa ne su ne Angas da Bole da Ngizim. A }ididdigar masana akwai mutane kimanin miliyan hamsin Hausawa da wa]anda suke jin Hausa (masu jin harshen a matsayin harshe na biyu da na uku). Hausa tana da gidanta na gado a wani sashe na arewacin Nijeriya da kudancin Jumhuriyar Nijar. Wannan gida na gado, shi ne mazaunin Hausawa, wa]anda harshensu na gado shi ne Hausa. Hausawa sun kai Hausa wurare daban-daban irin su }asashen Ghana da Togo da Benin da Cameroon da Chad da Sudan da Mali da Jumhuriyar Afirka ta Tsakiya. A cikin Nijeriya kusan ba jihar da Hausawa ba su kai Hausa ba.

Masana sun amince cewa {asar Hausa tana shimfi]e a Arewacin Nijeriya da kuma kudancin Jumhuriyar Nijar a cikin Afirka ta yamma. Daga gabas ta yi iyaka da Kogin Kwara, daga arewa ta yi iyaka da }asar Adar a cikin Jumhuriyar Nijar. Daga wajen kudu kuma ta yi iyaka da }abilun Gwari da }abilun kudancin Zariya da na kudancin Bauci. A yanzu, }asar ta ha]a da jihar Kano da jihar Sakkwato da arewacin jihar Kaduna da kuma arewacin jihar Bauci a

Nijeriya. Ta kuma ha]a da }asashen Kwanni  da na Damagaram a Jumhuriyar Nijar. Yawancin }asar Jigawa ce amma akwai ‘yan duwatsu jefi-jefi a ciki, akwai koguna manya da }anana da suka ratsa }asar, wasu suna kai ruwansu Kogin Kwara, wa]ansu kuma tafkin Cadi, (Ibrahim, 1982:29). A yau a Nijeriya, {asar Hausa ta ha]a da jihohin Jigawa da Katsina da Kano da Sakkwato da Zamfara da Arewacin jihar Kabbi da arewacin jihar Kaduna da wani sashe na jihohin Bauci da Gwambe. A Jumhuriyar Nijar kuwa, babbar {asar Hausa ita ce hedikwatar Jumhuriyar, wato Niamey,  (Yamai), sai kuma jihohin Mara]i da Dogon Dutsi da Zindar da {wanni da Dosso da Gaya da Tawa da Adar . Kusan duk jihohin da ke }asar Nijar, babu inda za a iske babu Hausawa, saboda suna da kason hamsin da uku cikin ]ari (53%) na harsuna ashirin (20) na }asar.[1]

Ainihin {asar Hausa ta asali tana Afirka ta yamma ne, a farfajiya nan da ke tsakanin hamadar Sahara da zuzzukan da suka doshi ga~a tekun atlantika daga hudu, kuma ana kiran }asar da sunan ‘Sudan ta Yamma’, watau tsakanin tafkin Cadi da gwiwar Kogin Kwara  a can yamma. Idan aka duba taswirar Afirka, za a sami {asar Hausa a tsakanin layi na goma sha biyar (15N) zuwa na goma sha takwas (18N) da Ikwaita.  {asar Hausa tana tsakanin layi na takwas (8E) da na goma sha biyu (12E) a gabas da layin  Greenwhich, Alhassan da Wasu (1982:1)

Mahdi (1978:1-2), ya bayyana cewa {asar Hausa wuri ne da ba a bu}atar na]a Sarkin Hausawa. Ya ci gaba da bayani cewa, {asar Hausa ta asali ta fara ne daga Lalle da Asodu, can arewa maso gabas da Agadas (da ke Jumburiyar Nijar), inda daga nan ne Gobirawa suka taso zuwa inda suke a yau, a Nijeriya. {asar Hausa tana da girma }warai da gaske. A mi}e,

---

[1] Hira da Dokta Garba Musa na Jami’ar Abdulmumini, Niamey Jumburiyar Nijar.

daga arewa zuwa kudu, {asar Hausa ta fara daga Azben har zuwa kusurwar arewa maso gabas da tsaunukan Jos. Daga nan kuma ta yi arewa maso yamma, ta dangana da wani }aton kwari na gulbin Kabi, sannan ta karkata ta nufi arewa maso gabas har Azben. Wannan zagaye shi ne iyakokin {asar Hausa a gabas da yamma da kudu da arewa. {asar da wa]annan iyakoki suka iyakance ita ce {asar Hausa. Har ila zuwa yau, wannan }asa, wato {asar Hausa, ita ce mazaunin Hausawa, (Amfani, 2011:2). Fadojin da wannan bincike ya nazarta, duk suna wani sashe na {asar Hausa da ke Arewacin Nijeriya. Watau, Kabin Argungu da Daura da Ha]eja da Kazaure da Kano da kuma Zazzau

Idan aka koma kan Hausawa, a ra'ayin Alhassan da Wasu (1982:6), Hausawa taro ne na }abilu daban-daban, kuma suka taru suke magana da harshe ]aya, wato Hausa. Masanan sun kare kansu da cewa, idan aka nemi yawancin haifaffen {asar Hausa ko shi wace }abila ce, sai ya ce Bafillace ne ko Babarbare ko Buzu ko Banufe. Alhali kuwa ko 'sannu' bai sani ba a wannan harshe. Yakasai (2012: 234), ya tabbatar da haka, a inda ya ce 'Hausa harshe ne na mu'amula ga }abilu masu tarin yawa da suka koyi harshen Hausa kuma suke magana da shi'. Magaji (1985) da Bunza (1990), na da ra'ayin cewa Hausawa su ne wa]anda tun fil-azal harshen Hausa shi ne harshensu, ba su da wani harshe sai 'Hausa', sannan kuma dukkan al'adunsu da ta'adunsu na Hausa ne. Har ila yau, addinin Musulunci ya yi cikakken tasiri a kansu. Idan an ]auki wannan ra'ayi, Maguzawa wa]anda suke ganin kansu a matsayin su ne asalin Hausawa, me za a kira su? Maguzawa ba ba}i ba ne a {asar Hausa. Kodayake kalmar ba}uwa ce, amma tun kafin zuwan wannan kalma, akwai wa]annan mutane zaune a {asar Hausa, wa]anda dalilin Musulunci ya sa aka la}aba wa wani ~angare na Hausawa suna 'Maguzawa'. Salahu (1981), ya jaddada wannan inda yake cewa: "Hausawa na asali sun sami sauyin suna lokacin da addinin Musulunci ya shigo }asar

Afirka ta Yamma. Saboda }arbar wannan addini da yarda da abin da yake koyarwa ya kawo ma Hausawa da suka bijire masa sabon suna, suka zama ‘MAGUZAWA’ tamata – BAMAGUJIYA ko BAMAGUZA. Asalin wannan kalma ba Hausa ba ce. Tarihi ya nuna kalmar Larabci ce daga sunan wata al’umma a }asar Farisa ( Iran). Bayanin ya ci gaba da cewa wannan al’umma ba ta yarda da Musulunci ba. Wani marubuci ya ce asalin kalmar shi ne ‘Majus’ wadda take a rubuce cikin Al}ur’ani mai tsarki, sura ta ashirin da biyu, aya ta goma sha bakwai (22.17)”,Salahu (1981:22).

Adamu (1978), ya bayyana cewa, Hausawa su ne da]a]]un mazauna {asar Hausa da dukkanin zuri’arsu ta fuskar maza (gefen uba), da suka kasance masu magana da harshen Hausa, kuma suke ri}e da addininsu. Wannan ra’ayi ma yana da tangar]a, saboda akwai Hausawa miliyoyi da suke zaune a doron }asa, da suke magana da harshen Hausa, suke gudanar da rayuwa irin ta Hausawa, su kuma ne za a kira su, tun da ba a {asar Hausa suke da zama ba? Junaidu (2008), a nasa ra’ayin kuwa yana cewa: “Hausa ta samar da Hausawa ,ita ce harshensu na haihuwa, ba su da wani harshe wanda ba Hausa ba. Wa]annan Hausawa ne da suka ]auki Hausa a matsayin harshensu a sakamakon zaman da suka a yi a {asar Hausa , wadda ta saba kar~ar ba}i daga ciki da wajen Afirka (musamman Asiya). Hausa ta kar~e su ta narkar da harshensu ta ha]iye shi, ya kuma shige cikin Hausa. Tun }arni na goma sha shida miladiyya, akwai unguwannin mutanen Barno da Mali da Shanghai da Azben da Gobir da Malamai (Larabawa) a Katsina. Haka a Kano, akwai Unguwannin Barebari da Larabawa da Azbinawa da Sharifai da Yamalawa da Jukunawa da Nufawa .Mulkin da aka yi wa al’ummomi makwabta ya sa suka saki harshensu. A Zariya akwai Barebari da Mallawa. Kafin jihadi da bayan jihadi a }asashen Hausa, Fulanin soro da gidajen sarautun Daular Usmaniyya masu martaba, Fulani ne tun daga tushe ko asali,

wa]anda Hausa ne a zahiri, kuma shugabannin al'umma da addini. Sannan bayan zuwan Turawa akwai Unguwannin Tudun Wada, wa]anda suka }unshi sauran harsunan Nijeriya, wadanda suka sake su a hankali suka kar~i Hausa", (Junaidu, 2008:5). A ta}aice, a iya cewa harshen Hausa ya narke harsuna da al'ummomi da dama, yanzu sun zama Hausawa, musamman }ananan }abilun Arewacin Nijeriya da na kudancin Nijar.

Yakasai (2012:231), ya bayyana bazuwar Hausawa da harshensu da cewa lamari mai rikitarwa dangane da lokacin da aka fara samun hakan. Wannan kuwa na faruwa saboda rashin rubutattun bayanai a kan hakan. To, sai dai akwai tabbacin cewa Hausawa da harshensu sun fara bazuwa cikin yankunan da ba nasu ba tun kafin kafuwar }asar Hausa. Ya ci gaba da bayani cewa, wasu kuma na ganin Hausawa sun fara cu]anya da }abilu kamar Wangarwa daga }asar Mali da kuma Larabawa daga Afirka ta Arewa tun a }arni na goma sha ]aya, wanda za a iya cewa, wannan hanya ta bu]e }ofofin ya]uwar Hausa a duniya. Haka kuma, }warewa da kuma goguwar Hausawa a harkokin kasuwanci da iya mu'amula da sauran jama'a sun sa duk inda suka je, cikin ruwan sanyi suke wayewa da sabawa da al'ummar da suka iske, wanda wannan yanayi ya samar da }afa da ya]a harshen Hausa da al'adun Hausawa.

## 2.3 Saraki a {asar Hausa

Alhassan da Wasu (1982), sun bayyana '*saraki*' da '*basarake*'. Wato wanda yake ri}e da wata sarauta ko kuwa jinin sarauta ya haife shi. Masanan, sun ci gaba da bayani cewa, '*saraki*', mutum ne wanda '*shugabanci*' da '*mulki*' da '*iko*' suke hannunsa, domin wa]annan sinadarai (uku), su suka tattaru suka yi sarauta, ko kuma a ce, suka haifar da ita. Kamar yadda suke cewa:

> … Yi wa mutane jagora da jan ragama a harkokinsu na zaman tare shi ne '*shugabanci'*. Yawan jama'ar da mutum ya shugabanta, da ya]uwarsu ko kuma girman muhallinsu da suke zaune a cikinsu, da }arfin jagorancin da yake iya yi masu, wa]annan abubuwa su ne '*mulki',* kuma sukunin bayar da umarni da hani da tsaro shi ne '*iko',* Alhassan da Wasu, (1982:66)

A maganar yau da kullum, idan aka ce, "Wane 'Saraki' ne". Wannan na nufin mutum mai 'ji da kansa', 'mai }asaita' da 'girman kai' da 'tun}aho', komin talaucinsa. Watau wanda ya ari rigar basarake ya yafa, domin ga al'ada, basarake aka sani da girman kai da iko da isa, saboda girma sarauta, musamman lokacin da sarauta take da }ima a idon jama'a.

To haka kuma, Malumfashi (1990), ya bayyana cewa 'saraki', suna ne na ]aya daga shugabar 'yan bori. Ke nan, saraki a al'adar bori, ]aya ce daga cikin masu zartar da hukunci a harkar bori. Wannan ma'ana na tabbatar da ma'ana ta farko, kamar yadda Alhassan da Wasu (1982), suka bayar, wadda ta bayyana 'saraki', da 'mutumin da shugabanci da mulki da iko suke hannunsa'.

Masana irin su Adamu (1978) da Alhassan da Wasu (1982) da Gusau (1988), sun yi ittifa}i cewa shugabanci a {asar Hausa ya fara ne daga gida, a inda '*maigida'* yakan jagoranci iyalinsa, wa]anda suka ha]a da matansa, biyu, uku, hu]u, har zuwa yawan yadda ya so ko kuma halinsa ya ba shi (kafin addinin Musulunci ya }ayyade matan da namiji zai iya aura), da 'ya'yansa da jikoki da barori. Wanda daga baya ya haifar da gidan gona/gandu. Bun}asar wannan iyali kuwa, ya haifar da unguwa/ unguwanni, zuwa al}arya, daga nan har aka sami gari /garuruwa. To, haka ma, ana samun shugabanci na masu sana'o'in gargajiya, a inda kowace sana'a ke da shugabanninta, masu gudanar da harkokin sana'arsu. Alalmisali, Barbushe ya shugabanci mafarauta 'yanuwansa a zamaninsa, ta hanyar tsare dokokin farauta da kula da abin bautarsu, wato, 'Tsumburbura'.

Ana sarauta ne domin a kare marasa }arfi da kiyaye martabar ]an Adam da ha]a kansu, ta hanyar jagoranci. Sannan kuma, shugaba yana nuna }arfin ikonsa a kan talakawansa, domin daidaita lamuransu, kamar yadda maka]a [an}wairo yake cewa Sarkin Daura, Muhammadu Bashar:

Daudu : Ri}e talakkawanka da kyawo,
Kai musu hairi,
Ka sa su hanyoyin Musulunci
In sun ham~are ka tan}waso su x2,
'Y/Amshi: In ko sun }iya a ba su kashi x2.."
([ankwairo a wa}ar 'Babban Jigo' na Yari)

Wannan na tabbatar da cewa shugabanci yana daga cikin al'adun Hausa, wanda tsarin dokoki a rayuwa shi ne kula da al'amuran mutane da suka shafi bin dokoki. Idan kuwa babu tsari a rayuwar mutane, tabbas za a sami ru]ani da rashin kwanciyar hankali. Domin ba a iya barin mutane su yi abin da suka ga dama, dole sai da wasu dokoki da za su tafiyar da rayuwarsu, Ramlatu (2012:469). Muhammad (1991:1), ya yi }arin bayani da cewa, damar da Sarki yake da ita na bayar da umarni ko hani ga talakawansa, shi ne sarauta.

A tsarin sarauta a {asar Hausa tun daga gida namiji ne shugaba. To haka ma a duk garuruwan Hausa, shugaba mai iko a kan }asa baki ]ayanta namiji ne da ake na]awa a matsayin '*Sarki'.* Kodayake tarihin Daura ya nuna cewa mata sun yi sarauta a masarautar, da mu}amin '*Magajiya',* haka kuma a Zazzau, an ta~a samun '*Sarauniya Amina'* . Masana irin su Alhassan da Wasu (1982), sun bayyana cewa Sarki shugaba ne mai cikakken iko wanda yake da iko ya zartar da hukunci a }asarsa, wanda ya sa a da can, Sarki yana da ikon

ya sa a kashe mai laifi ko a yi masa waso ko kuma a ladabtar da shi ko a kore shi daga }asa. Sannan kuma, yana da }arfin ikon na]a wani ko cire shi daga kowace irin sarauta a }asarsa.

Ramlatu (2012:469), ta yi }arin bayani a kan matsayin 'Sarki', a {asar Hausa. Watau Sarki shi ne wu}a, shi ne nama, wanda ya sa ake masa la}abi da 'Sarkin umarni a yi, ko ya yi hani, a bari dole. Kamar yadda ta bayyana, sarakuna suna da ayyuka wa]anda suka rataya a wuyansu, kamar ikon kiyaye zaman lafiya a gari ko }asarsu baki ]aya. Misali idan dole ta kama su yi ya}i, suke jagorantarsa. To haka kuma, Sarakuna ke tara ku]in haraji da na ganima da ku]in diyya da raba ku]in gado. Su suke aza haraji, kuma dukkan ku]in da aka tara za a sa su ne a baitulmali. Sarki shi yake da ikon amfani da ku]in da aka tara ko kuma ya bayar da umarnin yin amfani da su. Lokacin da duk wani ba}o ya zo {asar Hausa, ha}}in Sarki ne ya san ko wane ne, kuma da abin da ya kawo shi }asar da sana'arsa, wanda duk hanya ce ta kiyaye lafiyar talakawansa.

A {asar Hausa a bayanin Bunza (2009:67-68), masana al'ada sun amince da cewa gabanin bayyanar addinin Musulunci, sarauta ba ta gado ba ce. Jaruntaka ke sa a na]a wani sarauta, musamman ta 'Sarkin Yanka', domin haka a wannan zamani, sarauta wani ya}i ne gawurtacce, wanda duk ya nuna bajintarsa ta jaruntaka, shi ke hawa karagar mulki. Wannan ne ya sa da can a {asar Katsina, duk shekara ake shirya kokuwa da Sarkin da ke gadon mulki, wanda duk ya kayar da shi, zai sa wu}a ya yanka shi, shi kuma ya hau gadon sarauta. To haka kuma, Sarakunan Hausa sun jagoranci kai cafka/hari ga junansu, domin fa]a]a iko na masarauta da samun bayi da ganimar ya}i. Wannan kuwa ya haifar da zaman fargaba da shirin ko-ta-kwana a zukatun jama'a**.**

A yanzu kuwa, kamar yadda Alhassan da Wasu (1982), da Gusau (1988), da Bunza (2009) suka yi bayani, sarauta ana gadonta ne daga uba da kaka da kakan uba da kakan kaka har zuwa a }are adakar taliyon tarihi. Kodayake, ko cikin wa]anda suka gada, a kan yi la'akari da shekaru da hankali da ha}uri da adalci da cututtuka masu tauye rayuwas su nakasa ta, kamar cutar makanta, da kuturta, da kurunta da ta~uwar hankali. Alhassan da Wasu (1982:67), sun yi }arin bayani a kan gadon sarauta da cewa, wasu sarautun kuwa ana samunsu ne saboda 'yar uwantaka da Sarki. Wasu kuma bayin Sarki ne Sarki ya na]a su, saboda wata bajinta da suka nuna, musamman a fagen ya}i, 'ya'yansu da jikokinsu kuma suka gaje su. Duk da haka, sarautar Sarki ta kasance sai ' ]an gado' a {asar Hausa. Bayan masu jihadi sun ci wasu {asashen Hausa, an yi la'akari da addini wajen za~en wa]anda aka na]a suka maye gurbin Sarakunan da suka yi hijira, ko kuma aka kashe su. Wa]anda aka za~a dangane da la'akari da addini da nuna bajinta lokacin jihadi, su suka kar~i tuta domin su shugabanci }asashensu. Daga baya kuma, zuri'arsu suka ci gaba, suka gaje su.

Usman (1981), a fassarar Sambo (1993:108), ya tabbatar da wannan gado na sarauta (ta mu}amin Sarki a Masarautar Katsina a yanzu), cewa sai wa]anda suka gada daga iyaye da kakanni ake na]a su Sarki, kuma Sarakunan Karaga ne ke za~en wanda zai zama Sarki a masarauta 'Yan majalisa masu za~en sabon Sarki sun ha]a da Galadiman Katsina da {auran Katsina da Dur~in Katsina da kuma 'Yan]akan Katsina.

Sarakuna a {asar Hausa suna tafiyar da mulki na tsarin hawa-hawa. A kowace fada, Sarki yana da masu taimaka masa wajen tafiyar da mulki, masu ri}e da sarautun hakimi zuwa dagaci, zuwa mai unguwa. Hakimai su ne kan gaba wa]anda wasu daga cikinsu ake ba su

ri}on garuruwan da ke }ar}ashin masarauta, wa]ansu kuma 'yan majalisa (galibi hakimai sukan kasance na kusa da Sarki wa]anda suke da dangantaka ta jini). Hakimai su ne masu hakimcin gundumomi a matsayinsu na manyan mataimakan Sarki. Hakimai ke bayar da dukkan umarnin Sarki da tabbatar da su tare da taimakon dagatai a }auyukan da ke }ar}ashin gundumarsu, masu unguwanni kuma su kula da unguwanni.

Saraki a kan bambanta shi da sauran jama'a daga irin tufafin da yake sawa da wa]ansu kayayyaki ko alamomi da a kan ke~e shi da su, kamar sandar girma, ko takobi, ko wu}ar mulki, ko wani abu mai kama da wa]annan (Alhassan da Wasu, 1982:67). To, haka kuma, ba a raba saraki da shiga ta kamala wadda ita ce babbar riga da hula da rawani a {asar Hausa. Ba Sarakunan ba, hatta maro}an fada irin wannan sutura suke sawa, domin iyayen gidansu ke ba su kyautarsu. Akwai kuma ]abi'u wa]anda a al'adance ake so saraki ya siffanta da su, kamar ha}uri da dattako da kamun kai da rashin tsoro da gaskiya da adalci da kyauta da hangen nesa da magana ]aya da makamantansu. Maka]a [ankwairo na cewa:

Daudu: In kai magana ta zamna, x2
`Y/Amshi: Hohau ba ka da mai canzawa, x2…

([ankwairo: 'Ba takura kabrin gaba)

A {asar Hausa, al'umma ta rabu zuwa manyan rukunoni biyu, 'masarauta', (Sarki da sauran masu ri}e da mu}amai na mulki) da 'talaka' (ilahirin sauran al'umma da ke masarauta). Kodayake wasu daga cikin rukuni na biyu a yau sun koma rukuni na ]aya, ko dai saboda iliminsu na boko da mu}aman da suke ri}e da su na gwamnati, ko kuma hukumominta, da wa]anda arzikinsu ya sa suka kai ga wannan matsayi na samun mu}amai a masarautunsu. Irin wa]annan ne ake cewa, "Sarauta ta yi masu riga da wando".

## 2.4 Mata a {asar Hausa

Mace a {asar Hausa a da can (lokacin jahiliyya), kamar yadda sauran al'ummomin duniya irin su Larabawa da Indiyawa da na nahiyar Afirka da makamantansu suka ]auke ta, a nan ma maganar ba ta canza zani ba. An ]auki mace a matsayin halitta mai raunin gaske da kuma }as}anta, wadda ba ta da ta cewa a fannin rayuwarta, ballantana ta wani. Wannan ya sa sai yadda aka yi da ita, domin aba ce da ake mallaka, a sarrafa ta yadda aka so. A al'ummomin irin su Igbo da Tiv, babban ]a yake gadon matan mahaifinsa (kodayake ban da mahaifiyarsa).

Ayyukan Yeild (1960) da na Fafunwa (1974) da na Mack (1990) da na Talata Mafara (1999) da saura da dama sun bayyana halin }uncin da mace ta kasance a wannan zamani. A can da, Girkawa sun ]auki mace tamkar dabba, ana iya ]aukarta a yanka a duk lokacin da ta yi ba daidai ba. Misali, idan ta ri}a haihuwar 'ya'ya mata zalla, sai a yanka ta saboda ba ta da amfani ga al'umma, tun da ta kasa haihuwar jarumai (maza). A }asar Larabawa an yi lokacin da ake bisne ]iya mace da zarar an haife ta, domin gudun kada ta jawo wa al'ummarta abun kunya. A Sin ma, haka labarin yake, mace ba ta da daraja, domin ko wajen cin abinci, sai an ba maza sun ci, sun }oshi kafin a ba mata, duk kuwa da cewa su suka fi bayar da gudunmuwa wajen samar da abincin.

Ayyukan wa]annan masana, a ce an tsinci dami ne a kala, domin sun dubi matsayin mace a al'ada Bahushiya. Wato irin a matsayinta a al'ummar Hausa na halitta mai rauni wadda ba ta iya fitar da kanta, ballantana ta fitar da wani. Wannan ya sa Hausawa galibi ba sa ba ta jagoranci, kodayake, mata sun yi sarauta a Daura. Haka ma a Zazzau, an yi Sarauniya

Amina, an yi Magajiyar Argungu a Kabin Argungu, an kuma yi Innar Gobir, a Gobir. Duk da haka, mata sun kasance abin mallaka, domin namiji na iya ajiye yawan da ya yi masa a gidansa, gwargwadon bu}atarsa ko halinsa. Su kansu matan saboda duhun kai, suna ganin ba a halicce su ba, sai domin bautar aure (wadda ta wuce iyaka), ko da kuwa za su sa~awa ubangijinsu.

A wannan lokaci mace ba ta suturta jikinta saboda jahilci kuma babban aikinta a kullum shi ne kula da gida da harkokin da suka shafe shi. Ita za ta fita daji ta yi itace wanda za ta dafa abinci da shi, ta kuma kula da lura da yara, da makamantansu. Amma duk da haka, ko abin da ya shafi rayuwarta ba a shawara da ita, saboda an ]auke ta a matsayin mai }arancin hankali (}aramin hankali da hangen nesa).

Imam (1970), a matsayinsa na wakilin Hausawa, ya fito da tunanin Bahaushe game da mace a '*Magana Jari Ce'.* Hassan (2013:239-250), ya bayyana cewa, al'adar Hausa ta wancan lokaci, ta yi tasiri a kan mutuntakar Abubakar Imam ta fuskar matsayin mata a {asar Hausa. Yanayin }asar na lokacin, ya yi tasiri ga ginuwar tunaninsa a kansu da har ya rubuta wasu abubuwa da }ila za a iya cewa sun fifita maza a kan mata. A cewar masanin, al'adar Hausa ta yi tasiri cikin akasarin labaran *Magana Jari Ce*, domin matsayin da aka ajiye matan bai sauya da na al'adar ba, musamman idan aka yi la'akari da lokacin da aka rubuta littafin.

Hasssan (2013), ya bayyana yadda a *Magana Jari Ce,* aka ajiye matsayin mace a matakai biyu. Na farko mai rauni, na biyu kuma mai jure wa kowane tsangwama ta namiji. Wannan ya sa duk cikin labarun littafin, babu inda aka nuna mace a matsayin wata 'jaruma', mai iya gogayya da maza ta fuskar gwagwarmaya a rayuwa. Cikin labaran da ya kawo misalansu na

matsayin mace a Hausa shi ne na rashin shawara da mata, saboda mace tana da rauni, kamar yadda aku ya cewa Musa:

> Mamakin abin da ya sa ka ba mace shawara nake yi. Ai magana irin wannan sai mu tsakaninmu maza. In ba rashin hankalin mata ba, ina mutum zai ce za shi ga ]an'uwansa, sa'annan a hana shi? (Imam, 1, 1970:11).

Hassan (2013), ya kuma kawo misali na raunin mace a 'Labarin Wani Aku da matar Ubangijinsa" wanda aka nuna cewa matar attajirin fasi}a ce. An kuma fito da halin mata da }ulle-}ulle, da ya sa matar attajirin ta raba shi da sauran matansa ta hanyar shiga 'yan bori domin samun maganin da za ta mallake shi. A "Labarin Annabi Sulaimanu", an ga inda muguntar wata mata da bisa tsautsayi ta kwanta a kan ]anta ya mutu, a maimakon ta rungumi }addara sai ta ha'inci abokiyar zamanta, ta musanya ]anta matacce da na waccan mai rai, da sauran labarai da dama da ke nuni ga raunin halin 'ya mace, kamar yadda aka ]auka a al'adance.

Duk kuwa da haka, Adamu (1978), ya bayyana cewa, mata a {asar Hausa, tun a wannan zamani ba sa zaman banza, bayan sun kammala ayyukan gida, suna da sana'o'in hannu da suke aiwatarwa domin dogaro da kansu. Sana'o'i irin su ka]i da dakau da sa}a da kitso da sarrafa gya]a a fitar da mai, a yi }uli-}uli, da yin fura domin sayarwa da saura da dama. Har ila yau, suna kiwon dabbobin gida irin su kaji da tumaki da awaki, baya ga taya mazajensu aiki a gona a biya su ladansu. Abin sha'awa a wannan lamari, kamar yadda masanin ya bayyana mazansu babu ruwansu da abin da suka mallaka.

A wannan lokaci, ba kasafai mata ke aikin da aka fi sanin maza da shi ba, amma wannan bai hana a yi amfani da matan ba, musamman a wuraren bori, domin su ke wa}o}in bori, maza

kuma suna ka]a masu garaya. Suna kuma ki]an }warya, wato ki]an amada. Ana kuma amfani da mata a fada a matsayin jakadu da barori da sa]aku da Zabiyoyin Fada.

Ganin cewa wannan aiki ya shafi adabin baka (wato kirari) da al'adar da ke cikinsa, aka ga ya dace a duba mata a adabin baka. Balbasatu (2004: 42), ta bayyana cewa shahararrun masana da suka yi rubuce-rubuce a kan tarihin {asar Hausa, irin su Clapperton da Lander (1929) da Jeroma (1970, 1972,1973) da Joseph (1973) da Palmer (1978) da Mack (1985) da Boyd (1989) da kuma Hill (1972), dukkansu suna da'awar cewa, tun kafin zuwan ba}i {asar Hausa, matan Hausawa sun taka muhimmiyar rawa wajen tattalin arziki da siyasa da tarbiyya da fasaha da ciyar da harshen Hausa gaba, ta hanyar 'tatsuniya' da 'labarai' da 'kacici-kacici' da makamantansu. Wannan tatsuniya, ita ce masana irin su Fafunwa (1982), suka kira ta da 'makarantar farko', da ke koyar da halin zamantakewa. To amma, a duk inda aka tashi bayani game da gudunmuwar al'umma, maza ka]ai ake bayyanawa, ba a ambato mata, saboda ba a lura da haka. Zabiyar Fada na ]aya daga cikin matan da ke bayar da babbar gudunmuwa a fagen adabi da al'adun s Hausawa, musamman ma na fada.

Jihadin Shehu Usman [anfodiyo ma ya kawo sauyin rayuwar mata a {asar Hausa, domin ya karya maganar nan da ke ]aukar, ' namiji gumbar dutse mata kuma ta sakaina'. Mujaddadin kansa da'ya'yansa (musamman mata, kamar Nana Asma'u da Maryam Fodiyo) da almajiransa sun yi ya}in }wato wa mata hakkinsu ta hanyar wa'azi. A magance da wa}e-wa}e da kuma rubuce-rubuce da dama. Yadda jihadin ya yi tir da tauye hakkin talaka da saraki ke yi, haka ya yi horo ga mata musamman ma kan neman ilimin da za su yi amfani da shi su bauta wa ubangijinsu da takura ko danniya ta babu gaira babu dalili.

Wannan ya sa mata suka sami ilimin addini, suka san hakkinsu a kan mazajensu, suka san hakkin mazajensu a kansu, aka kuma daina sakinsu suna fita tsirara kamar dabbobi. Haka kuma suka san wasu harkokin rayuwa, kamar tsafta, musamman ta najasa da irin yadda addinin Musulunci ya koyar, tamkar yadda Talata Mafara (1999), ya kawo irin wa]annan sauye –sauye masu alfanu. To sai dai addinin ya raunana wasu al'adu da suka shafi mata, wanda ]aya daga ciki shi ne zabiyanci, wanda wannan aiki ya nazarta. Addinin Musulunci ya yi hani ga cu]anya wadda ba ta dole ba ce tsakanin maza da mata wa]anda ba muharramai ba ne, ya kuma yi hani ga ]aga muryar 'ya mace, ga shi kuwa zabiyanci ba ya yi wu wa sai da haka. Wannan ya sa yanzu al'adar take fuskantar barazana matu}a.

Zuwan Turawa {asar Hausa ma ya bayar da gudunmawarsa ga rayuwar mata. Sai dai kuma ya yi ~arna a wani fage, domin ya sa wasunsu sun saki reshe suka kama ganye. Ko kuma a ce an sami ci gaban mai shiga rijiya, kamar yadda Talata Mafara (1999), ya bayyana. An smi ru]ani tsakanin ha}}o}in mace a Musulunci da wanda Turawa suka zo da shi duk da cewa an ]auki lokaci mai tsawo kafin a fara sa 'ya'ya mata makarantun boko. Babbar matsalar ita ce gwagwarmayar jinsi domin a}idar Turawa ta nuna wa mata cewa su "'yan baya ga dangi ne", wanda ya sa matan suka fito domin su ma a dama da su a harkokin rayuwa. A wannan lokaci ne aka sami mata da suka yi ilimin boko suka bi gida –gida suka koya wa 'yanuwansu mata ya}i da jahilci. An kuma sami mata ungozomomi da likitoci da malaman makaranta, wa]anda ake bu}atarsu ainun a wannan lokaci. Sai dai a ce wasu al'adu, kamar na zabiyanci sun yi rauni. Alalmisali, a da can gadon zabiyanci ake yi yanzu kuwa 'ya'yan zabiyoyin da ake da su, sun yi ilimin boko, domin haka suke ganin wannan al'ada '}auyanci' ce ko 'jahilci'. Wannan ya sa yanzu fada ]ai]aiku ne na {asar Hausa suke da Zabiyar Fada sa~anin da.

## 2.5 Fada

Manyan {amusoshin Hausa wa]anda suka ha]a da *Bargery* (1934) da *Abraham* (1962) da *{amusun Hausa na Bayero* (2006) da kuma *Newman* (2007), duk sun bayyana fada da 'majalisar Sarki da gidansa da ma kewayensa'. A yayin da Mazawaje (1985:1), ya bayyana 'fada', da wurin da ake zartar da hukunci. Kamar kuma yadda Hauwa (2008:66-67), ta yi }arin bayani da ke cewa fada wuri ne na gudanar da mulki inda Sarki yake shugaban majalisa da sauran manyan mutane masu ri}e da mu}amai daban-daban wa]anda suka ha]u suka kafa majalisar zartarwa. A ta}aice, a iya cewa 'fada haraba ce ta mulkin Sarki a duk inda yake kuma nan ne muhallinsa ko tushen masarauta. Fada wuri ne na ba da umarni, saboda haka ba gini ne fada ba. Ko gari ko birni ko kuma daji Sarki ya sauka, to nan ma fada ce domin nan ma za a iya zartar da hukunci da kafa a}ida. To, haka kuma fada na ]aukar ma'anar *'samun shiga'*, masamman ga wani babba.

Masana da manazarta irin su Smith (1960) da Smith (1970) da Bello (1976) da Edward (1971) da Bagudu (1974) Usman (1974, 1981) da Boyd (1979) da Tsiga (1978) da Koforowola (1982) da Augie (1984) da Gusau (1988, 2008) da Tijjani (1990) da Ibrahim (1991) da Muhammad (1991) da Kafin Hausa (1997) da Bahago (1998) da Zara'u (2000) da Dalhatu (2002 da 2005) da Uba (2003) da Ibrahim (2004) da Wakili (2005) da Saleh (2006) da Hauwa (2008) da Umaru (2008) da Bunza (2009) da Guga (2010) da Muhammad (2012) da Fatima (2012) da Gaya (2012) da Maijidda (2012) da Ramatu (2012) da Shafa'atu (2012) da Abubakar (2013) da saura da dama duk sun nazarci tarihi da adabi da al'adun wasu daga cikin Fadojin {asar Hausa, a matakin digiri na tsakiya da na }oli, da bugaggun

littattafai da mujallu da mu}alu. To amma cikinsu babu wanda ya nazarci al'ada ko adabin Zabiyar Fada.

### 2.5.1 Tarihin Fada

Tarihi labari ne na abubuwan da suka wuce. Ta fannin tarihin kafuwar Masarautun {asar Hausa da Sarakunansu, ayyukan Smith (1960) da Smith (1970) da Bagudu (1974) a ce an tsinci dami ne a kala domin dukkansu sun nazarci kafuwar Masarautar Zazzau. Babbar matsalar da aka samu kan tarihin Zazzau kamar yadda Smith (1970:1-3), ya bayyana ita ce ta rashin gano garuruwan da suka kafu kafin kafuwar birnin Zariya. Wannan a cewar masanin ya faru ne saboda rashin gudanar da binciken tono kayan tarihi. Gusau (2010:45), ya yi }arin bayani da cewa garuruwan da aka tabbatar sun ginu kafin Zariya su ne Kufena da Turunku da kuma Gadas wadda ta samu wajen }arni na goma sha biyar, kodayake ba ta kai bun}asar Kufena ba. A cewar masanin wa]annan birane guda biyu (Kufena da Turunku), sun rayu kafin }arni na goma sha biyar kuma an yi masu ganuwa da kariya daga abokan gaba.

Shi kuwa Shehu (2012):141), cewa ya yi kafin a sami mazaunin Kufena da Turunku, al'ummomi sun fara zama ko sun yi wucin-gadi a Kawuri da Kargi da Gadas. Sannan suka zauna a Rikoci zuwa Wuciciri zuwa Turunku da Kufena. Daga }arshe kuma, suka kafa mazauninsu na dindindin da yanzu yake a birnin Zariya, gabas da Kufena. {asar Zazzau a cewar masanin tana arewacin Nijeriya cikin jihar Kaduna. Tana kuma tsakiyar {asar Hausa, domin haka duk ta inda ka ~ullo daga }asar za ka tarar cewa Zazzau na tsakiya. {asa ce mai kimanin murabba'in dubu goma sha uku kuma }asa ce mai yalwar }asa ta fuskar aikin noma. A da can baya babu }asar da ta kai Zazzau girma cikin {asashen Hausa kafin a raba

ta biyu, a }ir}iro masarautar Kudancin Kaduna, wurin da a da aka fi sani da 'Kudancin Zariya'. Fadar Zazzau na ]aya daga cikin fadar da aka nazarta a wannan bincike.

A yayin da [alhatu (2002), ya mayar da hankali a kan tarihin rayuwar Sarkin Zazzau Jafaru [an Isyaku. To haka aikin Usman (1981), ya yi tsokaci ne a kan sauye-sauyen mulki a Masarautar Katsina a tsakanin 1400 – 1883. Usman (1981:6), ya bayyana cewa marubucin tarihin Katsina na farko, 'Tarikh Imarat Qaryat Kashina' ya rawaito cewa Bagari Jirgo ne ya kafa Masarautar Katsina ta Ha~e, a kusa da inda {ofar Sauri take a wajen shekaru 3,500 da suka shu]e. Usman (1981), ya bayyana sauye-sauyen mulkin da ya gudana a masarautar Katsina a tsakanin 1400 – 1883. Musamman binciken ya mayar da hankali a kan tasirin da addinin Musulunci ya haifar a wannan lokaci. Kamar yadda ya fa]i a shimfi]arsa, Usman ya ce kafin jihadi tarihin Katsina da na dukkanin Masarautun {asar Hausa sun dogara ga tarihin baka, saboda haka an gudanar da nazarin domin sanin ainihin tarihin Katsina kafin zuwan masu jihadi. Nazarin ya kuma duba tsarin sarauta da sauye-sauyen da aka samu a Masarautar Katsina tsakanin 1400 – 1883.

Shi kuwa Gusau (2010:40), a nasa ra'ayin cewa ya yi asalin birnin Katsina yana komawa ne ga wasu maharba wa]anda ake wa la}abi da 'Adawa'. A bayani Gusau (2010), wa]annan maharba, sun zauna ne a gindin wasu duwatsu da suke a Dur~i–ta–Kusheyi da kuma birnin Bugaje. Bunza (1990:25), ya }ara da cewa an tabbatar da samun kufan kaburan mutanen Dar~i – ta-Kusheyi da wasu }auyuka na kusa da shi lokaci mai tsawon gaske. A inda ya yi }arin bayani cewa mutane sun zauna a dutsen domin ]ibar tama da samun nama.

A wani ra’ayin, an ce a }arni na sha biyu miladiyya wasu ba}i Dur~awa ne suka mallaki wurin da a yau ake kira Katsina (Hukumar Binciken Tarihi da Kyautata Al’adu ta Jihar Katsina, 2005:6). Shi kuwa Magaji (2002:26), cewa ya yi kundin tarihin nan, wato ‘Girgam’ ya bayyana Kumayau ]an Bawo kuma jikan Bayajidda, shi ne wanda ya kafa gidan sarautar farko a Katsina.

Gusau (2010), ya ruwaito Palmer (1928), yana cewa wai wani ne daga cikin Barebarin Diggare wanda ake kira Kumayau ya rayar da wata daula kusa da mazauna Dur~i-ta-kusheyi da garin Bugaje. A wani labarin Mamman (2010:1-2), ya bayyana cewa wani mutum da ake kira Katsi, wanda yana daga cikin zuri’ar Kumayau ne ya fara kafa masarautar Katsina a Dur~i –ta-Kusheyi, amma ya yi }aura zauna wani wuri da ake kira Ambutai wanda a yanzu unguwa ce a garin Katsina.Wai a lokacin da danginsa suka zo nemansa mutanen wurin sun ce masu,” Katsi na nan”.Wato Katsi yana nan ba zai koma [ur~i-ta-Kusheyi ba, daga nan sai kalmar ta kafu ta zama ‘Katsina’. A wata kissar kuma Mamman (2010), ya ce Katsina ta samu ne daga sunan wata attajira mai suna ‘Katsi’.

A wani }aulin Gusau (2010:42), ya ce Kumayau ne ya kafa kansa a karagar sarautar Katsina bayan cinye birnin Dur~awa. Daga nan kuma zuriyarsa suka ci gaba da ri}on Katsina har zuwa lokacin da aka sami Korau daga ‘Yantodo, ya kar~e mulki daga hannunsu ya tabbatar da nasa matsayin mulkin (Gusau, 2010:41). Wato bayan shekaru da dama zuri’ar Kumayau na mulki wani ba}o ya bayyana mai suna Korau a lokacin mulkin Sanau. Wannan ba}o ya kar~i mulki kuma yana cikin wa]anda suka yi suna cikin Sarakunan Katsina, domin ya yi fice saboda raya masarautar, ga shi kuma maya}i. Har yau akwai ‘[akin Korau’ da takobinsa a Fadar Katsina (wato takobin da aka fi sani da ‘bebe’) da kuma wata tukunyarsa (ta }arfe),

wadda aka ce yake amfani da ita domin dafa sauyoyi da ‘yan ji}e-ji}e na neman tsari. Kalmar Korau, ta zama kirari da alamci na zuga Sarakuna Katsin

Har ila yau Smith (1978), ya nazarci sauyin mulki a Masarautar Daura tsakanin 1800-1958, wato gwagwarmayar mulki tsakanin Ha~e da Fulani masu jihadi da rawar da Turawan Mulkin Mallaka da }asar Damagaran (Zinder) suka taka a tsakanin wannan lokaci. Nazarin ya bayyana cewa a tsakanin 1804-1910, Fulani masu jihadi sun ci {asashen Hausa irin su Gobir da Daura da Katsina da Kano da kuma Zazzau, wanda a sanadiyyar haka, Zazzagawa wa]anda suka }i biyayya, suka yi kudu da Zazzau suka sami matsuguni a Abuja, Katsinawa suka yi yamma zuwa Mara]i, Gobirawa suka nufi Tsibiri, Daurawa  wasu suka yi Zango (Zangon Daura), wasu Magarya, wasu kuma |aure. Kanawa kuwa suka yi Zazzau, wasunsu kuma suka tafi Mara]i. Abin mamaki, kamar yadda Smith (1978), ya yi bayani, cikin wa]annan }asashe Daura ce kawai sarauta ta dawo hannun masu mulkin }asar na asali wato Hausawa. Ya ci gaba da ba da yanayin Masarautar Daura da fa]inta da yawan al’ummominta (a wancan lokaci), tare da hanyoyin tattalin arzikinsu da kuma addininsu. Manazarcin ko marubucin ‘*The Affairs of Daura’,* ya kuma kawo tarihin Daura kafin jihadin Shehu Usmanu Bin Fodiyo, zuwa bayansa da zuwan Turawa da kuma yadda Turawan suka taimaka wa masu sarautar ta asali sarauta ta dawo hannunsu bayan shekara ]ari (100). Saura sun ha]a da yadda tsarin mulki yake a Masarautar Daura a da can har zuwa mulkin Sarkin Daura Abdulrahaman da mahaifinsa Sarki Musa.

Shi kuwa Tsiga (1978), ya za~i Sarauniya Daurama ne ya yi tsokaci a kanta, kamar yadda Boyd (1979), ita ma ta za~i Sarkin Gobir Bawa Jangwarzo, ta yi tsokaci a kansa a matsayin jarumin Sarki da Gobir ba za ta ta~a mantawa da shi ba a tarihin  Masarautar da ma {asar

Hausa. A ra'ayin Tsiga (1978), Sarauniya Daurama ita ce mafi mahimmanci a tarihin {asar Hausa ba wani ba saboda dalilai kamar haka:

- ita ce tarihi ya bar mana wadda ta ri}e wani mahimmin matsayi a asalin Hausa.
- abu ne sananne cewar tun daga lokacinta, wanda duk ya yi }o}arin shigowa Daura da ya}i, to shi kuwa wannan Sarki sai dai a yi ba da shi ba.
- sarauniya ba ta ta~a kaiwa kowa ya}i ba (Tsiga, 1978:28).

Wannan nazari na Tsiga bai ta~o *Dakama* ba, duk da cewa kuwa akwai ta tun da can da mata ke sarautar Daura. Wannan nazari ya nazarci *Dakama* da ma sauran zabiyoyin fadar Kabin Argungu da Ha]eja da Kano da Kazaure da kuma Zazzau.

Zara'u (2002), kuwa ta wallafa littafi ne a kan tarihin Masarautar Kano, kama tun daga kafuwarta zuwa mulkin Fulani wa]anda zuri'arsu ce har yanzu take kan gadon mulki. Marubuciyar ta bayyana tarihin kafuwar Kano da tsari da sigogin sarautu tun daga mulkin Ha~e har zuwa ga mulkin Fulani, }ar}ashin Daular Usmaniyya tare da irin ayyukan da Sarakunan Fulani suka yi wa Musulunci. Ta kuma ta~o salsalar 'ya'ya da jikokin Sarkin Kano Ibrahim Dabo, wato zuri'ar marigayi Sarkin Kano Mai Martaba Alhaji Ado Bayero. Zahra'u ba ta tsaya a nan ba, ta yi tsokaci kan wasu sarautu na hakiman Sarki da dagatai da jarumai da na 'ya'yan Sarki da bayi da na sauran jama'a. Ta kuma bayyana tarihi da yanayin wasu al'adun Masarutar Kano wa]anda suka ha]a da zaman Sarki da tsarin kai gaisuwa da mahimman bukukuwa a fadar da nau'o'in kayan adon dawaki. Cikin wa]annan al'adu ne a shafi na 77 ta yi bayanin wata mata a fadar, wato '*Magajiyar Gwanso'* wadda ta bayyana cewa aikinta shi ne yi wa Sarki kirari kuma ba ta yi wa kowa duk fadar, sai shi ka]ai. An yi }o}ari aka zanta da ita domin samun cikakken bayani.

A bayanin da ta yi, *Magajiyar Gwanso* Zabiyar Fada ce da ta yi wa Sarkin Kano Ado Bayero kirari a lokuta mabambanta, musamman lokacin da zai fita fada da yayin shagulgulan salla da mahimman lokutan da yake aiwatar da wani taro, amma Allah Ya yi mata rasuwa. To, sai dai babu ~ur~ushin kirarin da ta yi. A zamanin Zabiya Magajiyar Gwanso, tana shiga irin ta bayin Sarki irin na macen dogari, amma Allah Ya yi mata rasuwa. A kuma shafi na 91, cikin maro}a da mawa}an fadar Kano ta kawo '*Gawaji na Sarkin Kano',* wanda ta yi bayana shi a matsayin *Wawan Sarki a Fadar Kano.* Aikinsa kuwa shi ne yi wa Sarki kirari yana cewa, *"Giwa toro ya fito".* Yakan ri}e gora a hannunsa yana ihu a yayin da yake yi wa Sarki kirari. Shi ma yana da yara masu yi masa barantaka wa]anda suka ha]a da: Galadiman Gawaji da kuma Ciroman Gawaji. A yayin da Umaru (2008), shi ma a nasa ~angaren ya yi nasa kan tarihin daular Fulani a masarautar, [alhatu (2005), kuma ya taskace tarihin Sarki Abdullahi Bayero tun daga tsatsonsa.

Ibrahim (2004), ya taskace kirarin da yi wa Masarautar Kano domin fayyace nasabarsa ga tarihinta da al'ummarta da matsayinta na cibiyar kasuwanci a Arewacin Nijeriya. Kamar yadda Wakili (2005), ya taskace tarihin Masarautar Ha]eja kama tun dag kafuwarta zuwa gwagwarmayar da ta auku a tsakanin Turawan Mulkin Mallaka da jama'ar Ha]eja. A cewar Wakili, masana tarihi na da'awar an kafa garin Ha]eja a }arni na goma sha biyar. Wanda kuma ya samar da garin, wani maharbi ne Babarbare daga Machina, mai suna Ha]e, wanda ya taso daga can ya nufo kudu yana farauta har ya iso daji mai dabbobi da yawa ya yada zango, daga nan kuma zama ya kankama.

A wani }aulin, kamar yadda Wakili (2005:6-7), ya bayyana wasu Fulani ne makiyaya wa]anda suka fito daga zuriyar Har]o Abdure daga Machina a wajen }arshen }arni na goma sha bakwai suka kafa masarautar Ha]eja. Kowane }auli ne gaskiya, Babarbare Ha]e ko Fulani zuri'ar Har]o Abdure, }aulolin biyu sun ce sun fito ne daga Machina! Wannan }auli ya ci gaba da bayanin cewa da Har]o Abdure tare da jama'arsa suka iso Jama'are, wadda ke kusa da garin Ha]eja (tare da shanunsu), sun fara zama a nan (yada zango) domin ni'imar wurin saboda abincin dabbobi da ruwa. To wai bayan rasuwarsa Har]o ]ansa Umar ya taso ya yi fice har aka na]a shi Sarkin Fulanin Ha]eja.

### 2.5.2 Al'adun Fada

Kusan a ce bakin masana bai sa~a ba dangane da ma'anar al'ada, sai dai abin da ba a rasa ba na amfani da harshe musamman za~en kalmomi. Domin haka a iya cewa sun dubi kalmar ta fuska ]aya. Masana irin su Ojo (1966) da Umar (1981) da Ibrahim (1982) da Gusau (1983) da Ager (1990) da Mu'azu (2003) da Bunza (2006) da Bodley (2009/2010) da Taylor (2009/ 2012) da Yakasai (2012) da saura da dama sun bayyana al'ada da ]aukacin tafarkin rayuwar al'umma baki ]ayanta daga haihuwa har mutuwa. Wannan ya ha]a da irin zamantakewar da ta ke~anta ga al'umma da fasaharta da }ere-}ere da tunaninta da hanyar tattalin arziki da a}ida da sana'o'in gargajiya da ]abi'u da sauran harkokin rayuwar ]an Adam ta yau da kullum.

Bunza (2006:xxv), ya bayyana cewa a harshen Hausa kalmomin da suka fi kusa da al'ada su ne 'sabo' da 'gado' da 'hali' da 'sada' da kuma 'gargajiya'. A cewar masanin za a iya yarda da haka idan aka yi la'akari da yadda Bahaushe yake gina karin magana da wa]annan kalmomi. Misali, '***Sabo jini ne ba ya sauyawa'*** da '***Gado kyawun ]a***" da "***Hali zanen dutse***" duk suna bayyana abin da aka saba yi yau da gobe da ya zama jiki, abin da ya

ke~anta musamman ga wani/ wasu. Shi kuwa Ibrahim (1982: xiii), cewa ya yi ainihin kalmar ba Bahaushiya ba ce aro ta aka yi daga Larabci,'Al'adab' wadda a Larabce take nufin wani abu da aka saba yi. Su ma Hausawa ba su canza mata ma'ana ba domin a Hausa al'ada tana nufin abubuwan da aka saba yi a rayuwar yau da gobe.

Al'ada madubi ce ko hanyar da ke sheda al'umma, domin ita ke bambanta wannan al'umma da waccan. Ko cikin al'ummar Hausa wasu al'adu sun bambanta daga wannan wuri zuwa wancan kuma a duk muhallin da ]an Adam ya iske kansa al'adar wurin ke tasiri a rayuwarsa. s

Bunza (2006:xxxii), ya fayyace haka inda ya ce al'ada rayuwar ]an Adam ce tun daga haihuwarsa har zuwa kabarinsa. Kamar yadda ya yi }arin bayani ya cewa wannan ya sa babu wata al'umma da za ta rayu a doron }asa face tana da al'adar da take bi kuma da ita ake iya rarrabe ta da wata da ba ita ba. A kuma ko'ina mutum ya samu kansa duk wata ]abi'ar da ya tashi da ita, tun farkon rayuwarsa ya tarar a wurin da ya rayu ko yake rayuwa, ita ce al'adar da za a yi masa hukunci a kai.

A nasa ra'ayin Adamu (1980), cewa ya yi al'ada ita ce baki ]ayan fasahar al'umma da dukkan bu}atun wannan al'umma na rayuwa. Shi kuwa Ager (1990), kamar yadda [antumbushi (2009:161), ya ruwaito cewa ya yi al'ada aba ce mai tasiri }warai saboda ba maganar littattafai ko wurin wasannin kwaikwayo ko ilimi mai zurfi da bincike ba ce, a'a, amma, har ma akwai ]abi'u da abinci da jin da]in zaman tare da wasannin shekara – shekara da musayar ra'ayoyi da kuma ku~utar da }uncin rayuwa da kuma tsara makoma ingantatta.

Abdul}adir (2001:475), kuwa ya bayyana al'ada ne da dukkan ilahirin abubuwan da jama'a ta yarda da su kuma take amfani da su wajen harkokinta na yau da gobe.Ya ruwaito Umar (1981), na cewa siffar }asa da yanayinta na da tasiri wajen ginuwar al'adun kowace al'umma. Tabbas, rayuwar mutumin da ya tashi a }asar Turai ta bambanta da wanda ya tashi a saharar Nijar. Haka kuma wanda ya tashi a }auye da wanda ya tashi a maraya ko birni. Mu'azu (2005), da yake tofa albarkacin bakinsa ya bayyana cewa al'ada koyonta ake yi kuma aba ce da kowa yake aiwatar da ita a zuci, ya kuma gudanar da ita a aikace. Sannan kuma aba ce mai rai, tana kuma iya }aruwa, ko ta ragu a sanadiyyar cu]anya da ba}in al'umma. Ibrahim (1982: 310), ya yi bayani kan irin wanan }are-}are da al'adu kan samu daga waje, da cewa ba sa tauye darajar al'umma, a maimakon haka ma, }ara bun}asa take yi. Ya ce idan aka dubi tarihin Larabawa kansu, bayan zuwan Musulunci da cu]anya da wasu al'ummu, al'adunsu sun }ara ha~aka da bun}asa. Idan kuma aka duba al'adun Farisawa da na Romawa sun yi tasiri matu}a kan al'adun Larabawa. Haka kuma Turawa kafin su kai matsayin da suke yanzu sai da suka }aru daga al'adun Girkawa da Larabawa. Kamar yadda ya bayyana, al'adu biyu ne suka yi tasiri a rayuwar Bahaushe, na Larabawa a sanadiyyar addinin Musulunci da al'adun Turawa da suka kawo boko bayan mulkin mallaka wanda ya yi kanta musamman a zuciyar 'yan boko.

Shi kuwa Ojo (1966), ya bayyana al'ada ne da abubuwan zahiri da mutane ke yi wanda ya ha]a da irin maganganunsu da abincinsu da raye-raye da kayayyakinsu da yanayin gidajensu ko muhalli da yadda suke zamantakewarsu da irin ayyukansu da wasannin da suke gudanarwa.

Har ila yau Nwabara (1981:71), ya ruwaito Edward na bayyana al'ada da harshe na sirri, da ya ke~anta ga wata al'umma,wanda ya ha]a da irin maganganunsu da sauran matakan

rayuwa. A ta}aice, a iya cewa al'ada tamkar ita ce rumbun dukkanin tunane-tunane da falsafa da basira da sauran ginshi}an rayuwar ]an Adam.

Masana al'ada sun kasa al'ada ta fuskoki daban-daban. Bunza (2006:xxxiii) ya ce, za a iya fayyace al'ada daga }umshiyarta. Ya yi bayani cewa ta fuskar yanayi, ana kasa al'adar Bahaushe gida uku. Wadda ake furtawa da baki da wadda ake aiwatarwa da ga~o~i da kuma wadda ake }udurtawa a zuci ta zama a}ida. Kodayake ya ce a faifan nazari al'adar Bahaushe ta kowane zamani da fanni ana kallon ta a manyan ~angarori biyu, al'adun gargajiya da caku]a]]un al'adu. Al'adun gargajiya su ne al'adu zalla da aka gada tun fil azal, daga kaka da kakanni. Caku]a]]un al'adu kuwa su ne wa]anda wasu ba}i suka kawo wa Bahaushe, wato al'adun addinin Islama da na Bani Isra'ila da na zamani.

Bodley (2009/2010), cewa ya yi a fannin nazari za a iya kasa al'ada zuwa manyan rassa hu]u. Kashi na farko shi ne na kayayyakin gargajiya da suke da dangantaka da samar da abinci da nau'o'in musayar kayan al'adu da fasahar }ere-}ere, domin samar da kayan aiki da muhalli da tufafi. Kashi na biyu shi ne al'adun zamantakewa da ya }unshi aure da haihuwa da yanayin shugabanci da siyasa a al'adance. Kashi na uku kuwa, shi ne na al'adun da suka shafi a}ida, kamar yarda da tunanin al'umma a kan abin da suka amince ko suka yi imani da shi. Misali, addini da sauran }a'idojin da kowacce al'ada ta gindaya ga al'ummarta. Kashi na }arshe shi ne na fasahar al'umma da suka ji~anci wa}e-wa}e da raye-raye da zala}ar baka da irin girke-girkensu ko abincinsu da gine-gine da adonsu da makamantansu. Wannan na nuni da cewa ba mutum ]aya kawai ke }ir}iro al'ada ba. A'a al'umma ke ha]uwa su ga abubuwan da suka dace da su, su aminta a kansu, sannan kuma su yi watsi da wa]anda ba su amince masu ba. Bodley (2009) ya ci gaba inda ya kawo sigogin al'ada guda uku a inda ya ce al'ada a ba ce wadda ake gani a zahiri, al'ada tarayya ta haifar

da ita, muhalli da al'umma suka ha]u suka samar da ita. Sannan al'ada koyonta ake yi ba kawai kara zube take ba. Bahaushe ya jaddada haka a karin maganarsa da yake cewa "Zama da ma]auki kanwa shi ke kawo farin kai" da "Abokin ~arawo ~arawo ne", da kuma "Zomo ba ya gudu ]ansa ya yi rarrafe". Watau bayan muhalli da al'umma sun gina al'ada, jama'a za su koye ta.Sannan al'ada kuma ba ~oyayyar aba ba ce a zahiri take.

Bunza (2006:xxxi) ya yi }arin bayani a kan nau'i na biyu inda ya yi da'awar cewa al'ada mutane ke yin ta ba dabbobi ko }wari da tsirrai ba. Mutanen da ke gudanar da al'ada suna sarrafa ta ta fuskar da suka gaje ta kamar yadda suka tarar da ita.Wannan ne ya sa imanin da mutane masu al'ada ]aya suka yi da al'adar da suke yi, ya sa suke kallon junansu ta fuskar al'adun da suke aiwatarwa. Wannan kallo da suke yi wa juna, wani mataki ne na musamman da zai ba mai nazari damar auna abubuwan da suke kallon junansu da su, da irin imanin da suka yi da ya }unshi yarda ko imani da al'adunsu.

Yakasai (2012:31), ya ruwaito Nelson (1960), shi kuma a tasa fahimtar yana cewa a fannin walwala da ya ji~anci dangantakar al'ada da harshe, ana iya kallon al'ada ta hanyoyi biyu. Hanya ta farko ita ce ta basirar ]an Adam, ta biyu kuma ta kimiyyar rayuwar ]an Adam ]in. Watau jimilar dukkan ilimin zaman tare da hanyoyin cu]anyar yau da kullum na kowacce al'umma. Wannan na nuni da cewa al'ada ita ce tamkar rumbun dukkan tunani ko falsafar al'umma da basirarsu. Ya kuma tabbatar da dangantakar al'ada da harshe da dangantaka irin ta jini da tsoka domin da wuya a iya ware harshe daga al'ada. Harshe ya zama wani ginshi}i na dogaro ga kowacce al'ada. Wnnan ya sa nazarin harshe ba zai yi wu ba sai tare da sanin al'adar al'ummar da wannan harshe yake da ita. Wannan ya tabbatar da cewa nazarin Zabiyoyin Fada ba zai kammalu ba ba tare da an ha]a da kirarin da suke aiwatarwa ba. Wato harshe ~angare ne na al'ada wanda za a iya yi masa la}abi da' tagarta', domin ba a

le}a tagar ]aki ba tare da ganin abin da ke cikin ]akin ba, kamar yadda Yakasai (2012), ya kawo:

> Dangantakar da ke tsakanin harshe da al'ada dangantaka ce tabbatacciya wadda }ullinta ya fi gaban a kwance shi, musamman ma da yake ba a iya tantancewa ga ainihin lokacin da ta }ullu. Bugu da }ari, dangantakar harshe da al'ada dangantaka ce sananninya, don haka ne ma ya sanya ake cewa al'ada ba za ta samu ba idan babu harshe. Wato dai, idan har al'ada na nufin sabo cikin hanyar rayuwa, ashe ke nan, harshe ne tantagaryar al'ada, Yakasai (2012:46).

Yakasai (2012), ya ci gaba da fayyace wannan dangantaka da cewa ita ta samar da muhalli daban-daban na magana, a inda kowane muhalli akwai kalmomin da suka ke~anta da shi, kuma a duk lokacin da aka yi amfani da wata kalma inda ba muhallinta ba, za a ji abin banbarakwai, wato ba a saba jin wannan kalma a wannan muhalli ba. Ya kuma kawo misali da yanayin malami ya ri}a yin amfani da kalmomin batsa a cikin wa'azinsa ko kuma saurayi ya ri}a furta kalmomin soyayya a gaban iyayen budurwarsa (ko ma nasa), za a ga cewa an sa~a wa al'ada da magana da muhalli. Al'ada aba ce mai matu}ar mahimmanci ga al'umma musamman al'ummar Hausawa, domin sukan ri}e ta tamkar abin biya gare su dangane da yadda suke tafiyar da harkokin rayuwarsu gaba ]ayanta. Al'ada ke koyar da harshe, ta ilmantar, ta shirya tattalin arzikin al'umma da tsarin zanantakewarsu sannan kuma ta nisha]antar, (Yakasai,2012:33:34).

Kasancewa mafi yawan Hausawa Musulmi ne, ya sa addinin Musulunci da al'adun Larabawa suke da dangantaka da al'adun Hausawa. Ibrahim (1982:298), ya yi bayanin cewa a wasu wuraren, Musulunci da al'adun Larabawa ne suka shiga cikin al'adun Hausawa, a wasu wuraren kuma, su al'adun Hausawa ne suke shiga cikin wani abu da Musulunci ya

kawo. A }arshe addini da al'ada sun ha]u suka zama abin da yanzu ake kira al'adun Hausawa.

A iya cewa bayan Bahaushe ya amshi addinin Musulunci, yanayin maganarsa ma ya canza (domin wani abin da zai iya furta shi a da yanzu ba zai iya ba). Suturarsa ta canza, muhallinsa ya canza, abincinsa ya sami }ari, yanayin zamantakewarsa ya canza, ya sami }ari a bukukuwan da yake aiwatarwa, ya kuma yi watsi da wasu al'adu da a da yake aiwatarwa, wa]anda yanzu suka zama abun tir. Misali, a da Bamaguje yana iya auren mata barkatai, yanzu kuwa an }ayyade masa zuwa hu]u. Da yana shan giya wadda yanzu haramunce. Da gidansa a bu]e yake, yanzu kuwa ya yi katanga har yana kulle da sauran abubuwa da da dama a Msulunci ya zo masa da su.s

A ~angaren dangantakar al'ada da adabi kuwa Umar (1987), ya tabbatar da cewa: adabi musamman na baka tamkar hanya ce da al'umma ke amfani da ita domin bayyana al'adunta.

- Adabin baka yana zayyana hoton rayuwar al'umma domi fito da al'adun al'umma a gansu }uru-}uru.
- Adabin baka ma'ajiya ce wadda al'umma ke amfani da ita domin adana al'ummarta.
- Adabin baka madubi ne da ake amfani da ita domin ganin taswirar rayuwar al'umma, musamman ta fuskokin mulki da tattalin arziki.
- Adabin baka makaranta ce da ke gyara rayuwar al'umma.

Wannan na tabbatar da cewa dangantakar al'ada da adabi, makusanciya ce ainun, domin suna tafiya kafa]a-kafa]a. Da farko dai kamar yadda Umar (1987), ya bayyana za a iya ganin wannan dangantaka ta yadda al'umma ke amfani da fasaharsu su bayyana al'adunsu. Misali, zantukan hikima na al'umma da wa}e-wa}ensu, suna nuna yanayin rayuwarsu ta yau da

kullum. Kamar zamantakewa tsakanin babba da yaro da ta maigida da matansa ko magidanta a unguwa ko kuwa a wurin sana'a da ma gari baki ]aya da makamantan haka. Alalmisali, ana cewa:

babba juji ne,
babban  wa uba,
yaro ba shi kai gayya, sai da hannun babba,
yaro maraki  ne ba abokin tafiya ba,
yaro da rarrafe yakan tashi,
laifin yaro }iwa, laifin babba rowa.

Wannan duk yana nuni da rayuwar al'umma a kan dangantaka tsakanin babba da yaro kowa da huruminsa.

To haka kuma, adabin baka ma'ajiya ce ta adana al'adun al'umma. Za a iya ganin haka daga wasu al'adun Hausawa wa]anda da can aka aiwatar da su, amma duk da cewa sun gushe ana sanun ~ur~ushinsu a adabin baka, musamman a wa}a. Misali, da a {asar Hausa idan sarauta ta fa]i, Sarki ya rasu ko aka sauke shi, a al'adance  kokawa ake yi, wanda ya nuna bajinta ta jaruntaka ya yi nasara, shi ne sabon shugaba. Wanda ke nuni da cewa mai }arfi ke rinjaye.

Har ila yau, da adabin baka ne ake amfani a ga taswirar rayuwar al'umma. Alal misali ta fuskar mizanin da talaka ya ]auki saraki, ya fito }arara a kirari da wa}o}in fada. A iya cewa kamar yadda yanzu (a al'adance), sarauta ta zama ta gado, mawa}an baka kan jaddada asalin basarake na cancantar gadon sarautar gidansu. A wa}ar Alhaji Shehu  Sa'idu (Garkuwan Gwambe), ta Alhaji Musa [ankwairo, tun daga gindin wa}ar, '*kak ka sake `yan maza su hwa]a ma, [an Umar Sa'idu Garkuwan Gwambe'*,  masu sauraro aka sanar da su

cewa Alhaji Shehu gadon sarautar ‘Garkuwan Gwambe’ ya yi daga mahaifinsa, Alhaji Umaru Sa’idu Garkuwan Gwambe, watau ‘ ]an na gada’ ne.

Sannan kuma adabin baka makaranta ce da ke gyara rayuwar al’umma. Babban misali shi ne na tatsuniyoyin da ake yi wa yara da yawaitar karin maganganu daga bakin manya, yara sukan }aru da darussan rayuwa daban-daban,musamman ta fannin rungumar kyawawan ]abi’u irin su gaskiya da ri}on amana da zumunci da jaruntaka da ha}uri da adalci da gujewa akasinsu.

Wannan ya tabbatar da cewa za a iya amfani da adabi a nazarci rayuwar al’umma, kamar yadda wannan nazari ya yi amfani da al’adar Zibiyancin Fada ya bibiyi adabin da ke cikin al’adar. Wato kirarin Zabiyoyin Fadojin {asar Hausa, sannan ya nazarci al’adar da ke ciki, kamar yadda taken aikin ya nuna, “Kirarin Saraki a Bakin Mata: Nazarin Zabiyancin a {asar Hausa. An yi amfani da al’adar Zabiyanci, a matsayin mahanga aka hango adabin da ke cikinsa, wato kirari. Sannan kuma aka fitos da wasu muhimman abubuwa da ya shafi rayuwar al’umma, musamman game da tunanin Bahaushe a kan saraki da sarauta a {asar Hausa.

Mahanga a nan sinadari ne na hange, ko wurin hange wanda a wannan bincike shi ne ‘al’ada.’ Sanannan abu ne cewa al’ada a aikace ake aiwatar da ita, adabi kuwa a magance ake furta shi, a matsayinsa na fasahar bayyana al’ada. Saboda haka irin suturar da Zabiyoyin Fada ke sanyawa a lokuta na musamman da yanayin da suke aiwatar da zabiyanci a fada, misali a gaban Sarki suke ko a baya, a gefen dama ko hagu? Duk wannan al’ada ce amma kirarin da suke yi wa saraki adabi ne, domin a magance yake. To sai dai kirarin yana tattare da rayuwar al’umma ciki da wajenta. Alalmisali, kirarin mizani ne da talaka yake auna

saraki, kamar asali a sarauta domin a al'adar Bahaushe a yau ana gadon sarauta ne. Haka kuma ana son shugaba ya kasance jarumi ba rago ba. Har ila yau kowacce al'umma tana fatan ta sami shugaba adali da tausayi da son jama'arsa. Kamar yadda ake son shugaba mai kare martaba da jaddada addinin al'ummarsa. Sannan kuma ana son shugaban da hannunsa yake bu]e  (mai bayarwa musamman ga masu bu}ata).

Kirarin yana kuma sanya nisha]i / annashuwa ga mai sauraro da wanda aka yi dominsa. Baya ga fito da hikima da zala}ar harshe da koyar da yanayin rayuwa a dun}ule. Yana kuma fito da tarihin masarauta, musamman zayyano Sarakunan da suka gabata da fito da wani batu na musamman da masarauta ta shahara a kansa.

Ta fuskar al'adun fada akwai ayyuka irin na Muhammad (1991), da ya dubi tasirin zuwan Turawa kan sarautun gargajiya a {asar Hausa. Muhammad (1991),  ya yi tsokaci dangane da tasirin zuwan Turawa ga sarautun gargajiya a {asar Hausa, musamman ma a Kano. Kodayake nazarin bai tsaya a Kano ba ka]ai ya ta~o tasirin da aka samu a Masarautun Gobir da Daura da Katsina da kuma Kano. Nazarin ya fi ba da hankali kan sauyin sunayen sarautu a masarautun kafin jihadi da bayansa da kuma bayan zuwan Turawan Mulkin Mallaka.s

Magaji (2002), ya nazarci wasu bukukuwa na al'adu da suka ke~anta musamman ga Masarautar Katsina, ya fito da su duniya ta san su, duk kuwa da cewa yanzu ba aiwatar da su. Wa]annan al'adu da kamar yadda Magaji ya bayyana,bukukuwa ne da ke nuni ko tabbatar da karar Katsinawa. Wato '*Bikin [iya'* wanda ake gudanarwa a lokacin kaka da '*Bikin' Dubu'*, wanda ba shi da tsayayyen lokacin da ake aiwatar da shi, sai dai biki ne na nuna bajinta ba na }arfi ba, a'a na dukiya. Biki na uku shi ne 'Bikin Tambarci'. Wannan biki ne da matan Katsinawa ke gudanar da shi domin nuna }asaita. Wa]annan bukukuwa sun

ji~anci Masarautar Katsina ne, to amma Katsina na cikin wannan nazari, sai dai shi a kan Zabiyoyin Fada ne na {asar Hausa.

To haka kuma ayyukan Saleh (2006) da Hauwa (2008) da Abubakar (2013), duk sun yi tsokaci ne a kan sarautun Shamaki da [anrimi da kuma Mai Babban [aki da Sarkin Hatsi a Fadar Kano. Hauwa (2005), ta yi nata binciken ne kan abin da ya shafi mata a fadar, amma ba a kan Zabiyar Fada ba. Ta yi }o}ari ne ta fito da tarihi da asalin sarautar 'Mai Babban [aki'a Masarautar Kano.Nazarin ya ba da }arfi kan tarihin Hajiya Hasiya Bayero, mahaifiyar marigayi Sarkin Kano Alhaji Ado Bayero, wadda take ri}e da wannan sarauta a lokacin da aka gabatar da nazarin. Aikin na Hauwa ya yi tsokaci kan aikace -aikacenta da gudunmuwarta a Fadar Kano. A }arshe aikin ya yi }o}arin kwatanta sarautar 'Mai Babban [aki' da ta 'Magajiyar Daura' da ta Innar Gobir, domin gano kamancin da bambancinsu. Kodayake wannan aiki na Hauwa (2005), na da danganta da wannan za a iya cewa abin da ya ha]a su shi ne fada.

Domin raya da kuma fito da martabar wani ~angare na al'adun Hausa, wato sarautu (kamar yadda manazarcin ya ce), Saleh (2006), ya ]auki wasu daga cikin sarautun bayi a Masarautar Kano ya nazarce su.Sarautun kuwa sun ha]a da na Shamaki da [anrimi, saboda haka nazarin ya bayyana tsarinsu da ayyukansu da kuma tasirinsu, musamman ma a Masarautar Kano. Wannan aiki ba a kan Shamaki ko [anrimi aka aiwatar da shi ba, a'a an nazarci kirarin saraki ne a {asar Hausa daga bakin Zabiyar Fadar. Fadar Kano kuma na ]aya daga ciki. A yayin da Khalil (2007a), ya nazarci bayi a Fadar Kano. Nazarin ya yi cikakken bayani kan tarihin zuwan Fulani {asar Hausa, musamman ma fadar Kano da yanayin bauta a Musulunci, tare da hanyoyin da ake bi a mallaki bawa. Misali, ta hanyar kyauta ko sakayya ko biyan bashi ko ganimar ya}i da makamantan haka. An ci gaba aka bayyana tsari da

ayyukan bayi a Fadar Kano da kuma yadda ake za~ensu, da kirarin kowanensu. Aikin musamman ya fi mayar da hankalin kan Shamakin Kano Alhaji Inuwa ]an Sarkin Zage. A iya cewa shi ma ya mamaye littafin, kodayake da ma taken littafin shi ne, *Bayi a Gidan Dabo: Tarihin Shamakin Kano Inuwa ]an Sarkin Zage.*

Khalil (2007b), a wata fuskar ya nazarci Hausar Sarauta a Fadar Kano, inda ya bayyana cewa a masarautar, ana amfani da al'adu da ]abi'un Hausawa da Fulani, wato sakaya magana a maimakon a fa]e ta gatse –gatse, saboda alkunya da girmamawa, wa]anda aka fi sani da *fulako*, a Fulatanci. Khalil kawo misalai da cewa, duk Sarakunan Kano da suka shu]e da wa]anda suke gadon mulki ba a kiran sunayensu ko sunan abin da ke kama da furucin sunan a Fadar Kano, a'a sai dai a yi masu la}abi. Alalmisali, 'Sulaiman'ko 'sulai' (na ku]i) a kan sakaya a ce '}arfe', 'Ali' da 'allura', sai a ce 'Gadanga' da 'ma]inkiya', 'Abbas' da 'albasa', 'Mai girma', ko '[an makaranta' da `yar lambu', sunan 'Inuwa' da 'inuwa' , sai a kira ssu 'mahuta' 'Ado' da 'ado''Maikano' da 'kwalliya'. Haka kuma, duk kalmomin da Bahaushe ba ya fa]insu (kamar kalmomin batsa), ba a ambatonsu a cikin Fadar Kano. Nazarin ya kuma ta~o yadda Fadawa a Masarautar Kano suka }ir}iro hanyar sadarwa cikin kiran' lafiya', misali:

Lafiya sarkin Musulmi  
Lafiya mai da garin wani kango  
Lafiya barden Mahadi  
Lafiya sukulan bakaka (kama giwa)  
Lafiya darzaza amalen Sarakuna …  
(Khalil, 2007:11)

Idan an yi nazarin abin da ke sama, a iya cewa wannan ba wani sabon abu ba ne illa 'kirari' ne fadawa suke yi wa Sarkin Kano. Aikin nasa na da dangantaka ta }ut-da-}ut da wannan kasancewarsu duk a kan kirari, to sai dai wannan ya nazarci kirarin da zabiyoyin ke yi wa saraki ne,wanda Zabiya Kano na ciki. Saura sun ha]a da Zabiyoyin Fsadojin Kabin Argungu da fadar Daura da Ha]eja da Kano da Kazaure da kuma Fadar Zazzau.

Guga (2010), a nasa aikin ya yi }o}arin nuna hoton sarauta na zahiri, kamar yadda Imam (1970), ya fito da shi a *Magana Jari Ce*. Aikin ya bibiyi kyawawan ]abi'u ko halaye wa]anda suka zama jini da tsoka ga Sarakunan {asar Hausa, wa]anda daga cikinsu wasu halaye ne kyawawa, wasu kuma munana. Ta fuskar kyawawa ]abi'u akwai *gaskiya* da *hikima* da *wayo* ko *dabara* da *jaruntaka* da *ha}uri* da *adalci* ko kyauta da al}awari da kuma kunya. Munanan ]abi'un kuwa sun ha]a da *munafunci* da *zalunci* da *girman* kai da *fishi*.

Tasirin siyasa a kan masarautun gargajiya, a masarautun Kano da Daura da Katsina da Sakkwato shi ne Gaya (2012), ya yi tsokaci a kai, musamman ma yadda Sarakuna suka rasa martabarsu. Misali, aikinsu na zartar da hukunci ga jama'arsu da tara ku]in shiga da ake amshe daga hannunsu sakamakon tsarin mulkin dimokira]iya da aka }ir}iros tsakanin 1960-2000. Nazarin ya kuma yi bayani kan yadda a da ake za~en Sarki da na]insa, sa~anin yadda ake yi a yau. Kodayake wannan nazari ya nazarci Masarautar Daura da Kano da Katsina, amma ba kirarin Zabiyar Fada aka nazarta ba.

Abubakar (2013), ya bayyana asalin sarautar Sarkin Hatsi a Fadar Kano da yadda ake za~en Sarkin da ire-iren ayyukan da yake gudanarwa, tare da sunayen sarautun da suke }ar}ashin wannan sarauta. Sarkin Hatsi, kamar yadda ya bayyana shi ne mutumin da yake kula da

abincin gidan Sarki da na yari (lokacin da yari take }ar}ashin Sarki). Shi ne kuma yake kar~ar kyautar da aka yi wa Sarki ta kayan abinci. Haka kuma, duk kayan abincin da Sarki zai raba, a kan bayar ne ta hannunsa da sauran ayyuka da ke da ala}a da haka.Sai dai ]aya daga cikin aikin Sarkin Hatsi kamar yadda Abubakar (2013: 407), ya bayyana wai Sarkin Hatsi ba ya zuwa Sallar Idi lokacin salla }arama saboda 'fid da kai', wanda za a ce ya sa~a wa addini. Ala}ar wannan aiki shi ne dukkansu a fada ake aiwatar da su. Kamar yadda Abubakar ya mayar da hankali kan Sarki hatsi, wannan kuma a kan kirarin Zabiyar Fada ya sa al}iblarsa

Akwai irin wa]annan ayyuka na fada da aka gabatar a matakin digiri na farko. Ayyuka irin na Udu (1972) da Muhammad (1977) da Alhassan (1979) da Zagga (1980 da Sa'id (1981), da Mika'il (1982) da [anlami (1982) da Nuraddeen (1982) da Suleiman (1982) da Halliru (1983) da Ahmed (1984) da Nakke (1984) da Usman (1985) da Magaji (1985) da Hassan (1986) da Usman (1986) da Maimuna (1987) da Ako (2002) da Aminu (2002) da Altine (2007) da Baba (2007) da Garkuwa (2007) da Farou} (2010) da Ibrahim (2011) da Kabir (2011) da Muhammad (2011) da Umar (2012) da saura da dama. To sai dai, babu wanda ya ta~o adabin Zabiyar Fada ko kuma al'adunta. Wa]annan ayyuka duk sun yi }arin haske ga wannan bincike domin wasu suna da dangantaka ta }ut- da-}ut, wasu kuma ta nesa, kodayake dukkansu an yi su ne a kan masarautu ko fada a {asar Hausa. Wannan kuwa ya mayar da al}iblarsa ne a kan kirarin da Zabiyoyin Fada a {asar Hausa suke yi wa saraki.

### 2.5.3 Adabin Fada

Ayyukan masana irin su Sa'id (1978) da Skinner (1980) da [angambo (1984) da Ibrahim (1985 da Baldic (2004) da Eagleton (2008) da Gusau (1991 da 2011), sun yi tsokaci a kan ma'anar wannan kalma ta 'adabi' gwargwadon fahimtarsu. Sa'id (1978:1-2), ya bayyana adabi da wani fanni na ilimi da ya }unshi labaru da wa}o}in baka da rubutattu da wasan kwaikwayo da al'adu da nau'oin fasaha da hikimar al'umma. Misali kirari da wa}a.

Baldic (2004: 144-142) da Elegleton (2008:3), a nasu ra'ayin sun bayyana adabi da duk wani rubutaccen aiki da ya danganci fanni ko fannonin wani batu. Misali adabin }idaya ko na harshe. Sun ci gaba da cewa adabi abu ne da yake zayyana tunanin zuci, wanda hakan ya sa ya bambanta da maganar yau da kullum. Sun kuma }ara da cewa manyan nau'o'insa su ne wa}a da wasan kwaikwayo da zube. Kodayake kamar yadda suka bayyana a tsakiyar }arni na ashirin (20th[C]) an fara lissafa rubuce-rubucen da suka shafi falsafa da siyasa da tsarin bugun rubutu da tarke da ba }agaggu ba ne a matsayin adabi. Idan aka duba wannan bayani da idon basira, za a ga cewa an danganta shi ne da tunanin Turawa a kan rubutaccen adabi. To, amma sanin kowa ne cewa tun kafin cu]anya da wasu ba}i al'ummomin Afirka da dama, musamman ma na Hausawa suke da adabi. Saboda haka ba rubutaccen adabi ne kawai adabi ba. Muhammad (1977:8-9), ya jaddada haka da cewa fiye da shekaru da suka shu]e (tun a 1950), aka gano cewa a Afirka akwai adabi wanda duk da cewa ba rubutacce ba ne amma daidai yake da rubutacce.

Sa'id (1978:1-2), ya kare wannan hujja da cewa: tarihin wannan adabi na Hausa abu ne mai rikitarwa ainun. Gano tabbataccen bayani kansa yana bu}atar dogon bincike da bin diddi}i na gaske, saboda rashin samun wani abu takamaimai da aka rubuta aka ajiye kafin jihadi, wanda za a dogara da shi, shi ne ya da]a wuyatar da abin. Wannan kuwa ya samu ne saboda }arancin masana a lokacin da rashin damuwa da muhimmancinsa. Sa'id ya ci gaba da bayyani cewa a fili yake kowane harshe tilas ya kasance yana da adabin kansa, wanda masu shi kan sha}ata da shi, ransu ya kwanta ta hanyar jin hikimomin da ke cikinsa, duk kuwa inda al'umma ta kau da yawan jahilci da rashin ci gaba. Harshen Hausa ma ba a bar shi a baya ba, yana da cikakken adabi mayalwaci wanda yake da]ewar harshen shi ne da]ewarsa.

Elegleton (2008:3), a nasa ~angaren ya bayyana harshen adabi a matsayin tsirfaffen harshe mai rauji da sauti na daban da nuna hoton zuci da kuma ginin jimla mai dabarun warwara, sa~anin maganar yau da kullum wadda take mur]a]]a, sandararra, baibayayya, juyayya kuma wagagga.

[angambo (1984:1) da Ibrahim (1985:219), sun bayyana adabi a Hausa da ma Larabci a matsayin wani batu da ya }unshi harkokin rayuwar al'umma, musamman ma hikima da fasaha, kamar azancin maganarsu da wa}e-wa}ensu da sana'o'insu na gargajiya da ]abi'unsu da tufarsu da sauran hanyoyin dabarun zaman duniya. *{amusun Haus*a (2006), ya yi }arin bayani a kan ma'anar adabi da cewa, adabi wani fannin ilimi ne da ya }unshi labarai da wa}o}in baka da rubutattu da wasannin kwaikwayo da al'adu da abubuwan fasaha da na hikima. A ta}aice, adabi hoto ne na rayuwar al'umma baki ]ayansa da ya gina al'umma.

Masana adabin Hausa sun kasa adabin Hausa zuwa manyan rassa guda biyu. A adabin baka da rubutacce. Adabin baka da aka fi sani da adabin gargajiya shi ne wanda al'umma ta bu]e ido da shi (wanda aka gada tun kaka da kakanni). Sa'id (1978), ya bayyana adabin baka da duk abubuwan da ke gudana a bakunan mutane na hikima a cikin ta]e-ta]ensu na yau da kulum, kamar su karin magana da habaici da tatsuniya da wa}e-wa}en maka]a da dai sauran irin su. Adabin baka ya }unshi wa}o}in baka da zantukan hikima da fasaha da sana'o'in gargajiya da sauransu. Rubutaccen adabi kuwa, shi ne wanda ya wanzu bayan al'ummar Hausa ta iya karatu da rubutu (bayan cu]anyar al'ummar Hausawa da Larabawa da Turawa). Rubutaccen adabi shi ne rubutattun wa}o}i da zube da wasannin kwaikwayo (ana kuma kiran wannan adabi 'adabin zamani'). Kirarin da Zabiyoyin fada ya fa]o }ar}ashin adabin baka. Masana irin su Hisket (1975) da Sa'id (1978) da Ibrahim (1985) da Furniss (1996) sun bayyana cewa adabin baka ya haifar da rubutacce bayan Hausawa sun sami rubutun Arabi da boko.

Akwai wasu nau'o'in adabin Hausa masu dangantaka ta }ut da }ut da kirarin Zabiyar Fada.Wa]annan nau'o'in adabi kuwa su ne take da wa}a. Kafin Hausa (1997:99), ya bayyana cewa a wasu lokuta, a kan hargitsa wa]annan nau'o'i na adabi domin ana kallon su da zummar abu guda saboda dangantakarsu ko kuma kamanci da juna har ma ba a gane bambancin da ke tsakaninsu.

Idan aka duba ayyukan da aka gabatar kan adabin fada akwai na King (1967) da na Edward (1971) da Bello (1976) da Koforowola (1982) da Gusua (1988) da Tsoho (2002) da Muhammad (2012), wa]anda suka yi tsokaci a kan maka]an fada. Ayyukan Kofoworola (1982) da Gusau (1988/2002) da Tsoho (2002) da Muhammad (2012), duk sun nazarci

maka]an fada domin shaidar digiri na }oli da na tsakiya, baya ga bugaggun littattafai irin na Gusau (2002 da 2010) da Bunza (2009).

King (1967), ya gabatar da bincike kan ire-iren ka]e-ka]en da ake aiwatarwa a Fadar Katsina. Aikin ya nazarci kayan ki]an sarauta irin su algaita da tambari da ire-iren nau'o'in sautinsu, wato hawa da saukar sauti a tsakanin kayan ki]an. Nazarin nasa ya ke~anta ga kayan ka]e-ka]e ne kawai a Fadar Katsina. Wannan kuwa an yi shi ne a kan Zabiyar Fadar {asar Hausa. Aikin Kofoworola (1982), kuwa ya mayar da hankali a kan maka]an fadar Zazzau. Aikin ya fi mayar da hankali kan masu ka]a take da nau'o'in kayan ki]ansu, irin su algaita da kakaki da kuge da tambari. Ya kuma duba sauran adabin fada na raha kamar Wawan Sarki da 'yan kama. Kamar yadda Gusau (1988), ya nazarci wa}o}in fada ]ari hu]u da hu]u (404) daga cikin maka]an fada talatin da uku (33). Wa}o}in sun }unshi na Sarakunan Yanka da hakimai da iyayen }asa da dagatai da masu ri}e da sarautun gargajiya ko masu jinin sarauta. Ya kuma nuna mahimmancin wa}o}in fada kan sauran wa}o}i ta la'akari da abin da ma}asudin jigon wa}o}in fada, wato yabo da zuga da ro}o da nuna nasaba da jaruntaka da habaici da zambo da makamantansu. Haka kuma, Gusau (2010), a }o}arinsa na bayyana sigogin wa}o}in fada, ya ce ki]a da kirari ko ambaton turken wa}a (tun farkonta) ne mabu]in wa}o}in fada.

Tsoho (2002), kuwa ya nazarci nau'in yabau a kirarin da ake samu a wa}o}in baka na Hausa, musamman wa]anda ake yi wa Sarakuna a lokutan ya}i. Bincike ya za~o wa}o}in wasu Sarakunan Hausa aka yi tsokaci a kansu.Wa}o}i da suka ha]a da 'wa}ar Sarkin Kabin Argungu Muhammadu Sama' da ta 'Gagara {arya Sadauki' da ta 'Sarkin Kabin Argungu Sama'ila' (Sama) da ta' Sarkin Gobir Umaru Shawai' da ta 'Bahagon Gulbi' da ta 'Sarkin Gobir Isa Amadu Bawa' da kuma ta Sardauna, 'Mai Dubun Nasara'. Kodayake bincike ya

ta~o wa}o}in jarunta da na gagara da kuma na bajinta. Tsoho ya bayyana cewa an }ir}iro kalmar ‘yabau’ ne domin a fa]a]a da baddala kalmar ‘yabo’, musamman a nazarin yabon da ya shafi gwarzo ko gwaraje. Aikin ya kasa ‘yabau’ zuwa manyan rassa hu]u da suka ha]a da: yabau na kwalliya da yabau siffantau da yabau aikatau da yabau dangantau da kuma yabau mai sigar jimla.

Muhammad (2012), ya za~i ]aya daga cikin mawa}an fada, maka]a Sa’idu Maidaji Ramba]awa ya baje koli a kan tarihinsa da wa}o}insa. Aikin Muhammad za a ce an tsinci dame ne a kala, domin ya waiwayi ayyukan maka]a Sa’idu Maidaji Sabon Birni, maka]in Sarkin Gobir Sabon Birni. Aikin ya nazarci jigo da tsari da salon sarrafa harshe a wa}o}in maka]in. Kodayake kamar sauran wa}o}in fada, shi ma wannan maka]i, jigonsa bai wuce ‘yabo’ da ‘zuga’, to sai dai, yakan ta~o jigon ‘fa]akarwa’ da ‘siyasa’ da ‘noma’. Sannan kuma, aikin ya gano cewa ba kasafai mawa}in yake ‘zambo’ a wa}o}insa ba. Ta fannin tsari kuwa, maka]in yana amfani da tsarin ‘]iya da rerawa’, wato tsarin ‘jagora + }ulla + }ari + }arbi. To haka kuma, binciken ya gano irin salon sarrafa harshe a wa}o}in maka]in, musamman amfani da adon harshe. Wannan aiki na Muhammad (2012), yana da dangantaka ta kusa da wannan domin shi ma ya nazarci jigo da salo da zubin wani adabi na fada amma ba wa}a ba, kirarin da zabiya take yi wa saraki domin fayyace al’adar da ke cikin kirarin.

Har ila yau akwai ayyukan Gusau (2002) da Bunza (2009), wa]anda suka nazarci Salihu Janki]i da Maka]a Naramba]a. Gusau (2002), ya gabatar da nazari kan rayuwa da wasu wa}o}in Salihu Janki]i Sarkin (Taushin Sarkin Musulmi) wanda ]aya daga cikin mawa}an fada ne. Kodayake Jankidi ya yi wa}o}in fawa da noma, sai Sarakunan fawa da noma ya yi wa wa}a. Nazarin ya nuna cewa turke a wa}o}in Janki]i sun ha]a da na yabo zalla da zuga zalla da turken yabo garwaye da zuga da na siyasa. Haka kuma, Janki]i yana k yawaita

amfani da nau'o'in adon harshe irin su kamantawa da siffantawa da kuma alamtarwa. Kamar yadda nazarin ya gano cewa wa}o}in Salihu Janki]I, }unshe suke cunkus da nuni kan falsafar rayuwar mutanen da ya wanzu cikin nisha]i dangane da yadda mutanen da ya yi wa wa}o}i suka yi rayuwarsu. Kamar yadda shi kuma Bunza (2009), ya za~i maka]i Naramba]a ya baje kolinsa, tun daga farkon rayuwar maka]in zuwa wa}o}insa da rayuwar iyali, har zuwa mutuwarsa. Nazarin kuma ya fayyace jigogin wa}o}in mawa}in, aka fe]e ire-iren salalan da ke cikinsu da irin fasahohin da ke cikinsu. An kuma zuba bakandaniyar mawa}in a gadon fe]e wa}a aka fitar da jigoginta sannan kuma aka sa wa}o}in Naramba]a bisa faifan Sidi (CD), bisa la'akari da rabe-rabensu da abubuwan da suka fuskanta. A ta}aice, nazarin ya tattaro wa}o}in maka]in, aka taskace su aka adana muryarsa da amon tandunsa da za}in muryar `ya`yansa. Wannan ayyuka na Gusau (2002) da Bunza (2009), duk suna da dangantaka ta }ut-da-}ut da wannan aiki da ya nazarci kirarin Zabiyar Fadojin {asar Hausa.

Himma ba ta ga rago, Gusau (1996/2005) ya tattaro maka]a da mawa}an Hausa ya yi tsokaci kan rayuwarsu tun daga haihuwa da }aruciya zuwa shahara a fagen wa}o}in baka na Hausa. Nazarin ya taskato mawa}an fada ]ai-]ai har guda ashirin da ]aya wa]anda suka ha]a da Buda [antanoma da Abubakar Akwara da Muhammadu Dodo Mai Tabshi da Aliyu [andawo da Sa'idu Faru da sauransu.

Shi kuwa Uba (2003), ya yi tsokaci ne a kan kirarin wa]ansu garuruwan Hakiman Masarautar Kano ashirin (20), ta la'akari da tarihin kafuwar gundumominsu daga ire-iren kirarin da ake yi masu, ya kuma duba dangantakar kirarin da ra'ayoyin al'ummomin masarautar hakiman. Kamar yadda Kafin Hausa (1997), ya yi nasa a kan kirarin wasu garuruwan {asar Hausa da na Sarakuna. Aikin Kafin Hausa (1997) da na Mode (2004),

tamkar [anjuma ne da [anjummai domin duk sun nazarci kirarin da ake yi wa wasu garuruwa na {asar Hausa, sai dai abin da ba a rasa ba. A yayin da Mode (2004), ya mayar da hankali kan nau'o'in salon da ke cikin kirarin garuruwan da ke shiyyar jihohin Arewa maso yamma. A yayin da Kafin Hausa (1997), ya yi tsokaci kan batutuwan da ake la'akari da su wajen yi wa garuruwa kirari wa]anda suka ha]a da shahara wajen kasuwanci ko ya}i da ilimi. Ya kuma kawo wasu daga cikin ire-iren kirarin da ake yi wa Sarakuna da sauran masu sarauta ta hanyar amfani da nasabarsu ta dangantaka da hali da jaruntaka da bajinta da ilimin duniya da na addini da kuma kyawun halitta.

Ita ma Ramatu (2003), ta nazarci take da kirari ne a Fadar Zazzau . Ramatu (2003), ta za}ulo irin rawar da maka]an sarauta a Fadar Zazzau suke takawa, sannan ta ]ora ayyukansu bisa mizanin adabi domin gano gudunmuwar da suke bayarwa. Binciken ya mayar da hankali a kan maka]an sarauta wa]anda suke ka]a taken sarautar Zazzau da masu yin kirari. Ta kuma nazarci kayan ki]an da suke amfani da su da mahimmancinsu. A }arshe an kammala da sharhi a kan take da kirarin Sarkin Zazzau da wasu daga cikin hakimansa da manyan 'yan majalisar masarautar. Aikin na da dangantaka da wannan. Farko dukkansu sun fa]o a muhalli ]aya, wato fada. Na biyu kuma Fadar Zazzau na ]aya daga cikin muhallin wannan nazari, to sai dai cikin masu yi wa Sarki kirari ko ka]an nazarin Ramatu (2003) bai ambato mata da ke yi masa kirari ba duk kuwa da cewa akwai su.

Aikin Shafa'atu (2012) da na Maijidda (2012), kuwa sun mayar da hankali ne kan abubuwa mabambanta. 'Kirarin Mata a {asar Sakkwato', wato kirarin da ake yi wa matan da mazajensu ke ri}e da sarautun gargajiya a {asar Sakkwato, kamar Sarkin Musulmi da Magajin Garin Sakkwato da Marafan Sakkwato da Sarkin Dawaki da Sarkin Rafi da sauran matan sarakin Sakkwato.Sauran kirarin mata da aikin ya nazarta sun ha]a da kirarin mata

gama gari irin su uwargida da amarya da mace mai fa]a a ji da mace mai alheri da kuma saunar mace. A yayin da Maijidda (2012), ta nazarci wa}o}in amada a Fadar Kano ta hanyar fito da turaku da awon baka daban-daban da wa}o}in suke da shi. Sakamakon binciken ya gano cewa mahaifiyar Sarki Ado Bayero, Hajiya Hasiya Abdullahi Bayero (Mai Babban [aki) ce ta fara na]a zabiyoyin amada a Fadar Kano (kodayake ba a ambaci shekara ba). An kuma gano cewa zabiyoyin gado suke yi, kuma wa}o}in nasu maimai suke yi, sai dai ana samun 'yan }are-}are da ba a rasa ba. Baya ga haka zabiyoyin suna da sani na addinin Islama, to amma kuma wasu daga cikinsu suna wa}o}in bori.Wa]annan ayyuka suna da ala}a da wannan saboda shi ma a fada ne, fadar Kano da wasu sai dai ya ke~anta ga Zabiyoyin Fada masu yi wa saraki kirari.

Fatima (2012), kuwa ta kwatanta jigon yabo ne a wa}o}in Sarakuna baka da rubutattu, kamar yadda Bello (1976), ya yi tsokaci a kan shikashikan cim ma yabo a wa}o}in fada a {asar Hausa wa]anda suka ha]a da asali (gami da ambaton zuri'a) da ri}o da addini da jaruntaka da kyauta da kuma iya ri}e jama'a (iya mulki), wa]annan shikashikai kamar yadda aikin Bello ya bayyana suke nuna dangantakar maka]i da ubangidansa.

Sa'id (1978), a }o}arinsa na tsokaci kan adabin baka kafin bayyanar masu jihadi {asar Hausa, ya kawo ire-iren kirarin da ake yi wa, Sarakunan {asar Hausa a wancan lokaci. Ire-iren wa]annan kirari da ya kawo sun ha]a da na Sarauniya/ Magajiyar Daurama da na Sarkin Gobir Bawa Jangwarzo da na Sarkin Kabin Argungu na farko, Muhammadu Kanta. Kodayake ba a ambaci wa]anda ke kirarin ba, to amma wanda ake yi wa Magajiyar Daura, shi ne har yau ake yi wa duk wata mai ri}e da sarautar, kuma tun da can har yanzu, Dakamar Sarkin Daura take aiwatar da shi. Manyan adabin fada sun ha]a da kirari da take da kuma wa}a.

### 2.5.1 Kirari

Masana da manazarta irin su Besmer (1973) da Zarru} da Alhassan (1976) da Zarru} da wasu (1986) da Powe (1981) da Gusau (1980 da 2000) da Kafin Hausa (1985 da 1997) da [angambo (1984) da Furniss (1996) da Sharifai (1997) da Muhammad (2001) da Mode (2005) da Junaidu da Yar'adua (2007) da Bunza (2009) da Shafa'atu (2013) da sauransu sun nazarci kirari ta fuskoki daban-daban, bayan sun tofa albarkacin bakinsu kan ma'anarsa da ire-irensa da mahimmancinsa da dangantakarsa da take da wa}a da makamantansu.

A ra'ayin Zarru} da Alhassan (1976:1), kirari shi ne ku]a da kurari cikin hikima, ishara da isar baka, rurawa da razanarwa da ruba azancin magana da alfaharin mai sana'a. Kamar yadda yake ruhin adabi da rumbin tara shi da ke inganta sa}o da isar da shi. Zarru} da Wasu (1986:50), sun ci gaba suka bayyana kirari da wasa kai ko wasa wani cikin da]a]un lafazi. Sun yi }arin bayani da cewa, shi kirari haka yake wa}a-wa}a magana –magana. Shi dai ba wa}a ba saboda ba a rangwa]a murya, shi kuma ba kara zube ba, saboda kana iya jin wani kari a cikinsa, amma duk da haka a kan sami kirari ya fito a wa}a.

Shi kuwa Gusau (1980:38), ya bayar da tasa ma'anar ne da cewa, kirari shi ne fa]in wasu kalmomi ga kai ko ga wani wa]anda za su iya sa a ji da]i ko cim ma wani girma a idon jama'a. Kamar yadda Ibrahim (1985:228), ya ce ba wani abu ba ne kirari, illa wasu kalmomi na azanci wa]anda Hausawa suke amfani da su domin yabo ko zuga ko ba'a ko kuma yabon wata kyakkyawar al'ada ko kuma sukar wata mummuna.

Kalmar kirari, a ganin Kafin Hausa (1997:99), ana iya fassara ta da kalma, ko kalmomi da a kan fa]e su da wani salo na musamman don kambamawa ko zuga ko girmama mutum ko wani abu. Haka kuma, mutum yakan ambaci irin wa]annan kalmomi domin ya kambama kansa. Ya }ara da cewa kalmomin kirari a kan fa]e su da wata irin murya mai }arfi, ta yadda mai sauraro zai san ba magana ce ta yau da kullum ba.

Sharifai (1997:12-13), ya bayyana kirari ne a matsayin maganganu da ake shirya su da nufin kwatance ko kamance domin ku]a ko washi ga wanda ake yi wa. Shi kuwa Bunza (2009:140), ya fara kallon kariri ne daga asalin kalmar. Ya cewa kalmar kirari ta samo asalinta daga 'kira'. Ma'ana, kirari kamar a sa kalangu ne ko ganga ko murya a kira wani da }arfi don ya fito a ]ebe tantamar abin da ake fa]a a kansa. Ya }ara da cewa, maka]i ke yin 'kirari' ko san}ira. Idan maka]i ya kira tauraronsa da ganga ba da baki ba, to take ya yi ke nan. Idan kuwa ya sa baki ne ya fara ku]a, to kirari ya yi

A ganin Ibrahim (1985:111), Hausawa sun fara kirare-kirare daga ki]an farauta wanda daga baya ya wanzu zuwa sauran ka]e-ka]e. Gusau (2000:37), ya }ara da cewa yawancin mawa}an baka da zabiyoyi da sarakunan magana da sauran mutane ke yin kirari. A ta}aice, daga ma'anonin da masana da manazarta suka bayar, a iya cewa kirari ]aya ne daga nau'o'in adabin baka da ake tsarawa cikin balagar harshe domin cicci~a ko ko]a wani ko wani abu.

Zarru} da Alhassan (1976:1) sun bayyana cewa a kan yi kirari don ko]a wani mutum ko wani abu, a yi masa washi ko talla ko zuga. Kuma a kan yi nuni ta hanyar kirari, a yi wa mutane hannuka mai – sanda. Masanan sun }ara da cewa, kirari ba ya inganta sai da azancin magana domin zance ne ginanne wanda ake ]ebowa daga rumbun adabi da ake kuma }awata adabin da shi. A yayin da Gasau (2000:35), ya fayyace haka da cewa kirari wani muhimmin

abu ne wanda ya shafi yanayin sarrafa hikimomin bakan Hausawa da ke bun}asa harshe da adabi da kuma al'ada. Masanin ya kuma bayyana cewa kirari ya yi naso a duk sassan rayuwar Hausawa, domin har ta kai ga babu wani abu a {asar Hausa da Bahaushe bai yi wa kirari a kan nasabar mutane da halayen da ke zagaye da shi ba.Misali, aure da haihuwa da mutuwa da garuruwa da duniya da abubuwan da ta }unsa. Shi kuwa Ibrahim (1985:229), ya bayyana a matsayin kirari da ]aya daga cikin nau'o'in adabin baka da suke taimakawa wajen kawo zaman lafiya, musamman tsakanin ma'aurata. Ya kawo misali da yadda auren mace fiye da ]aya yana daga cikin al'adun Bahaushe.Ya ce a yayin da galibi kuma matan sukan zauna a cikin gida ]aya su yi kishi, wanda irin wannan zama yana da wuya, to amma idan aka ba kowa ha}}insa a kan zauna lafiya. Domin haka ne ma, kamar yadda ya bayyana, aka sami kirarin da zai ba uwargida ha}}inta, ya kuma ba amarya ha}}inta, sannan ya ba maigida nasa ha}}in. Misali (kamar yadda ya kawo):

**Kirarin Uwar gida:**

Uwargida sarautar mata
Kwari tankarin gida
Fara gutsura mai farar akaifa
Kin dasa, dashen ya kama.

**Kirarin Amarya:**

Amarya amarsu ta ango mai
da]in tuwo da miya
Amarya ba kya laifi ko
Kin kashe ]an masu gida.

**Kirarin maigida:**

Maigida bawan gida.

Kodayake wannan kirari na 'maigida' ba maganar hikima ba ce, kusan an fi amincewa da 'maigida takobin fama' ko kuma 'maigida kan gida', a matsayinsa na shugaba, duk kuwa da cewa bawan ne a ba]ini domin nauyin gida da ke wuyansa.

Masana sun ci gaba da }o}ari wajen  kasa kirari zuwa rassa daban-daban. Zarru} da Alhassan (1976:20-21),  sun raba ire-iren kirari zuwa gida uku. Kirarin garga]i  da nasiha da tsawatarwa da kirarin yabo da zuga da zambo da kuma kirarin bayyana al’ajabi. Sun ce sun yi wannan rabon ne dangane da sa}on da ke cikin kirari. Shi kuwa Gusau (2000:36-37), cewa ya yi raba kirari zuwa rassa daban-daban ba abu ne mai sau}in yi ba, domin akwai hanyoyi da yawa na kusa da na nesa da za a duba lamarin. Misali , mai nazari zai dubi karari ta fuskar dalilin da kan haifar da shi, kamar kirarin sana’a ko na sarautu ko na }alubale ko nisha]i  ko na ban mamaki da sauransu. Haka kuma, ana iya duban kirari ta yanayin ginin harshe ko balaga ko fannonin da ke }unshe a cikinsa. A }arshe ya kasa kirari zuwa kashi biyu manya, dangane da yadda ake yinsa da kuma ta lura da mai yinsa, wato kirarin kai da kuma kirarin wani.

Dangane da tubalan da ake amfani da su wajen ginin kirari, Umar (1985:38-39), a cikin Gusau (2000:36), yana cewa a kullum kirari yana zuwa ne da sigar siffanta ko kamanta abin da ake yi wa shi da wani abu ko mutum mai shahararren }arfi ko alfarma ko daraja ko dai wani hali na musamman da ya fifita shi. Abubuwan siffantawa ko kamantawa wajen kirari sukan ha]a da su giwa da zaki da aljani da gobara da ruwa da ba}in kumurci da iyaye da kakanni, musamman ga Sarakuna da jaruman ya}i.

Shi kuwa Gi]a]awa (2007), cewa ya yi kirari kan zo da sura biyu. Ko dai ya fito kamar take (wanda shi ne wanda maro}a/mawa}a ke yi wa wani) ko kuma ya fito kamar zuga, wato mai fitowa da surar tumasanci. Kamar yadda Zarruk da Wasu (1986:50), suka bayyana cewa kirari ba ya kammala sai tare da nuna wani hali na mutum ko wata sifa tashi. Haka kuma, cikakken kirari yakan ha]a da ambaton sunayen iyaye zuwa‘yanuwa ko masoya.

Game da mahimmanci ko amfanin kirari, Zarru} da Wasu (1986:15-52), sun bayyana cewa: “kodayake a wajen biki da bushara da wasanni aka san kirari, duk da haka abin da yake koyarwa ya fi gaban wasa. Hikima da luggar da ke }unshe cikinsa suna da ban sha’awa, da ba da nisha]i, da amfani }warai da gaske. Wata}ila ma kirari yana cikin shi}ashikan da ke }ara shaharar mawa}i. A lura da mashahuran wa}o}i irin na su Naramba]a da [an}wairo da Shata da [an Anache da sauran irin su. Za a ga wa}o}in wa]annan mutane duka cike suke da kirari. [aya daga cikin hikimomin kirari shi ne bayani a dun}ule na rayuwa ko halayen wasu halittu, tamkar darasi a ilimin kimiyya ko ilimin rayuwar zaman jama’a”. Sun ci gaba da bayani cewa ana yi wa mutum kirari domin a tuna masa da halinsa ko siggoginsa. Wannan shi zai sa mutum ya nuna wani hali ko na jaruntaka ko na kyauta ko kuma }warewa kan wani abu. Gararuwa kuma ana yi masu ne don a ambaci bun}asarsu da mahimmancinsu Don haka idan an lura akwai ilmantarwa a kirari saboda a ka ji tarihin mutum ko wani abu.

Junaidu da ‘Yaradua (2007:89), sun bayyana kirari ne a matsayinsa  rukunin salon sarrafa harshe. Sun yi }arin bayani da cewa ana amfani da kirari domin gwaninta da }imar harshe,wanda ya sa Hausawa suke amfani da basira ta hanyar fasaha wajen yi wa kusan dukkan abubuwan da ke cikin duniyar nan tamu kirari.

Kafin Hausa (1985), ya fayyace cewa ba Hausawa ka]ai ke da basira ko hikimar sarrafa kirari ba, kowace al’umma ta duniya tana da nata kirari da take yi wanda ya dace da al’adunta da muhallinta da wasu halaye da ]abi’u ko wata bajinta  wadda take ganin ta dace da kirari. Kamar yadda al’ummomi irin su Bare-bari da Fulani da Nufawa da Yarabawa ke aiwatar da nasu kirari, domin haka za a iya cewa kirari ruwan dare ne gama duniya. Kafin Hausa ya }ara da cewa ]aya daga cikin mahimmancin kirari shi ne raya harshe, saboda a cikinsa ana samun tsofaffin kalmomi. Haka kuma kirari yana bayyana tarihi da al’adun

alumma baya ga sa raha da nisha]i. Sannan kuma yana zuga ko }arfafa zuciya da sa mutum ya yi abin }warai (misali kyauta da nuna gwaninta), wanda a yi cewa shi ne babban dalilin da ya sa kirari ya yawaita a wa}o}in fada da na maza.

Kafin Hausa (1997:102-7), ya bayyana cewa bisa ga al'ada, Sarakunan Hausa su suka fi kowa shan kirari fiye da kowane rukunin mutane a al'ummar Hausawa. Ya }ara da cewa muhimmancin kirarin Sarakuna a Hausa bai tsaya a kan adabi ba, ya shafi irin halin zaman rayuwar jama'a, da kuma tarihi. Da farko dai yana nuna bayyanar Sarki a wuri, sannan kuma yana zaman gaisuwa ga Sarakuna. Yana kuma sa su sami gamsuwa da zarar sun ji an yi musu kirarin, musamman idan aka ambaci iyaye da kakanni da kuma irin bajintar da suka yi. Bayan haka, a iya cewa kirari bayani ne da ya ke~anta ga saraki. Kirarin da Zabiya ke yi a fada ya tabbatar da wannan bayani na Kafin Hausa (1997).

Sauran ayyuka masu dangantaka da wannan aiki sun ha]a da na Besmer (1973), da Powe (1981) da Gusau (2000) da kuma Argungu (2007). Besmer ya nazarci kirarin manyan iskokai da na 'yan bori da ake yi a {asar Kano. A yayin da Powe (1981), ya duba kirari ta fuskar nahawu da ya ji~anci gundarin ma'ana a kirarin da ake yi wa duniya a harshen Hausa. Shi kuwa Gusau (2000), ya mayar da hankali ne kan kirarin da maka]an Hausa suke yi a lokutan da suke gudanar da wa}o}insu. To amma shi Argungu (2002), ya yi tsokaci ne kan ire-iren kirarin da ake yi a lokacin bikin kamun kifi na Argungu. Wa]annan kirari a cewar Argungu sun }unshi wa]anda ake yi wa nau'o'in kifi daban-daban da gidajen manyan masunta da sarautun masunta da makamantan wa]annan. Dukkan wa]annan ayyuka suna da ala}a ta kusa da wannan bincike, kasancewa ya mayar da hankali ne kan kirarin da zabiyoyin fada ke yi wa saraki a {asar Hausa.

### 2.5.3.2 Take

Cikin nau'o'in adabi wa]anda ke da dangantaka ta }ut da }ut da kirari shi ne take, wanda sau da yawa wasu na hargitsa su, suna ]aukarsu a matsayin abu guda. Masana irin su Kafin Hausa (1985) da (1997) da Zarruk da Alhassan (1976) da Zarru} da Wasu (1986) da Suleiman (1990) da Furniss (1996) da Sharifai (1997) da Muhammad (2001) da Ramatu (2003), sun ba da ma'anar take daidai gwargwadon fahimtarsu. A iya cewa ba a sami sa~anin ra'ayi dangane da ma'anoninsu ba, sai dai za~en kalmomi ya bambanta su.

Kafin Hausa (1985:42), ya bayyana take da wata magana wadda tana iya zama karin magana ko habaici ko zambo ko kirari da ake ka]a wa da bakin ganga. Ya ci gaba da bayani cewa wanda duk ya ji amon wannan ganga, ya san mutumin da maka]in yake kira. Zarru} da Wasu (1986.52), kuwa a tasu fuhimtar sun ce take shi ne wasa mutum ta hanyar ki]a amaimakon lafazin baki.Shi kuma Sharifai (1997:3), cewa ya yi take wani ki]a ne na musamman da ake ka]a shi kuma a fassara shi da magana don a sa tsokar jiki ta tashi a yi wani aiki ba tare da gajiya ba. Suleiman 1990:26), ma ya bayyana take da tsararriyar magana mai kamar wa}a wadda a kan ka]a da ki]a domin girmama ko kambana wani mutum ko wata al'umma. A ta}aice, a iya cewa ba wani abu ba ne take illa lafazin wani furuci amma da ki]a ko wani abin bushe-bushe kamar algaita ko tambari ko kuma }aho.

Galibi a kan ka]a wa mutum take da kowane irin abin ki]a. Sarakuna ana ka]a nasu da kakaki ko algaita, manoma kuma da ganga. Mafarauta a yi masu da duma ko kuma ganga. Sauran jama'a maza da mata kowa yana samun takensa muddin dai ya shahara kan wani abu. A ganin [angambo (1984:42), za a danganta take da bayyana wanda ake yabo, wato taken wani ya sha bamban da na wani.

Wata matsala da take ci wa masu nazarin adabi tuwo a }warya ita ce ta kasa bambancewa tsakanin ‘kirari’ da ‘take’. Kafin Hausa (1985:42), ya bayyana cewa, sau da yawa a kan ]auke su abu guda ko kuma a ce ‘yan’uwa ne, wanda kuwa sam ba haka ba ne. Hasali ma a ra’ayinsa ‘take’ ba ya cikin adabin baka, domin adabi ne wanda ake aiwatar da shi da ganga (ki]a ko wani abin bushe-bushe), kirari kuwa da fatar baki ake aiwatar da shi ta hanyar furuci. Domin haka, idan ana maganar adabin baka sam bai kamata a ri}a sa take ba

Su kuwa Zarru} da Alhassan (1976:11-12), sun bayyana cewa kirari da take `yan`uwa ne sha}i}ai, don haka ba mutum duka ne ya damu ya san bambancinsu ba, kamar yadda suka ce, “Dukkansu dabaru ne na yabo da washi da tunzurawa da tsokana. Babu shakka, kirari da take sun bambanta. Bambancin farko shi ne kullum kirari zance ne, take kuwa an fi }addamar da shi ta hanyar ka]e-ka]e da bushe-bushe. Don haka, ba a faye cewa “an ka]a kirarin wane ba, amma wani ji}on a kan ji ana maimaita take cikin zance, bayan an gabatar da shi cikin ki]a ko busa kuma ko cikin zance take yakan ]auki ma’ana mai kama da karin magana, wato ma’anar kowa da kowa”.

Bambanci na biyu kuwa kamar yadda Zarruk da Alhassan (1976), suka bayyana shi ne ana yi wa kowane abu kirari ba sai mutum ba, take kuwa sai mutum. Wanda ya sa ko an ji ana kama sunan wata dabba a take ba da ita ake ba, tashabihinta ake yi wa wani mutum. To sai dai kuma ana ka]awa }asa take. Misali ‘Taken Nijeriya’ da sauran }asashe, ana kuma ka]a taken wasu sana’o’in na musamman, misali ‘taken noma’.

Take da kirari ]an kaso ne daga adabin baka na gargajiya. Domin haka, abubuwa ne masu nuna gwanintar harshe wajen bayyana kai ko wani ko kuma wasu, (Sharifai, 1997:7-8). Shi kuwa Suleiman (1990:26), cewa ya yi take da kirari sun kasance [anjuma da [anjumai domin

kuwa kafa]a-kafa]a suke tafiya a kodayaushe kuma mahimmancinsu da illolinsu duka ]aya ne.

Zarru} da Wasu (1986:52), sun yi }arin bayani inda suke cewa:"dangantakar da ke tsakanin kirari da take ta yi yawa }warai da gaske, don haka ne ma kusan mahimmancinsu ]aya ne. Sai dai a ce take ya ]ara mu}ami saboda har wa]anda suke ba sa yin kirari saboda ganin darajarsu suna da nasu taken. Watau kamar Sarakuna da malamai. Haka kuma don tsananin mahimmancin take har gadonsa ake yi. Sai ka ji mutum na cewa, "Ai tun da aka ka]a taken gidanmu sai na yi rawa". Ko kuma ranar da mutum ya bushi iska sai ya ba maka]i ku]i ya ce, "A sa mini taken kakana". Don haka mahimmancin take a nan yana da wuyar fayyacewa don kuwa a jinin Bahaushe yake. Ba za a gane haka ba sai ka ga mutum a yayin da ake ka]a takensa ko na kakansa".Wannan ya sa duk lokacin da mai kirari yake son yin kirari, ba ya jin da]in yi matu}ar ba take ne ya ratsa shi ba, Kafin Hausa (1997:8).

Haka kuma ana iya cewa take a wani lokaci shi ke haifar da kirari, kamar yadda aka sani, sigar take ita ce ki]a ko busawa. Saboda haka ki]a abu ne mai ratsa jikin ]an Adam, ta yadda ko da kuwa yaro ne a goye, ki]an da ya yi masa da]i yana iya masa zullo ko a bayan wa yake! Haka abun yake ga manya, suna ka]a kai ko su rausaya har ma su taka a lokacin da ki]a ya ratsa su, babba da yaro da mace da namiji da basarake da attajiri da talaka. Adamu (1978:189), ya kare haka inda ya bayyana cewa, "In ban da karatu da cin abinci kusan babu wani aikin da Bahaushe zai yi wanda ba shi da ki]a na musamman".

Ha}i}a take na taka mahimmiyar rawa wadda za a iya cewa ko ba komai yana }ara kwarjini ga wanda ake ka]a wa. A wani lokaci ma ya tunzura shi musamman sa'ar da ya ji taken

gidansu (na kaka da kakanni). Take hanya ce kuma ta sanarwa. Misali, ko da jin taken wani basarake ka ce ga wani basarake nan, yana kuma bayyana tarihi a wani lokaci. Baya ga cewa ka]a take na kawo nisha]i ga duk wanda ya saurare shi da kunnen basira, musamman wanda aka ka]a dominsa. Zabiyar Daura na ]aya daga cikin masu ka]a take a Masarautar Daura. Tana ka]awa Sarki da Magajiyar Daura kawai, tana kuma ka]awa da wani tambari na gado da ake kira ‘Dajinjir’.Wannan aiki ya nazarci kirarin nata ne kawai ban da take.

Nazarin Sharifai (1990) da Suleiman (1990) sun yi kunnen doki, domin dukkansu sun yi tsokaci ne kan tasirin ‘take’ a sana’o’in gargajiya na Hausa. Ayyukan nasu sun dubi dangantakar adabin Hausa da sana’o’in Hausawa na gargajiya, ta yadda aka fito da irin yalwar harshen Hausa da bajintar Bahaushe wajen ko]a sana’o’insa da yake alfahari da su. Manyan sana’o’in gargajiya irin su noma da }ira da fawa da farauta da makamantansu an nazarci taken da ake yi masu a ayyukan. Kodayake aikin Sharifai (1990), ya ha]a har da ire-iren kirarin da ake yi wa wa]annan sana’o’in gargajiya. An kuwa yi haka ne saboda a mafi lokuta take ke haifar da kirari. Misali, manomi da ya ji taken noma ya shige shi (ya tsuma), ba za a san lokacin da zai fara kirari ba.

### 2.5.3.3 Wa}a

Wa}a nau’i ne daga cikin adabin da yake da dangantaka ta }ut-da-}ut da kirarin Zabiyar Fada. Besmer (1971) da King (1980) da Koforowola (1982) da Umar (1984) da Gusau (1988 da 2002 da 2010) da Tsoho (2002) da Bunza (2009) da Muhammad (2012) sun nazarci maka]a da mawa}an fada, a matakin neman digiri na tsakiya da na }oli da ma a littattafai.

Yahya (1997) da Gusau (2003) da (2009) da Mukhtar (2006) da [angambo (2008, 2011) da saura da dama sun bayar da gudunmawa wajen fayyace ma'anar wa}a. A ra'ayin Yahya (1997:4), wa}a tsararriyar maganar hikima ce da ta }unshi sa}o cikin za~a~~un kalmomi da aka auna domin maganar ta rerus ba fa]uwa kurum ba. Kamar yadda Mukhtar (2006:5), ya bayyana wa}a da sa}o cikin faruci da lafazi da ake gabatar da shi ta hanyar daidaitattun kalmomi wa]anda ake rerawa cikin kalmomi masu tsari da kuma fa'ida da sauran dabaru masu jawo hankali. To haka kuma, '[angambo (2008: 5), shi ma ya bayyana ra'ayinsa da cewa, wa}a sa}o ne da ake gina shi kan tsararriyar }a'ida ta baiti ko ]ango da rerawa da kari da amsa-amo da sauran }a'idojin da suka shafi daidaita kalmomi da za~ensu da amfani da su cikin sigogin da ba lalle ne haka suke a maganar baka ba.

Wa}a a ra'ayin Funtua (2010:64), takobi ce ta raya al'ada da adana tarihin al'umma. Funtua ya }ara bayani da cewa tasirin wa}a ga rayuwar kowacce al'umma ba }arami ba ne, domin wannan ne ya sa za a ga cewa babu wata al'umma a duniya wadda ba ta da salon wa}arta. [angambo (2011:6), ya yi }arin bayani a kan haka, inda yake cewa wa}a wani sa}o ne mai farin jinni da yake ]aukar hankali domin yana da saurin shiga zuciyar ]an Adam. Ya kuma ratsa illahirin zuciyarsa cikin sauri tare da tasiri mai }arfi. Shi kuwa Muhammad (2012:6-5), ya siffanta wa}a da abin da ke bun}asa tunanin ]an Adam tare da ala}anta ko ji~anta ta da nau'o'in abubuwan da ke wasa }wa}walwa tare da daidaita tsinkayar al'umma. Ya kuma bayyana wa}a da abin da ke ]aukaka alfarma da kare mutuncin ]an Adam da inganta darajarsa.

Ko ba komai,wa}a aba ce wadda ke nuna hoton rayuwar al'umma ta fuskar zamantakewa kuma ma'adani ne na bayyana tunanin al'umma. Matsayin wa}a ga al'umma a iya cewa makami ne na ya]a ko kawar da ]abi'u da al'adu ko manufofinsu, masu kyau da marasa kyau. A ta}aice a iya cewa wa}a hanya ce ta isar da sa}onni cikin raha da annashuwa wanda ake rerawa ko dai ta hanyar amfani da kayan ki]a, domin }ara wa sa}on armashi, ko kuma rerawa ba tare da ki]a ko kayan bushe-bushe ba. Wa}a ta }unshi wani babban rukuni na adabin al'umma domin hanya ce ta jawo hankalin jama'a maza da mata, babba da yaro, (Halima, 2010:108).

Masana sun raba ko kasa wa}o}i zuwa manyan azuzuwa biyu, rubutattu da na baka. Wa}ar baka zance ne sarrafaffe, aunanne wanda ake aiwatar da shi ta bin hawa da saukar murya. Wa}ar baka ita ce ake rerawa da fatar baki kai tsaye ba tare da an rubuta ta ba. Galibi ana rera wa}ar baka da ki]a domin }ara mata armashi. Rubutacciyar wa}a kuma tsara ta ake yi a rubuce sannan a rera ta. A zamanance a kan rera wa}ar baka da ki]a irin na fiyono.

Masana da manazarta adabi da suka ha]a da Abdul}adir (1975) da Ibrahim (1976 da 1983) da Yahaya (1983 da 1985), da Tajo (1980), da [angambo (1981 da 1982 da 1984) da Gusau (1984 da 1988 da 2003 da 2005) da Umar (1980 da 1984 da 1987) da Alhassan da Wasu (1982) da {auran Namoda (1984) da Salihu (1978 da 1987) da Zarru} da Wasu (1987) da sauransu sun bibbiyi rukunonin ka]e-ka]e da maka]an baka na Hausa suk raba su gida-gida gwargwadon manufa da }udurin kowannensu, (Gusua, 2008:132:133).

Gusau (2008:137), ya ci gaba da cewa an raba rukunin maka]an zuwa manyan rukunoni guda biyu, wato maka]an fada da maka]an gama-gari. Maka]an fada suke yi wa fada da

jama'arta ki]a da wa}a da ka]a take. Suna ki]a da wa}a da ka]a take ga Sarakuna zuwa ga sauran masu ri}e da mu}aman sarauta ko 'yan jinin sarauta. Daga cikin maro}a masu yin ki]a da wa}a a fada a {asar Hausa akwai maza da mata, amma yawanci mata sun fi yin ki]a irin na Zabiyanci da Zibiyancin Fada.

Mawa}a da maro}an fada su ne wa]anda tun fil azal an san su da yi wa Sarakuna wa}a da ro}on baka kuma yawancinsu sun gaji kakanninsu da kuma mahaifansu. Zabiyar Fada na ]aya daga cikin rukunin maro}an fada. Idan aka kasa su dangane da abubuwan da suke aiwatarwa tana cikin '`yan mu'abba' ko 'bamba]o' ko kuma 'kwando', wa]anda ba su da kayan ki]a amma suna yi wa saraki kirari.

A cewar Kafin Hausa (1997:49), kirari }ashin bayan wa}a ne saboda shi ke taimakawa wa}a ta dogara ta mi}e. A bayaninsa ya ce wa}a ta baka ko rubutaciyya, ta }unshi kirari fiye da sauran nau'o'in adabi, wanda idan da za a cire kirarin, wa}ar za ta kasa tsayawa da kanta. Kodayake kirari na da dangantaka da kowacce irin wa}a, amma dangantakar ta fi }ut da }ut da wa}ar baka. Kirari na da dangantaka ta fuskoki biyu da wa}ar baka, ta fuskar tsari da salo. Wajen tsari idan aka dubi dogon kirari da wa}a tsarinsu na kama da juna, musamman ta fuskar layi da aka samu a dukkaninsu. A fagen salo kuwa, idan aka yi la'akari da halayyar aiwatarwa, kirari ana yin sa ta halin bu]e murya ta hanyar fa]ar magana da }arfi da kuma karkarya murya, yadda idan ka ji za ka yi zaton wa}a ce, to haka ma a wa}a. Sai dai a wa}a ana magana ne mai rauji.

A }o}arinsa na nuna dangantakar wa}a da kirari Gusau (2003: 5-14), ya bayyana cewa cikin ra'ayoyin da masana suka bayar dangane da asalin wa}ar baka a {asar Hausa, akwai

ra'in da ke hasashen cewa wa}a ta wanzu ne daga bautar iskoki ko dodanni da Hausawa suka yi lokacin maguzanci. Masanin ya kafa wannan hujja da bikin cikar shekara wanda shi ya samar da maka]an garaya da na 'yan bori. Wanan ra'i ya yi nuni da cewa a wajen irin wa]annan bukukuwa, Hausawa suna yi wa abubuwan bautarsu zuga da yabo da ta hanyar kirari ko ka]a take. Alalmisali, a bikin cikar shekara zamanin' *Tsumburbura'* da Barbushe ya yi a Kano a kan yi kirari kamar haka:

Jamuna, akasa, mun gama,
Ga Tsumburbura Kanawa,
Ga Magajin Dala.

Burbushe yakan amsa ta cewa:

Ni ne Magajin Dala,
Da kun }i da kun so,
Ku bi ni ba ra'i ba.

Masanin ya kuma kawo kirarin Dodo na "Kyauka" a Kwatarkwashi:

Dodo maye,
Dodo na ba kasha,
Kashe mutum mu tai gida,
Dodo ]an doguwa,
Dodo na ba kasha,
Birki]i ba kyakya.

Gusau (2003:8-9), ya bayyana cewa ana kuma kyautata zato Hausawa sun }agi wa}a ne ta hanyar farauta da kirare-kirarenta. Wanda daga nan ya bun}asa sakamakon noma da ya}e-

ya}e. Ke nan, a iya cewa kirari ne ya haifar da wa}ar baka daga nan kuma zuwan Larabawa da Turawa ya samar da rubutacciyar wa}a.

Wa}a da kirari suna da dangantaka ko nasaba mai }arfi. Tsoho (2010:65), ya kawo wata hira wacce shi da Rigachikun (08/08/84) suka yi da Sa'idu Faru, cewa }anin Sa'idu, da aka tambaye shi asalin wa}ar baka, sai ya ce:

> Dukkan ki]a da wa}a, abin da af farko kirari. Don shi Manzon Allah, ba ai mashi ki]a da wa}a ba, amma an yi mashi kirari. Shi Sasana kirari yai wa Manzon Allah. To shi an mafari, wato kirari, shi ne babban usuli dagga ki]i da wa}a, daga Sasana. Don kowane maki]i in shina ki]a in bai gama da ]an kirari nan ba bai cika, bai gursun ba…

Wannan na nuni da cewa dangantakar kirari da wa}a ta tsoka ce da jini ko kuma mu ce dangantaka ta tsakanin uwa da ]anta, yadda ba mai raba su sai jalla.

Hisket (1975:1-2), ya nazarci ~ur~ushin wa}o}in da aka samu bayan Hausawa sun amshi addinin Musulunci, suka kuma sami hanyar rubutu musamman wa}o}in masu jihadi. Aikin ya bayyana da]ewa ko wanzuwar wa}o}in fada a {asar Hausa ga lokaci mai nisa wa]anda jijoginsu a kullum yabo ne ga saraki. Ya kuma raba wannan nau'i na yabo zuwa rassa biyu, wanda ake samu a kirarin da ake yi wa saraki da kuma wanda ake samu a wa}o}in da ake shiryawa dominsu wa]anda su ma cike suke da kirari. An kawo misalai daga kirarin da ake yi wa Sarkin Kano Yaji da Sarkin Gobir Bawa Jangwarzo da na Sarki Daura Lukudi, da aka yi shekaru da suka shu]e kafin zuwan Musulunci {asar Hausa.

Shi kuwa Bichi (2013), ya yi tsokaci ne kan tasirin shirin game duniya ga hikimomin al'ummar Afirka, ya kawo misali da 'wa}o}in yabo' - wanda nau'i ne na jigogin wa}o}in fada. Aikin Bichi ya fito da alfanu tarna}in da wannan shiri ya kawo. A fannin alfanu ko ci gaban da aka samu daga wannan shiri, kamar yadda Bichi (2013) ya kawo, akwai kawar da wasu al'adu na cin zarafi, musamman na }untata rayuwar mata da ake yi masu. Misali kaciya wacce a da ake yi wa kowace mace da aka haifa. Sai kuma bu]ewa jama'a hanyar sanin al'adun wasu da wannan shiri ya haifar. Rashin alfanunsa kuwa, kamar yadda Bichi ya bayyana sun ha]a da gurgunta kyawawan al'adunmu da yayata munanan ]abi'u da al'adu musamman na mutanen yamma. Al'adun da wannan nazari yake ganin wannan shiri ya fi shafa, su ne wa}o}in yabo da tatsuniya da karin magana da kacici – kacici da kuma tarihinmu. Wannan shiri nazarin ya bayyana cewa ya sami wanzuwa ta hanyar na'urorin zamani na sadarwa wanda ya yi illa ko ya yi tarna}i musamman ga wa}o}in yabo wa]anda yanzu suke so su zama tsohon yayi. Wannan aiki na Bichi yana da kusanci da wannan nazari kasancewa kirarin Zabiyar Fada yana fuskantar wannan barazana ta shirin game duniya wanda burinsa shi ne ya la}ume al'adunmu,kamar yadda Bichi (2003), ya bayyana.

## 2.6 Zabiyanci

*Bargery* (1993) da *Abrahams* (1962) da *{amusun Hausa* (2006), duk sun bayyana 'zabiya' da 'matar da kan jagoranci wa}a. A yayin da *{amusun Hausa* ya bayar da ma'ana ta biyu da: 'matar da a kan ajiye a fada domin yi wa Sarki da sauran saraki kirari'. Wannan ma'ana ta biyu, ta yi daidai da 'Zabiyar' da wannan bincike yake nufi. Saboda haka idan ya ambaci 'zabiya', ita ake magana a kai. Zabiya tana ]aya daga cikin maro}an sarauta a {asar Hausa kuma kamar sauran maka]a da maro}an fada/ sarauta da sukan gaji ki]a da ro}o na sarauta,

to haka ma Zabiyoyin Fada, yawancinsu sun gaji Zabiyanci ne daga iyaye. Kodayake sauyin zamani ya sa wa]ansu sun yi haye, musamman saboda albashin da ake biyan Zabiyoyin Fada a yanzu.

Aikin Zabiya na musamman a fada shi ne yi wa saraki kirari, wato Sarki da matansa da ‘ya`yansa da hakiman yanka, musamman a da, da ba a ba kowa sarauta a {asar Hausa sai ]an-na-gada. Babban aikin Zabiya shi ne fito da Sarki fada daga cikin gida duk safiya, tana gaba, jama’ar Sarki na bayanta, tana yi masa kirari. Bayan da aka kammala zaman majalisa kuma, Zabiya takan  mayar da shi gida, cikin kirarinta. Kirarin ke sanar da fadawan waje fitowar Sarki, ita kuma take sanar da mutanen gida dawowarsa. A nan a iya cewa ‘kirarin nata yana matsayin ‘sanarwa’ da gaisuwa ga saraki. Wannan kirari da Zabiyar Fada kan aiwatar shi ne Zabiyanci. Kirarin Zabiya yana kwarzanta Sarki da }ara masa }ima da martaba da kwarjini da }ara tabbata da matsayinsa da mutuncinsa, musamman a idon talakawansa. Kirarin yana kuma tunzura saraki ya ji babu kamarsa, baya ga nisha]antar da sauran jama’a. A da can da ake ya}i a {asar Hausa da Zabiya ake tafiya filin daga domin kwarzanta maza, su sami }arfin gwiwar fatattakar abokanan gaba, a ci nasara a kansu. Idan kuma ba a tafi da ita ba tana rakiya bayan gari, ta kuma tarbi maya}a lokacin da  suka dawo. Wannan ya sa za a iya cewa ‘Zabiya’ jaruma ce cikin jarumai.

Ibrahim (1988:1-7), ya kasa maka]an sarauta zuwa kashi uku. Kashi na farko shi ne na masu ka]e-ka]e. Misalin wannan rukuni shi ne masu ka]a tambari da taushi da kotso da banga da jauje da sauran irin su.

Kashi na biyu na maka]an shi ne masu bushe-bushe, wa]anda masanin ya sake kasa su zuwa gida biyu. Masu busa kawai da wa}a, misali kakaki da fare da }aho. Na biyu kuma su ne masu busa da ki]a da wa}a, kamar masu algaita.

Na ukun kuma shi ne na 'yan bamba]o /'yan ma'abba /'yan magana (ana kuma kiransu 'kwando'). Wannan kaso na uku shi ne na wa]anda ba su da abin ki]a ko busa, sai dai kawai kirarin baki. Irin wa]annan maka]a, galibi su ka]ai suke yin ro}onsu ba su da 'yan amshi. Zabiyar Fada ta fa]o cikin wannan kaso na uku. Nazari kan Zabiyar Fada a {asar Hausa, a iya cewa bai sami kulawar da ta dace ba. Kusan dukkan ayyukan da suka gabata kan zabiya an yi su ne kan zabiyar da take jagoranci wa}a, ba Zabiyar Fada ba. Za a iya cewa 'Zabiya' takan samu ne saboda, ' za}in murya'. Dokta Mamman Shata, a wa}arsa ta Amadun Gaya yana cewa:

{ul}yel-}ul}yel in ji 'zabuwa'
Ga Amadu mai ba mu magana

Haka ma, a tahamisin wa}ar Malam Sa'adu Zungur ta Arewa Jumhuriya ko Mulu}iya; wadda Malam Yusuf Kantu ya yi yana cewa:

In zance za ka yi kai tsaye,
In nuna ma hanya ]aya,
In ka san ka isa zabaya,
In za ka fa]i- fa]i gaskiya,
Kome taka ja maka ka biya…

Gaskiya mai jin barci ga gado,
Ga abin kallo kuma ga ido,

Ga misali bisa gwargwado,
Gaskiya ba ta neman ado,
Ko na da]in muryar zabaya.

Wata karin magana ta Hausa kuma tana cewa:

"Maruru ya fito a bakin zabiya /magu]iya.

Gusau (2013:6), ya bayyana cewa a {asar Hausa, a da can, samari da 'yan mata sukan taru a ranakun kasuwanni su dinga rera wa}o}i, suna tuna wa kansu abubuwan al'adu a nisha]ance. Masanin ya ci gaba da cewa, a irin wannan ha]uwar ce, samari da 'yan matan suke yin gasa da tseren rera wakoki inda har ake zabar Sarkin Wa}a da Zabiya. Sannan kuma, irin wannan fage ne aka sami wa}o}in Asauwara.

Wa]annan sun tabbatar da cewa za}in murya ya haifar da zabiya, wanda da ma an san za}in muryar mace ba za a ha]a shi da na namiji ba. Tarihi ya nuna cewa, da can a {asar Hausa, maza na ki]a ne,. mata kuma suna yi masu wa}a, saboda za}in muryarsu, wanda sau da yawa, mawa}i yana samun kar~uwa ne saboda 'yan amshinsa (wa]anda kuwa akasari mata ne). Furniss (1996:146-147), ya tabbatar da wannan batu, domin ya bayyana cewa zabiya Uwaliya Mai Amada, farkon wa}arta, tana ki]an }warya ne tare da mijinta, sannan kuma ita ke rera wa}a. Kamar yadda Uwani Zakirai ta sami kar~uwa a dalilin wa}ar 'Habibu ]an makaranta'. A cewar masanin wa}ar 'Habibu' ta fito da ita, duk da cewa ba ita ta tsara ta ba, amma saboda za}in muryarta wa}ar tasa ta yi farin jini. Misali shi ne na 'wa}ar rayuwa', ta Fati Musa. Wannan wa}a ta yi suna cikin tsaranta na wannan lokaci saboda za}in muryar da aka rera ta, duk kuwa da cewa ba Fati ta rubuta ta ba, a'a malaminta ya rubuta, ita kuma ta

rera, Halima (2010). To haka ma Hitti (1961:325-28), ya kawo wani tasiri na za}in murya a al'ummomin Ummayyad da Abbasiya, inda ya kira `yammatan da ke wa}e-wa}e a wuraren sha}atawar Larabawa da *'signing girls'*, wato `yammata mawa}a. Wa]anda sau da yawa suke ]aukar hankalin masu sauraronsu, saboda za}in muryarsu. Wasannin dandali ma sun bayar da gudunmuwa wajen fito da zabiyoyin da aka yi a {asar Hausa, domin yawancinsu sun fara ne daga wa}e-wa}en dandali. Ana kuwa za~en zabiya ne daga cikin 'yammata saboda za}in muryarta.

Babu tabbacin asalin samun wannan kalma ta 'zabiya', to amma wasu na hasashen kalmar ta samo asali ne daga 'za}i', wasu su ce 'za~i/ za~a~~u', wasu kuma suka ce 'zabo/zabuwa'. Masana da manazarta kamar su Maryam (2012) da Mack (2004) da Furniss (1996) da Turai (1983) sun nazarci zabiya ta hanyoyi mabambanta. A yayin da Maryam (2012), ta nazarci adon harshe a wa}o}in Barmani Coge da Uwaliya Mai Amada, wa]anda dukkansu maka]an amada ne. Aikin ya yi tsokaci ne kan jigogin wa}o}in nasu da ya ha]a da kunya da soyayya da ro}o da makamantansu, an kuma nazarci ire-iren nau'o'in adon harshen da zabiyoyin suke amfani da su, irin su alamci da tamka da kwalliya da sauransu. To haka ita ma Mack (2004), a }o}arinta na fito da gudunmuwar mata a wa}ar baka da rubutatta, musamman wajen nuna hoton rayuwarsu a cikin al'umma cikin wa}a, misali matsayin mata a al'umma da addini da siyasa da tarihi da kula da lafiya da sauransu. Nazarin ya yi tsokaci kan wa}o}in Hauwa Gwaram da Zabiya `Yar Shehu da Faji Mai Daula da Barmani Coge da Binta Zabaya. Har ila yau, nazarin ya ta~o gudunmuwar Zabiyoyin Fada irin su Zabiya Ajuji Maitazargade (Zabiyar Sarkin Kano) da kuma Hauwa Mai Daula (Zabiyar Sarkin Ningi). Misali, aikin ya kawo wani nau'in kirari da Maitazargade take yi wa Sarki Ado Bayero Kamar haka:

Mai gadin birnin Kano,
Mai gidan birnin Kano,
Mashasha Toron giwa,
Jarma yanka mutane,
Toya matsafa Magajin Kano.

Furniss (1996), kamar Mack (2004), ya yi tsokaci kan ayyukan masana kan adabin Hausa, musamman abin da ya shafi wa}a rubutatta da ta baka da wasan kwaikwayo da tatsuniya. {ar}ashin wa}o}in baka na mata masanin ya ta~o zabiyoyi irin su Binta Zabiya da Uwaliya Mai Amada da Uwani Zakirai, kama tun daga tarihinsu da ire-iren wa}o}insu. Ita kuwa Turai (1983), ta nazarci Binta Zabaya ne ita ka]ai. Aikin ya kawo tarihin zabiyar da kayan ki]inta da ire-iren wa}o}inta da aka kasa su zuwa manyan rassa uku, na aljanu da na mutane zalla da kuma na mutane da aljanu. Aikin ya kuma nazarci adon harshe a wa}o}in Binta Zabaya da jigoginsu. A ta}aice, aikin ya nazarci wa}o}in Binta Zabiya guda goma sha shida (wa]anda suka ha]a da wa}ar Barhaza da Danko da Halima `Yar Buzaye da Sarkin Rafi da Goje da sauransu).

Kamar yadda masana suka bayyana, Zabiyar Fada tana cikin maro}an fada a {asar Hausa, za a iya cewa aikin Smith (1957) da Aminu (1978) Bappah (1984) da Ibrahim (1988) da Tsoho (2010) da Elizabeth (2007) da Bichi (2013), an tsinci dami ne a kala, domin sun yi tsokaci ne kan muhimmancin maro}o da canje-canjen zamani da ro}o ya samu, musamman a sanadiyyar shirin game duniya da makamantan haka.

Smith (1957), ya bayyana cewa a {asar Hausa, maro}a, sun ]auki 'ro}o' a matsayin sana'a, kuma kamar yadda 'ma}era' da 'mahauta' da sauran masu sana'o'i suke ba sana'arsu muhimmanci da kulawa, su ma haka suke }o}ari su kula da ro}on da suke yi. Binciken ya yi nuni da cewa, yawancin maro}a a Hausa maza ne, in ban da mata da suke yi wa saraki kirari a fada, wato zabiyoyin fada. Nazarin ya kuma yi tsokaci a kan ire-iren kayan ki]a da bushe-bushe da maro}an kan yi amfani da su, misali ganga da algaita da kuge da }aho da kakaki. Aikin ya bayyana cewa, maro}a sun fi baje kolinsu a wuraren ajo da bikin salla da lokutan da 'yan bori ke hawa da fadoji da gidajen attajirai da makamantansu. Smith ya kuma yi hasashe da cewa, a rayuwar al'ummar Hausawa kusan ro}o yana da matsayi na musamman.

Aminu (1978: 203-217), ya yi }arin bayyani kan muhimmancin maro}an baka a {asar Hausa, inda ya bayyana cewa, duk mutumin da ya zauna {asar Hausa, ya yi hul]a da Hausaawa, zai yi imani da muhimmancin wa}o}in baka ga rayuwar Bahaushe. Kamar yadda ya yi bayani, a iya tabbatar da haka, domin duk shagalin da aka ambata a Hausa, sai lamarin ya zama 'lami' muddin babu 'maro}a. Ya kawo misali da wurin ra]in suna ko kuma ]aurin aure, a inda limami yakan ambaci, "Salati goma ga Annabi", san}ira ya mamaita saboda jama'a kowa ya ji, to, amma muddin babu maro}i (san}ira) kusa, limamin da kansa ba zai ji da]i ba. Ya kuma kawo misali da yadda maro}a ke tunzura saraki ta hanyar kambama shi da kwarzanta shi da baka ko kuma da nau'in kayan ki]a da bushe-bushe. Masanin ya kawo misali da yadda sautin kakaki ke }ara tunzura da kambama Sarkin Kano Ado Bayero, cewa shi fa saraki ne, ko a cikin Sarakuna:

Ga bajimin sarakai,
Ga sarkin sarakai,
Ga madadin sarakai,

Ga shi a fili,
Ga shi ya fito.

Ibrahim (1988:VII -XI), ya ci gaba ya yi bayani a kan muhimmancin maro}a, a inda ya bayyana cewa, wa}o}in baka ke bayyana halin rayuwar Hausawa da kuma hikimominsu. Ya }ara da cewa, ko a fagen fama, zugan da mawa}an suke yi wa maya}a (a fagen fama), yana taka babbar gudunmuwa wajen samun nasarar abokanan gaba, baya ga nisha]antanwar da ake samu daga kayan ki]ansu da da]in muryar wa}arsu.

Aikin Bappah (1984) da na Tsoho (2010), duk sun yi tsokaci a kan ro}o, musamman fasahar 'san}ira' na iya za~en kalmomi wajen isar da sa}o a wurare daban-daban, kamar a kasuwa da wurin bikin suna da na aure da wuraren da ake ka]awa 'yammata kalangu da fada da wurin wasannin gargajiya, kamar wasan kallankuwa, da yadda san}iran mawa}an Hausa suke kambama iyayen gidansa. Misali, san}iran Shata, yana wasa ubangidansa da kirari (wanda hanya ce ta tallata shi), kafin ya fara wa}a da ba da }iryar wanda za a yi wa wa}a. Sankira yana taimakowa, ya ]aga wa}a, musamman ga ba}on mawa}i. A kuma lokacin da ake yin wa}a, san}ira yana taimakawa mawa}i da ambaton nasaba da makusantar wanda ake yi wa wa}a da yi wa maka]i }ari a wa}a (Tsoho, 2010). Binciken Bappah (1984), ya ci gaba ya yi tsokaci a kan sauyin zamani da 'san}ira' ya samu. Misali, a Fadar Zazzau, 'San}iran Zazzau' da ya gada daga muhaifinsa amma saboda ilimin boko da ya yi, duk ranakun Litinin zuwa Juma'a, yana Kaduna bakin aiki, sai Juma'a da yamma zuwa Lahadi yake zuwa fada, saboda haka dole aka tanaji wani Bagobiri da yake maye gurbinsa a lokutan da ba ya nan.

Elizabeth (2007), a nazarin da ta gabatar ta waiwayi maro}a ne jiya da yau da kuma gobe. A yayin da nazarin ya gano cewa maro}an da da na yanzu kusan bori ]aya suke wa tsafi, wato ba su da bambancin a zo a gani, domin dukkansu muhimmin aikinsu shi ne `yabo', sai dai abin da ba a rasa ba. A yayin da maro}an da suke fito da tarihi musamman na al'umma da jaruntar wani, misali saraki ko ]an tauri ko mafarauci da nasaba ko kuma dangantakar wanda ake yi wa ro}o, maro}an yanzu kuwa a ce sun ci gaba, domin ana tsuntar su a bikin saukar karatu (a makarantun boko) da wuraren taron siyasa, duk kuwa da cewa yanzu maro}an an fi jin amonsu a }auyuka saboda addinin Kirista ya }yamaci ro}on jama'a da suke yi, kamar yadda wannan aiki ya gano cewa addinin Musulunci ma ya yi hani mai tsanani a kan ro}o. Haka ya sa kamar yadda nazarin Elizabeth (2007), ya gano cewa maro}a da dama yanzu a Afirka ta Kudu sun koma masu wa}o}in yabo a coci (gospel music).

A iya cewa maro}a suna ba da babbar gudunmuwa wajen nisha]antar da jama'a kuma mutane ne da suka shahara wajen sarrafa harshe domin samun kar~uwa ga wanda aka yi kirari ko wa}a dominsa da burge mai sauraro, baya ga isar da sa}o cikin ]an }an}anin lokaci.

## 2.7 Jigo

A maganar yau da kullum, 'jigo' na nufin turakun da wasu muhimman abubuwa suka dogara da su domin samun tsaro ko }arin inganci ko madogara (ga wa]annan abubuwa). Ana kuma amfani da wannan kalmar a lambu, watau a matsayin wata 'yar itace (guga), da ake amfani da ita, wajen ]ebo ruwa daga rijiya domin a yi ban ruwa. A mahauta kuwa, 'jigo', tarke ne na itace da ake gwafawa, wanda ake amfani da shi domin rataye nama. Ana

kuma haka ne domin tsaftace shi, da samun sau}in sarrafa shi (kodayake yanzu ana amfani da }arfe maimakon itace, duk da haka sunansa 'jigo').

A fagen ilimi, masana adabin Hausa sun kalli 'jigo' ta fannoni mabambanta, amma duka sun dire da ma'ana ]aya. Gusau (2003) da [angambo (2008), sun kalli kalmar ne ta fuskar nazarin wa}a. Shi kuwa 'Yar'adua (2007), ya kalli kalmar ne ta fuskar wasan kwaikwayo, a yayin da Mukhtar (2004), kuma ya dube ta ta fuskar nazarin zube. [angambo (2008:12), a tasa fahimtar ya ce abin da ake nufi da jigo shi ne 'sa}o' ko 'manufa' ko'abin da wa}a ta }unsa'. 'Yar'adua (2007: 43), a nasa ra'ayin ya ce 'jigo' kalma ce da masana adabin Hausa suke amfani da ita da nufin 'ma}asudi' ko 'manufa' ko 'sa}o' A yayin da Mukhtar 2004:33), ya ce 'jigo' shi ne }ashin bayan labari,wato ma}asudin da aka gina labari a kansa. To haka kuma Bunza (2009:63), ya bayyana cewa, a adabi, na baka da rubutacce, idan ana maganar 'jigo', ana magana ne a kan sa}on da ke }unshe cikin adabi da abubuwan da adabin yake karantarwa, da manufar }ago ko shirya shi, da muhimman abubuwan da adabin yake karantarwa da muhimman abubuwan da aka tunkara ko aka fayyace su a ciki, wa]anda ya ce a ganinsa da wuya wa]annan batutuwa su tsallake manufar jigo, kowane iri. Shi kuwa Gusau (2008), ya yi amfani da kalmar 'turke' ne a maimakon 'jigo' a nazarin wa}ar baka, a inda ya bayyana cewa 'turke', wata kalma ce da aka amince da ita domin nuna 'manufar' wa}a ko 'sa}on' da wa}a take ]auke da shi.

'Jigo' ko 'turke', kamar yadda masana suka bayyana, bakinsu bai sa~a ba, kalma ce da take nufin 'manufa' ko 'sa}o' ko 'ma}asudi' na adabi. Jigo shi ne }ashin bayan adabi, kowane iri, rubutacce ne ko na baka. Ana amfani da harshe a gina 'jigo' saboda haka, irin salon

marubuci ko dabararsa ko azanci da }a}ale-}a}ale, duk manufarsu ya isar da sa}onsa ko manufarsa ga masu sauraronsa ko makaranta. A iya cewa maka]a, musamman na fada galibi jigon wa}o}i da kirarin da suke yi wa saraki ya fi yawaita a jigogin yabo da zuga.

### 2.7.1 Yabo

Masu iya magana sun ce, “Yaba kyauta tukwici”. Tukwicin da mawa}a ke yi wa jama’ar da suke ba su abin hannunsu shi ne ta hanyar ambaton abubuwa na gari a cikin wa}o}insu ko kirari. Ibrahim (1983:10-12), ya bayyana cewa yabo na daga cikin muhimmin jigon da maka]an sarauta suke wa}a a kansa, a inda sukan yabi Sarakuna da iya mulki da kuma ri}e addini da rushe tsafi. Masana irin su Bello (1976) da Furniss (1996) da Diso (1997) da Gusau (2008) Tsoho (2002), sun yi tsokaci a kan ‘yabo’.

Bello (1976) ya ce “Yabo shi ne fa]in abubuwa na gari game da mutum, abubuwan da idan an ji su za a so shi ko a }ara ganin girmansa. Wa]annan kalamai na abubuwan alheri suna cikin abubuwan da maka]an sarauta suka fi }arfafawa” (Bello, 1976:24). Shi kuwa Diso (1997), ya bayyana yabo ne da }o}arin ]aukaka daraja, ko }imar mutum ko wani abu a idon mutane ta hanyar fa]ar kyawawan maganganu game da shi, yadda duk wanda ya ji wa]annan maganganu, zai ji yana }aunar wannan mutum ko bin zuciyarsa.

A kuma ra’ayin Kafin Hausa (1997:100), cewa ya yi, yabo tamkar a sa sabulu ne a wanke mutum tasita hanya fa]in duk kyawawan halayensa. Masali, halayen bajinta da kwarjini da martaba wa]anda Allah ya ba shi. Tsoho (2002), ya rawaito cewa, a wata hira da suka yi da

Alhaji Sa'idu Faru (1984) da aka tambaye shi abin da ake nufi da wa}a, sai ya bayyana ta da cewa:

> Abin da aw wa}a? Yabo … yabo ne kawai …
> Da fara da ba}a. Don wada anka sa zambo ta zama ba}a, wada anka sa lele, yabo, halin mutum na kirki, shi kai ta zan wa}a.

Gusau (2008:461), ya yalli yabo ne a matsayin ambaton kalmomin sambarka da nufin nuna amincewa da hali ko wani abin da mutum ya yi na gari, ko wani lafazi da ake yi ga mutum domin a nuna halayensa abin }auna ne.

A ta}aice, a iya cewa yabo furuci ko maganganu ne na godiya ta hanyar fito da wani domin sauran jama'a su san shi, su san }imarsa da darajarsa, sannan kumasu }aunace shi. Yabo na daga cikin manyan turakun da maka]an baka suka fi yawaita yin wa}o}insu a kansu. Kusan shi ne ma fitaccen tarken wa}o}in Hausa, musamman wa}o}in fada domin mafi yawansu munufarsu kan kasance yabon wanda aka yi wa}a ko kirari dominsa.

Furniss (1996:178), ya bayyana cewa a kodayaushe mawa}a na yawaita yaba mutunci da ri}on addini da jaruntaka da adalci da karamcin Sarki ta hanyar alamci. Wato ta hanyar alamta Sarakuna, kamar yadda Umar (1984), ya yi }arin bayani da cewa mawa}an na yin haka ne domin a ga girma da daraja / }ima da kwarjinin saraki, ko dai matsayinsu a ta}aice. Masanin ya jaddada cewa babu abin da saraki ya fi jin da]i kamar a yabe shi da asalinsa ko tushensa. Watau a nunawa jama'a musamman abokanan hamayya cewa sarautar nan ta gidansu ce, ya gaje ta kaka da kakanni.

Gusau (2008:376), na da ra'ayin cewa wa}o}in yabo na baka na da nau'i biyu. Akwai wa}o}in yabo budunaye, wanda ya ji~anci sha'anin duniya kamar yabon Sarakuna da

sauran masu ri}e da mu}aman gwamnati da sojoji da sauran wa]anda suka yi wani aikin bajinta. Na biyun shi ne yabon da ya shafi sha'anin addini, kamar wa}o}in da ake yi da suka danganci yabon ubangiji ko Annabawa ko sahabbai ko waliyyai da sauran malamai.

"Fara wa}a da yabo ko yin salati, ha}i}a wata hanya ce da marubuta wa}o}in Hausa ke fara wa}o}insu da shi" (Sar~i, 2007:55). A wa}o}in baka, ana yi wa mutum yabo ta hanyar nuna halayensa kyawawa ko siffanta shi da wasu ]abi'u ko ayyuka wa]anda za su }ara masa kwarjini da martaba a idon mutane, Gusau (2008:20).

A ra'ayin Bello, (1976:26), mawa}an fada suna ]ora yabo kan shikashikai biyar. Wa]annan shikashikai kuwa su ne addini da asali, ha]e da ambaton zuri'a, da jaruntaka wajen ya}i da iya mulki da kuma kyauta. Masanin ya jaddada cewa wa]annan shikashikai, suke }ara nuna dangantakar maka]i da ubangidansa, sannan su razana abokanan hamayya. Yana kuma }ara wa Sarakuna }arfin gwiwa da faranta masu rai, su }ara sha}atawa su yi abin da suka so.

Junaidu da 'Yar'adua (2007:95), sun }ara 'zuga' cikin wa]annan shikashikai da maka]an fada suke bi domin yabon Sarakuna suka zama shida. A iya cewa maka]an fada sun shahara wurin yin yabo da zuga da habaici da zambo. A wani lokaci, a ce Sarakuna ke sa maka]an yin zambo da habaici domin magabata su razana su kuma daina hamayya da su, Mazawaye (1985:10).

Maka]an fada suna amfani da yabo a duk wa}o}insu da kirari, domin sun ]auki yabo kamar shi ne wu}a shi ne nama a wa}ar fada. Idan an yabi mutum, ana fa]in abubuwansa na gari, domin a girmama shi. A wani gefe kuma ya }ara masa farinjini a idanun jama'a (Mazawaje, 1985:16).

Tsoho (2002:150-202), ya yi amfani da kalmar ‘yabau’ domin a fa]a]a da baddala kalmar ‘yabo’ musamman yabon da ya shafi wani gwarzo ko gwaraje. A cewa masanin, yin amfani da kalmomi na musamman wajen yabon saraki alamci cikin kwalliya da shi ne ‘yabau’. Kalmomi wa]anda ke kambama da gwada ]aukakar saraki a kan talakawa ta hanyar danganta shi da manyan dabbobin dawa }arfafa masu kwarjini da abubuwan ban tsoratarwa wa]anda ke fayyace }imar saraki da raunana zuciyar abokanan hamayya. Ya kuma kasa yabau a wa}o}in Hausa zuwan manyan gidaje ko rassa biyar. Yabau na kwalliya da yabau siffantau da yabau aikatau da yabau dangantau da kuma yabau mai sigar jimla. Ya ci gaba ya bayyana cewa, ma}ir}irin wannan kalma wadda  asalinsa a Turanci take (Buloques), shi ne D.P. Kunene (1971), wani shehun malami a }asar Afirka ta Kudu.Tsoho (2002), ya yi bayanin wannan kaso na yabau kamar haka:

**Yabau kwalliya**: shi ne inda maka]i ke amfani da kwalliya. Misali, amfani da dabbobi masu kwarjini da }arfi domin nuna isa ko ]aukaka wanda ake yi wa wa}a, musamman basarake ko wani babban attajiri. Ana kwalliya da dabbobi irin su zaki da giwa da damisa da ~auna da makamantansu.

**Yabau siffantau**: shi ne amfani da siffa ko ]abi’u da halayen wanda ake yi wa wa}a domin sauran jama’a su ji, su ga girmansa, shi kuma ya ji da]i. Kalmomi irin su ‘gamda’are’ (mai sanar da isowar ya}i) da ‘sadauki’ (jarumi) da ‘katakore’ (}ato) da sauransu.

**Yabau aikatau**: shi ne amfani da kalmomin aikatau, a ha]a su da suna, a haifar da har]a]]an suna, domin burge wanda ake yi wa wa}a, ko fito da aikin wanda ake yabo. Misali,‘}i-sake’, da  ‘ma-}i-gudu’ da ‘cifansa’ da sauransu. Alalmisali, a wa}ar Sarkin Zazzau, Shata yana cewa:

Kai da garaje ka }i garaje…

Na Garba jikan Malam Sambo…

**Yabau dangantau**: shi ne inda mawa}a ke danganta wanda suke yi wa wa}a da musamman iyayensa da kakanninsa da iyalansa da sauran makusanta, misali fadawa da ‘yan majalisar Sarki (idan basarake ne) da abokansa.

**Yabau mai zuwa da sigar jimla**: kamar yadda sunansa ya nuna, yabau ne da yake zuwa a siga ko yanayin jimla. Misali” Shata a wa}arsa ta Sarkin Daura Muhammadu Bashar ya ce:

Giwa ]an Ummaru,

Mai ]amarar ya}i ]an Musa.

A kuma wa}ar Sarkin Kano yana cewa:

Ga mai tamburan ya}i nan…

Maka]a, a ganin Usman (2009:120-124), suna yabo ne a kan dalilai biyu. A kan gwaninta da kyauta. Ya kawo misalai daga wa}o}in mashahurin maka]in zare, Garba Namata a wa}arsa ta [antallu Tattalai da [andare [ankola, wanda wa}o}insa sun ha]a da yabo kan gwaninta a fagen sana’ar }ira da yabo bisa ga karimcin wanda ake yi wa wa}a da ro}o, kamar yadda yake cewa:

Dodo }ira gare shi,

Dantallu na Tattalai.

(wa}ar [antallu Tattalai)

Don mu hwa]i a kan ba mu kyauta,

In ba mu hwa]i ba a ba mu kyauta

Tsare tama za ni in ishe mai,
[andare [ankola ka hi koyo,
(wa}ar [andare [ankola)

[iyan wa}a ta biyu ya tabbatar mana da cewa masu ba mawa}in alheri na bu}atar a gaya wa mutane irin karimcin da suke yi, domin rashin fa]ar na iya sa a daina ba shi. Na farko kuma ya nuna bajintar wanda aka yi wa wa}ar a fagen sana'ar }ira.

Yabo ya wuce a wa}a kawai. Ko Allah Ma]aukakin Sarki ana yabonsa tare da yi masa zuga ta hanyar amfani da kyawawan sunayensa da siffofinsa, musamman idan ana neman wata bu}ata daga gare shi. Domin haka a iya cewa yabo da zuga suna da dangantaka ta }ut da }ut, har wani lokaci ba kowa ke iya bambanta su ba saboda shigar gizagizai da suke yi wa juna.

### 2.7.2 Zuga

Ibrahim (1983: 13-14), ya bayyana cewa a lokacin da maka]a suke yabon Sarakuna, har sukan ha]a da zuga. Sukan zuga Sarakunan da suke yi wa wa}a su kai su inda Allah bai kai su ba. Har sukan ce Sarkinsu ya fi kowane Sarki a duk {asashen Hausa, ko kuma a duniy baki ]aya. A }o}arin bayyana zuga, Yahya (1997) da Kafin Hausa (1997) da Dunfawa (2004) da Gusau (2008) da Bunza (2009), sun bayyana ma'anar wannan kalma kamar haka:

> Zuga jigo ne wanda kalmominsa ke kambama basarake, su cicci~a shi, su ingiza shi ga yin abubuwan da in da babu wa}ar, da wata}ila ba zai yi mafarkin aikata su ba" (Yahya, 1997:131).

> Zuga a cikin wa}a shi ne yin amfani da kalmomi da jimloli masu harzu}a wanda ake yi wa wa}a har ya ji ya kumbura ya harzu}a. Wani lokaci har ya ji yana iya aikata wani abu dalilin wannan zugar (Dunfawa; 2004:224).
>
> Zuga na nufin amfani da wasu kalmomi na kambamawa da cicci~awa zuwa ga wani da za su sa ya ji da]i har ya kumbura ya cika sosai. A ta}aice, amfani da wasu kalmomi don a ko]a wani mutum da cicci~a shi da nuna fifikonsa kan wasu, shi ne zuga, Gusau (2008:461).
>
> Zuga dabara ce ta ]aukaka abu sama, a iza shi, ko a tura shi a ce ya yi wani abu, ko ya saba wani abu, ko zai iya wani mawuyacin abu. (Bunza, 2009:147-148).

Daga ma'anonin da masana suka bayar, a iya cewa ba wani abu ne zuga, illa amfani da kalmomin harzuka wani, ta hanyar kambama shi matu}a. Masana duk sun amince da cewa zuga ya }unshi wani sashe na wa}a wanda ke }o}arin sosa zuciya, saboda nuna fifiko da ake yi. Zuga kan tsuma mutum ya ji babu kamarsa, sannan ya sa masa kuzari da }warin giwa, har ya ]auki duman Magaji da nishi, ko bai iya ba, ya ce zai yi. To sai dai a ce ba a wa}o}i ka]an ake samun zuga ba, ana samun zuga ma a kirari musamman na fada. A kan zuga mutum a motsa zuciyarsa ta fusata ta hanyar ka]a masa take ko a yi masa kirari ko kuma haka a cikin zance a nuna 'shi kawai ya isa'.

Kirari da zuga a ganin masana irin su Kafin Hausa (1997), da Bunza (2009), bori ]aya suke yi wa tsafi saboda duk lokacin da kirari ya tsaru sosai, ba a rasa zuga a cikinsa. Kamar yadda a kan fa]i kalmomi masu kambamawa a kirari, a zuga mutum ta hanyar fa]in kalmomi masu tunzura shi, har ya aikata abu na bajinta ko na assha, wanda a haka nan salin-alin ba zai yi su ba, in ba an zuga shi ba.

Kirari da zuga sun bambanta ta hanyar aiwatar da su, amma aikinsu kan zama ]aya. Haka kuma, mutum ba ya zuga kansa da kansa, sai dai wani ya zuga shi, amma yakan yi wa kansa kirari, sannan kuma a yi masa (Kafin Hausa, 1997:100). Wannan ya sa Hausawa kan ce, `Yabon kai jahilci'.

Wa}o}in baka na Hausa, musamman na Sarakuna, cike suke da zuga. Dunfawa (2004:224), ya bayyana cewa ta la'akari da ma'anar da masana suka ba zuga, za a iya cewa zuga a cikin wa}a shi ne yin amfani da kalmomi da jimloli masu harzu}a wanda aka yi wa wa}a har ya ji ya kumbura ya harzu}a, wani lokaci ya ji yana aikata wani abu dalilin zugar.

Wa}a da kirarin fada sun }unshi zuga matu}a, inda za a ga maka]i ya zuga Sarki, shi kuma ya cika ya batse. Wannan shi ke sa Sarakuna tun}aho, suna ji da kansu, suna ta}ama, suna yin abin da suka ga damar yi. Alalmisali, akwai inda Naramba]a ke cewa Sardauna Ahmadu Bello:

> Daga Kaduna har Gusau }arewar Hausa yau kowace shawara ta zamanin Turawa Ahmadu ba a yinta sai ya sa hunnunai Don ko }o}ari ga rai da sanin hujjoji. . . .
> Gwarzon Shamaki (Mazawaje, 1985:16-17).

Maka]a [an}wairo ma ya zuga Sarkin Daura Muhammadu Bashar inda yake cewa:

| | |
|---|---|
| Marafa: | Ka zama Sarki ka fashe haushi, |
| | : Kai ne Audu ka gaji Musa, |
| 'Y/Amshi: | Kai aka tsoro wa kaka tsoro, |
| | :Yaro ba ya gardama da Sarki, |
| | :Faufau yaro ba ya gardama da shi. |

Ya kuma ci gaba a wani ]iyar wa}a inda yake cewa:

| | |
|---|---|
| Marafa: | Muhammadu Sarkin Sarakuna, |
| `Y/Amshi: | [an Musa na Salisu Shirarre, |
| Marafa: | Kai kad da martaba, |
| `Y/Amshi: | [an Musa Salisu shirarre, |
| Marafa: | Muhammadu hasken Nijeriya, |
| `Y/Amshi: | [an Musa Salisu shirarre, |
| Marafa: | Shi anka sani ba a san su ba, |
| `Y/Amshi: | [an Musa Salisu shirarre, |
| Marafa: | Muhammadu ya haye mahassada, |
| `Y/Amshi: | Kai ag gaba saura suna a baya. |

( Maka]a [ankwairo, wa}ar 'Babban Jigo na Yari') '

Baya ga Sarakuna, wa]anda mawa}a suke zugawa su ne 'yan dambe, saboda jaruntaka. A nan Tsoho, (2002) ya ce:

> Zuga da kambamawa bayan an kafsa kan }ara wa jarumi }warin gwiwa nan gaba. Ganin an yaba wa jarumi kam, an san cewa za a yaba wa duk wanda ya yi bajinta kan sauran jarumai jajircewa da fatan su ma su sami haka (Tsoho, (2002:93-92).

A wa}o}in noma kuwa, bayan an zuga manoma (a matsayinsu na masu bajinta da ciyar da al'umma) ana kushe raggo, a nuna gazawarsa duk domin a kambama manomi/manoma, kasancewa noma aikin maza ne na jaruntaka, domin haka, raggo ba ya iya yinsa. Wannan ya sa maka]an noma ba sa yi wa raggo ki]an noma, maimakon haka, sai su siffanta shi da wata ]abi'a marar kyau ko wata halayya ta kasawa ko gazawa. Misali:

Damuna ta dawo raggo na kuka,
Ya zo shi yin noma rana ta hana,
Ya dawo gida ba tsabar daka,
Ba ku]]in awo, ya kama bara,
Mata sun hana,
Kowa kir~a gona za ya yi,
Tsohon shegen kuka ya cira,
Raggo yac ce wayyo Allah, wayyo Annabi,
Wayyo yunwa wai me nai miki,
Ko ko yunwa ji mi za ta yi,
(Idris, 2009:73)

Ta la'akari da wasu mahimman kalmomi da masana suka yi amfani da su wajen bayyana abin da ake nufi da 'zuga', Dunfawa (2004:224-230), ya kasa zuga zuwa nau'o'i uku, zuga kumburau da zuga ingizau da kuma zuga kariyau, kamar haka:

**Zuga kumburau**: ita ce nau'in zuga da mawa}an fada ke amfani da ita su kumbura wanda suke yi wa wa}a har ya ji yana cika yana batsewa tamkar dai an hura shi. . . .

**Zuga kariyau**: ita ma mawa}an fada ke amfani da ita don kare wanda suke yi wa wa}a daga hawan }awarar abokan hamayya. Wani lokaci kuma don kare wanda ake yi wa wa}ar daga wa]anda yake wa shugabanci a kan kada su kuskure su yi wata jayayya da shi. A cikin irin wannan zugar, sukan ri}a bayar da tsoro game da shi ta hanyar nuna cewa wanda suka yi wa wa}ar gagarau ne wandare. Sukan nuna a cikin wa}ar tasu cewa duk wanda bai ji bari ba, to zai ji hoho, domin duk wanda ya ja da shi, to shi ne a }asa, Har wani lokaci sukan ambaci irin nasarorin da ya ta~a samu a kan wasu abokan hamayya…

**Zuga ingazau**: ita ce wadda mawa}an fada ke amfani da ita domin su tunku]a ko su ingiza basarake ya aikata wani abu wanda da ba don zugar ba da ba zai aikata shi ba. Wannan abun na iya zama kyauta ce ko kuma wani abu daban. Haka kuma ta wajen irin wannan zugar, ana iya ingiza basarake ya }i yin wani abu da kafin wannan zugar ya yarda zai aikata shi. Ita irin wannan zugar wani lokaci ana danganta ta da wani abu na tarihi, sai ta zama kamar an yi hami (ciwo cikin wani rauni), ga wani rauni da ya yi bayan ya kusa warkewa… Kowane nau'i daga cikin nau'o'in zugar nan, yana da aikin da yake ga wanda ake yi wa wa}a, haka kuma kowane nau'in zugar mawa}a na amfani da shi domin biyan wata bu}ata, ya Allah tasu ko ta basaraken da suke yi wa wa}a, (Dunfawa, 2004:231).

A iya cewa wa}o}in fada cike suke da yabo da zuga a kodayaushe. Ko dai ana yabon basarake ko kuma ana zuga shi, musamman game da abokanan hamayya. Dunfawa, (2004), ya bayyana cewa lamirai biyu ke bambanta zuga da yabo a cikin wa}o}in fada. Ya yi }arin bayani da cewa, yayin da ake amfani da lamirin abokin magana ya zama zuga ga wanda ake yi wa wa}a, ana amfani da lamirin ga'ibi ya zama yabo ne kawai ga wanda ake yi wa wa}a. Masanin ya }arfafa da cewa:

> Amfani da lamirin aboki kodayushe yana nunin wanda ake yi wa wa}a ana zuga shi ta hanyar tunatar da shi game da wasu abubuwa wa]anda ko da ya san su, to ana }ara tuna masa. Shi ko amfani da lamirin ga'ibi ba wanda ake yi wa wa}a ake magana da shi ba, mawa}i na magana ne da sauran jama'a ta hanyar nuna masu girma da martabar wanda yake yi wa wa}a, domin su dube shi da girman da mawa}in ke da'awar yana da shi (Dunfawa, 2004:231).

A ta}aice, a iya cewa yabo da zuga na daga cikin manyan turakun (jigogin) wa}o}in baka, musamman wa}o}in fada. Zuga da yabo }ila 'ya'ya ne na kirari, domin idan aka yi maka kirari zuga ne  ko yabo ake yi a ta}aice.

## 2.8 Salo

Salo, kamar yadda masana irin su Crystal (1991) da Yahya (2001) da Gusau (2003) da Baldic (2004) da Yar'adua (2006) da [angambo (2007) da Garba (2011), suka bayar da gudunmuwa wajen bayyana ma'anarsa, shi ne dabarun isar da sa}o cikin hikima domin ya sami armashi.

Crystal (1991), a tasa fahimtar ya bayyana salo ne da hanyar da ake bi a }wan}wance matani a magance ko a rubuce. A yayin da Yahya (2001:3) da [angambo (2007:34), suke cewa, salo shi ne duk wata dabara ko hanya da aka bi aka isar da sa}o. Kamar yadda Yahya (2001), ya kira salo 'asirin wa}a', shi kuwa [angambo (2007), ya yi }arin bayani ne da cewa, salo yanayi ne da ya }unshi za~i  cikin rubutu ko furuci, dangane da batu, wanda kan yi tasiri ga sa}on da ake so a isar. Ko dai ya yi armashi ko kuma ya kasance mai lami.

Gusau (2003:53), kuwa ya siffanta salo ne da hanyoyi uku, wa]anda ya bayyana cewa, su ne ma'aunin raba za}in wa}a ko ]acinta. Watau dabarar da ake yi wa harshe ado, ko kuwa hanyar sarrafa harshe, a jujjuya shi, ta yadda da za a ta}aita manufa ko sakaya ma'anarsa da kuma kaifafa tunani.

Har ila yau, Gusau (2003:52), ya ruwaito Sa'id (1981:35), yana bayyana salo ta fuskar nazarin wa}a rubutacciya inda yake cewa salo, shi ne yadda mawa}i ya zana tunaninsa a takarda. Shi kuwa Baldic (2004:94-100), cewa ya yi, salo hanya ce da fasihi ko zamani ko mazabaha ko kuma wani fanni ya shahara wajen sarrafa harshe. A yayin da Mukhtar (2004), kuma yake cewa, "salo wani tsari ne cikin rubutu, salo harshe ne na wani mutum, salo tsarin amfani da harshe ne na marubutan zamanin da ake ciki, salo shi ne za~i cikin harshe, salo shi ne bayyana ma'ana, salo shi ne sa~a }a'ida".

Shi kuwa Bunza (2009:13), ya bayyana salo ne da, matakan sarrafa kalmomi, wato dabara ko fasaha da wayon tafiyar da wani abu cikin basira da natsuwa domin kai ga wata manufa ta musamman. Ya ci gaba da bayani cewa masana adabi da al'ada da harshe na kowane harshe, a babin salo suke baje guminsu yadda ya kamata domin a san hikimomin da ke cikin harshensu. Kamar yadda Garba (2011), yake cewa, salo shi ne }ashin bayan isar da sa}o cikin hikima da fasahar harshe. Hassan (2013: 62-63), ya }ara jaddada rawar da salo ke takawa da cewa, dabara da hikimar fasihi ke }ara wa adabi armashi, har a ji da]in karantawa.

A ta}aice, a iya cewa ba wani abu ba ne 'salo' illa hanyar da aka tantance tunani ta hanyar za~en kalmomin da suka dace da batu da iya sarrafa su, domin kwalliya da jawo hankalin mai sauraro ko makaranci da ma wanda aka aiwatar da batu dominsa. Salo muhummin abu ne kuma ginshi}i wajen sa sa}on ya yi armashi har ya sami kar~uwa. Shi ne kanwa uwar ha]i, musamman a adabin baka domin shi ke fito da sa}on adabi.

Al'ummar Hausawa ta ginu bisa fasahar harshe, ta haka ne adabin baka ya damfaru ainun a rayuwar Hausawa, tun ma ba na farko ba a inda ayyukan adabin baka, kamar kirari da karin

magana da salon magana da wa}e-wa}e da sauran hanyoyin sakayawa da gajarce zance cikin hikima da balaga suka zama ruwan dare. Irin wannan al'umma mai son gwanintar harshe, da karakainar amfani da kalmomi da jimloli masu ma'ana daban-daban, ta haifar da mutane masu kirarin baki da maka]a da mawa}a masu yawan gaske a zangunan rayuwa da lokuta mabambanta, Gusau (2012:20). Zabiyar Fada na ]aya daga cikin wa]anda Allah Ya horewa wannan fasaha ta shirya kirari da gabatar ko aiwatar da shi ga saraki.

### 2.8.1 Salon Sarrafa Harshe

'Salon sarrafa' harshe kusan a ce }auli ne da ya bayyana kansa da kansa, wato da 'gani babu tambaya'. Harshe tunani ne na ]an Adam a magance ko a rubuce, harshe kuwa shi ne kayan isar da sa}o – saboda haka 'salon sarrafa harshe' dabara ce da kisisina na sarrafa harshe. Masana irin su Muhammad (1977) da [anganbo (2008) da Gusau (2003) da Bunza (2009) da wa]ansu da dama sun tofa albarkacin bakinsu kan wannan batu.

Muhammad (1997), ya bayyana salon sarrafa harshe da abubuwan da kayan adon harshen wa}a ya kunsa wa]anda ya ce sun ha]a da amsa-kama da }arangiya da kamance da mutuntarwa da tamka da sa~i-zarce da makamantan haka. Shi kuwa [angambo (2008: 49-50), cewa ya yi 'salon sarrafa harshe shi ne 'nahawu a harshen adabi', wanda ya }unshi amfani da kalmomi da tsarin jimla da gi~in jimla da kwance }ullin jimla.

Gusau (2008:53), a tasa fahimtar cewa ya yi, salon sarrafa harshen wata hanya ce ta nuna gwanintar harshe a rubuce ko a magance. Ya }ara bayani da cewa za a iya kasa salon sarrafa harshe zuwa gidaje biyu, 'adon harshe' da 'aiwatar da shi'. Haka kuma, Bunza (2009:182), ya bayyana salon sarrafa harshe da 'batun da ya ke~anta ga za~en kalmomi', wa]anda ya

ha]a da amfani da kalmomin fannu da tsofaffin kalmomi da kuma }ir}irar sababbi. Har ila yau kuma da aron kalmomin daga wasu harsuna su dace da harshen da fasihi yake amfani da shi.

### 2.8.2 Adon Harshe

Wannan aiki, aiki ne da ya nazarci adabi domin fito da rayuwar al'umma, saboda haka, a fagen nazarin salo, an za~i a nazarci salon na gaba ]aya, da ya ji~anci tasirin harshen da aka yi amfani da shi, amma za a fi mayar da hankali a kan adon harshe na kirarin Zabiyoyin Fada a {asar Hausa. Ke nan, ba za a nazarci sauran fannoni da suka ji~anci salo ba, kamar gundarin ma'ana da tsarin nahawu da makamantansu. Kirari, musamman na fada cike yake da fasahar harshe mai nuna azanci da gwaninta. Masana adabin Hausa, irin su Muhammad (1981) da Sa'id (1987) da Dikko da Macci]o (1991) da Gusau (1993/2003) da Yahya (1997/2001) da Amin (2002) da [angambo (2007) da Bunza (2009), duk sun tofa albarkacin bakinsu a kan ma'anar adon harshe.

A nasa ra'ayin, Muhammad (1981), cewa ya yi, adon harshe hanya ce ta gyara harshen zance. Sa'id (1987), kuwa ya bayyana adon harshe ne da aron ma'ana, ta hanyar ba kalma ma'ana daban wadda ba tata ba ce amma za ta maye gurbinta. Kamar yadda Dikko da Macci]o (1991), suka kira shi da 'tarin kalmomi biyu ko fiye da haka, da ke haifar da ma'ana mabambanta. A yayin da Gusau (2003), kuma ya ce adon harshe shi ne dabarar yi wa harshen wa}a kwaliya. Shi kuwa [angambo (2007), cewa ya yi, adon harshe za~i ne cikin rubutu ko magana. Masanin ya yi }arin bayani da cewa, wannan za~i, hanya ce ta ]aukar hankalin mai sauraro/karatu.

Yahya (1997/2001), a nasa ra'ayin ya bayyana adon harshe ne da salon siffantawa da ke kyautata wa}a domin ta yi tasiri ga mai sauraro. Kamar yadda Amin (2002), ya siffanta adon harshe da kwalliya }arara a zance ko matani. Bunza (2009) kuwa, ya suranta adon harshe ne da amfani da dabarun nahawu daban-daban domin }awata wa}a ko zance. A inda kuma Dija (1997), ta bayyana adon harshe da ma'aunin da ke nuna iyakar hikimar zance da ke }arawa zance armashi.

Su ma masanan yamma ba a bar su a baya ba, domin idan aka duba ayyukansu, an tsinci dami ne a kala. Masana irin su Aristotle, (Butcher, 2000) da Bolinger (1968), da Cuddon (1979), da Honstman da shifly (1970), sun bayyana adon harshe ta fuskoki mabambanta. A yayin da Aristotle, a rawaitowar Butcher (2000), ya kira shi da 'gishirin wa}a/zance', domin jawo hankali ta hanyar nuna muhimmancin abu ko akasinsa, Bolinger (1968), ya suranta shi ne da hanyar ]aukar hankalin mai sauraro. Shifly (1970), kuwa cewa ya yi, adon harshe hanya ce ta karkatar da wani abu daga siffarsa ta asali, zuwa wata daban ta hanyar kwalliya da kamantawa da tamka da jirwaye. Shi kuwa Honstman ( ), cewa ya yi, ba wani abu ne adon harshe illa basira ko hikimar da ke }awata zance domin ]aukar hankalin mai sauraro. A kuma ra'ayin Cuddon (1979), adon harshe shi ne sinadarin da ke fito da zance ko wa}a har ya sami armashi.

Adon harshe, kamar yadda masana suka bayyana, shi ne dabarar yi wa harshe kwalliya domin ya }awatar. Watau salo ne na amfani da ire-iren dabaru a sarrafa su domin kyautata matani. Za kuma a iya fahimtar cewa ba harshen wa}a ka]ai ake yi wa kwalliya ba, ana samun kwalliya a fannonin adabi da dama wa]anda suka ha]a da 'kirari', musamman na fada. Wannan bincike ya gano cewa Zabiyoyin Fada galibi suna amfani da nau'o'in adon

harshe irin su abuntarwa da kwalliya da tamka da hoto cikin bayani da makamantansu a kirarin da suke yi wa saraki.

**2.9 Zubi da Tsari**.

Zubi da tsari na daga cikin hanyoyin nazarin adabi, musamman ma na baka. Ta hanyar zubi ko tsari ne ake gane cewa wannan nau'in adabin zube ne ko wasan kwaikwayo ko kuma wa}a ce. Masana ba su bar wannan fage kara zube ba, sun tofa albarkacin bakinsu domin samun jagoranci ga manazarta.

Mukhtar (2004:33), ya bayyana cewa zubi da tsari a }agaggen labari ya }unshi labarin gaba ]ayansa, musamman muhimman abubuwa a cikinsa wa]anda za a iya tunawa da su kamar sunayen taurari manya da }anana da wurare da garuruwa cikin labarin, da yanayin da marubucin ya sako wuraren da kuma abubuwan da suka faru manya da }anana a cikin labarin.

Masanin, ya kawo misali da *Nagari na Kowa, a* inda ya nuna cewa abubuwa muhimmai da suka gina labarin, wa]anda kodayaushe za a tuna da su sun ha]a da sunayen muhimman taurari, kamar [anduna da ]ansa Salihi da kuma Zibu da Maidubu. Haka kuma, dole kuma a tuna da irin rawar da suka taka da muhimman wurare irin su Birnin Tsira da Zangon Gyara da abubuwan da suka faru a wa]annan wurare.

`Yar'aduwa (2007:24), ya dubi zubi da tsari ne a wasan kwaikwayo. A inda ya bayyana cewa kyakkyawan tsari a wasan kwaikwayo shi ke haifar da wasa. Ya ci gaba ya bayyana sharu]]an da suka wajaba a wasan kwaikwayo, wa]anda suka ha]a da tsari na musamman dangane da 'yan wasa da kayan wasa da muhallin wasa. Saura sun ha]a da jagora, wato mai

shela da tsarin fitowa a dandali da ba kowane ]an wasa muhallinsa da aikin da ya dace da shi domin samun kamanto da kamance.

Haka kuma, shi ma [angambo (2008:17-32), ya dubi zubi da tsari a wa}a gaba ]ayanta, a inda ya bayyana cewa ana duba tsarin wa}a gaba ]ayanta dangane da yadda aka shirya ta. Watau, ‘Carbin tunanin mawa}i', kamar yadda ya la}aba masa suna. Kamar yadda ya bayyana, ta haka ne ake gane ko marubuci ya jera tunaninsa ko kuwa yana kwan-gaba-kwan-baya, ko kuma yana maimaita batutuwa da saura makamantansu.

[anganbo ci gaba da bayani cewa, shara]i na biyu a nazarin wa}a shi ne zubi da tsari cikin baitoci. A nan ana duba danganta}ar ]ango a cikin baiti da kuma gano ko baitocin sun }unshi jimlatattun manufofi ko kuwa sun dogara da juna. Za a kuma duba yawan ]ango a baiti. Ana kuma nazarin yawan baitoci da ]ango a wa}a, domin a san wa}ar ‘yar }war biyu ce ko uku.

A ta}aice, a iya cewa zubi da tsari a nazarin adabi hanyoyi ne na warwarar adabi, watau siffa ce ta adabi a wa}a ce ko wasan kwaikwayo ko zube da makamantansu. Zubi a adabi musamman na adabin baka, alalmisali kirari ya }unshi sigogi ko fasalinsa da suka ha]a da mabu]i da marufi da sigar layuka (wanda ya danganci yawansa da tsawonsa) da amshi ko kar~i da amsa-amo (idan akwai) kama da sigar tsarin tambaya da amsa, su ma idan sun zo a kirarin. Kirari nau’i ne daga zantukan hikima, }ar}ashin adabin baka. Sauran nau’o’in zantukan hikima musamman a adabin baka na Hausa sun ha]a da: karin magana da habaici da ba}ar magana da take da kacici-kacici da kuma barkwanci.

A wannan nazari, an duba irin zubi da tsarin da ke cikin kirarin Zabiyar Fada kamar haka:

- A zube yake ko yana zuwa cikin baitoci?

- Yana da amsa-amo?
- Yana da amshi ko kar~i?
- Yana zuwa a tsarin tambaya da amsa?
- Akwai maimai? Da sauran makamantan bayanai haka.

**2.10 Kammalawa**

A wannan babi, an waiwayi wasu batutuwa da ke da ala}a ta kusa da ta nesa da aikin da aka gabatarwar. An yi bitar batutuwa kamar: Hausa da {asar Hausa da Hausawa, tare da bita da sharhi a kan saraki da mata a {asar Hausa. Sannan kuma aka ha]a da wasu nau'o'in adabin baka masu dangantaka da kirarin zabiya a fada, wato take da wa}a da manyan jigogin adabin fada, wato yabo da zuga tare da ayyukan da masana da manazarta suka yi a kan fada, musamman a {asar Hausa. An }al}ale da bitar ma'anar salo da jigo da zubi a ta}aice. Ba shakka bitar ta haskaka, domin ta kuma zama jagora ga wannan aiki.

# BABI NA UKU

# HANYOYIN GUDANAR DA BINCIKE

## 3.1 Gabatarwa

Bincike a fannin ilimi ba ya kammaluwa sai an bi hanyoyin da suka dace a gudanar da shi, domin ya sami }ar~uwa,musamman a fagen ilimi. Saboda cim ma burin abin da aka sa gaba, an bi manyan hanyoyi uku a lokacin gudanar da wannan bincike. Hanyoyin kuwa sun ha]a da: za~en fadar da aka gudanar da binciken da hanyoyin tara bayanai da ya ha]a da hira da Zabiyoyin da aka nazarta da wasu al'ummomin fada domin samun madogara, tare da hanyar da aka bi aka tace bayanan da aka samo. An kuma yi bayani a kan ra'in binciken da aka za~a domin ]ora wannan nazari a kansa.

## 3.2 Dalilan Za~en Fada

A babi na ]aya, an yi bayani cewa, domin samun kaiwa ga manufar aikin har ya sami kar~uwa, ba a gudanar da binciken a dukkan Fadojin {asar Hausa ba, wadda ta raba }afa tsakanin arewacin Nijeriya da kudancin Jumhuriyar Nijar. Haka ya sa aka za~i wasu daga cikin tsofaffin daulolin {asar Hausa da ke Arewacin Nijeriya domin su wakilci sauran. Wa]anda suka ha]a da: Fadar Kabin Argungu dtaa Daura da ta Ha]eja da ta Kano da ta

Katsina da kuma Fadar Zazzau. To sai dai, da aka ziyarci Fadar Katsina, an iske yanzu babu zabiya, an kuma da]e a haka, babu kuma tarihi a rubuce na kirarin da zabiyoyin suka yi a zamaninsu, ba a kuma sami wanda ya haddace wani kirari a ka ba. A Fadar Kabin Argungu kuwa, an sami wani maro}i (Magajin [anmusa), da ya haddace kirarin da Zabiyar Fadar kan aiwatar kafin rasuwarta, duk da cewa biyu ne kawai aka samu. Wato kirarin Sarki Kanta da na Sarki Sama.Wa]annan kirari biyu, su ne ake yi wa Sarakunan Argungu a matsayin kirarin kakanninsu. Haka ya sa aka sauya Fadar Katsina da ta Kazaure, aka za~i fadar Kazaure saboda ita ce fada mafi kusa da ba a ta~o ba cikin wannan bincike.

A Fadar Kano ma an iske haka, wato babu zabiya, amma an sami faifan Sidi (CD) na wata zabiya da ta yi suna a fadar, wadda kuma ta yi zamani da Sarkin Kano Marigayi, Alhaji Ado Bayero, wato Hajiya Ajuji Maitazargade. An kuma sami tarihinta a Mack (2004), sannan kuma, an tattauna da wasu jami'ai a fadar, aka sami cikakken bayani a kanta da adabinta. A Fadar Zazzau kuma, babu zabiya a halin yanzu, sai dai akwai wasu mata biyu da suke gudanar da aikinta, duk kuwa da cewa ba a na]a su a matsayin zabiyoyi ba. Ta farko ita ce wata dogariya, Hajiya A'i da kuma Rabi Bazamfara. A Fadar Kabin Argungu, a ziyara ta farko an iske Zabiya a kwance, ba ta da lafiya. A ta biyu kuma aka iske ta rasu, haka ya sa aka sami wani daga takwarorinta (]an mu'abba, da ya haddace kirarin da take yi wa Sarkin Kabin Argungu, wanda nazarin ya yi amfani da shi. A ta}aice, za a iya cewa nazarin ya ta}aita ga wasu garuruwan {asar Hausa (da ke sashen Arewacin Nigeriya) da suka yi fice bayan jihadin Shehu Usman [anfodiyo, duk kuwa da cewa wasu da]a]]u sun yi fice kamar su, to amma saboda ba a sami abin da ake nema ba, dole aka bar su. Alalmisali, Gobir da Katsina.

### 3.3 Hanyoyin Tattara Bayanai

An za~i hanyoyi guda biyu }warara domin tara bayanan gudanar da wannan bincike. Akwai }wa}}warar hanya (Primary Source) da kuma sauran hanyoyi (Secondary Sources).

#### 3.3.1 {wa}}warar Hanya

A wannan hanya ta farko, an gana da wa]anda aka gabatar da nazarin a kansu, watau Zabiyoyin Fadoji shida da aka lissafo. Sannan kuma aka gana da wasu jami'an fada a masarautunsu da kuma wasu daga cikin saraki, wa]anda kirarin ya shafa. An tsara tambayoyin da aka yi wa Zabiyoyin Fada da sauran wa]anda aka gana da su, kamar yadda aka kawo samfurin tambayoyin a 3.6 (shafi na110-112). Binciken ya yi tattaki zuwa garuruwan da suka ha]a da Daura da Kabin Argungu da Kazaure da Katsina da Kano da Sakkwato da Gobir (Sabon Birni da Gobir Isa) da Kaduna da Mara]i da Niemey da kuma fadar Ha]eja da ta Zazzau.

#### 3.3.2 Sauran Hanyoyi

Hanya ta biyu ta ha]a da ziyartar ]akunan karatu na wannan sashe (Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya) da masu ala}a da shi, kamar na Sashen Nazarin Tarihi da na Nazarin Wasan Kwaikwayo da na Ingilishi da na Halayyar ]an Adam da kuma Cibiyar Nazarin Tarihin Arewa, (Northern History Research Centre) da ke wannan jami'a. Sai kuma sauran jami'o'i da aka ziyarci wasu sassansu masu al}ala da wannan bincike, kamar Jami'ar Jihar Kaduna da ta Bayero Kano da ta Usman [anfodiyo, da ke Sakkwato da kuma ta Jihar Katsina. A wa]annan jami'o'i, an ziyarci ]akunan karatu

mabambanta, kamar yadda aka bayyana a baya. Ba a tsaya a nan ba, an ziyarci Cibiyoyin Nazarin Harsunan Nijeriya na Jami'ar Bayero, Kano, da na Jami'ar [anfodiyo, Sakkwato, tare da ]akin tara takardun tarihi (achieves) da Gidan Tarihi na Arewa (Arewa House) da ke Kaduna. Sannan kuma an ziyarci Hukumomin Adana Tarihi da Raya Al'adu na jihohin Kaduna da Katsina da Kano da Sakkwato da kuma na Jigawa. Har ila yau, an shiga yanar gizo. An kuma tattauna da masana al'ada da adabi da kuma tarihi, musamman tarihin {asar Hausa.

### 3.4 Ra'in Bincike

An ]ora wannan bincike kan mizanin ra'in tarihin al'umma (ethnographic theory). Ra'in tarihin al'umma, ra'i ne da yake amfani da tarihiko al'adu ko adabin al'umma ko kuma shiga cikin al'umma a zauna da su domin nazartar al'adunsu, wanda a }alla kada ya gaza zama cikinsu na shekara ]aya. Wannan ra'i ne da wani shehun malami (farfesa), a fannin tarihi da yanayin }asa, watau Muller, G.F, ya }ir}iro a tsakanin shekara ta 1733 -43. Kodayake ba a fara amfani da wannan ra'in a fannin ilimi ba, sai daga baya da Farfesa Ludwig A, na jami'ar Gottingen da ke }asar Jamus, ya yi amfani da shi, a }o}arinsa na sabunta tsara tarihin duniya. Labor(1975), na ]aya daga wa]anda suka yi amfani da wannan ra'i a shekara ta 1975, (Crystal, 2009: 174). Labor a nasa binciken, ya nazarci dalilan da suka sa lafazi Turanci da ]abi'un ba}a}en Amurkawa suka bambanta da na fararen Amurkawa, duk kuwa da cewa an haife su a Amurka kuma a nan suka tashi, suka yi rayuwarsu baki ]ayanta.

Ra'in tarihin al'umma wani ~angare ne daga cikin ra'o'in al'ada, wanda yake nazartar duk wata }abila dangane da al'adunta. Wannan fanni yana da dangantaka da ilimin

zamantakewar  rayuwar ]an Adam  da kuma na ilimin walwalar harshe. Har ila yau, ra'in yana nazartar al'umma / }abila ko samo bayanai ta hanya uku }warara. (i) ta hanyar ganawa ko kuma hira da wa]anda ake bincike a kan su, da (ii) shiga cikin al'ummar dumu-dumu domin saninsu sosai da abubuwan da suke aiwatarwa, da kuma (iii) sa ido ga abin da ake nazarinsa, watau  gani da ido. Saboda haka, wannan bincike ya bi wa]annan hanyoyi, domin cim ma }udurinsa.  Bin wa]annan hanyoyi kan sa bincike (nazari), ya zama mai alfanu, saboda:

- ana amfani da jama'ar da ake nazarta, domin yin haka kan taimaka a cim ma }udurin da aka ]auka. Wannan tsari, yana bayar da dama a sami abin da ake bu}ata, kai tsaye. Babu shakka, shiga cikin al'umma yana  sa su saki jiki da mai nazari.

- masu iya magana sun ce, "Gani ya kori ji", Saboda haka, sa ido ko ziyartar al'ummar a ga abin da ake nazarinsa, ido da ido,  yana bayar da cikakken sakamako, domin. "Zuwa da kai ya fi sa}o". Saboda haka, binciken ya yi tattaki ya ziyarci  dukkan fadojin da aka nazarci kirarin Zabiyoyinsu.

- haka kuma, "Tambaya mabu]in ilimi" kuma, " Matambayi ba ya ~ata". Wannan hanya ma ta gana wa da al'ummar da ake nazarinsu, a kuma yi masu tambayoyi tana kaucewa shakku ko hasashen binciken. Wannan ya sa aka gana da dukkan Zabiyoyin da aka yi nazarin kirarin da suka yi wa saraki, a fadojin da suke, in ban da Zabiya Ajuji Maitazargade, wadda ta rasu tun 1992.

## 3.5 Hanyoyin Tace Bayanai

Daga bayanan da aka samo, ayyukan da suka ji~anci bita, an yi bitarsu a babi na biyu. An yi bitar ayyukan masana da manazarta dangane da tsarin }anana batutuwan da suka ha]a da '{asar Hausa, Hausa da Hausawa' da 'Saraki a {asar Hausa' da 'Mata a {asar Hausa' da 'Al'ada' da 'Adabi', wanda a }ar}ashinsa aka waiwaye kirari da wasu nau'o'in adabin baka masu ala}a da kirari, watau take da wa}a. An kuma gabatar da bita a kan 'Zabiyanci' da 'Jigo' da 'Salo' da kuma 'Zubi', musamman a adabin baka. Ko shakka babu, wa]annan sun zamo jagora ga wannan aiki. Kirarin da Zabiyoyin Fada ke yi wa saraki kuwa, an yi taciyarsu a babi na hu]u da na biyar. Da farko, kirarin da aka ]auko muryarsa a kaset da faifan CD, an juya shi zuwa rubutu, sannan aka yi taciyarsa. A taciyar an nazarci jigon kirarin, da salonsa (ta fannin salo gaba ]aya da adon harshe) da kuma irin tsarinsa, da zubinsa. Ra'in binciken da aka za~a domin gudanar da wannan aiki wanda shi ne, 'Ra'in Tarihin Al'umma', ya yi tasiri matu}a, domin an yi amfani da adabin al'umma, aka fito da tunaninta dangane da saraki da sarauta a {asar Hausa. Kamar yadda Labor (1975), a ruwaitowar Crystal (2009), ya nazarci adabin Amurkawa ba}a}en fata, ya gano dalilin da ya sa suka bambanta da 'yanuwansu Amurkawa farare, dangane da ]abi'unsu, wanda ke nuni da tasirin bambancin al'adu a tsakanin farare da ba}a}en Amurkawa. Wannan taciya ta tabbatar da hasashen da aikin ya yi a babi na ]aya. Babu ko shakka, babi na hu]u da na biyar su suka }unshi ma}asudin wannan bincike.

### 3.6 Tarihin Zabiyoyin da aka Nazarta

Daga bayanan da aka samo na tambayoyin da aka yi wa zabiyoyin, da sauran al'umomin da aka yi hira da su, an sami ta}aitaccen tarihin zabiyoyin da aka nazarci kirarin da suke yi wa saraki, daga bakinsu a fadoji shida na {asar Hausa. An samo tarihin daga tambayoyin da aka yi. Kodayake, Zabiya Ajuji Maitazargade Zabiyar Kano, an kuma sami }arin bayani daga Mack (2004), Zabiyar Kabbin Argungu an sami }arin bayani a kanta daga Wakilan Kanta, Alhaji Yakubu Bagayi.

#### 3.6.1 Zabiyar Daura, Hajia Zulai (Dakamar Sarkin Daura)

An haifi zabiyar Daura, shekaru tamanin da wani abu da suka wuce a garin Daura. Ta gaji zabiyanci, kaka da kakanni, domin tarihi ya nuna, tun fil azal zuri'arsu ke zabiyanci a fadar. Ta gaji, mahaifiyarta Dakama Fatsuma, wadda ta yi zamani da Sarkin Daura Abdulrahman, wadda ta rasu farkon zamanin Sarki Muhammadu Bashar, sai yarta, Zulai Babba ta gaji mahaifiyarsu, wadda rasuwarta kuma Dakama ta yanzu ta gaje ta. Zabiya Zulai ta fara zabiyanci da Sarki Bashar ya zuwa yanzu (da Sarki Umar Faruk Umar). Ta kai a }alla shekara arba'in da zama zabiyar Sarki, amma kafin nan, tun tana yarinya ta bu]e ido, ana zuwa da ita fada zabiyanci. Tarihi ya nuna cewa ga al'ada cikin zuri'arsu, 'ya'yansu mata dukka suna iya gadonsu amma ban da `ya`ya maza, sai dai `ya`yan mazan su yi. Yanzu haka Dakama tana tare da `ya`yan yayyanta maza har su biyar da suke zabiyancin take. Akwai Laure, `yar shekara sittin (wadda tun tana yarinya ake yi da ita), akwai kuma Amina `yar shekara 55 wadda yanzu shekararta 20 tana zabiyanci. Saura sun ha]a da Nafisa (`yar shekara 35, ita kuma yanzu shekararta 12), sai Hasiya (`yar shekara 40, ita ma shekarunta 10 tana zabiyanci) da kuma Bera'a (`yar shekara 35, wadda ita kuma shekararta biyar ke nan).

Ana sa ran Laure za ta gaji Zabiya Zulai, domin cikin `ya`yanta da jikoki, babu wadda ta nuna sha'awar ta gaje ta, dukkansu suna gidajen aurensu/mazajensu. Ana za~en Dakama ta la'akari da babba daga cikin zabiyoyin (wato wadda ta jima tana yi cikinsu, domin ita ake zaton ta san ciki da wajen al'adar). Idan aka za~i Dakamar Sarkin Daura, na]i ake yi sosai a fada. Jakadu, ke sa mata doguwar riga da babban mayafi, sannan su ]aura mata saro (wani babban kallabi na gado). Daga nan sai Sarki ya yi jawabi, sauran `yanuwa da mata da abokanan arziki su raka ta gida, ana ka]e-ka]e. Za a yi kwana bakwai ana shagali, a gidanta.

Baya ga fito da Sarki fada da mayar da shi gida, bayan an tashi zaman majalisa, Dakama tana wasu al'adu a fadar Daura. Da farko tana ka]awa Sarki da Magajiya take da wani tambari na gado, wato 'Dajinjin'. Tana kuma ka]a shi a duk lokacin da aka sami }aruwa a fada, wato idan matar Sarki ta haihu. A kullum safiya, ita ke kai matan sarki ]aya, bayan ]aya domin su gaishe shi (suna tafe tana yi masu kirari). Daga nan kuma sai ta raka Sarki Shira'i (wani soro da `yanuwa da sauran wa]anda ke zama a cikin gida, za su je su gaishe shi kafin ya fita majalisa). Bayan nan, sai ta kai shi fada, da zarar an tashi kuma ta dawo da shi gida. Idan tafiya ta kama Sarki, tafiyar da ba da ita za a je ba, za ta raka shi ya shiga mota, da dawowarsa kuma, ita za ta tar~e shi.

A da can lokutan salla }arama da babba da sallar gani, Dakama da tawagarta suna sa fararen kaya. Yanzu kuwa suna sa kowane kaya da aka ]inka masu, amma a mafi lokuta, sukan sa riga ta atamfa da zani da ]ankwali da farin gyale. Suna kuma bin Sarki a }asa har masallacin idi, da lokacin hawan daushe da na Magajiya. Da hasafi ake yi masu, amma wannan Sarki yana ba su albashi duk wata. Har ila yau, a lokacin da aka za~i sabon sarki, Dakama tana ka]a masa Dajinjir sau bakwai (7). A ranar da aka yi na]i aka gama, za ta kai shi gidan Shamaki ya yi kwana bakwai a can. Ranar da ya cika kwanakin kuma, ita za ta kai shi har

]akinsa da zarar an gama sallar asuba, tare da Magajiya da sauran `yan'uwa mata. A lokacin da yake gidan Shamaki, tana ka]a masa Dajinjir sau uku kowace rana (da safe, da la'asar, da kuma da dare). Baya ga yi wa Sarki kirari, tana yi wa matansa da `ya`yansa da sauran saraki kirari. Ba ta yi karatun boko ba, amma ta yi na Muhammadiya. A Daura ne ka]ai zabiyar Sarki take da tawaga daga cikin zabiyoyin da aka yi nazarinsu, saura kuwa mace ]aya ce (kodayake a Fadar Kazaure akwai zabiyoyi biyu, kowacce tana zaman kanta) 'Yan amshin suna yi wa Dakama amshi a farkon kirarin da take yi wa Sarki, saura kuma tare suke rerawa.

### 3.6.2 Zabiyar Ha]eja, Malama Hajara Alhassan

An haifi Hajara a garin Ha]eja, amma ba za ta iya tuna shekarunta ba, a ce ta kai shekaru sittin da wani abu. Zabiyar Ha]eja ta gaji ro}o uwa da uba. Mahaifinta Malam Alhassan, kafin rasuwarsa shi ne Sarkin Kugen Fadar Ha]eja, mahaifiyarta kuma, Hajiya Aishatu Ibrahim ita ce Zabiyar Ha]eja hafin rasuwarta. Duk da cewa ta gaji ro}o, ta bayyana cewa ba ta ta~a mafarkin za ta shige shi ba, kasancewar mijinta malami, to amma rasuwarsa da ta mahaifiyarta suka sa zabiyanci ya zamar mata larura. Ta bayyana cewa bayan rasuwar mahaifiyarta, an sami tsawon lokaci babu zabiya a Fadar Ha]eja, an nemi wadda za ta yi, amma ba a samu ba. Bayan da Sarki ya yi shawara da magabata, sai ya aika ta zo. Bai shawarce ta ba, ya ce ya na]a ta zabiyarsa. Alkunya da girmamawa tsakanin talaka da saraki, ya sa ta kasa cewa }ala, amma bayan da ta koma gida ta yi kuka ma'ishinta. Abubuwa biyu suka sa ta kuka, kasancewarta matar malam da kuma tunawa da cewa, ko mijinta ba ya raye, da babban ]anta yana raye, ba zai yarda ta yi zabiyanci ba. Shekararta goma sha ]aya (11) tana zabiyanci. Ta haifi `ya`ya bakwai (7) amma ]aya ka]ai take raye. Ba ta yi ilimin boko

ba, sai dai na Muhammadiya. Ba ta da wata al'ada da take aiwatarwa a fada, ban da yi wa saraki kirari. Tana yi wa Sarki da matansa da mahaifiyarsa (Mai Babban [aki) da matan babansa biyu, da manyan hakimai da wasu daga cikin `yan majalisar Sarki, musamman masu dangantaka ta jini da shi kirari. Ta bayyana cewa, zabiyancin yana rufa mata asiri saboda nan take ci, ta sha, har ta yi wa ]iyarta da ke gidan aure. Zabiyar Ha]eja tana da kaya na musamman da Sarki ya ba ta, wa]anda taka sa a ranaku na musamman, misali, ranar salla, tana sa jamfa da wando da rawani. Ba ta hawa doki, sai dai ta bi tawagar Sarki a }asa lokacin hawan salla. Aikinta na yau da kullum shi ne ta rako Sarki fada daga cikin gida, tana yi masa kirari. Bayan an tashi fada kuma, ta raka shi gida. Tana zuwa fada da safe, ta koma gida da misalin }arfe hu]u zuwa biyar a kullum. Ana biyanta albashi, baya ga hasafi idan hali ya yi.

### 3.6.3 Zabiyar Kano, Hajiya Ajuji Maitazargade

An haifi Hajiya Ajuji a garin Ningi na jihar Bauchi. Ta gaji ro}o daga mahaifinta. Ta baro Ningi tun tana }uruciyarta ta zo Kano (ba a fa]i dalilin da ya kawo ta Kano ba). Ta ta~a yin aure amma ta da]e ba ta da aure kafin ta rasu a shekara ta 1992. A hirar da ta yi da Mack (2002:54), Maitazargade ta bayyana cewa, zuwanta Kano, adon }ofofin shiga fada suka ba ta sha'awar ta fara ro}o a fadar, daga baya kuma har ta zama Zabiyar Sarki. A zamaninta, ta yi wa Sarkin Kano, Ado Bayero kirari tare da mahaifiyarsa (Mai Babban [aki) da matan Sarki da `ya`yansa. Kamar sauran zabiyoyin fada, ita ma a zamaninta, ita ke fito da Sarki fada, ta kuma mayar da shi gida bayan an kammala zaman majalisa. Haka kuma, al'adar Sarkin Kano ce ya gana da manyan ba}i maza da dare, da misalin }arfe goma zuwa sha biyu (10pm – 12am) , saboda haka ita ke raka shi da kirarinta, ta kuma dawo da shi gida. A

lokutan salla, tana bin sa Sarki a kan doki. Takan kuma sa babbar riga ta yi ]amara, bayan ta ]aura rawani. Ba kamar sauran zabiyoyin fada ba, Maitazargade an ba ta `yancin yi wa wasu da ba saraki ba kirari da wa}a (An sami tarihinta daga Mack (2002:54-56) tare da }arin bayani daga al'ummomin da aka gana da su a Fadar Kano).

### 3.6.4 Zabiyar Kazaure, Hajiya Indo 'Yarsukola.

Sunanta na yanka Indo Yahaya , amma ana mata la}abi da 'Yarsukola. Ba ta san shekarunta na haihuwa ba, amma ta haura kimanin shekara sittin zuwa saba'in da haihuwa. An haife ta a garin Kazaure, a Bakin Kasuwa. Da ta isa yaye, an yaye ta a Lokon Maro}a, domin haka a nan ta koyi ro}o, saboda ba ta gaje shi ba. Ta ta~a kamuwa da ciwon hauka, har ta kwanta a Asibitin Mahaukata na Gwauron Dutse da ke Kano. Wannan rashin lafiya ta sa ta yi aure – aure da dama saboda larura. Ta yi sana'ar abinci, a inda ta sayar da koko da, ta yi taliya da nakiya, duk a garin Kazaure, har ta biya wa kanta ku]in Hajji. Bayan dawowarta, ta ci gaba da sana'arta na yin nakiya, kafin ta shiga ro}o. Daga baya da ta shahara da ro}o, Zabiya 'Yar Daudu ta kai ta fada, ta ci sa'a Sarkin Ha]eja na wancan lokaci, Ibrahim, ya amshe ta, ta zama ]aya daga cikin zabiyoyinsa. Bayan rasuwarsa kuma, ta ci gaba da zabiyanci da Sarki Hussaini, har yanzu kuma tana yi da Sarki Najib Hussaini (jikan Sarki Ibrahim). Ba ta yi ilimin boko ba, amma ta yi na allo daidai gwargwado. Zabiya Indo 'Yarsukola ba ta haihu ba.

### 3.6.5 Hajiya A’i (Dogariyar Zazzau)

Shekarun Hajiya A’i sittin da shida a duniya (66). An haife ta a Za~i, wani }auye da ke hanyar Kano, dab da Dogarawa, Mahifinta shi ne Santalin Iya Aminu, kafin ya zama Sarki, amma da aka na]a Iya Aminu Sarki, sai ya na]a mahaifinta ‘Shugaban Tsofaffin Gida’, sarautar da ya ri}e har ya rasu. Tun da aka na]a Sarki Aminu, iyayenta suka dawo fada da zama. Mahaifiyarta ta yi jakadanci a fadar Zazzau zamanin Sarki Aminu. Bayan mijinta na fari ya rasu, ta auri Madakin Kakakin Zazzau, Malam Jafaru, wanda shi ne mijinta har yau. Tana da `ya`ya da jikoki, har ma da tatta~a kunne ashirin da tara (29). An da]e a Fadar Zazzau babu Zabiya, tun wadda ta rasu lokacin Sarki Aminu, Hajiya Ai ta fara da yi wa Sarki gu]a, daga baya kuma ta ci gaba da kirari. Tana aikinta na dogariya da kuma Zabiyancin da ta ]ora wa kanta. Tana sa doguwar riga irin ta dogarai da hula, tana kuma ri}e bulala, kamar yadda dogarai maza suke yi. Ba a biyanta albashi, sai dai ana mata hasafi idan hakan ta taso. Hajiya A’i ba ta yi ilimin boko ba, amma ta yi na Muhammadiyya (Makarantar allo). ‘Ya`yanta ba su da sha’awar su gaje ta. Baya ga Hajiya A’i akwai Rabi Bazamfara da ke zabiyanci a fadar Zazzau.

### 3.6.6 Rabi Bazamfara

Kamar A’i dogariyar Zazzau, ita ma Rabi Bazamfara ba na]a ta aka yi zabiyar Zazzau ba, ara ta yi ba kuma gada ta yi ba. `Yar shekara sittin da takwas (68), Rabi Bazamfara haifaffiyar Ri~e ce, wani gari da ke Masarautar Kwatarkwashi, da ke Jihar Zamfara. Ta yi aure har sau hu]u, amma a yanzu ba ta da aure. Tana da `ya`ya biyar (5), da jikoki ashirin da uku (23). Bayan mijinta na }arshe ya rasu, ta baro garinsu ta zo Zazzau tana sana’ar bayar da magani, watau ‘yar mai ganye. Kodayake tana fada yanzu, amma tana ba da

magani idan an zo nema. Shekararta ashirin da shida (26), a Zazzau, shekarunta ashirin da uku a fada (23). Marigayi Madakin Zazzau, Kabiru, ]an Sarki Shehu Idris, ya kawo ta fada, wanda shi ne ubangidanta a da. A da, tana zuwa fada ne amsar abincin masu bindiga, daga baya ta zama `yar gida. Bayan rasuwar ubangidan nata, ta so ta bar fada, amma Sarki ya hana ta, aka ba ta muhalli. Kullum da safe take shigowa fada, bayan la'asar ko magariba ta koma mazauninta. Tana yi wa Sarki da matansa da `ya`yansa kirari, tana raka Sarki majalisa ta kuma raka shi ya koma gida. Ba ta da albashi, sai dai hasafi. Cikin `ya`yanta babu wadda ta nuna sha'awar ta gaje ta, duk suna gidajensu na aure. Ba ta aiwatar da wata al'ada a fada, ban da zabiyanci. Ba ta kuma sa wani kaya na musamman. Ba a yawan salla da ita saboda tsufa da larurar ciwon }afa. Ba ta yi ilimin boko ba amma tana da ilimin Muhammadiyya.

### 3.6.7 Zabiyar Kabin Argungu (magu]iya) Fati Manukwai

An haifi Zabiyar Kabin Argungu, Malama Fati Manukwai a garin Argungu. Shekarunta tamanin da biyar (85), a lokacin da aka gana da ita, kodayake ta rasu ana cikin gudanar aikin. Fati Manukwai Bazabarma ce ta Kabin Argungu, ta kuma ta~a yin aure, amma auren ya mutu, sai dai ba ta sami haihuwa ba. Ta shekara goma sha bakwai tana zabiyanci a Fadar Kabin Argungu, wato farkon zamanin Sarki da ke kan gadon sarauta yanzu, Alhaji Sama'ila Muhammadu Mera, CON. Ba ta gaji zabiyanci ba, daga uwa ko uba. Ana kiran ta 'magu]iya', saboda baya ga kirari da take yi wa sarakin Kabin Argungu, tana yi wa Sarki gu]a (amma shi ka]ai). Wato magu]iyar Sarki ce (a wasu fadojin a kan sami zabiya daban, magu]iya daban). Aikinta a kullum shi ne tarbar Sarki daga soro (soron gida), ta raka shi fada, tana kirari, tana kuma yi masa gu]a, har sai bayan da fadawa da sauran `yan majalisa suka yi gaisuwa, sannan ta tafi. Bayan an kammala zaman majalisa kuma, takan raka Sarki

zuwa soron da ta tarbe shi, ta bar shi hannun jakadiyya. Takan kuma raka shi ya shiga mota, a duk lokacin da zai yi tafiya , sannan kuma ta tarbe shi idan ya dawo. A lokutan hawan salla, ana hawan salla da ita. Takan sa kayan }awa, wato babbar riga, irin wadda ake ]inkawa bayin Sarki (masu }yalli-}yalli, irin na kayan adon dawaki ), a lokuta na musamman, misali bikin salla. Ana biyanta albashi duk wata, ana kuma yi mata kyauta / hasabi a lokuta da dama. Ta yi wa Sarki da matansa da `ya`yansa da sauran sarakin Kabin Argungu kirari, sai dai saboda rashin lafiya, na Sarki ka]ai aikin ya samu, shi ma ]in, daga Magajin [anmusa (]aya daga cikin maro}an Fadar Kabin Argungu, mai yi wa saraki kirari). Ba ta yi karatun boko ba, amma ta yin na Muhammadiya, wato makarantar allo. An kuma sami tarihinta ne da sauran }arin bayani daga Wakilan Kanta, Alhaji Yakubu Bagaye, domin lokacin da aka je, ba ta iya magana sosai saboda ciwo, bayan ]an lokaci ka]an da aka koma, aka iske ta rasu.

### 3.6.8 Zabiya {arangiya (Zabiyar Kazaure ta biyu).

Sunan Zabiya {arangiya na asali Hauwa Usman Mai Salati, amma ta yi wa kanta la}abi da' {arangiya', saboda lamarin rayuwar yau da gobe. Kamar yadda ta yi }arin bayani cewa, "Dole a tashi". Ma'ana, dole a tashi a nemi na kai. An haifi Zabiya {arangiya a garin Wailare kimanin shekara hamsin da takwas (58) da suka wuce. Ba ta yi karatun boko ba, amma ta yi na Muhammadiyya daidai gwargwado. Mijinta ya rasu shekara goma sha ]aya (11), ke nan. Allah Ya albarkace su da 'ya'ya goma sha biyu (12), amma tara (9), daga ciki sun rasu. Ukun da suka rage mata ne, kuma sun sami damar yin ilimin boko, sai dai dukkansu sun yi aure suna gidajen mazajensu, ba su da sha'awar su gaje ta. Zabiya {arangiya ta shekara takwas (8) tana Zabiyanci a Fadar Kazaure, ta kuma gaji }anin

mahaifinta wanda maro}i ne da ya yi yawo gari-gari yana ro}o, to, amma ba ta~a bin sa ba. Hasali ma, bayan rasuwarsa ne ta shiga ro}o. Zabiya {arangiya mace ce mai murya da baiwar iya sarrafa harshe, wannan ya sa ta samu }ar~uwa. Baya ga Zabiyanci, tana sana'ar tuwo , kimanin shekara ashirin da biyar (25) da suka gabata.

## 3.7 Tambayoyin da Aka Yi wa Zabiyoyin Fadojin da aka Gana da su da na Sauran Jama'ar Fada.

An shirya tambayoyi da aka yi wa Zabiyoyin Fada da ma sauran al'ummomin fada da aka gana da su domin cim ma burin wannan nazari.

### 3.7.1. Tambayoyin da aka yi wa Zabiyoyin Fadojin da aka Nazarta.

An yi wa zabiyoyin tambayoyi guda talatin da biyar (35) kamar haka:

1. yaya sunan Zabiyar?
2. shekarunta nawa (na haihuwa)?
3. mene ne ta}aitaccen tarihinta?
4. addininta fa?
5. mene ne matsayin iliminta?
    (a) na Islama kawai.
    (b) na boko kawai
    (c) na boko da Islama
    (d) babu ko ]aya daga ciki
6. idan ta yi ilimin boko, a wane matakin ilimi aka tsaya?

(a) firamare

(b) sakandare

(c) gaba da sakandare

(d) digiri na farko

7. ko tana da aure?

8. idan tana da shi yaya dangantakarta da mijinta kan zabiyancin da take yi?

9. ko ta gaji zabiyancin?

10. daga uwa ko uba?

11. tana da `ya`ya?

12. guda nawa?

13. ko `ya`yan suna da sha'awar gadonta?

14. ko tana da sana'a ban da zabiyanci?

15. su wa take yi wa kirari a fada?

16. ko tana amfani da wasu kayan ki]i?

17. ko tana da wata al'ada da take aiwatarwa ban da kirari?

18. yaya take tsara kirarin da take yi wa saraki?

19. ko ta ta~a zuwa wata fadar?

20. ko wani abu ya ba ta sha'awa a wata fadar dangane da zabiyanci?

21. ko zabiyoyin suna koyon kirari daga takwarorinsu maza?

22. zabiyar ita ka]ai ce, ko kuwa tana da `yan amshi?

23. wace dangantaka ke tsakaninta da Sarki?

24. ko ana biyanta albashi, ko kuwa hasafi ake yi mata?

25. ko akwai wasu tufafi da take sawa a wasu lokuta na musamman?

26. shekerun zabiyar nawa tana zabiyanci?

27. yaya take ganin zabiyanci a da, da kuma yanzu?

28. kirarin yana samun sauyi?

29. kirarin da take yi gadonsa ake yi, ko kuwa kowace zabiya tana tsara nata?

30. kirarin a rubuce yake?

31. yaya dangantakarta da sauran masu kwarzanta Sarki a fada, kamar su:

    (a) wawan Sarki

    (b) Sarkin busa

    (c) Magajin banga

    (d) Sarkin kuge

    (e) Sarki tambura

    (f) sauran `yan ma'abba.

32. Yaya dangantakarta da sauran matan fada, kamar su?

    (a) jakadiyya

    (b) barori

    (c) sa]aku

    (d) dogarai mata

33. yaya suke ganin zabiyancin nata?

34. yaya sauran al'umma suke ganin zabiyanci?

    (a) saraki….

    (b) attajirai…..

    (c) talakawa….

    (d) matan gari

35. ko tana da wani }arin bayani da za ta yi?.....

An gana da Zabiyoyin goma sha ]aya. Kodayake Kazaure na da Zabiyoyi biyu kowace na zaman kanta. a Zazzau ma mata biyu ne suka maye gurbin Zabiyar Zazzau. A Daura kuwa a }ungiyace suke, su biyar ne da shugabarsu (Dakamar Sarkin Daura). Ayayin da ba a sami Zabiyar Fada a Kano ba, amma an sami tarihinta a bakin mutane tare da aikin Mack (2004), da kuma faifan CD na kirarin da ta yi a zamaninta.

### 3.7.2 Tambayoyin da aka yi wa Sauran Jama'ar da ke Fada.

Su ma jami'an fada, an yi musu tambayoyi goma sha biyar (15) ne, kamar haka:

(1) mene ne aikin jami'in a fada?

(2) shekarunsa nawa (na haihuwa)?

(3) shekarunsa nawa a fada?

(4) yana da wata sana'a?

(5) mene ne matsayin iliminsa?

(6) ko akwai zabiya a fadar da yake?

(7) zabiyar mace ce ko namiji?

(8) yaya ake za~en zabiya a fadar da yake?

(9) ana na]i ne?

(10) yaushe aka fara zabiyanci a fadar da yake?

(11) wa]anne abubuwa kirarin da zabiyar fada take aiwatarwa yake nunawa a zahiri?

(a) tarihi?

(b) yabo da zuga?

(c) nisha]antarwa?

(12) mene ne dangantakarsa da kirarin zabiya?.

(13) adabin zabiya yana raye?

(14) yaya za a farfa]o da shi?

(15) ta yaya za a kwatanta zabiya da takwarorinta maza masu ala}a da kirari a fada.

### 3.8 Kammalawa

Babi na uku ya kawo bayani kan hanyoyin da aka bi aka gudanar da wannan bincike. An bayyana hanyar da aka bi aka za~i fadojin da aka gudanar da binciken a kansu, da hanyoyin tara bayanai, musamman kirarin da aka yi taciyarsa a babi na hu]u da na biyar. An kuma kawo ra'in binciken da aka za~a, wato ra'in tarihin al'umma aka bayyana yadda aka bi, aka tara bayanai, kamar yadda yake a ra'in. Sannan aka kawo nau'o'in tambayoyin da aka yi wa Zabiyoyin Fada da wasu daga cikin jami'an fada da sarakin da aka gana da su. A }arshe, an kawo tarihin zabiyoyin da aka nazarta, an kuwa sami wannan ne daga tambayoyin da aka yi masu, tare da }arin bayanan da aka samu daga wasu al'ummomin fada da aka gana da su.

# BABI NA HU[U

# TARKEN ZABIYANCI A FADAR {ASAR HAUSA

## 4.1 Gabatarwa

A babi na uku an yi bayani a kan hanyoyin da aka bi domin gudanar da wannan bincike, wato, hanyar da aka bi aka za~i fadojin da aka nazarta, da hanyoyin tattara bayanai, da kuma yadda aka tace bayanai a wannan babi da na gabansa. An kuma kawo ra'in binciken da aka za~a domin ]ora nazarin, wato ra'in tarihin al'umma (etnnographic theory), sannan kuma aka kawo ta}aitaccen tarihin Zabiyoyin da aka nazarci kirarinsu. Saboda haka a wannan babi na hu]u aka fara taciyar bayyanan da aka tattaro, ma'ana kirarin Zabiyoyin Fada shida na {asar Hausa da suke yi wa saraki, wato Fadar Kabin Argungu da Daura da Ha]eja da Kano da Kazaure da kuma Fadar Zazzau. Babi na hu]u da na biyar su suka

}unshi gundarin wannan aiki, domin an nazarci jigonsa filla-filla. An kasa babin zuwa manyan rassa biyu. A sashe na farko an nazarci jigon kirarin, a sashe na biyu aka nazarci tasirin addinin Musulunci da na wayewar kai a sanadiyyar ilimin da suka samu daga jigon kirarin da kuma aiwatar da shi.

### 4.2 Jigo a Zabiyancin Fada

'Jigo' ko 'turke' kamar yadda masana suka bayyana, bakinsu bai sa~a ba. Jigo kalma ce da take nufin 'manufa' ko 'sa}o' ko 'ma}asudi' na adabi. Jigo shi ne }ashin bayan adabi kowane iri, rubutacce ne ko na baka. Ana amfani da harshe a gina 'jigo', saboda haka irin salon marubuci ko dabararsa ko azanci da }a}ale-}a}ale, duk manufarsu ya isar da sa}onsa ko manufarsa ga masu sauraronsa ko makaranta.

#### 4.2.1 Yabo

Kamar sauran maro}an fada, wa]anda a kodayaushe jigonsu ba ya wuce 'yabo', to haka ma kirarin Zabiyar Fada, galibi jigonsa na yabo ne, kasancewarta ]aya daga cikin maro}an fada. A ta}aice, a iya cewa yabo furuci ne ko maganganune na godiya, ta hanyar fito da wani mutum ko wani abu domin sauran jama'a su ga }imarsa da darajarsa.Yabon, tamkar a ce a fakaice ana tallar wanda ake yabo ne, wanda kuma masana suka amince shi ne fitaccen turken wa}o}in Hausa, musamman wa}o}in fada, domin mafi yawancinsu manufarsu kan kasance yabon wanda aka yi wa}a dominsa.

Galibi maro}an fada suna ]ora yabo a kan shikashikai biyar, wa]anda suka ha]a da addini da asali (gami da ambaton zuri'a) da jaruntaka (wajen ya}i) da iya mulki (iya ri}on jama'a) da kuma kyauta. Kodayake wasu masana sun }ara da 'zuga' cikin shikashikan cim ma yabo, da ya sa suka zama shida. A yayin da wasu kuma suka }ara da habaici da zambo. Wa]annan shikashikai suke nuna dangantakar maka]i da ubangidansa, su ne kuma mizanin da Bahaushe yake auna saraki , wato sinadaran da ke nuna }imar da Bahaushe ya ]auki saraki. Ke nan, a tunanin Bahaushe, dole basarake ya kasance mai asali, mai kyauta, jarumi, mai ri}o da addini, sannan kuma mai iya ri}on jama'arsa. Wa}ar *'ya ]au girma ya san yabo'* ta Ibrahim Naramba]a wa}a ce wadda jigonta shi ne yabo. Wa}o}in al}alai ma suna shiga cikin wa}o}in fada, saboda kusantar al}ali da Sarki. Al}ali a fada shi ke taimakawa Sarki da shawara a yanke hukunci, shi kuma Sarki ya ba da doka a zartar. Naramba]a a wa}ar ya yabi Al}ali Moriki Bubakar saboda yadda yake aiwatar da aikinsa na al}alanci cikin gaskiya ba tare da son rai ko son abin duniya ba. Ya kuma yaba shahararsa ta kasancewarsa mai ilimi da amfani da shi da jajircewarsa ga gaskiya komai ]acinta da bijirewa ga }arya kamar yadda yake cewa:

| | |
|---|---|
| Jagora: | Ai tsaya matsayarka Abubakar, |
| | A ]auki batun mai gaskiya. |
| Yara: | Mai }arya komi yah hwa]i, |
| | Kohin a jima ta walwale. |
| | (Maka]a Naramba]a wa}ar *Ya ]au girma ya san yabo, mu zo mu ga Al}ali Abu).* |

Amfani da yabo a matsayin jigo musamman a wa}o}in fada shi ke }ara wa saraki farinjini a idanun talakawansa da sauran jama'a. Babu shakka, kirarin da Zabiyoyin Fada ke yi wa saraki a {asar Hausa ya }unshi wa]annan shikashikai na yabon saraki, kuma a iya cewa,

wa]annan shikashikai mizani ne na yadda talaka yake auna basarake. Muhimmi daga ciki kuwa shi ne jaddada nasaba ta iyaye da kakanni a gadon sarauta. Wannan na ]aya daga cikin abubuwan da ke }ara wa saraki }arfin gwiwa da faranta masa rai da sa shi tun}aho.

### 4.2.1.1 Tarihin Asali

Wannan kalma ta 'asali 'tana da ma'anar 'mafari' ko 'tushe' ko 'salsala'. Asali kamar yadda ma'anarsa ta nuna, asalin mutum shi ne tushensu ko salsalarsa. Asali idan na gari ne abin tun}aho ne matu}a, musamman ma a ce na sarauta ne ga saraki. Haka ya sa ga duk wanda ya san yana da asali na fa]i yake alfahari da shi, yake kuma jin da]i a fa]i a gaban kowa ba tare da tababa ba. Wannan ya sa maro}an fada a kullum suke }ara jaddada tarihin asalin saraki na sarautar gidansu, ba ga shi kansa kawai ba har ma da sauran jama'a, musamman abokanan hamayya domin a razana su. Alalmisali, basaraken ]an wane ne jikan wane. Ana kuwa danganta shi da magabatansa ne wa]anda duniya ta san su domin a nuna salsalarsa ga sarauta ta hanyar gado wanda ke tabbatar da cewa sarauta ba hayenta ya yi ba. Masu iya magana dai sun ce, "Sanin asali ya sa kare cin alli". Galibi a sha'anin sarauta ba a son mai gajeran asali, wato wanda yake a sarautar haye ya yi ba gadonta ya yi ba. Saboda haka, maka]an fada a kodayaushe }o}arinsu shi ne su nuna cewa shi basarake, sarauta da ma abin sa ce, ']an na gada ne' wanda ya fi ']an na koya'. To, haka kuma, sun fi jin da]in yi wa basaraken da ya gaji iyaye daga kakanninsa wa}a domin sun fi samun abin da za su fa]a game da nasabarsa.

Wurin wannan nuni na asali ga saraki, Zabiyar Fada ba a bar ta a baya ba, domin takan jero ko ambato salsalar saraki daga kaka da kakanni a kirarinta, tana nuna bajintarsu ta iya mulki

da jaruntaka da kuma dangantakar basarake da su. Tana kuma ambato su ta yi ta'aziyyar rashinsu. A fagen nuna salsala ko asalin basarake, Zabiyar Kabin Argungu ba ta yi wa kowane Sarki da ke gadon sarauta kirari sai ta fara da kirarin kakanninsa, musamman Sarki Kanta da Sarki Sama (kasancewa zuri'a ]aya ce ke mulki), wa]anda ake ganin har yau ba a yi Sarakuna masu bajinta a }asar ba kamarsu domin sun kwashe shekara ]ari biyar suna sarauta ba tare da ta kubce masu ba. Misali, a kirarin Sarki Sama bayan ta ambato Sarakunan Argunguda suka gabata a }arshe takan dire kirarin nata da ambaton sunan duk Sarkin da ke gadon sarauta, ta wasa shi da asalin gidansu. Za a iya ganin haka a inda take zayyano dukkan Sarakunan Kabin Argungu daga Muhammadu Kanta, ta hanyar jaddada wa Sarkin da ke mulki cewa, a yau shi ne madadin iyayensa da kakanninsa. Kamar yadda take cewa:

…Yau kai agga Muhammadu Kanta na farko,
Yau kai agga Ibrahim ]an Muhammadu Kanta,
Yau kai agga Sulaiman ]an Dauda
Yau kai agga Muhammadu ]an Kanta.
Yau kai agga Maliki ]an Ibrahim,
Yau kai agga Umaru Giwa,
Yau kai agga Muhammadu Kaye,
Yau kai agga Ibrahima,
Yau kai agga Muhammadu Na Saifawa,
Yau kai agga Ahmadu,
Yau kai agga Tomo…
(*Kirarin Sarki Sama*)

Sarki Muhammadu Kanta (uban Kabawa), shi ne Sarki na farko a jerin Sarakunan Kabi wanda ya yi mulki tsakanin 1515-1561 a mazaunin Kabawa na farko da ke Surame. Tarihi ya nuna cewa Sarki Muhammadu Kanta tsatso ne na Uthman Nann Ibn Mas'ud, shugaban }ungiyar Si}aya wa]anda ke da alhakin samar da ruwa a Ka'aba.Wannan }ungiya ta yi hijira daga Makka zuwa Fezzan ta }asar Masar inda daga nan ne Gimba, ]aya daga cikinsu ya sake hijira har ya iso Katsina ya zauna. A Katsina ]an Gimba, wato Mukata ya auri ]iyar Sarkin Katsina na wancan lokaci, kuma Allah Ya albarkace su da Kanta. Bayan rasuwar mahaifinsa, Kanta ya shiga yi wa Fulani kiwo, daga nan kuma ya fara shiga gasar kokawa da dambe. Wannan ya sa ya yi suna saboda haza}a, har aka yi masa la}abi da 'Kotal.' Haza}arsa ta sa ya zauna }ar}ashin Sarkin Askiya a matsayin manyan jarumin ya}insa kafin ya ~alle, ya yi tawaye. Bayan Kanta, Zabiyar Kabi ta tsallake Sarakunan Kabi na biyu da na uku, wato Sarki Ahmadu (1561-1596) da Sarki  Dauda (1596-1619), wa]anda ]a da jika ne ga Sarki Kanta**.**

Daga nan ta ci gaba ta ambato Sarki Ibrahim (1619-1621),wanda shi ne Sarki na hu]u kuma ]a ga Kanta. Sarki na biyar, Sarki Sulaiman (1621-1636), wanda ]a ne ga Sarki Dauda kuma jika ga Sarki Ahmadu. Daga nan Zabiyar ta tsallake Sarki na shidda, Sarki Muhammadu (1636-1649), wanda shi ma ]a ne ga Sarki Kanta, sai ta ambato Sarki na bakwai,wato Sarki Maliki (1649-1660,1665-1675), wanda shi kuma ]a ne ga Sarki Ibrahim, ]an Sarki Kanta. Sai Sarki na takwas, Sarki Umaru Giwa ]an Sarki Ahmadu (1662- 1674), wanda ya yi sarauta a lokacin da masarautar ta sami yamutsi, a tsakanin Mulkin Sarki Maliki. Zabiyar ta ci gaba da ambato Sarki na tara, Sarki Muhammadu Kaye (1674-1676), wanda ]a ne ga Sarki Sulaiman. Ba ta }asa a gwiwa ba, ta ambato Sarki na goma, Sarki Ibrahim na biyu (1676-1684), ]an Sarki Muhammadu Kaye. Sai Sarki na goma sha ]aya, Sarki Muhammadu

Sifawa (1684-1686), wanda ]a ne ga Sarki Umaru Giwa. Ba ta tsaya a nan ba, ta ambato Sarki na biyu, Sarki Ahamadu na biyu, ]an Kanna wanda ]a ne ga Sarki Kanta amma bai yi sarauta ba. Sai Sarki Tomo (1696-1700, 1722-1726), wanda shi ne Sarki na goma sha uku.Sarki Tomo ne ya yi hijira daga Surame ya dawo Kabi a shekara ta 1700. Zabiyar Kabi ta ci gaba da lissafo sauran Sarakunan Kabi kamar haka:

Yau kai agga Muhammadu [angiwa,
Yau kai agga Isama'ila Tagandu,
Yau kai agga Muuhammadu [an Tagandu,
Yau kai agga Sulaimanu,
Yau kai agga Abubakar Ukar,
Yau kai agga Muhammadu Hodi,
Yau kai agga Sama'ila Karari,
Yau kai agga Yakubu Nabame,
Yau kai agga Yusufu Mainasara,
Yau kai agga Muhammadu Ba'are,
Yau kai agga Abdullahi Toga,
Yau kai agga Sama na Yakubu,
Yau kai agga Sule Dobe,
Yau kai agga Muhammadu Sama,
Yau kai agga Muhammadu Sani,
Yau kai agga Muhammadu Shehi,
Yau kai agga Muhammadu Mera.
(*Kirarin Sarki Sama*).

Kamar yadda aka gani, Zabiyar Kabin Argungu ta ci gaba ta ambato Sarki Muhammadu [angiwa (1700-1717), Sarki na goma sha hu]u wanda kamar Sarki Sifawa, shi ma ]a ne ga

SarkiMuhammadu Giwa. Daga nan ta ci gaba ta ambato Sarki Sama'ila Tagandu (1717-1750), Sarki na goma sha biyar, kuma ]a ga Sarki Sifawa. Bayansa kuma sai Sarki na goma sha shidda, wato Sarki Muhammadu Tagandu ]an Sarki Sama'ila Tagandu (1750-1754). A nan ne ta tsallake Sarki na goma sha bakwai, Abdullahi Toga na ]aya, sai ta ambato Sarki Sulaiman (1775-1803), ]a ga Sarki Abdullahi Toga. Ta ci gaba ta ambato Sarki na goma sha tara, a jerin Sarakunan Kabi, Abubakar Akar (1803), ]an Sarki Sulaiman, sai Muhammadu Hodi (1803-1826), ]an'uwan Sarki Abubakar Akar. Sannan sai Sarki Sama'ila Karari, wanda shi ma ]an'uwa ne ga Sarki Hodi , wato 'ya'ya ne ga Sarki Sulaiman. Bayan haka, ta ci gaba ta ambato Sarki Yakubu Nabame (1849-1854), Sarki na ashirin, wanda kuma shi ne ya taso da masarautar daga Kabi zuwa Argungu a zamaninsa.

Har ila yau, Zabiyar ta ci gaba da Sarki na ashirin da uku, Sarki Yusuf Mainasara (1854-1859), ]a ga Sarki Karari, sai kuma Sarki Muhammadu Ba'are, wanda shi ma ]an Sarki Karari ne. Daga nan sai Sarki Abdullahi Toga na biyu (1860-1883), ]an Yakubu Nabame, sannan ta ci gaba ta ambato Sarki Sama'ila Sama (1883-1915), ]an Sarki Nabame. Sai Sarki Sule Dobe (1915-1920), wanda shi ma ]an Sarki Nabame ne. Ba ta tsaya a nan ba, ta ci gaba da Sarki na ashirin da takwas, Sarki Muhammad Sama (1920-1934), ]an Sarki Sama, daga nan sai Sarki Muhammadu Sani (1934-1942), wanda ]a ne ga Muhammadu Sama. A nan ne ta tsallake Sarki na talatin, Sarki Sama'ila (1942-1953), wanda tsatso ne na Sarki Muhammadu Giwa. Ta ci gaba da Sarki Muhammadu Sheshe (1953-1959), Sarki na talatin da ]aya, kuma ]a ga Sarki Muhammadu Sama. A }arshe Zabiyar Kabin Argungu ta ambato Sarki Muhammadu Mera (1959-1996), Sarki na talatin da biyu kuma ]a ga Sarki Muhammadu Sani, mahaifin Sarkin da ke gadon sarauta, Sarki Sama'ila Muhammadu Mera.

A nan, za a iya ganin yadda Zabiyar ta jero asalin sarautar Kabin Argungu ga Sarki mai mulki daga kakanninsa ko kuma daga kakan – kakansa, Muhammadu Kanta har zuwa Sarakuna ashirin da takwas (28), wa]anda dukkansu zuri'ar Sarki ce, zuwa mahaifinsa marigayi Sarki Muhammadu Mera. Ta kuwa yi haka ne duk domin ta nuna salsalarsa ko salsalar gidansu ga sarautar da a yau yake ri}e da ita. Ke nan, ta }ara }arfafa masa cewa, sarautar ta gidansu ce kaka da kakanni wanda  ke }ara fito da }imarsa a idon talakawansa. Yana kuma fito da tunanin Bahaushe game da saraki da ke nuni da cewa sarauta a yanzu a {asar Hausa ta gado ce.

Wannan ambato na tushe yana zuga saraki domin yana }ara tabbatar da cewa shi ba mutumin banza ba ne, shi mutumin kirki ne saboda mutumin banza ba ya jagorantar jama'a. Har ila yau kuma, yana }ara tunatar da shi cewa daidai yake da Sarakunan duk da ta zayyano. Wannan isa ce ta matu}a, wajen fito da ainihin darajar salsalar mutum da nuna muhimmancinsa ga al'umma. Ga irin wannan dogon asali, a  iya cewa Sarakunan Kabin Argungu ba sa shakka da asalinsu, saboda suna da ]oranran asali musamman na jarunta. Ambato dogon asali ga Sarki, a ce ruwan dare ne game duniya a wa}o}in fada da ma kirari. Alalmisali, Maka]a Sa'idu Maidaji Sabon Birni, ya yi wa Sarkin Zazzau Shehu Idris irin wannan a wa}ar 'Balaraben Sarki', duk kuwa da cewa Sarkin bai fito zuri'a ]aya da dukkan Sarakunan da suka gabace shi ba. Ga yadda maka]in ke cewa:

| | |
|---|---|
| Jagora: | Yamusa ya dawo, |
| \`Y/Amshi: | Kullum ana buga mai tambura, |
| Jagora: | Sambo ya dawo, |
| \`Y/Amshi: | Kullum ana buga mai tambura, |

Jagora: Kwasau ne yad dawo,

`Y/Amshi: Kullum ana buga mai tambura,

Jagora: Aminu ya dawo,

`Y/Amshi: Kullum ana buga mai tambura,

Jagora: Ga Sidi ya dawo,

`Y/Amshi: Kullum ana buga mai tambura…

Jagora: Abubakar da yad dawo,

`Y/Amshi: Kullum ana buga mai tambura,

Jagora: Kuma Abdu ya dawo,

`Y/Amshi: Kullum ana buga mai tambura…

(Maidaji Sabon Birni, wa}ar 'Balaraben Sarkin').

Bayan Zabiyar Kabin Argungu ta zayyano wa]annan Sarakuna, ta ci gaba da matani kamar haka:

> ….. Zaman yau duk ]aukakarsu da martabarsu da muhibbarsu na wajjenka,
>
> Wadda duk gidan sarauta ya yi girma,
>
> Bai da salsala da martaba da muhibba irin gidan Muhammadu Kanta,
>
> Yau rinjaya da ]aukaka da martaba da muhibba tana gidan Nabame…
>
> (Kirarin Sarki Sama).

Idan aka nazarci abin da Zabiyar Kabin Argungu ta fa]i a sama, ta kwarzanta wannan gidan sarauta matu}a, ta hanyar nuni da cewa komai girman gidan sarauta, duk kuwa yadda ya kai, ba shi da salsala da martaba da muhibba irin gidan Muhammadu Kanta, saboda har yau, tushensa ke sarautar Kabin Argungu tun daga ]ansa Ibrahim har zuwa Sarki da ke kan gadon mulki (watau Sarki da ke kan gadon sarauta) wanda shi ma ya gada daga mahaifinsa Muhammadu Mera. Za kuma a iya ganin yadda ta }ara jaddada haka inda take cewa:

…..Yau rinjaya da ]aukaka da martaba da muhibba tana gidan Nabame…

Gidan Nabame abiyar tsohon tarihi….

(Kirarin Sarki Sama).

Gidan Nabame a yanzu gidan tarihi ne na a zo a gani a Masarautar Kabin Argungu, wanda nan ne gidan sarauta na farko, da Kabawa suka zauna bayan sun yi hijira daga Birnin Kabi zuwa daular Argungu. Sarki Yakubu Nabame (1849-1854), ne ya kafa sarauta a Argungu,wanda ya sa ake wa wannan gida la}abi da 'Gidan Nabame'. Ambato wannan gida da Zabiyar Kabi ta yi, na }ara nuni ne ga salsalar Sarki ga sarautar gidansu. Zabiyar ta bayyana haka a cikin kirarin, inda take cewa:

Kanta mai gidan Bame abiyar tarihi,

Gidan Nabame mai wuyar shiga ga Fulani…

(Kirarin Sarki Sama).

To haka kuma, a farkon kirarin Sarki Sama, Zabiyar Kabin Argungu ta }ara da:

Na Abdu gatarin Ya}uba…

(Kirarin Sarki Sama).

Sarki Sama kamar yadda tarihi ya nuna ]a ne ga Sarki Yakubu Nabame. A nan, ta }ara nuni ne ga asalin sarautar Sarki Sama wacce ya gada daga mahaifinsa Sarki Nabame, ta danganta salsalar da 'gatari'. Akwai kuma inda take cewa:

Mai da waiwaye na Muhamman…
Da}ili - }ishali ]an Yakubu Nabame…
Farshin wuta na Ya}uba….
Ka sare kaya na Muhamman…
Hurde mai idon ~ata na Muhamman…
(Kirarin Sarki Sama).

Muhamman da Yakubu Nabame kamar yadda Zabiyar Kabi ta ambato, kakan Sarki Sama ke nan, watau Muhammadu Kanta da mahaifinsa. Duk kuwa ta yi haka ne domin nuni da salsalarsa da su na sarautar Kabin Argungu, kamar yadda ya gada.

Shi ma Sarkin da ke gadon mulki, Zabiyar Kabin Argungu ta }ara nuni da tabbatar asalinsa da sarautar da ya gada daga mahaifinsa marigayi Sarki Muhammadu Mera, kamar yadda take cewa:

[an Mera ba a kai maka ya}i…,
Ai ga zamaninka ]an Yakubu Nabame…
Da arzikinka ]an Yakubu Nabame…

Dukiya ta isa kaya sun isa …

Jigon Sarakuna ]an Muhammadu Uban Kabawa Kanta…

(Kirarin Sarki Sama).

Wannan na nuni ga salsalar Sarkin Kabin Argungu da muhaifinsa Muhammadu Mera, ta yadda Zabiya ta jaddada cewa shi ne madadin kakansa, Sarki Yakubu Nabame. Sannan ta kira shi jigon Sarakuna (jagoran Sarakuna), kasancewar tushensa daga kakan-kakansa Muhammadu Kanta ne wanda ake yi wa la}abi da 'Uban Kabawa'.

To haka kuma, idan muka koma ga kirarin Zabiyar Sarkin Daura (Dakamar Sarkin Daura), za mu ga wannan nuni na dangantaka ta salsala ga Sarkin Daura, ya fito a inda take cewa:

Zabiya:  Hawan 'yan Bawo,

`Yan amshi: Hawan 'yan Bawo,

Zabiya: Kakan anna,

`Yan amshi: Kakan anna,

Zabiya: Hazo na Muhamman,

`Yan amshi: Hazo na Muhamman…

(Kirarin Sarki Daura).

Kamar yadda tarihi ya nuna, Bawo ya yi sarautar Daura, saboda haka, wannan matani na Zabiyar Daura, na nuni da asalin Sarki daga kakansa Bawo, har zuwa ga iyayensa, har sarauta ta kawo kansa. Watau gado ya yi na Sarautar Daura, ba haye ya yi ba. Ta hanyar nuna tushen Sarkin daga Muhamman Bawo. A iya cewa sarakin Daura, a kodayaushe suna

tun}aho da asalinsu na ‘Bawo’, domin zuri’arsa ke mulki har yau, in ban da jihadin Shehu Usman Danfodiyo da ya fatattake su, suka yi hijira har na shekara ]ari, (100), amma, sarautar ta dawo hannunsu. Haka kuma, a kirarin Magajin Garin Daura da na [an Buran Daura (Hakimin |aure), Zabiyar tana cewa:

> In gado rashin magada gado girman Allah…
>
> (Kirarin Magajin Garin Daura /[an Buram).

A masarautar Daura Sarautun Magajin Gari da Hakimin |aure, sarautu ne na musamman na manyan `ya`yan Sarki, wa]anda kuma ake sa ran ]aya daga cikinsu ya gaji sarautar mahaifinsu, saboda haka, a nan, Zabiyar Daura tana nuni ne ga salsalarsu/asalinsu ga gadon sarautar gidansu. Kasancewa sarautar da suke kai sun gaje ta ne, ba haye suka yi ba kuma ko gobe za su iya gadon sarautar mahaifinsu, wato ta sarautar gari. Neman magaji ga saraki, a iya cewa babban rumbu ne da ya mamaye adabin Hausa, wanda ya fito da tunanin Bahaushe ga muhimmancin samun magaji, domin gudun kada sarauta ta fita waje. Ana iya ganin haka a *Magana Jari Ce* (ta ]aya), a Uwar Labarin da *Shehu Umar* da sauran rubutattun adabi ( musamman zube), na Hausa da suka }ara fito da tunanin Bahaushe game da Magaji. A kirarin Sarkin Fulanin Daura (Hakimin Rijiyar Tsamiya), Zabiyar ta }ara tabbatar da wannan nuni na asali ga sarautarsa, a inda take cewa:

> In har magajin Har]o aminin makazaki da Korau…
>
> (Kirarin Sarkin Fulanin Daura).

‘Magaji’, shi ne ]a namiji mai jiran gadon sarauta, mace kuma ‘Magajiya’. Saboda haka a nan Zabiyar tana nunawa jama’a cewa Sarkin Fulanin Daura, gadon sarauta ya yi, shi ne ‘Magajin Har]o, ]an na gada ne ba ]an na koya ko ]an haye ba, yana da salsala da sarautar gidansu.

A kirarin Markan Daura, Dakamar Sarkin Daura ta ambaci makamancin wannan inda take cewa:

In bawa magajin tale mammaye…

(Kirarin Mar}an Daura).

Zabiyar ba ta yi kuskure ba, kasancewar sarautar ‘Marka’ ta manyan ‘ya’yan Sarki ce, wanda shi ma magaji ne cikin masu jiran fa]uwar sarauta. Ita ma Magajiyar Daura a kirarinta, Zabiyar na cewa:

In yar sasarin mutu ko dai ri}o…

(Kirarin Magajiyar Daura).

A nan, wannan na nufin ‘yar manya kuma mazan fama. Manya a nan na nuni ga matsayin ]iya ga Sarki, domin a Daura ba a ba kowace mace sarautar Magajiyar Gari, sai ‘yar Sarki, cikin ‘ya’yan Sarkin ma, babbarsu ake na]awa. Haka ma, a duk kirarin ‘ya’yan Sarki, Zabiyar takan ambaci haka (watau in ‘yar/]an/’yan sasarin mutu ko dai ri}o…). Takan ambaci haka, a kusan kirarin duk kirarin da take yi wa sarakin Daura, in ban da na {auran Daura da Sarkin Fulanin Daura da na Galadiman Daura da na Babban Al}ali (n fada/al}alin garka), saboda sarautu ne wa]anda ba na ‘ya’yan Sarki ba. Ke nan ba su da dangantaka da

Sarki ta jini. Sauran kuwa da Zabiyar ta yi wannan matani a kirarinsu, salsala ne na Sarki, wa]anda kowannensu na iya gadonsa.

A kirarin da Zabiyar Daura ke yi wa Markan Daura, tana cewa:

In bawa magajin tale mammaye,
In da zaman homa ]an }arfaffa
Sandar }arfe da zaki Marka…
(Kirarin Markan Daura)

A nan, '[an }arfaffa' na nufin ]an Sarki, saboda a da }arfaffa a gari, wanda ya nuna bajinta ta jaruntaka , shi ke hawan gadon sarauta, ya zama Sarki. Wannan ya nuna asali ko salsalar Markan Daura da sarautar Daura, kamar yadda aka yi bayani a baya,' Marka' sarauta ce ta manayan `ya`yan Sarki a Daura.

Shi ma Durbin Daura, Zabiyar tana danganta shi da haka, watau tushensa na ]an Sarki, a inda take cewa:

[an }otar ma}era fure babba,
In ko sungumi babban ]an Korau…
(Kirarin [urbin Daura).

A kirarin Sarkin Sudan da na Sarkin Kudu ma tana cewa:

[an ]akin Kangiwa mai tsotsai ka le}a,
[an }otar ma}era fure babba.
(Kirarin Sarkin Sudan /Sudan Daura)

Da ‘[an ]akin Kangiwa’ da ‘[an }otar ma}era’, da Zabiyar ta ambato dukka a nan suna nufin ‘ya’yan Sarki. Kamar yadda aka sani a da, sana’ar }ira, masana da dama sun amince ita ce da]a]]iyar sana’a, wadda ta girmi sana’ar noma, saboda haka cewa ]an fure babba, ]an manya ke nan. ‘Manya’, kuwa a nan shi ne Sarki, domin Sarki shi ne babba kuma mai babban matsayi da ya fi na kowa a }asarsa. Wanda ya sa ake kiran Sarakuna, ‘Sarkin yanka’, domin su ne wu}a su ne nama a masarautunsu, musamman a da lokacin da suke da }arfin iko. To haka kuma, a duk manyan garuruwan {asar Hausa, Unguwar Kangiwa, unguwa ce ta saraki, wurin da galibi gidajen ‘ya’yan Sarki suke zauneda iyalinsu. Sarautar Sarkin Sudan da ta Sarkin Kudu a Daura kuwa, sarautu ne ko dai na ‘ya’yan Sarki ko kuma jikokinsa. Duk dai a nan, ana nuna salsala ce ta sarauta, domin haka wa]anda aka danganta da wannan matani na nuni da ‘yan gado ne ba ‘yan haye ba a sarautar gidansu.

Idan kuma muka koma ga nazarin kirarin Zabiyar Ha]eja, irin kirarin da take yi wa sarakin Ha]eja, an ce an tsinci dame ne a kala, ko kuma a ce dodo ]aya ake yi wa tsafi, domin ita ma a kullum tana }o}arin fito ko nuna asalin saraki ne a kirarinta. A iya cewa, ita ~aro-~aro, ko a kai tsaye take nuna wannan salsalar, domin tana yawan ambaton matanin da ke tabbatar da cewa a sarauta, ]an na gada ya fi ]an na koya, a kirarin mafi yawan sarakin Ha]eja, in ban da na Mai Martaba Sarki, watau:

[an na gada wanda ya fi ]an na koya…

(Za a nazarci kirarin Sarki kafin a zo ga sauran saraki).

Zabiyar Ha]eja, a kirarin Sarki tana nuna salsalarsa ko tushensa kamar haka:

Kai ne Buhari kai ne Sambo,

Kai ne gagara gammo da Sarki Jatau,

Ya gaji gadon Hari da Haru,

Ya mayar da gadon Sarki {adir,

Ya mayar da gadon Sarki Karamba…

(Kirarin Sarkin Ha]eja).

Sarki Buhari da Sarki Sambo da Sarki Hari, da ma Sarki Haru, da Sarki {adir, da kuma Sarki Karamba, dukkansu Sarakunan Ha]eja ne na da. A nan Zabiyar Ha]eja, ta ambato su ne domin ta jaddada tushen Sarkin da ke kan gadon sarauta, domin dukkansu, daga uba ga Sarki sai kaka da kakan uba da kakan-kaka. Watau ya gaji sarauta ne daga iyaye da kakanni, ba haye ya yi ba, da ma sarautar ta gidansu ce, musamman idan aka yi la'akari da wa]annan Sarakuna da ta zayyano.

Zabiyar Ha]eja, tana kuma nuna tarihin asalin Sarkin Ha]aja na gadon sarauta, daga dangin uba da na dangin uwa, wanda ke tabbatar da cewa daga tushen biyu, Sarkin ya gaji sarauta gaba da baya. Kamar yadda a kirarin da take yi masa na dangin uwa ta ambato Turaki Abubakar:

Allah Ya ji }an Turaki Abubakar….

(Kirarin Sarkin Ha]eja).

Turaki Abubakar kaka ne ga Sarkin Ha]eja daga gefen uwa, wanda ke nuni da cewa, ko daga dangin uwa Sarkin Ha]eja basarake ne. A na dangin uba kuma, bayan ta zayyano

Sarakunan Ha]eja (kamar yadda aka yi bayani a baya), takan ambato [an Iya da Ciroman Ha]eja, wa]anda dukkansu `yan`uwa ne sha}i}ai ga mahaifin Sarki, kamar yadda take cewa:

> Allah Ya ji }an [an Iya Abdu,
> Allah Ya ji }an Ciroma Ali,
> Allah Ya bar mana [an Iya na yanzu…
> Kirarin Sarkin Ha]eja).

Zabiyar Ha]eja ba ta yi }asa a gwiwa ba, a kullum tana jaddada wannan nasaba ta asalin sarauta ga sarakin Ha]eja, ta hanyar }ara tabbatar da jaddada cewa, a sarauta, gado ya yi ba haye ba. Wannan kuwa a ce yana raunana zuciyar abokin hamayya, domin a kan sami wasu da ilimin boko da arzikinsu ya kai su matsayin da suke, suna }o}arin takara da saraki, wajen neman sarauta. Kamar yadda take cewa a kirarin Sarkin Arewan Ha]eja:

> [an na gada wanda ya fi ]an na koya Sarkin Arewa Aliyu… (Kirarin Sarkin Arewan Ha]eja).
>
> Haular Mabu]i Muhamman,
> [an na gada wanda ya fi ]an na koya…
> (Kirarin Mabu]in Ha]eja).

A nan, tana nuni ga asali na sarauta ga basaraken, cewa wanda ya yi gadon sarauta ko ]an asali ga sarauta, ya fi wanda ya haye ta rana tsaka, duk kuwa da irin bajintarsa, wajen iya ri}on jama'a ko jaruntaka da makamantansu. Wannan ya sa a kodayauke Zabiyar Fada takan ambato salsalar saraki daga magabatansa, wa]anda suka ha]a da iyaye da kakanni da suka

ri}e sarautar da yake ri}e da ita domin nuna asalinsa. Misali, a kirarin Galadiman Ha]eja, Zabiyar tana cewa:

Allah Ya ji }an Galadima Yusufu,

Allah Ya ji }an Galadima Zakar,
Allah Ya ji }an Galadima Usman,
Allah Ya ji }an Galadima Adamu,
Allah Ya ji }an Galadima Habibu.
(Kirarin Galadiman Ha]eja).

Galadima Yusuf da Zakar da Usman da Adamu da Habibu, kakanni ne da uba ga Galadima na yanzu, wanda ke nuni da cewa sarautar 'Galadima' ba hayenta ya yi ba, gado ya yi, kaka da kakanni har sarautar ta zo kansa.To haka kuma, a kirarin Magajin Garin Ha]eja da Turakin Ha]eja da Ciroman Ha]eja da [an Buran Ha]eja da Tafidan Ha]eja da [an Ruwatau Ha]eja, su ma kasancewarsu salsala ]aya da Sarki, duk a kirarinsu Zabiyar Ha]eja tana ambato kakanninsu da iyayensu da suka ri}e Masarautar Ha]eja a da, kamar yadda take ambato su a kirarin Mai Martaba Sarkin Ha]eja, kamar haka:

Kai ne Buhari kai ne Sambo,
Kai ne gagara gammo da Sarki Jatau,
Kai ne Sarki Abubakar,
Kai ne Sarki Haruna,
Kai ne Sarki Usman…
(Kirarin Tafidan Ha]eja/Ciroma/Ruwatau /[an Buram).

Wannan duk yana nuni da tushen wa]annan saraki, cewa ba haye suka yi wa sarauta ba, a'a, gadonta suka yi, kaka da kakanni. Ta kuma }ara jaddada haka a kirarin Magajin Garin Ha]eja da Ciroman Ha]eja da [an Ruwatau Ha]eja da kuma Turakin Gida, inda take cewa kamar haka:

Assalamu Alaikum ]an babban amale…
(Kirarin Magajin Garin Ha]eja).

Assalamu alaikum Baba Ciroma,
[an babban amale…
(Kirarin Ciroman Ha]eja)

Assalamu alaikum 'yar babban amale…
(Kirarin Turakin Gida)

'Amale, gawurtacce ri}a}}en ra}umi ke nan a cikin garke. Masu iya magana na cewa, "Wani kaya sai amale." Ana amfani da kalmar 'amale' a siffanta Sarki da ]abi'a ko hali da yanayin amale, kasancewa amale dabba ce mai ha}uri da juriya, musamman ta ]aukan kaya. To haka kuma, babban amale shugaba ne cikin garken ra}uma kamar yadda Sarki yake shugaba a garinsa ko cikin jama'arsa. A nan, abin nufi shi ne, wa]annan saraki, Zabiyar Ha]eja tana nuna salsalarsu ne  da Sarki, wanda aka kira da 'babban amale'. Amalen mutane, mutum ne mai fa]a-a-ji. A iya cewa wannan ya sa maka]an  Hausa suke amfani da wannan kalma su siffanta sarakunan yanka, saboda girman mulkinsu da iya ri}e nauyin

jama’arsu. Za a iya ganin haka daga misalan wasu wa}o}in fada, misali wa}ar da Shata ya yi wa Sarkin Zazzau, ya kira shi ‘amalen Sarakuna’.

Jagora: Tsaya ba ni shan ruwa in huje buta,
`Y/Amshi: Alhaji Sarki Zazzau Shehu,
Jagora: Amalen Sarakuna baban Jekada,
`Y/Amshi: Alhaji Sarkin Zazzau Shehu.
(Shata a wa}ar ‘Alhaji Sarkin Zazzau Shehu, 1975)

Maka]a [an}wairo ma ya kira Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris ‘amale’, kamar yadda ayek cewa:

Jagora: Shehu tun da kak kashe shago kek kashe [andunawa,
:Shehu kai ka]ai gayya amale aiki nai yay kyawo,
`Y/Amshi: Ba maza kashi tilas su bi ka Malam ]an Idirisa.
(Maka]a [an}wairo, a wa}ar ‘Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau).

Shi ma Sarkin Arewan Ha]eja, haka Zabiyar take ambato iyaye da kakanninsa da suka ri}e wannan sarauta kafin ya hau, duk domin nuna salsalar basaken ga gadon sarauta ‘Sarkin Arewa’. Misali, kamar haka:

Allah Ya ji }an Abubakar Garba,
Allah Ya ji }an Sarkin Arewa Abubakar,
Allah Ya ji }an Sarkin Arewa Sulaimanu,
Allah Ya ji }an Sarkin Arewa Idrisu,

Allah Ya ji }an Sarkin Arewa Usman da Kakagana…
Irin Magarya Sarkin Arewa.
(Kirarin Sarkin Arewan Ha]eja)

‘Magarya’ da Zabiyar ta ambato a nan, wata sarauta ce daga dangin mahaifiyar Sarkin Arewan Ha]eja. Duk dai abin nufi a nan shi ne, nuna salsalar sarakin na gadon sarautar da yake ri}e da ita, ta ‘Sarkin Arewa’, wanda da ke tabbatar da cewa, ba ]an haye ba

A kirarin Ciroman Ha]eja ma, bayan Zabiyar ta zayyano masa kakanninsa da iyaye da suka yi sarautar Ha]eja, irin su Sarki Buhari da Sarki Abubakar da Sarki Haruna da Sarki Usman, takan }arasa da }ara jaddada masa cewa shi fa ]an Sarki ne jikan Sarki, watau basarake ne. Zabiyar tana cewa:

[an Sarki jikan Sarki Ciroma.
(Kirarin Ciroman Ha]eja).

Duk dai ta hanyar nuna asali ko salsalar saraki, Zabiyar Ha]eja a kirarin da take yi wa sarakin Ha]eja, tana }ara nuni ga dangantakar basarake da sarautar gidansu, domin jama’a, musamman talakawa da abokan hamayya su san gado ya yi ba haye ba. Alalmisali, a kirarin [an Buran Ha]eja tana cewa:

Haular Mabu]in Hausa,
Haular Mabu]i Sulaimanu,
Haular Mabu]i Materi,
Haular Mabu]i Abubakar,
Haular Mabu]i Muhamman,

Kai ne Mabu]i  Muhamman,
 [an na gada wanda ya fi ]an na koya.
(Kirarin [an Buran Ha]eja)

Haka kuma, a kirarin Mabu]in Ha]eja, tana cewa:

Haular Mabu]i  Sulaimanu,
Haular Mabu]i  Ibrahim,
Haular Mabu]i Muhamman,
[an na gada wanda ya fi ]an na koya.
(Kirarin Mabu]in Ha]eja).

‘Haula’, na da ma’anar rassan bishiya ko karan dawa ko kuma dangi ko zuri’a. A nan, za a iya cewa Zabiyar Ha]eja ta danganta [an Buran Ha]eja, da Mabu]in Ha]eja da tsatso daga zuri’ar Mabu]i Sulaiman da Mabu]i Materi da Mabu]i Ibrahim da Mabu]i  Muhamman. Watau, ta danganta sarakin da rassan bishiya a inda ta zayyano kakanninsu da iyaye da suka ri}e sarautar Mabu]in Ha]eja. Cewar, “Haular Mabu]in Hausa”, da Zabiyar Ha]eja ta yi, da ma wannan kirari ne da ake yi wa Ha]eja, kasancewarta hanyar da ake bi a shigo {asar Hausa, domin  masarautar ce da ta raba daular Barno da ta Sakkwato daga {asar Barno. Ke nan, Mabu]in Ha]eja tsatso ne na gidan Sarautar Ha]eja.

A kuma kirarin Tafidan Ha]eja, labarin bai canza ba, domin bayan ta ambato masa kakanninsa da suka ri}e sarautar Ha]eja, ta yi ta’aziyya da rasuwarsu, kamar yadda take yi wa sauran saraki masu ala}a ta jini da su, takan }ara da:

Jikan Tafida Umaru…

(Kirarin Tafidan Ha]eja).

Wannan matani na }ara tabbatar da cewa Tafidan Ha]eja ba hayen sarautar Tafidan Ha]eja ya yi ba, domin kakansa Tafida Umaru ma ya ri}e sarautar /mu}amin. Saboda haka wannan ya jaddada salsalarsa ga sarautarsa da yake ri}e da ita, ba haye ya yi rana tsaka ba.

Shi ma [an Iyan Ha]eja, Zabiyar ba ta yi }asa a gwiwa ba, ta ambato kakansa da mahaifinsa da kakansa wa]anda suka ri}e sarautar a da, a kirarin da take yi masa, duk kuwa domin ta nuna salsalarsa da sarautar Iyan Ha]eja, kamar yadda take cewa:

Allah Ya ji }an Iya Abdu…,
Allah Ya ji }an Iya Ashararudu.
(Kirarin [an Iyan Ha]eja).

Ita ma Mai Babban [akin Ha]eja, wadda uwa ce ga Mai Martaba Sarkin Ha]eja Mai mulki, kuma ]iya ga Ciroman Ha]eja na da kuma 'yar uwa ga Ciroma da Iyan Ha]eja na yanzu, Zabiyar Ha]eja na nuna salsalarta da su, a kirarin da take yi mata (baya ga cewa mai Babban [akin, matar Sarki ce marigayi muka uwa ga Sarki na yanzu). Wanda ke nuni da cewa 'Mai Babban [akin Ha]eja' saraki ce ko a gefen iyayenta.

Salamu alaikum 'yar Abdu,
Allah Ya ji }an Ciroma Ali da gafara,
Allah Ya ji }an Iya Salma,
Allah Ya bar mana Iya na yanzu…
(Kirarin Mai Babban [akin Ha]eja).

Haka ma matar Sarki ta uku (Hajja Aisha), kasancewa tushe daga Ciroman Ha]eja Sambo da Iyan Ha]eja Abdu, Zabiyar Ha]eja ta ambato su a kirarin da take yi mata, domin nuna salsalarta da su wanda ke tabbatar da cewa saraki ce ko ba ta auren Sarki. Kamar yadda take cewa:

> Salamu alaikum ‘yar na gada…,
> Allah Ya ji }an Ciroma Sambo da gafara,
> Allah Ya ji }an [an Iya Abdu,
> Abdu bugun tama…
> (Kirarin Matar Sarkin Ha]eja ta uku).

A iya cewa wannan duk yana nuna asalin saraki ne, wanda yake }ara jaddada cewa sarauta ba hayenta ta yi ba, a’a ita da haife shi.

Haka yake idan muka le}a Fadar Kazaure, tatsuniyar ba ta wuce ta ‘gizo da }o}i' ba, domin Zabiyar Kazaure Hajiya Indo`Yarsukola, kasancewarta Zabiyar Sarakuna uku, watau Sarki Ibrahim Adamu da }aninsa Sarki Hussaini Adamu da kuma Sarki na yanzu, Sarki Najib Hussaini Adamu, a wasu lokuta kafin ta yi wa Sarki Najib kirari, sai ta fara da na iyayensa. A kuma kirarin Sarki Najib, takan jaddada dangantakarta da sarautar Kazaure, daga iyayensa da ma Sarkin Kano Ado Bayero, kamar haka:

> Sarki Magajin Sarki,
> Sarki Magajin Sarki Ado,
> Sarki Magajin Sarki Ibrahim,
> Sarki Magajin Sarki Hussaini Adamu…
> (Kirarin Sarkin Kazaure, Najib Hussain Adamu).

Kodayake Sarki Najib ba shi da dangantaka ta jini da Sarki Ado Bayero, Zabiyar Kazaure (‘Yarsukola), ta danganta su saboda girma da martaba da muhibbar Masarautar Kano, musamman lokacin da Jigawa take }ar}ashin Jihar Kano da Majalisar Masarautun Jihar Kano.  A ta}aice, ta danganta asalin Sarki Najib da magabatansa wa]anda suke tsatso ]aya, wan mahaifinsa (Sarki Ibrahim)  da mahaifinsa (Sarki Hussaini), wanda yake nuni a sasari ba hayen sarauta ya yi ba, ]an na gada ne, domin kakansa mas Sarkin Kazaure Alhaji Adamu ya ri}e Sarautar Kazaure tsakanin 1941- 1968, wanda shi ma ya gaji sarautar ne daga ]an’uwansa Sarki Umaru (1922 – 1940).

Ita ma Zabiya {arangiya ( Zabiyar Kazaure ta biyu), tana nuna salsalar Sarki Najib Hussaini a kirarinta kamar haka:

…Allah Ya ji }an Sarki Hussaini,
Allah Ya ji }an Sarki Ibrahim,
Ubangiji Ya ji }an Sarki Adamu toshiya mafarar dawa,
Ubangijinmu Allah Ya ja ran Sarki
Sarki  magajin Sarki Alhamdulillahi…,
[an Ummaru Alhamdulillahi,
Mai Martaba Sarki Najib ]an Sarki Hussaini…
(Kirarin Sarkin Kazaure Najib Hussain Adamu).

A nan, Zabiyar ta ambato iyayensa Sarki, Ibrahim da Sarki Hussaini , ta }ara ta nuna salsalarsu daga kakansa Sarki Adamu wanda ta kira shi ‘toshiya mafarar dawa’, sannan

kuma ta ambato Sarki Umaru, wanda wa ne ga kakan Sarki Najib (Sarki Adamu), ta kuma nuni da cewa Sarki Najib ]a ne ga Sarki Hussaini, kamar 'yar'uwarta Zabiya 'Yarsukola, ta jaddada salsalar Sarki Najib da Sarautar Kazaure, a bayanin da aka yi a baya.

Shi ma Wamban Kazaure, Hakimin Cikin Gari ]an'uwa ne ga Sarki Najib, a nasa kirarin, Zabiya 'Yarsukola tana ambaton kakanninsa da suka yi sarautar Kazaure, misali Wambai Audu (wanda daga baya ya zama Sarki) da wan mahaifinsa Sarki Ibrahim da kuma kakansa Sarki Hussaini Adamu, kamar yadda take cewa:

Wambai Magajin Wambai Audu,
Allah Ya ji }an Sarki Audu,
Allah Ya ji }an Sarki Ibrahim,
Allah Ya ji }an Sarki Hussaini Adamu…
(Kirarin Wamban Kazaure).

Wannan kirari na tabbatar da cewa Wamban Kazaure, ]an gado ne a sarautar gidansu domin ya gada daga kakanninsa zuwa ga iyaye, da ke nuni da cewa yana da dogon asali. Haka kuma, a kirarin Yariman Ha]eja, Zabiya `Yarsukola ta jaddada salsalarsa na gadon wannan sarauta wadda ya gada, inda take cewa:

…Yarima Magajin Yarima…
(Kirarin Yariman Ha]eja).

'Magaji' kamar yadda aka yi bayani a baya na nuni da gado. Saboda haka Yariman Ha]eja magaji ne na Yarima magabacinsa. Sannan ta ci gaba ta ambato iyaye da kakanninsa da suka ri}e sarautar Yarima kamar haka:

…Allah ji }an Yarima Tsahiro ([ahiru),
Allah ji }an Yarima Shehu,
Allah ji }an Yarima Audu,
Allah ji }an Yarima Muhamman Sulaiman.
(Kirarin Yariman Ha]eja).

Wannan nuni ne ga tushe. Haka yake a kirarin Ciroman Kazaure, wanda shi ma tsatso ne daga zuri'ar Yariman Kazaure [ahiru. Kamar yadda Zabiya 'Yarsukola ta ambato masa iyaye da kakanninsa da suka ri}e sarautar Yariman Kazaure, yadda ta ambato wa Yarima. Duk dai ma}asudin wannan shi ne a nuna wa jama'a cewa a sarauta, wa]annan saraki gado suka yi, ba haye ba, domin suna da asali. Asali na sarautar da suke ri}e da ita, wanda kuma ke tsorata abokan hamayya su ja da baya.

A kirarin Baraden Kazaure ma Zabiya 'Yarsukola ta nuna wa jama'a asalinsa da sarautar Kazaure, domin haka takan ambato Sarakunan Kazaure daga Sarki Audu (wanda kuma a da ya ri}e mu}amin Wambai da Galadiman Kazaure) da Sarki Ibrahim da Sarki Hussaini da Ciroma Ummaru da Wambai Sanusi da kuma Jarman Kazaure Ummaru. Duka dai manufa a nan shi ne, a nuna salsalar basaraken, a matsayinsa na saraki ]an gado ba ]an haye ba, kamar yadda take cewa:

Barka da hutawa Baraden Kazaure,
Allah Ji }an Galadima Audu,
Allah ji }an Sarki Ibrahim,
Allah ji }an Sarki Hussaini Adamu,
Allah ji }an Ciroma Ummaru,
Allah ji }an Wambai Audu,

Allah ji }an Wambai Sanusi…,
Allah ji }an Jarmai Ummaru…
(Kirarin Baraden Kazaure).

Haka yake a kirarin Wamban Kazaure, shi ma kirarin da Zabiya ‘Yarsukola ke yi masa na nuni da salsalarsa ga sarautar da yake ri}e da ita. Wato daga Wambai Sanusi da Wambai Audu da [an Iyan Kazaure, uwa-uba Sarki Ibrahim Adamu, wanda shi ne mahaifinsa, kamar yadda take cewa:

Wambai ]an gagarabadon Sarakuna,
Wambai magajin Wambai Sanusi,
Wambai magajin Wambai Audu,
Allah ji }an Wambai Audu,
Allah ji }an [an Iyan Kazaure,
Allah ji }an Sarki Ibrahim x2…
(Kirarin Wamban Kazaure).

Ita ma matar Sarkin Kazaure, duk da yake ba ]iyar basarake ba ce, amma a matsayinta na matar Sarki Najib, Zabiya ‘Yarsukola a kirarin da take yi mata tana nuna asalinta na ‘yar limamin Kano, kamar yadda take cewa:

Allah ji }an Alhaji Mukhtar,
Allah ji }an limamin Kano x 2…
(Kirarin Matar Sarkin Kazaure Najib).

Ko ba komai malamai da al}alan karaga makusanta ne na Sarki da duk sauran saraki. Ita ma Zabiya {arangiya ta }ara nuna wannan salsala na matar Sarki Najib a nata kirarin, kamar yadda take cewa:

…`Yar Sarki ji}ar Sarki ‘yar malamai…
(Kirarin Matar Sarkin Kazaure Najib).

A iya cewa Zabiyar ta yi wa matar Sarki Najib kara a nan, na kiranta `yar Sarki ji}ar Sarki, saboda mijinta ]an Sarkin ne jikan Sarki. Ita ma za a iya ce mata haka, domin a kambama ta. Da ma dai, maro}an fada su kambama saraki ba ba}on abu ba ne. Kamar yadda Shata a ‘Wa}ar Sarkin Zazzau Shehu’ ya danganta Sarki Shehu Idris da Sarkin Musulumi, wanda yake suruki ne ga Sarkin:

Jagora: Shehu jikan Mujaddadi a wajen matarshi
`Y/Amshi: Alhaji Sarkin Zazzau Shehu.
(Shata, a wa}ar ‘Alhaji Sarkin Zazzau Shehu).

Idan kuwa muka koma Fadar Zazzau, nan ma an ce an tsinci dami ne a kala, dangane da nuni ga tarihin asalin saraki, daga kaka da kakanni. A kirarin Zabiyar Fadar Zazzau, Dogariyar Zazzau (wadda ita ce a matsayin Zabiyar Fadar Zazzau a lokacin da aka gabatar da wannan bincike), a kirarin Mai Martaba Sarkin Zazzau, Shehu Idris, a kodayaushe tana nuna salsalarsa ne da Sarki Sambo, wanda kaka ne ga Sarki. Tana kuma ambato mahaifinsa Idirisa, wanda kodayake bai yi sarautar Zazzau ba, amma ]an Sarki ne, kuma ya ri}e sarautar Mai Unguwa. Ba za a kwatanta sarautar Sarkin `Yanka da ta Mai Unguwa ba, to

amma sanin kowa ne cewa Idirisa ]an Sarki ne, kuma ko ba komai shi ne uba ga Mai Martaba Sarkin Zazzau Shehu. Zabiyar ta ambato salsalar Sarki kamar haka:

Shiga da }arfin Allah,
[an Idirisa autan Sambo…
Ka dawo lafiya ]an Idirisa autan Sambo…
Allah Ya }ara maka son Annabi ]an Idirisa autan Sambo.
(Kirarin Sarkin Zazzau).

Haka ita ma Rabi Bazamfara,ta jaddada wannan salsala ta Sarkin Zazzau, musamman dangantaka da Sarki Sambo, kamar yadda take cewa:

[an Idirisa autan Sambo,
Ji kan Sambo…,
Idan babu Sambo kai ne Sambo….
(Kirarin Sarkin Zazzau).

Idirisa autan Sarki Sambo ne kamar yadda ta ambato, shi kuma Sarki Shehu Idiris, jika ne ga Sarki Sambo. Zabiyar kuma }ara jaddada wa da cewa 'a yau da babu Sarki Sambo, Sarki Shehu shi ne madadinsa', watau shi ne ya maye gurbin kakansa a sarautar gidansu. Duk dai manufa a nan shi ne nuna salsala ta sarauta, ko da kuwa mahaifinsa bai yi sarautar Zazzau ba, kakansa Sarki Sambo ya yi. Kamar yadda sauran maka]a suke nuna wannan dangantaka ta Sarki Sambo da Sarki Shehu Idris a duk wa}o}insu. Misali:

Jagora: Mani na Garba jikan Malam Sambo,
`Y/Amshi: Alhaji Sarkin Zazzau Shehu,

Jagora: Shehu gusun da Sakkwato jikan Sambo,

`Y/Amshi: Alhaji Sarkin Zazzau Shehu…

(Wa}ar ‘Sarkin Zazzau Shehu’ ta Mamman Shata)

Haka ma marigayi Sarkin Daura Muhammadu Bashar, a kullum maka]a sun fi danganta shi da kakansa marigayi Sarki Abdulrahman, duk kuwa da cewa mahaifinsa ya yi Magajin Garin Daura, to amma sarautar da Sarki Bashar ya ri}e a zamaninsa ba ta ‘Magajin Gari’ ba ce, ta ‘Sarki’ ce mai cikakken iko kuma ya gaji kakansa ne.Kamar yadda kakansa ma gado ya yi:

Jagora: Jikan Abdu ya yi Sarki, $x^2$

`Y/Amshi: Wa ke iya fa]a mai, $x^2$

(Wa}ar ‘Ginshi}in maza mai hana }arya a gode ma’, ta Sarkin Taushin Katsina Alhaji Muhammadu).

Kamar yadda shi ma maka]a [ankwairo yake danganta Sarki Bashar da kakansa, Sarki Abdulrahaman:

Daudu: Jikan Abdu mai }asad Daura, $x^2$

`Y/Amshi: Taho namijin zaki ya cika da }arhi, $x^2$

Daudu: Mai takkakaf fa]a da arna,

`Y/Amshi: Muhammadu mai takakkaf fa]a da arna,

Jagora: Bashari ]an Musa, $x^2$

`Y/Amshi: Giwa ba a ta~a jan gardama da kai ba, $x^2$

(wa}ar ‘Babban jigo na Yari’, ta maka]a [ankwairo)

A nan za a ga yadda maka]an suka danganta Sarkin Daura Muhammadu Bashar da kakansa Sarki Abdulrahman da kakan mahaifinsa, Sarki Musa domin su nuna tushensa na sarautar Daura, duk kuwa domin su jaddada cewa ba hayen sarauta ya yi da rana tsaka ba.

Haka su matan Sarkin Zazzau Shehu Idris, ta uku da ta hu]u wa]anda dukkaninsu 'ya'yan Sararkunan Yanka ne, Dogariyar Zazzau tana nuni ga salsalarsu a kirarin da take masu kamar haka:

Ranki ya da]e gimbiya,
Allah Ya }ara martaba,
[iyar Sarki matar Sarki.
(Kirarin Matar Sarkin Zazzau ta uku Yaya, Hajiya Binta)

Hajiya Binta ]iya ce ga Sarkin Zazzau, Sarki Muhammadu Aminu kuma mata ga Sarkin Zazzau, Shehu Idris. Saboda haka Zabiyar ta kira ta 'gimbiya' a matsayinta na 'yar Sarki. Kalmar 'gimbiya', kamar yadda aka sani a Hausa, la}abi ne da ake yi wa 'yar Sarki. 'Jam'in kalmar kuwa shi ne, 'gimbiyoyi'. Zabiyar ta }ara, ta jaddada mata da ma sauran jama'a, domin su sani cewa, ita ]iyar Sarki ce kuma matar Sarki.

Ita ma matar Sarkin Zazzau ta hu]u, haka salsalarta take. [iya ce ga Sarkin Musulmi Abubakar na III, wato Hajiya Mariya (wadda ake yi wa la}abi da 'Goggo'). A kirarin da Dogariyar Zazzau take yi mata, tana ambaton asalinta kamar haka:

Allah Ya taimake ki gimbiya,
[iyar Sarki matar Sarki…

(Kirarin Matar Sarkin Zazzau ta hu]u).

To haka kuma, Zabiyar Kano, Hajiya Ajuji Maitazargade ta yi amfani da wannan hanya ta nuna tarihin asalin saraki ga sarauta a kirarinta, a matsayin ]aya daga cikin shikashikan cim ma yabo. Kamar yadda take cewa:

Ina godiya ]an Lami]o ka biya ni,
Goyon Malam Maje ka biya ni…,
Magajin Muhammadu ]an tukura jikan tukura…,
Irin Yusufa Nadabo ka biya ni…
(Kirarin Sarkin Kano).

A nan Zabiyar ta ambato wasu daga salsalar Sarkin Kano Ado Bayero, kamar yadda da farko ta fara da kakanninsa, daga Sarkin Kano na hu]u (4), a salsalar Sullubawa,watau Abdullahi Maje Karofi, sai Sarki na goma sha ]aya (11), Sarki Muhammadu Sanusi, sannan Galadima Yusufa Nadabo wanda ]a ne ga Sarkin Kano Abdullahi Maje Karofi, watau }anin mahaifin Sarki Ado Bayero. Duk kuwa an yi haka ne, domin a nuna cewa sarautar Kano ta gidansu ce, kaka da kakanni, ba haye ya yi ba rana tsaka. Ta ci gaba inda take cewa:

Allah ji }an mai Kanon Galadima,
Allah taimaki jikan ‘mai suka da mashi’,
Jikan Alu mai Kano…,
Allah jikan Abdu jikan Abdu,
[an Maje Nassarawa…
(Kirarin Sarkin Kano).

La}abin ‘Mai Kanon Galadima’ da ‘[an Maje Nassarawa’, dukka la}abi ne na Sarkin Kano, Abdullahi Bayero, mahaifin Sarki Ado Bayero. ‘Mai suka da masu’ kuwa shi ne Sarki Abdullahi Maje Karofi, kakan Sarki Ado Bayero. ‘Alu mai Kano’ kuma, shi ne Sarki Aliyu, Sarki na bakwai (7) a salsalar Sullu~awa. To haka kuma, ‘Abdu jikan Abdu’, Sarki Abdullahi Bayero ke nan, mahaifin Sarki Ado Bayero (wanda kuma jika ne ga Sarki Abdullahi Maje Karofi- wannan, shi ya sa Zabiyar Kano, ta kira Sarki Abdullahi Bayero, ‘Abdu jikan Abdu’). Manufar ambatonsu a kirarin mai Martaba Sarkin Kano Ado Bayero ba ya rasa nasaba da nuni ga tarhin salsalar basaraken, musamman domin a jaddada cewa sarauta gadonta ya yi tun tali-tali, daga kakanninsa masu nisa, tun daga Sarkin Kano Malam Sulaiman har zuwa kansa, a matsayin Sarki na goma sha uku (13), wanda duk daga tsatso ]aya suke, watau gidan Sullu~awa.

A wani ~angaren kuma, Zabiya Ajuji Maitazargade, a kirarin Sarki Ado Bayero, ta ambato Sarki Yaji, ]aya daga cikin mashahuran Sarakunan da aka yi a Kano, domin nuna muhibba/martabar Sarki, duk kuwa da cewa ba zuri’arsu ]aya ba, amma saboda sarauta da martabar Kano, kamar yadda take cewa:

> Na yi godiya na gode jikan Yaji…
>
> (Kirarin Sarkin Kano).

Haka kuma, a kirarin Mai Martaba Sarki Ado Bayero, Zabiyar Kano ta ambato ]aya daga cikin matansa, watau Hajiya Saude wadda ]iya ce ga Sarkin Musulmi Abubakar III. Zabiyar ta yi nuni da salsalarta na ]iya kuma jikar Sarkin Yanka, wanda kuma Sarkin addini ne, kamar yadda take cewa:

Allah zaunar da Sarakuna dai Hajiya Saude,
A  yi mana gudummuwa da idanu,
Ga `yar mai yanka mutane,
Jikar mai yanka mutane…

(Kirarin Sarkin Kano)

Sarakuna a nan na nufin Sarkin Musulmi Abubakar III  (mahaifinsa) da Sarki Ado Bayero (mijinta), wa]anda dukkaninsu Sarakunan Yanka ne. Duk ba domin komai Zabiyar ta amboto su ba (musamman mahaifin Hajiya Saude), sai domin ta jaddada cewa, da ma ita sarauta ta haife ta, ko da kuwa ita ba matar Sarki ba ce. Wannan shi ne da]i kan da]i, "Matar Sarki ]iyar Sarki". To haka kuma, Zabiyoyin Fada kan yi amfani da damar ambato zuri'ar saraki a kirarin da suke yi masu.

**Ambato Zuri'a:** Idan aka ce 'zuri'a', wannan na nufin 'dangin mutum', wa]anda suka ha]a da `ya`ya da }anne da iyaye da yayye. A iya cewa zuri'ar mutum su ne makusantansa na jini. Kodayake za a iya sa mata/miji a matsayin zuri'ar mutum saboda kusancinsu. Wannan yabo dangane da zuri'ar saraki shi ne Tsoho (2002), ya kira `Yabau Dangantau', watau yabau na dangantaka, a inda maka]a ke amfani da dangantakar da ke tsakanin wanda ake yabo, ko ta jini ko ta aure ko ta abokantaka ko dangantaka ta zama wuri ]aya da makamantansu domin nuna nasaba da matsayin mutum a cikin al'umma. A wani lokaci ma har da aminai ana kiransu cikin wa}a ko kirari.

Jero sunayen Sarakunan da suka gabaci wanda ake yi wa kirari ko wa}a da ya ha]a da kakanni da iyaye da yayu, ana fa]in kyawun halayensu da bajintarsu da kwarjini ana dangatawa da shi ga saraki, musamman iyaye da kakanni, na da matsayi na matu}a, domin kuwa albarkacinsu yake ci. Tun ma ba a ce sun yi wata bajinta ba a lokacinsu, wanda yakan kasance abin alfahari a gare shi. To haka yake a kirarin Zabiyar Fada, takan ambaci makusantan saraki ta nuna dangantakarsu, misali:

jikan…
]an …/ `yar….
matar…/angon…
uban… da sauransu.

Idan muka duba kirarin da Zabiya Ajuji Maitazargade ta yi wa Sarkin Kano Ado Bayero, ta fara ne da ambato wasu daga cikin zuri'arsa, kamar haka:

Allah ji }an Muhammadu Adananu,
Allah shi gafarta mai fa,
Sannan da Alhaji Muntari,
Mijin Fulani mai gadon Masar Bilkisu…

(Kirarin Sarkin Kano).

A nan, Muhammadu Adananu kaka ne daga kakannin Sarki Ado Bayero daga gefen mahaifiyarsa, wanda kuma tsatso ne daga salsalar Fulani Dambazawa. Alhaji Muntari kuwa, amini ne na Sarki kuma surukinsa, wato mijin Fulani Balkisu, wacce 'yar'uwa makusanciya

ce ga Mai Martaba Sarkin Kano Ado Bayero, domin ]akinsu ]aya. Kamar kuma yadda take cewa:

> Na yi godiya na gode jikan Yaji…,
> Allah Yaimaki jikan mai suka da mashi,
> Jikan Alu mai Kano….
> Allah ji }an Abdu ji }an Abdu,
> [an Maje Nassarawa…..
> (Kirarin Sarkin Kano)

Zabiyar Kano Ajuji Maitazargade ta danganta Mai Martaba Sarkin Kano, Ado Bayero da kakansa Sarki Yaji da Sarki Aliyu (Alu) da kuma mahaifinsa Sarki Abdullahi Bayero. Ta ci gaba inda take cewa:

> Ina Bashir ]an masu gida?
> Saboda Mai Babban [akin Kano yake ba ni riga…
> (Kirarin Sarkin Kano)

Bashir (Hakimin Takai), ]a ne ga Sarkin Kano Ado Bayero wanda Zabiya Ajuji ta yaba da kyautar da yake yi mata, inda ta yi nuni da cewa, musamman yana haka ne saboda martabar kakarsa, Mai Babban [aki. Mai Babban [aki dai sarauta ce ta mahaifiyar Sarki, a wasu daga cikin Masarautun Hausa, kamar Kano da Ha]eja. Saboda haka, ita ce mahaifiyar Mai Martaba Sarkin Kano Ado Bayero. Zabiyar ba ta tsaya a nan ba, ta ambato wasu daga zuri'ar Mai Martaba Sarkin Kano, kamar haka:

> Ina Bashar………

Ina godiya ina }arawa na gode,
Goyon Fulani Duduwa,
Na yi godiya na gode goyon Fulani Nafi
Goyon Malam Maje ka biya ni,
Kyauta ba bashi ba…
(Kirarin Sarkin Kano)

Fulani Duduwa da Fulani Nafi, duk `yan'uwa ne ko }anne ga Sarkin Kano (kodayake a nan ta ambato su ne tana danganta su da Bashir Ado Bayero, kamar yadda aka yi bayani a baya). 'Malam Maje', kamar yadda tarihi ya nuna, a nan tana nufin 'Maje [an Jatau,' Hakimin Jahun wanda }ani ne ga mahaifin Sarki Ado kuma uban goyonsa (uban goyo ga Sarki Ado Bayero).

Zabiyar ta ci gaba inda take cewa:

Kuma na yi bege mai ta da rai,
Allah ji }an Sarkin {araye Ibrahim,
Allah sa mutuwa hutawa,
Allah ji }an Hajiya Hadiza uwata…,
Allah ji }an Alhaji Ibrahim na Ahmadu..,
Sarki mai garin {araye,
Amanar Sarki autan Bawo,
Magajin Ila Garba Magajin Garba…
(Kirarin Sarkin Kano)

Sarkin {araye Ibrahim amini ne kuma suruki ga Mai Martaba Ado Bayero domin ya auri }anwarsa a lokacin da yake raye. Wannan kusancin ne ya sa Zabiyar ta ambato shi a kirarin Mai Martaba, baya ga cewa Hakiminsa ne. Ba Sarkin {araye Ibrahim ba, har da mahaifiyarsa (Hajiya Hadiza) ta ambace ta kuma amininsa Sarkin Rano Garba (Magajin Garba) wanda shi ma suruki ne ga Mai Martaba Ado, watau suna auren 'yan'uwa, shi da Sarkin {araye Ibrahim. Ambaton zuri'a a kirarin da Zabiyar Fada take yi wa saraki, yana }ara dan}on zumunci da jaddada dangantaka.

Zabiyar ta ci gaba a kirarin Mai Martaba Sarkin Kano Ado Bayero,s ta ambato wasu daga cikin }wara}waransa kamar haka:

> Ina godiya ubangijin `Yar Jo]a,
> Ubangijin Zainabu Abu ka biya ni,
> Ubangijin Lami da Dada….
> (Kirarin Sarkin Kano)

'Yar Jo]a da Zainabu Abu da Lami da Dada, dukkaninsu }wara}warai ne na Sarki Ado,wa]anda saboda matsayinsu ga basaraken, Zabiyar ta ambace su. Da ma ko cikin }wara}warai, a kan samu manya da }anana. Manya galibi su ne wa]anda suka haihu ko kuma suka fi fada wurin ubangidansu.

Akwai kuma inda Zabiyar Kano take cewa:

> …Godiya Uwar Hadiza na gode,
> Uwar Yalwa cikin hairi (hairan)
> Na yi godiya na gode…

(Kirarin Sarkin Kano)

Uwar Hadiza /*Yalwa* a nan ita ce Fulanin {araye, matar Sarkin {araye Ibrahim, wadda }anwa ce ga Sarki Ado Bayero. A nan, Zabiyar ta ambace ta a kirarin Mai Martaba Sarkin Kano Ado Bayero ne saboda dangantakarsu ta jini.

Zabiyar ta ci gaba ta ambato matan Mai Martaba Sarki Ado Bayero, kamar yadda take cewa:

Mai tagwayen mata,
Balaraben Aishatu Nafi'u,
Mijin Yalwa Mijin 'Yar Aba,
Mijin Rakiya ka biya ni…
Allah zaunar da Sarakuna Hajiya Saude…
(Kirarin Sarkin Kano)

Zabiyar ta kuma ambato wasu daga cikin `ya`yan Sarkin Kano Ado Bayero kamar haka:

Ina Bashir ]an masu gida?….
Allah raya man Abdu jikan Abdu….
Ina godiya ina }arawa Abdu jikan Abdu…
(Kirarin Sarkin Kano)

Bashir kamar yadda aka yi bayani a baya, ]a ne ga Sarkin Kano Ado (wato Hakimin Takai), shi kuwa 'Abdu jikan Abdu' a nan, Zabiyar na nufin Abdul}adir Ado Bayero, ]aya daga

cikin manyan ‘ya`yan Sarkin Kano, Ado Bayero, jika kuma ga Sarki Abdullahi Maje Nassarawa, Sarki Abdullahi Bayero, wanda ya sa ta kira shi:

Abdu jikan Abdu.

Wannan hanya ta ambato zuri’ar basarake da Zabiyar Fada kan yi, domin cim ma shikashikan yabo, idan aka nazarci kirarin Zabiyar Kabin Argungu, za a iske cewa an tsinci dami ne a kala. Misali, a kirarin Sarki Sama takan ambatci zuri’arsa kamar haka:

Na Abdu gatarin Ya}uba
Yau ina laifin na Garba gwarzon dangi…
Na Garba ka yi ramkon gayya…
Mai da waiwaye na Muhamman…,
Na Garba }ona wanda ya take ka…,
Ka sare kaya na Muhamman…,
Da}ili }ishali ]an Ya}uba…,
Farshin wuta na Ya}uba…,
Muna Birji ka tarar da sansani ]an Yaku~a Nabame…,
Damisau na Ya}uba ana ganinka anka ]ora bi]arka…,
Hur]e mai idon ~ata na Muhamman..,
Na Garba ba ka tsoron taro…,
[an Alu ma}erin doki…,
Na Garba Sarkin nasara na…,
Ai ga zamaninka ]an Ya}ubu Nabame..,
Gira ba ta maganinka ]an Ya}uba Nabame…,
Gadan –gadan naYa}uba…,

Na Garba kai ka wa mutum ba shi yi wu wa…,

Gulbin teku mai wuyar iyo ]an Bawa…

(Kirarin Sarki Sama).

A nan, za a ga inda Zabiyar Kabin Argungu ta ambaci Sarki Yakubu Nabame har sau takwas (8), wanda uba ne ga Sarki Sama. Ta kuma ambaci Garba sau shida (6), wanda shi kuma babban amini ne ga Sarki Sama kuma ]aya daga cikin manyan jarumai a lokacinsa, sannan kuma ta ambaci Muhamman har sau uku (3), wato kakan Kabawa Sarki Muhammadu Kanta. Ta }ara ta ambaci Alu da Bawa sau ]ai -]ai, wa]anda su kuma 'yayye ne ga Sarki Sama. Ba domin komai aka ambace su ba, sai saboda a nuna dangantakarsu ko nasabarsu ga sarakin. Da ta koma ga Sarkin Kabin Argungu na yanzu, ta ambato mahaifinsa Sarki Muhammadu Mera kamar yadda take cewa:

[an Mera ba a kai maka ya}i…

(Kirarin Sarki Sama).

Ta ci gaba ta ambato Galadima Umaru, kamar haka:

{ara shirin duniya uban Galadima Umaru…,

(Kirarin Sarki Sama).

Galadima Umaru ]an majalisa ne, a masarautar Kabin Argungu kuma amini ga Mai Martaba Sarkin Kabin Argungu na yanzu, Alhaji Sama'ila Muhammadu Mera.

Idan kuma muka juya kirarin Zabiyar Daura, haka abin yake kirarin da take aiwatarwa na danganta saraki da zuri'arsa. Alalmisali a kirarin Mai Martaba Sarkin Daura, takan ambaci

‘Muhamman’, wanda la}abi ne da ake yi wa Sarki Bawo, wato kakan-kaka ga Sarakunan Daura, kamar yadda take cewa:

> Zabiya: Hawan `yan Bawo,
>
> `Y/Amshi: Hawan `yan Bawo,
>
> Zabiya: Hazo na Muhamman,
>
> `Y/Amshi: Hazo na Muhamman...
>
> (Kirarin Sarkin Daura).

To haka kuma, Zabiyar tana kiran wannan suna a kirarin da take yi wa Magajiyar Daura da na Sarakin Daura:

> ...Maharbatu}au ta Mamman
>
> (Kirarin Magajiyar Daura)

> …Magajiyar Fatimatin ta wabai,
>
> Hazo ta kimaimaye ]iyan `yan Mamman.
>
> (Kirarin Sarakin Daura)

A kuma kirarin {auran Daura, takan ambato Sarki Abdullahi (Mai Gwari), kakan Sarakunan Daura kamar yadda take cewa:

> In magajin Audu magajin tafi gwauron mashi
> {auran Daura.
>
> (Kirarin {auran Daura).

Haka ma a kirarin Sarkin Fulanin Daura, kamar yadda take cewa:

> In har magajin Ar]o…

(Kirarin Sarkin  Fulani Daura).

Ar]o dai la}abi ne na Shugaban Fulani wanda yake a matsayin Sarki. Saboda haka,wannan na nuni da cewa Sarkin Fulanin Daura, magaji ne na ‘Ar]o’, kuma duk wani da zai ri}e sarautar shi ma haka za a ce masa.

Ita ma Zabiyar Ha]eja, a dukkanin kirarin da take yi wa sarakin Ha]eja, ba ta yi }asa a gwiwa ba, tana tabbatar da cewa ta ambato wasu daga cikin zuri’ar saraki, musamman makusantansu, wa]anda kuma kowa ya san da su. Misali, a kirarin Sarkin Ha]eja tana ambaton wasu daga cikin kakanninsa da suka ri}e Masarautar Ha]eja a baya da kuma kakanninsa na dangin uwa, wa]anda su ma saraki ne, kamar haka:

Kai ne Buhari kai ne Sambo,
Kai ne gagara gammo da Sarki Jatau,
Ya mayar da gadon Sarki {adir…
Ya gaji  gadon Sarki Hari da  Haru…,
Ya mayar da gadon Sarki Karamba…,
Allah Ya ji }an [an Iya Abdu…,
Allah ya ji }an Ciroma Ali.
(Kirarin Sarkin Ha]eja).

A kirarin dabZabiyar take yi wa Sarkin Ha]eja na dangin uwa tana cewa:

…Allah Ya ji }an Turaki Abubakar,
Allah Ya ji }an  Hauwa’u
Allah ya ji }an Sa’adatu…,
Abban Halima ji }an Halima.
(Kirarin Sarkin  Ha]eja).

A nan, bayan ta ambato kakannin Mai Martaba Sarki, irin su Turaki Abubakar da Hauwa'u da Sa'adatu, ta kuma ambaci Halima wadda kakarsa ce kuma sunan ]aya daga cikin 'ya'yansa.

Haka Zabiyar take ambato zuri'ar sarakin Ha]eja, misali a kirarin Uwargidan Sarkin Ha]eja ta ambaci mahaifinta kamar haka:

Allah ya ji }an Baba Malam Sambo…

(Kirarin Uwargidan Sarkin Ha]eja).

Ita ma mai Babban [akin Ha]eja, haka Zabiyar ta ambato wasu daga cikin iyaye da kakanninta wa]anda duniya ta san su kamar haka:

Assalamu alaikum uwa 'yar Abdu,
Allah Ya ji }an Ciroma Ali..,
Allah Ya ji }an Iya Salma…
(Kirarin Mai Babban [akin Ha]eja).

Zabiyar Kazaure ma ba a bar ta ba, takan ambaci zuri'ar saraki a kirarinta, kamar yadda ta yi a kirarin Mai Martaba Sarkin Kazaure, Najib Hussaini Adamu:

Na Audu jikan Jibir…,

(Kirarin Sarkin Kazaure, Najib H. Adamu).

Audu, kamar yadda tarihi ya nuna, kakan Sarki ne wanda shi ma ya ta~a ri}e Masarautar Kazaure a zamaninsa. Shi kuwa 'Jibir', kakansa ne na gefen uwa, watau Makaman Daura, Muhammadu Jibir. Tana kuma ambato mahaifin Sarki Najib, watau Sarki Hussaini Adamu da Sarki Ibrahim Adamu (wanda wan mahaifinsa ne) da kuma matarsa Hajiya Umma, kamar haka:

> Sarki Magajin Sarki Ibrahim,
>
> Sarki Magajin Sarki Hussaini Adamu,
>
> Lafiya angon Hajiya Umma….
>
> (Kirarin Sarkin Kazaure, Najib Hussaini).

A kirarin Wamban Ha]eja kuma, bayan ta ambaci kakansa da iyayensa, Sarki Audu da Sarki Ibrahim da Sarki Hussaini Adamu, takan kuma ambato mahaifiyarsa kamar haka:

> Allah ji }an Hajiya Ade…
> (Kirarin Wamban Ha]eja).

To, haka ma a kirarin Marafan Kazaure, Hakimin Rorai, Zabiyar Kazaure ta ambato iyaye da kakannin Marafa kamar haka:

> Allah ji }an Dambo Maya}i,
>
> Allah ji }an Muhamman Tura,
>
> Allah ji }an Ummarun Dambo,
>
> Allah ji }an Madawakin Kazaure,
>
> Allah ji }an Mamudu da Mudi,

Allah ji }an Fatsima x2
(Kirarin Marafan Kazaure).

Haka wannan batu yake idan aka nazarci kirarin Sarkin Zazzau da Zabiyar Fadar Zazzau ke aiwatarwa. Alalmisali, a kirarin Sarkin Zazzau Shehu Idris, takan ambaci musamman, mahaifinsa Idirisu da kakansa Sarki Sambo da mahaifiyarsa da `ya`yansa kamar haka:

[an Idirisa jikan Sambo…,
[an Aminatu baban Aminatu..,
Baban Kabiru baban Sambo,
Baban Ali baban Umar..,
[an Abdul}adir ]an Zainaba.
(Kirarin Sarkin Zazzau).

Kamar yadda maka]a Maidaji Sabon Birni ya ambato matan Sarkin Zazzau Shehu Idris, kamar haka:

Jogara: Mijin Hadiza mijin Mariya,
‘Y/Amshi: Sarki mijin Binta da Binta, Balaraben Sarki…
(Ma}ada Mai daji Sabon Birni, Wa}ar ‘Balaraben Sarki

A iya cewa Zabiyoyin Fada suna amfani da damar cim ma yabo, watau ambaton zuri’ar saraki domin a kambama shi, a cicciba shi, a kuranta shi, a faranta masa rai, a kuma tunatar da shi musamman wa]anda suka riga mu gidan gaskiya a cikinsu. Shi kuma wanda aka ambace shi yakan ji da]i, }ila ma idan yana kusa ya yi hasafi gwargwadon hali.

#### 4.2.1.2 Addini

Addini hanya ce ta bauta wa ubangiji. Sarakuna a {asar Hausa a wannan lokaci Musulmi ne, watau suna bin tafarkin addinin Musulunci. Wannan ya sa kirarin Zabiyoyin Fadojin {asar Hausa, a kodayaushe yabon Sarakuna yake da ala}a da batun ri}e addinin Musulunci da tabbatar da shi, a masarautunsu. Sarakuna suna tabbatar da addinin ne ta hanyar kare martaba da muhibbarsa da zama abin koyi ga hukunce - hukuncen Allah. Ga abin da Zabiyar Kabin Argungu take cewa ga Sarki Muhammadu Kanta:

Zullufi – wullufi yawanyin alaihin…,
Sidi mai taimako da na Allah…,
Yau a duniya kowa ya kwana lafiya,
Ya tashi lafiya yakan yi mi}a,
Ya yi tasalimi ya tambayi al}ur'ani,
A kawo masa ya yi alwalla,
Ya mayar da gabansa gabas,
Ya ce ni wane na gode Allah,
Na gode wa Muhammadu rasulillahi…
(Kirarin Sarki Kanta).

A nan Zabiyar ta siffanta Sarki Muhammadu Kanta a matsayinsa na 'mai taushin hali kuma mai tausasawa (Zullufi Wullifi), mai taimakon talakawansa saboda Allah, mai godiya ga Allah da yawaita ibada, musamman wajen yin salla da karatun Al}ur'ani da yawaita salatin Manzon tsira, Annabi Muhammad, Salallahu Alaihim Wassalam. Wannan, ya tabbatar da cewa Sarki Kanta yana da ilimi, ilimin kuma na addinin, watau ba jahili ba ne. Sarki a

}asarsa shugaba ne na al'umma kuma jagora na addini, kamar yadda Sarkin Kotson Kano Abdulrahman yake cewa Sarkin Kano Muhmmadu Sanusi (1954 - 1963):

Jagora: Duk Sarakuna shugabanci guda su kai,
:Shi ko biyar Mamman na Abashe,
:Ga shi Sarki mai adalci,
:Ga shi Limani na Juma'a,
:Ga shi Shaihi ne na Mu}addamai,
:Ga shi Al}alin al}alai,
:Ga shi Minista ne na Alhazai,
'Y/Amshi: Sarkin Kano Mamman na Abashe.
(Sarkin Kotson Kano Abdulrahaman, a wa}ar 'Sir Sanusi Sarkin Ya}i, Zakin Daga na Abashe').

Ita ma Zabiyar Daura ba ta yi }asa a gwiwa ba, wajen jaddada ri}on addini ga Sarkin Daura kamar yadda take cewa:

Zabiya: Alhajin Saraki,
Amshi: Alhajin Saraki,
Zabiya: Gaba gare ka Allah,
Amshi: Gaba gare ka Allah,
Zabiya: Dama gare ka Allah,
Amshi: Dama gare ka Allah,
Zabiya: Nasara dai,
Amshi: Nasara dai,
Zabiya: Allah mai iyawa!

Amshi: Allah mai  iyawa…

(Kirarin Sarkin Daura).

Wannan matani na Zabiyar Daura yana nuni ga dogaro da tabbatar da ikon Allah da Sarkin yake da shi, musamman ga samun nasara a mulki da rayuwa baki ]aya, domin ya amince da Allah ne mai iya yin komai ga bawansa. Kuma shi 'Alhaji' ne ko a cikin Sarakuna. Alhaji dai, kamar yadda aka sani, la}abi ne da ake yi wa mutumin da ya je Makka, ya yi haji. La}abi ne kuma wanda ake yi wa wanda aka haifa ranar babbar salla. Sannan kuma suna ne da ake siffanta rago ko zakara ko dokin da ba shi da sofane (ratsi ko dabbare-dabbare a jikinsa). Ana iya cewa, Zabiyar na nufin ma'ana ta uku. Wato Sarkin fari yake tas a zuciyarsa, saboda ri}on addini da amfani  da hukuncinsa. To haka kuma, 'Alhajin Saraki', da Zabiyar ta kira Sarkin Daura, yabo ne da 'maka]a ke amfani da shi domin ]aukaka darajar ubangidansu.

Haka kuma, a kirarin Sarkin Sudan da na Sarkin Kudu da na Al}alin Garka da Babban Limamin Fada, Zabiyar Daura tana cewa:

Karan masana kogin malamai,
In ba }in gaskiya ma}aryata sa haye biri matsayin kishi…
(Sarkin Sudan da Sarkin Kudu).

In Alfa matambayan sani karaf da masana kogin malamai,
In ba }in gaskiya ma}aryata sa haye kogin malamai..,
(Al}alin Garka da Babban Limamin Fada)

A nan, Zabiyar Daura tana nuni ne ga wa]anda aka yi wa kirarin dominsu, ga }urewa na sani, a matsayinsu na masana/malamai na addinin Musulunci, domin dukkaninsu suna taimaka wa Sarki a fada wajen warware abin da ya shafi sasantawa da shari'a ko zartar da duk wani hukunci kamar yadda addini ya tsara.

Shi ma Sarkin Zazzau, a kirarin da Zabiyar Zazzau ke yi masa tana fa]in haka:

> Taka da }arfin Allah toya matsafa,
> Fito da }arfin Allah toya matsafa…
> Barka da zuwa toya matsafa,
> Barka da zuwa duddugen addini…
> (Kirarin Sarkin Zazzau).

Wannan yana nuni ga Sarkin Zazzau cewa basaraken ya shahara ga hana ayyukan ~arna a masarautarsa, musamman kamar yadda addini ya yi hani da su. Sannan kuma a tsaye yake wajen tabbatar da duk hukunce-hukuncen addini a masarautarsa, wato mai jaddada addini ne, kuma mai hani ne ga duk abin da ya sa~awa Islama, kamar }ona 'matsafa', wurin da ake 'tsafi' da makamantansu. Watau a tsaye yake kan tabbatar da addinin al'ummarsa, shi ya sa ma Zabiyar ta siffanta shi da 'duddugen addini'. Akwai kuma inda kirarin ke cewa:

> Taka da }arfin Allah…

Wannan na nuni da cewa Sarkin Zazzau Shehu Idris basarake ne da ya yi imani da ikon Allah da buwayarsa, saboda ri}on addini. Baya ga haka,'Toya matsafa',`yabau ne na aikatau', kamar yadda Tsoho (2002), ya bayyana 'yabau aikatau' a matsayin sunayen da suke nuna irin ayyuka da wanda ake yabo ya yi. 'Yabau aikatau' kamar yadda masanin ya yi }arin bayani, yawanci har]a]]un sunaye ne, a inda ake ha]a aikatau da suna, domin a same

su. Alalmisali ‘toya’, kalmar aikatau ce, da ta tsiro daga ‘tuya’, ‘matsafa’ kuma suna ne na inda masu bautar tsafi suke bautarsu. To haka ma ‘daddugen addini’, shi ma yabau ne na aikatau da Zabiyar ta yi amfani da shi.

Idan kuma aka nazarci kirarin da Zabiyar Kano ta yi wa Mai Martaba Sarkin Kano, Ado Bayero, za a ga yadda take jaddada ri}on addinin basaraken, musamman kasancewa kakanninsa malamai ne (Fulani Sullu~awa masu jihadi). Alalmisali, inda take cewa:

> Abin da nake mana fata ranar tashin kiyama,
> Allah sa mu tashi a tutar maluma,
> Abin  da nake fata ranar tashin kiyama,
> Mu tashi a tutar Annabi…
> Yadda ka yi aiki lafiya Allah sa ka wanye lafiya,
> Ko yau ka bar duniya alhamdulillahi..,
> Na kai shukura wurin Annabi…,
> Babu mai yi ban da Allah,
> Waye mai yi Allah bai yi ba?
> (Kirarin Sarkin Kano).

Wannan yabo na  Mai Martaba Sarkin Kano Ado Bayero a kan addini, yana nuni da dangantakar gidansu/salsarsa, kasancewarsu malamai wa]anda suka yi jihadi. A iya cewa wannan martaba ta sa Zabiyar take masa fata ko gobe kiyama, Allah Ya tashe shi tutar malamai, a tutar Manzon Allah Annabi Muhammad (S.A.W). Ta kuma }ara da yabon ayyukansa na alheri, har ma ta ce ba ta shakku ko yau ya bar duniya, sai dai a yi godiya ga Allah. Ta }arasa wannan yabo na addini, inda ta  yi nuni da halin basaraken na yarda da

ikon Allah babu kokwanto ko kuma tababa. Kamar yadda Zabiyar ke nuni da cewa, basaraken yana neman shawara ne daga malamai. Watau su ke taya shi jagoranci a kan hujjojin addinin Musulunci:

*Don ka ce a je gida a huta boka,*
*Malamai su za su fa]a ma shawara.*
*(Kirarin Sarkin Kano).*

Ita ma Zabiyar Kazaure, a kirarin Sarki Hussaini Adamu tana cewa:

Mai iko da ikon Allah,
Lafiya Sarkin Musulunci Sarkin adalci…
Ga ka Sarki ga ka malami,
Ga ka Bature ga ka Balarabe…
(Kirarin Sarkin Kazaure, Hussaini Adamu).

Sarki Hussaini Adamu, shi ne wanda tarihi ya nuna cewa cikakken ]an boko ne kuma masanin addinin da ya ri}e Masarautar Kazaure, wanda ya sami ilimin addini ba wai kawai daga malaman zaure ba, a'a ya halarci Makarantar Nazarin Koyon Harshen Larabci ta Kano, tsakanin 1951 – 1955. A cikin shekara ta 1957 – 1960 kuma, ya yi karatu a sashen Nazarin Al'amuran Afirka da {asashen Larabawa na Jami'ar Landan, inda ya sami nasarar samun takardar shaida a fannin harkokin shari'a. Domin haka ne a cikin kirarin Zabiyar Kazaure take jaddada cewa ga sarauta, ga malamta, ga Turanci, ga kuma Larabci. Sannan kuma Sarki Hussaini Adamu ya yi aiki a wurare daban-daban, a mataki daban-daban a Arewacin Nijeriya da jihar Kano kafin ya yi ritaya a 1976. Wannan dama, ta sa a zamaninsa, ya }arfafa bin dokokin addini a duk harkokinsa na mulki. Saboda haka, wannan kirari ya dace

da shi matu}a, ya gabatar da mulki da bin dokokin addinin Musulunci kuma ya kasance adalin Sarki, kamar yadda Zabiyar Kazaure ta kira Sarki, ‘Sarkin Musulunci’, domin haka adali ne.

Masu iya magana na cewa, “Barewa ba ta gudu ]anta ya yi rarrafe”. Wannan ya sa ko da Sarki Najib ]an Sarki Hussaini, ya hau gadon sarautar Kazaure, ya ci gaba daga inda mahaifinsa ya bari. Kamar yadda Zabiya `Yarsukola ke fa]i a kirarin da take yi masa:

> Lafiya mai }arfi da }arfin Allah,
> Mai iko da ikon Allah,
> Lafiya Sarkin Musulunci Sarkin adalci …,
> Ga ka Sarki ga ka malami,
> Ga ka Bature ga ka Balarabe…
> (Kirarin Sarkin Kazaure, Najib H. Adamu).

Watau kamar mahaifinsa, Sarki Najib Hussaini, Bature ne kuma Balarabe, domin yana da ilimin addini da na boko, dukka ya kwankwa]e su matu}a. Yana kuma amfani da ilimin da ya samu wajen zartar da mulki, wanda ke nuni da ri}o da addini da jaddada shi a aikace. Yabon saraki a kan tabbatar da addinin al’ummarsa da jaddada shi, na ]aya daga cikin mizanin da talaka bke auna saraki, wanda akasin haka ke rage }imarsa a idanun talakawansa.

#### 4.2.1.3 Jaruntaka

Masu iya magana na cewa:

Fa]uwar gaba asarar namiji.

A sayar da rai a nemo suna.

Jarunta ma na ]aya daga cikin ginshi}an da maka]a, musamman na fada, suke ]ora yabo a kansa. 'Jarunta' da halin nuna juriya ko }arfin hali ko bajinta (ta }arfi), a yayin aiwatar da wani abu. Wanda kuwa aka same shi da wannan hali shi ne 'jarumi' ko kuma 'gwarzo'(gwarzon namiji). A da can a {asar Hausa, ana hawan gadon sarauta ne sakamakon nuna bajinta ta jaruntaka, kafin sarauta ta koma ta fuskar addini (watau lokacin masu jihadi kafin daga baya kuma ta koma ta gado). Tarihi ya tabbatar da cewa, an ta~a zamani a {asar Hausa da idan sarauta ta fa]i ko Sarki ya yi murabus, jarumai kan fito a fafata a nemi sarauta ta hanyar kokawa, kamar yadda ya bayyana a adabin baka, wanda shi ne babban rumbun tarihin {asar Hausa da jama'arta. A baya, neman sarauta ya kasance wani ya}i ne na }arfin jiki ta fuskar kokawa ko dambe ko ya}i, saboda haka duk wanda ya rinjayi wani, shi ne yake hawa karagar mulki. {asar Katsina ta yi suna a kan irin wannan tsari na hawan gadon sarauta. Wasan kwaikwayon 'Yanka Masabki Ba}on Sanau', na East (1936:69-80), babban misali ne na wannan kokuwa domin hawa karagar mulki a masarautar Katsina. A wasan an ga yadda Korau, ba}on Sanau kuma amininsa a da, ya kayar da Sarki Sanau a kokawa, ya kuma sa wu}a ya yanka shi, wanda ya ba shi nasarar zama Sarkin Katsina. Sarki Korau na da muhimmin tasiri a Masarautar Katsina har gobe, domin sunan gidan sarautar ma 'Gidan Korau'. Korau ya shahara ne saboda jaruntakarsa wannan ya sa ake yi masa kirari kamar haka:

Korau rakasa,

Yanka masabki ba}on Sanau,

Abu gungurun maganin mai gigi,
Tukunyak }arfe sha kwaranniya,
Korau mafarin Katsina.

Wannan na nuna cewa, kokawa wani muhimmin abu ne a hawan sarauta a da. Baya ga nuna jarunta domin samun dammar hawa gadon sarauta, tarihi ya nuna cewa kafin jihadin Shehu Usman [anfodiyo, {asar Hausa tana rarrabe ne birni-birni, wanda haka ya haddasa rashin ha]in kai, wanda kuma ya yi sanadiyyar ya}e-ya}e ya yawaita tsakanin daulolin da suka zama dun}ulalliyar {asar Hausa a yau. Tarihi ya bayyana cewa, daulolin Hausa a da sun yi wa]annan ya}e-ya}e ne domin fa]a]a iko na masarautu da kuma hari irin na kamo bayi domin sayarwa ko wata bu}ata. Wannan ya sa babban burin kowane Sarki shi ne ya nuna bajintarsa ta jaruntaka, ta hanyar kai wa duk garuruwan da yake makwabtaka da su cafka. Wannan ya sa babu mai iya ri}e al'ummarsa a wannan zamani sai jarumi, domin haka a al'adance ake auna mizanin saraki da jaruntaka. Domin ya zama kariya ga jama'arsa. Hakan ya sa kirarin da ake yi wa wasu Sarakuna da ma garuruwa da dama a wannan lokaci yake da ~ur~ushin jaruntaka ta ya}i. Mawa}a kan kuranta iyayen gidansu ta hanyar za~en kalmomin da suke cicci~a su da kambama su, musamman tuna masu jaruntakar da iyaye da kakaninsu suka yi a zamaninsu. Wannan yana sa Sarakuna su ji babu kamarsu wajen nuna bajinta ta jaruntaka duk kuwa da cewa yanzu ba ya}i ake yi ba, ba kuma }arfin tuwo ake bi a za~i Sarki ba. Amma ga al'ada irin ta Hausa ko a gida ba a son ragon namiji.

Sigogin jaruntaka sun ha]a da rashin tsoro, na aiwatar da wani aiki mai cike da ha]ari da }wazo da tarar aradu da ka da }arfin hali. Wanda kuwa ya ha]a wa]annan, Hausawa na ganin shi ne 'Jarumi'. {arfin hali kuwa, hali ne na }arfafa zuciya na rashin tsoro, watau a

bigi }irji a yi wani abu komai ha]arinsa. Jan hali kuma hali ne na fuskantar ha]ari, duk kuwa da cewa an tabbatar da ha]arin da ke ciki.

Za a iya ganin wannan hali na jaruntakar saraki musamman a kirarin Sarkin Kabi, Muhammadu Kanta, wanda ya yi zamani lokacin ya}e-ya}e a {asar Hausa kuma tarihi ya tabbatar da cewa Kanta jarumi ne cikin jarumai. {asar Kabi ta ta~a zama }ar}ashin mulkin Songhai amma zamanin Sarki Kanta, }asar ta yi }arfi }warai da gaske, har ta yi wa Askiya tawaye ta ~alle,wanda ya yi sanadiyyar samun 'yancin kanta. Wannan ya sa saboda shahara ko bajintar Kabi, har }asar Barno ta ta~a kai mata hari amma ba ta ci nasara ba. Haka kuma, }asar Kabi ce }asa cikin {asar Hausa da masu jihadi ba su ci galaba a kanta ba, wanda ya sa har yau, zuri'a ]aya ke mulkinta. Jaruntar Sarki Muhammadu Kanta ta fito sarari a kirarin da Zabiyar Kabin Argungu ta yi masa, musamman ya}insa da garuruwan Fulani, kamar yadda take cewa:

> Oooh sha]i,!
> Arnan bagudu….
> Yau duniyag ga ba ta rago ta ba Kanta,
> Haka lahira ba ta rago ta ba Kanta,
> Idan da duniya gida ta matabbaci,
> Ka duba daga kassuwa idan safiya ta yi,
> Kassuwa cika za ta yi,
> Idan rana ta yi kassuwa cika za ta yi,
> Idan maraican nan ya yi,
> Wani ya sayar,
> Wani bai sayar ba,
> Da ita da jin da]in nan nata,

Kana gida za shi ko da jan masare,

Ko da zafi da garin damina gibiri- gibiri,

Ragasa tunku watarma son ya}i,

Gadaragam ba gadon kwanci ba,

Ba gadon }ai}ai ba,

Shi ke tarar da }wan}wani,

Du}usuman dusai ingantaccen dutse,

Mai uba ka sausawa ga ranar ya}i,

Ingarma anka ji anka ba ku Kanta domin ya}i,

Kowwag gane ka ya ga ya}i,

Wanda bai ganka ba bai ga mutuwa ba,

Guguwa sha da gatari,

Zangon farin wata arewa Kanta.

(Kirarin Sarkin Kabi, Muhammadu Kanta).

Wannan kirari na Sarki Muhammadu Kanta, shi ake yi wa duk wanda yake sarauta a masarautar Kabin Argungu, ba domin komai ba, sai saboda a tunatar da shi bajintar gidansu. Wannan na nuni da cewa gidansu gidan jarumai ne, domin ya yi gadon jaruntakane daga kaka da kakanni, saboda haka kada ya zama mai wargi. A kirarin, mun ga yadda Zabiyar Kabi ke yabon Sarki Kanta a kan jaruntakarsa wajen ya}i. Ta  jaddada cewa Kanta ba rago ba ne a kirarin nata, domin a kullum shirye yake idan dai maganar ya}i ce. Ba ya tsoro ballantana ya yi fargaba, gama ba a kai masa ya}i, sai dai shi ya kai. Ta yabi Sarki Muhammadu Kanta ainun, a inda tazuga shi ta hanyar kamanta ya}i (zaman duniya) da zuwa cin kasuwa cewa kasuwa idan safiya ta yi, zuwa yamma za ta cika amma idan maraice ya yi, ko an sayar, ko ba a sayar ba, gida za a ta fi. Watau abin nufi  a nan shi ne, ko a shiga fagen fama, ko kada a shiga, zaman duniya idan lokacinsa ya }are, za a mutu a bar ta,

saboda haka, gara a shiga fagen fama (ya}in), a yi suna domin ko da ya}in ko babu shi, idan lokacin tafiya barzahu ya yi, za a tafi. Masu iya magana na cewa, "Da a ji kunyar duniya gara a haukace". Ta kuma siffanta shi da ya}i saboda jaruntakarsa. Wannan ya sa take cewa wanda duk bai ga Kanta ba, to bai ga ya}i ba. Bai kuma ga mutuwa ba, domin muddin ya yi tarayya da abokin hamayya, to sunansa matacce:

Kowwag gane ka ya ga ya}i,
Wanda bai ganka ba bai ga ya}i ba,
Guguwa sha da gatari…
(Kirarin Sarkin Kabi, Muhammadu Kanta).

Ta ci gaba a kirarin Sarki Sama, kamar yadda take cewa:

*Marin ]aka mai ban haushi,*
*Rugga na gani kana yadda ka so,*
*[a mai zucciya ka ramkon gayya,*
*Na Garba ka yi ramkon gayya,*
*Kada in }ara jin gari Kibiyare,*
*Mai da waiwaye na Muhamman,*
*Rugga ta sauka zamaninka,*
*Na Garba ya yi ramkon gayya,*
*Da}ili - }ishali ]an Ya}uba Nabame,*
*Yawan magana kan sa }arya,*
*Ai ko kurum magana ta,*
*Farshin wuta na Ya}uba,*
*Na Garba }ona wanda ya take ka,*
*Gidan wani ya zama kango,*

*Ka sare kaya na Muhamman,*

*Muna Birji  ka tarar da sansani ]an Ya}uba Nabame,*

*A zamaninka rugga ta }are,*

*Yau ga wuya in suna ]urawa,*

*To su ]ura mu gani?,*

*Damamisau na Ya}uba ana ganinka anka ]ora bi]arka.*

*Ana fa]in magajin [anmusa ina Sarki ya yi?*

*Hur]e mai idon ~ata na Muhamman,*

*Na Garba ba ka tsoron taro,*

*Adamawa ta iso,*

*Zinder ta iso,*

*Barno ta iso,*

*Kano ta iso ka kare,*

*[an Mera ba a kai maka ya}i,*

*Gira ba ta maganinka ]an Ya}uba Nabame,*

*Amma a aika da shi a sami lafiya,*

*Domin birni tamanin da goma sha biyar ya tu~e na Fulani,*

*Kabawa ku yi hankali Sama ba wargi ba,*

*Ba a yi masa wargi,*

*Gadan-gadan na Ya}uba…,*

*Ka sha don ma}iya su ji kunya,*

*Hadari sa gabanka inda ka sammawa,*

*Katangar dutse daga gungura sai kallo,*

*Ai Kanta gandun aya-aya na,*

*Na gaba birjim na baya birjim!…*

*Katsantsan ra}umin da bai da akala,*

*Mai son mutuwa shi kama akalar…*

*Gabanka takuban fama bayanka masun daga,*

*Yamma gare ka 'yan kibau sun daza,*

*Kai ko da masu suna taya fansa….*

*(Kirarin Sarkin Kabin Argungu Sama).*

Kamar yadda Zabiyar Kabin Argungu ta yabi Sarki Kanta uban Kabawa, haka ta yabi Sarki Sama, musamman a kan 'ramakon gayya' da ya yi da garuruwan Fulani, wa]anda tun da can suka fafata da iyaye da kakanninsa (wannan na nuni da cewa, Sarki Sama ]a ne domin ]a ke rama cin zarafin da aka yi wa iyayensa). A lokacinsa Fulani sun kwashi kashinsu a hannu, wanda ya yi sanadiyyar barin garuruwansu, suka yi hijirar dole. Alalmisali, wani gari da ake kira 'Kibiyare', wanda Sarki Sama ya }ona shi gaba ]ayansa. A zamanin Sarki Sama ne 'ruga ta sauka', abin nufi, garuruwan Fulani suka }askanta. A kuma lokacinsa ne ya ya}i garuruwa da dama irin su Zinder da Barno da Kano kuma duk ya yi nasara,watau ya yi galaba a kansu. Wannan ya sa Zabiyar Kabin Argungu yin kambamawar zula}e, ta ce garuruwan Fulani tamanin da biyar Sarki Sama ya tu~e a zamaninsa. Ta kuma kira shi 'Arnan Bagudu' da 'Sadaukin Sarki kamar yadda ta ce:

Arnan Bagudu….

Sidi Manzon Sarakuna…

Farshin wuta na Ya}uba…,

Jigon Sarakuna ]an Muhammadu Uban Kabawa Kanta…

Sadaukin Sarakuna…

(Kirarin Sarki Sama)

A nan, 'arnan Bagudu' na nufin jarumin gaske, wanda ya}i  ba ya sa masa fargaba ko jikinsa ya yi sanyi, ko kasala har ya gudu, watau babu gudu babu ja da baya. 'Sidi  Manzon Sarakuna' kuwa, da Zabiyar ta ce na nufin sharifi mai isar da sa}o ga Sarakuna, wanda wannan sa}o ba wani ba ne, illa na ya}i, saboda jaruntaka. To haka kuma, 'Sadaukin Sarakuna', wato, Sarkin Kabi jarumi ne ko a cikin Sarakuna 'yanuwansa, saboda }arfin halinsa wajen nuna jaruntaka. A iya cewa, a da can duk Sarkin da ke da maya}a jarumai, yakan kasance jarumin namiji, wanda sauran Sarakuna suke shakkarsa matu}a. Sannan kuma kowa yake nemi abokantaka da shi.

Da kuma ta koma ga Fulani, wa]anda suka sha kashi a hannun Sarakunan Kabi, ta fara ne da yi masu shagu~e, a matsaynsu na wa]anda suka kasa nuna bajintarsu ta jaruntaka, watau ragwaye,  inda take cewa:

> Gidan Nabame mai  wuyar shigar Fulani,
> Kada in }ara jin gari Kibiyare…
> (Kirarin Sarki Sama)

Wannan matani shagu~e ne ga Fulani. A wannan lokaci ana kyautata zaton Sarakunan Fulani sun ji jiki a hannun Sarakunan Kabi. An sa su 'marin ]aka' mai ban haushi!. Suna ji suna gani aka fi }arfinsu, domin garuwansu irin su Kibiyaye an mur}ushe su suka zama tarihi a doron }asa.

Ita ma Zabiyar Daura tana yabon Sarakunan Daura da jaruntaka, kamar inda take cewa:

> Zabiya: Kakan anna,

`Yan Amshi: Kakan anna,

Zabiya: Hazo na Muhamman,

`Yan Amshi: Hazo na Muhamman,

Zabiya: Makazaki,

`Yan Amshi: Makazaki,

Zabiya: Makadodo,

Amshi: Makadado,

Zabiya: Kamunka nawa,

Amshi: Kamunka nawa…

In sha da rago saraki abokin Jiro,

Rana ta yi hwargaba rana taka,

In suke dai kimammaye,

Innuwal dare saraki abokin Jiro...

Saboda jaruntaka, Zabiyar Daura ta suranta Sarkin Daura da ‘kakan anna’ da ‘hazo’ da ‘makazaki’ da ‘makadodo’, da ‘inuwar dare’, wanda rana ke fargaba idan ta gan shi. Idan muka nazarci kirarin da idon basira, za a ga cewa ta kira Sarkin ‘kakan anna’ wanda ke da ma’anar jarumin namiji kuma gawurtacce, uban jarumai wanda ba ya fargaba, wanda ba ya tsoro, ba ya shakka. Kalmar ‘arne’ (wadda a kirarin aka kira ‘anna’), Bamagujiyar kalma ce wadda take nufin abokin gaba ko jarumi ko abokin hamayya, amma bayan bayyanar Musulunci, aka sami fa]a]a ma’ana zuwa ‘abokin gaban Allah’, wato Hausawan da suka }i kar~ar Musulunci. Haka kuma, Zabiyar Daura ta siffanta Sarkin Daura da ‘hazo’. Hazo kamar yadda aka sani, wata irin }ura ce da take fitowa a lokacin sanyin hunturu ta rufe sararin samaniya. Kamar yadda wannan hazo yake rufe sararin samaniya, to haka Sarki yake rufe abokanan hamayya a lokacin ya}i, ya sami galaba a kansu. To, haka kuma annurin

Sarki yake rufe garinsa da jama'arsa. Shata ma a wa}ar Sarkin Daura Muhammadu Bashar ta 'Lafiya Zaki,' yana cewa:

> 'Ina sarari mai kare gudun doki ]an Musa….'
>
> (Shata, a wa}ar "Lafiya Zaki Mamman baban Galadima ]an Musa)

Zabiyar ta ce Sarkin makashin dodo da zaki ne ('makadodo' da 'makazaki'). Wannan nuni ne ga irin bajintarsa na kashe dodo da zaki. Ke nan abokan hamayya a fagen daga, da Sarki yake mur}ushe su nan take. Hak**a** kuma, kasancewar rana 'ubangijiya' (saboda an yi kirarin lokacin da ake da sauran ~ir~ishin addinin gargajiya), amma wannan bai hana ta fargaba ba, a lokacin da ta ga Sarkin Daura a gabanta, saboda jaruntakarsa. Wannan ya sa Zabiyar ta kuma kira shi 'inuwar dare', duk kuwa da cewa aljani ne ka]ai ke da inuwa idan dare ya yi, amma saboda buwayar Sarki, ta ce shi ma yana inuwa da dare', watau Sarkin tamkar aljanin ne saboda jaruntarsa. Wannan duk nuni ne ga jaruntakar Sarkin Daura, kamar yadda Zabiyar take fa]i a kirarinta. Ita ma Magajiyar Daura, Zabiyar tana nuna bajintarta ta jaruntaka kamar haka:

> Giwa shigayi buwayi…,
> Gida zaman gida ga giwa gagara cinnaki,
> Baje –bajen toranke karnan tada damisa…,
> In sa abuyar tsohon zaki.
> (Kirarin Magajiyar Daura)

Wannan kirari ya kira Magajiya ‘giwa’ saboda }arfin ikonta a Masrautar Daura. Giwa, dabba ce wadda ko a dawa ta buwayi abokan hamayya saboda jaruntakarta. Wannan kirari na nuni da cewa Magajiya duk da kasancewarta mace, wadda bisa ga al’ada, yawanci take zaman gida, domin halitta ce mai rauni. To, amma, ita Magajiyar Daura ta zama akasin haka, hasali ma, ita duk abin da ta sa gaba, sai ta ga bayansa. Ta }ara ta suranta ta da ‘karnan tarar da damisa’, saboda buwayarta. Ke nan, Zabiyar Daura ta yi amfani da `yabau siffantau’, ta yabi Magajiyar Daura. Sanin kowane mafarauci ne cewa damisa ta fi }arfin kowane karen farauta sai gawurtacce, kamar yadda ba kowane karen farauta ke kama goggon biri ba. A sauran kirarin da take yi wa sauran sarakin Daura, tana yawan ambaton:

In ]an /’yar/’yan sararin mutu ko dai ri}o,

]an/’yar/‘yan mu je mu da anna.

(Kirarin Sarakin Daura).

Wannan na nuni da jaruntar iyayensu (sarakin Daura) na masu ra’ayin ko a mutu ko a yi rai a fagen fama, watau jan hali, cikin nau’o’in jaruntaka. A kirarin Markan Daura, Zabiyar tana cewa:

‘In da zaman homa ]an }arfaffa sandar }arfe da zaki Marka.’

(Kirarin Markan Daura)

Kalmar ‘}arfaffa’, kalma ce da ke siffanta }arfin abu ko kuma mutum ko wani abu mai }arfin gaske. Haka kuma, ‘}arfaffa’, kalma ce da take nufin ‘isar mutum’. Babu shakka, wajen nuna jaruntakar Marka, daga kakanni da iyayensa a matsayinsu na jarumai, kuma isassu a matsayinsu na saraki, wannan kirari ya yaba masu ainun. Domin Zabiyar ta yi

amfani da `yabau siffantau', ta siffanta Markan Daura '}arfaffa' kuma' sandar }arfe', wadda ba za a kwatantata da ta itace ba. Ga wani misalign kuma yadda take cewa a kirarin Galadiman Daura:

Ci da ma}iya,
Sha da ma}iya,
Kaf cizo,
Ka fi dawan ya}i…

(Kirarin Galadiman Daura).

Wannan ma yana nuni ne da jaruntar Galadima, wanda ke gamawa da abokan gaba nan take, su zama labari. Sannan saboda karimcinsa yake ciyar da shayar da bayin ya}i da suke }ar}ashin kulawarsa, a matsayinsa na shugaban rundunar maya}a a Masarautar Daura. Galadima da {aura su ne manyan maya}a a Masarautar Daura, wanda ya sa har gobe a lokutan bukukuwan salla }arama da babba, da sallar gani, suke ri}e mashi, su kuma soka a }asa a lokacin da suka kawo cafka gaban Sarki. A nan, Zabiyar ta yi amfani da `yabau aikatau', a inda take cewa:

'Ci da ma}iya sha da ma}iya.'

Haka kuma, Zabiyar Daura a kirarin Dur~in Daura tana cewa:

In wanda mara kunya ke kunya,
Wanda mara tsoro ke tsoro….
(Kirarin Dur~in Daura).

Sarautar ‘Dur~i’ a Masarautar Daura, a da can, sarauta ce da ake ba jajirtaccen jarumi. Saboda haka, wannan kirari na nuni da jaruntakar Dur~i, wanda mara kunya ke kunyarsa, haka kuma mara tsoro ke tsoransa saboda ba shi da wargi. Dur~i jarumi ne cikin jarumai domin haka ake shakkarsa. Wannan ya sa a duk inda aka sami jarumi, kasala da wargi abubuwa ne da ba su da muhalli a wajensa.

Zabiyar Zazzau, a kirarin Mai Martaba Sarkin Zazzau Shehu Idris, tana cewa:

> Taka/fito da }arfin Allah ni}atau,
> Fito /shigo da }arfin Allah ni}atau…
> (Kirarin Sarkin Zazzau).

‘Ni}atau’, kalma ce ta amsa kama, wadda take nufin ‘}arfaffa’. A nan, kirarin Zabiyar ya suranta Sarki da }arfaffa mai ni}e abokan adawa saboda }arfin jaruntarsa. Wanda kuwa aka siffanta da ‘}arfaffa’, to lallai babu kasala ko wargi tare da shi.

#### 4.2.1.4 Iya Mulki da Ri}on Jama’a

‘Iko ko sarauta’ ko kuma ‘gudanar da harkokin hukuma kan jama’a’ shi ne ‘mulki’. Idan aka ]auki ma’ana ta biyu za mu iya cewa, ‘gudanar da harkokin hukuma kan jama’a’, shi ne ya fi dacewa da ‘mulki’. Watau damar da shugaba yake da ita ta umarni da hani, ba tare da son kai ba. Wannan ya sa ake son shugaba mai ha}uri da gaskiya da adalci, sannan kuma mai son jama’arsa da tausaya masu a kowane hali.

A zamantakewa ta yau da kullum, akan so mutum mai gaskiya da ha}uri da adalci, musamman ma a ce wannan mutumin jagora ne na jama'a. Wannan ya sa Hausawa suke da karin magana a kan wa]annan kyawawan ]abi'u a kodayaushe domin tausasa zuciya. Ga misalai nan:

- Gaskiya ta fi Kwabo;
- Gaskiya dokin }arfe;
- Gaskiya nagartar namiji;
- Gaskiya haske ce, }arya wula}anci ne;
- Maha}urci mawadaci;
- Ha}uri maganin zaman duniya;
- Babba juji ne;
- Ha}uri hatsin tukunya ne ba ya wuyar }arewa;
- Adalci yakan ]aukaka al'umma;
- Allah mai hukunci da adalci;
- Addu'ar mai adalci tana da iko da yawa cikin aikinta;
- Adalci ginshi}in al'umma.

Bisa al'ada, muhimman abubuwan da ake bu}ata daga shugaba na gari, shi ne ya zamanto adali, mai tausayin jama'arsa, sannan ya ri}a kula da su, ya ba kowa ha}}insa, wato ya yi adalci. Wannan na nuni da cewa, iya mulki (shugabanci da ri}on jama'a), a wajen Sarakuna abu ne muhimmi, wanda ya sa maka]a suke siffanta su da shi. Zabiyar Kabin Argungu, a kirarin Sarki Sama, ta siffanta shi da '*gaskiya'*. Gaskiya tana da fa'ida a hul]a tsakanin jama'a musamman jagora da mabiyansa. Haka ne ya sa ko a tsakanin sauran jama'a, a kullum mai gaskiya yakan kasance wanda kowa yake amincewa da shi.

Zabiyar Kabin Argungu, a kirarin Sarki Sama ta siffanita shi da gaskiya, kamar yadda take cewa:

> Na Bawa hankalinka gare ka,
> Sama Kowwag }i gaskiya ka }i shi,
> Yawan magana kan sa }arya,
> Ai ko kurum magana ta,
> Jigon Sarakuna ]an Muhammadu Kanta,
> Sadaukin Sarakuna na Zarmakwai mai danda,
> Mulkinka ya wuce 'yar boda…
> (Kirarin Sarki Sama).

Wannan na nuni da cewa kamar yadda Zabiyar Kabin Argungu ta fa]i a kirarin, Sarki Sama mai gaskiya ne. Mai gaskiya kuwa shi ke iya ri}on amana. Kamar yadda ta ce, gaskiyar basaraken ta sa bai cika magana ba, domin yawan magana kan sa a yi }arya. A maimakon magana, a zamanin Sarki Sama, sai dai a gani a aikace, wajen gudanar da mulki da duk abin da ya dace a yi ko a bari, ko kuwa a ce, a duk abin da ya sa gaba, sai ya ga bayansa. Ke nan, yana da dattako, domin babba ba ya magana biyu. Ta kuma kira shi 'jigo/sadaukin Sarakuna', duk dai, saboda }warewarsa wajen iya ri}e jama'arsa. Da ta ci gaba kuma, ta bayyana basaraken da halayyar 'natsuwa', wato wanda yake cikin hankalinsa a kodayaushe, yake kuma zurfin tunani kafin ya aikata wani abu. Da ma dai, komin cancantar mutum ga Sarauta, muddin ba kamilalle ba ne dole a za~i wani. Ta tabbatarwa Sarkin da ke gadon mulki, cewa mulkinsa ya kai inda ba a tsammani, saboda shi ne Muhammadu Kanta, har zuwa Sarakunan Kabi, kakanni da iyayensa, ya zuwa mahaifinsa, marigayi Sarki

Muhammadu Mera. Wannan na tabbatar da }warewar Sarakunan Kabin Argungu wajen iya mulki, kamar yadda ta ce a kirarin Sarki Kanta:

> ‘Zullufi –wullufi yawanin alaihin.’
>
> (Kirarin Sarki Kanta).

‘Taushi da tausasawa’ke nan, wanda ya yi nuni da cewa Sarki Kanta mai taushin hali ne kuma mai tausasawa. Wannan ya tabbatar da halin basaraken na tausayi kuma mai aiki da tausayi, duk kuwa da cewa an san halinsa na nuna jaruntaka a fagen fama, wanda ke cire tausayi a zukatun jarumai. To amma a tsakaninsa da jama’arsa mutum ne mai taushin hali da tausaya masu matu}a.

A sha’anin mulki, ana son shugaba mai ha}uri saboda ha}uri na ]aya daga cikin muhimman sinadaran cim ma rayuwa, wa]anda suke kai mutum ga nasara, musamman ha}urin babba da wa]anda suke }ar}ashinsa. Wannan ya sa Bahaushe kan ce, “Babba juji ne”. Zabiyar Daura, ta suranta Sarkin Daura da ha}uri, kamar yadda take cewa:

> Zabiya : Dosono,
>
> `Yan Amshi: Dosono,
>
> Zabiya : Ai ya fi kyau,
>
> `Yan Amshi :  Ai ya fi kyau,
>
> Zabiya: Sannu ta fi kus…
>
> `Yan Amshi : Sannuta fi kus…
>
> (Kirarin Sarkin Daura).

Kalmar ‘dosono’, tsohuwar kalmar Hausa ce da take nufin ‘mai ha}uri’. Zabiyar ta nuna muhimmancin yin ha}uri, musamman ga shugaba. Kirarin ya jaddada cewa, yin ha}uri ya fi rashinsa, domin kuwa “sannu ta fi kusa”, kamar yadda ta fa]i a cikin kirarin. Ke nan, duk wanda ya yi ha}uri, a kwana a tashi zai cim ma burinsa. Dr. Mamman Shata ya kira Marigayi Mai Martaba Sarkin Daura Muhammad Bashar ‘damo’, saboda ha}urin basaraken:

Jagora: Baba damo Bashar ]an Sanda,
: Yana kallo ake cutar shi,
: Bai ce wa mutum komai ba,
: [an Mamuda gwauron giwa,
‘Y/Amshi: Kwana lafi mai Daura,
: Jikan Abdu gwauron giwa.
(Shata, wa}ar ‘Kwana lafiya mai Daura’)

Ita ma Zabiyar Ha]eja, a kirarin Tafidan Ha]eja da Jarman Ha]eja tana cewa:

Rumfa sha shirgi,
Kwano ba ka karaya….

Wannan na nuni da ha}urin sarakin kamar yadda rumfa take, komai aka kwaso, aka jaji~o ake ]ora mata a sama. Ta kuma suranta su da ‘kwano’, wanda ta ce, ba ya karaya. Akasin tukunyar }asa wadda }warinta bai kai na kwano ba. Wannan na }ara nuni da cewa a mulki

ba a son basarake mai nuna karaya. Ana bu}atar  gwarzon namiji kuma gawurtacce domin ya ba jama'arsa }arfin gwiwa na iya ri}e su da sama masu kariya, musamman lokacin da ake ya}e –ya}e.

Zabiyar Kano a kirarin Sarki Ado Bayero tana cewa:

> Allah mai da mu birnin Kano gari,
> Mun zo mun yi ziyara wacce ka taya ba naci,
> Gaisuwa kuwa ba a yin muguwa…
> Amanar Sarki autan Bawo,
> Magajin Ila Garba Magajin Garba…,
> Tun da na zo garin nan, kun ri}e kayan amana,
> Bayan mutuwar Abdullahi Dabo kun ri}e amana,
> Ya'alla shi gafarta masa,
> Ya matsa ya bar mu kun ri}e kayan amana…,
>
> (Kirarin Sarkin Kano).

Ana tsammani Zabiyar Kano ta aiwatar da wannan yanki na kirarin a lokacin da Sarkin Kano ya kai rangadi ga Sarakunan {araye da Rano a garuruwansu, ko kuma bayan sun dawo. Ziyara kuwa, ]aya daga cikin muhimman ayyukan da suka wajabta ga shugaba ne da ke nuni da iya ri}on jama'arsa, domin sanin halin da suke ciki. Zabiyar ta fito da wannan kyakkyawan aiki da Mai Martaba Sarkin Kano Ado Bayero yake yi, na kula da jama'arsa. Ta kuma tunatar da Sarkin Rano amanar Sarki da take kansa, kasancewarsu wakilai. Da ta koma kan Sarkin Kano Ado, ta yaba ta kuma jinjina masa da halin ri}e amana da ya gada daga iyayensa, kamar yadda ta ce:

Bayan mutuwar Abdullahi Dabo kun ri}e amana…

(Kirarin Sarkin Kano).

Akwai kuma inda Zabiyar Kano take cewa:

Yadda muka zo lafiya babu }ishin ruwa babu yunwa,
A gidan Alhaji Jakada na yi godiya babu }ishin ruwa babu yunwa,
Har mu koma gida dai lafiya…

Wannan nuni ne na halin iya mulki da ake bu}atar shugabanni su kasance suna da shi, na kula da wa]anda ke }ar}ashinsu, musamman ci da sha, domin abin tir ne ga shugaba, ya bar wa]anda ke }ar}ashinta cikin }ishi da yunwa da ma rashin sutura ta }warai da muhalli. Wannan ya sa maka]an fada ke shiga ta manyan riguna da al}yabba da rawani irin na iyayen gidansu, kasancewa su suke ba su kyautar wa]annan kaya. Kamar yadda Zabiyar Kazaure ('Yarsukola), ta yabi sarakin Kazaure da adalci da taimako da kuma tausayi.

Lafiya Sarkin Musulunci, Sarkin adalci,
Sarkin Gari, Sarkin Noma…,
Ramar shuka ba ki mugunta…,
Allah Ya taimaki Sarki,
Sarki ya taimaki jama'arsa.
(Kirarin Sarkin Kazaure, Ibrahim Adamu).

Zabiya `Yarsukola ta yabi Sarki Ibrahim da adalci da kuma taimakon jama'arsa da tausaya masu. Ta kuma kira shi 'rama'. Rama' wani irn tsiro ne mai doguwar sanda, wanda ake dafa ganyensa a yi kwa]o, ko a sa a fate, ana kuma amfani da ~awonsa wajen yin 'igiya'.

Wannan na nuni da cewa, basaraken ya kasance mai taimako da kula da jama'arsa matu}a, yadda a kowane hali ake amfani da shi, kamar kuma yadda ta kira shi 'Sarkin noma', wato manomi ne na gaske,ba irin sarakin da ke dogaro daga baitulmali ko talakawansu ba. A kirarin Sarki Hussaini Adamu da na Sarki Najib Adamu ta maimaita wannan matani:

Lafiya Sarkin Musulunci Sarkin adalci,
Sarkin gari, Sarkin noma…,
Allah Ya taya ka ri}on jama'a…
Kirarin Sarkin Kazaure Hussaini Adamu).

Lafiya Sarkin Musulunci Sarkin adalci,
Ramar Shuka ba ki mugunta,
Allah Ya }ara wa Sarki Lafiya da adalci…,
Allah Ya taya ka ri}on jama'a.
(Kirarin Sarkin Kazaure Najib Hussaini).

A kirarin Sarki Hussaini, Zabiya ta yi }ari a inda nan kuma ta ro}i Allah Ya taya shi ri}on jama'arsa. Watau Allah ya }ara taimaka masa wajen jagorancin al'ummarsa. Ke nan, a zamaninsa ya ri}e jama'arsa cikin ha}uri da amana da adalci da tausayi.

Zabiyar Kazaure ta biyu, Zabiya {arangiya ta yaba da }warewa da jajircewar Sarkin Kazaure Najib wajen iya ri}on jama'arsa:

Ni ce Zabiyar Mai Martaba Najib ]an Hussaini,
Ma so zama da shi ya bi doka a Kazaure…,
Kazaure namijin gari,
Garin Najib ]an Hussaini…

(Kirarin Sarkin Kazaure, Najib Hussaini).

Wannan na nuni da cewa zamanin Sarki Najib Hussaini, an sami zaman lafiya da kwanciyar hankali a masarautar Kazaure, domin an sami bin doka. Wannan ne ya sa Zabiya {arangiya ta kira Kazaure ‘namijin gari’.

#### 4.2.1.5 Kyauta

A rayuwa babu mai son marowaci ballantana maro}i, Bello (1976:28). Wannan ya sa tun da ‘kyauta’ ita ce babban abin da maigida zai yi wa maro}i, ya zama dole, shi kuma maro}i ya yabi ubangidansa da ita. Maka]a, musamman na fada suna yaba kyautar da iyayen gidansu suka yi masu, ta hanyar yawaita godiya, wanda hakan kan sa iyayen gidansu su ji da]i, su }ara kyautar da suke masu ko domin jama’a su ji, abokanan hamayya kuma jikinsu ya yi sanyi, su tsorata. Masu iya magana na cewa, “Yaba kyauta tukwici”. Bisa ga al’ada, a kodayaushe tunanin al’umma ya karkata da cewa hannun shugaba ke sama, domin shi ne mai bayarwa, jama’arsa kuwa masu kar~a. Masu iya magana ma na cewa,“Laifin babba rowa, laifin yaro }yuya”. Ke nan, a al’adar Hausa ana auna mizanin saraki da kyauta da kuma kyautatawa. Kafin Hausa (1997), ya bayyana cewa Sarakuna kamar kowane irin ]an Adam, mutane ne masu sha’awar nisha]i da son girmamawa da kambamawa. Domin haka, sukan ji da]i idan an yi masu kirari, kuma kamar yadda ]an tauri ko ]an dambe kan fito fili ya nuna jin da]i idan an kambama shi, yadda zai karya wu}a, ko ya mur}ushe wanda ya fi }Sarfinsa, to haka Sarki yakan nuna ya harzu}a idan kirari ya shige shi, ta hanyar yin gagarumar kyauta. Za a iya cewa, Zabiyoyin Fada suna }o}ari wajen yaba kyautar da aka yi

masu, watau ba su kasance butulu ba. Alalmisali, Zabiyar Kabin Argungu a kirarin Sarki Sama tana cewa:

> Da arzikinka ]an Ya}uba Nabame,
>
> Dukiya ta isa kaya sun isa…
>
> (Kirarin Sarki Sama)

Wannan na nuni da cewa zamanin Sarki Sama arziki ya wadaci kowa a masarautarsa, musamman ma, rukunin mai matanin (maro}an fada). Idan aka ce arziki ya wadaci jama'ar wani basarake, ko dai saboda hannunsa a bu]e yake ko kuma a ce iya gudanar da mulki ya sa jama'a suka sami walwala, kowa ya tashi tsaye ya nemi na kansa saboda kwanciyar hankali, wanda ya yi sanadiyyar wadata da walwala. Kyauta na ]aya daga cikin ]abi'un da ke kyautata zamantakewa. Alamisali, ko tsakanin miji da matarsa ko tsakanin ]a da mahaifi. Wannan ya sa masu iya magana na cewa:

> 'Alheri dan}o ne.'

A iya cewa Zabiyar Kano ta yaba kyautar Sarkin Kano Ado Bayero matu}a, domin godiya ce ta mamaye kirarin da ta yi masa, saboda hannun baiwa na basaraken. Kamar yadda take cewa:

> Ina godiya Lami]o ka bi ya ni,
> Goyon Malam Maje ka biya ni,
> Kyauta ba biyan bashi ba…
> Ina godiya ina }arawa na gode,
> Tsintsiya ma]aurinki ]aya,

Kun biya ni na gode,

Ina godiya ina }arawa na gode,

Kuma na yi bege mai tada rai,

Allah ji }an Sarkin {araye Ibrahim…

Ranar sunan Hadiza rannan riga da doki,

An biya ni ba bashi ba,…

Sarki da hakiman Kano na gode,

Autan Bawo Mai Ila ka biya ni na gode ma,

Ina godiya ina }arawa ‘yan Fulani sun biya ni,

Kyauta ba biyan bashi ba,

Riguna da riguna na gode,

Turmi da turame,

Ba na dakan gumba ba…

Irin Yusufa Nadabo ka biya ni,

Ka biya ni na gode ma,

Ina godiya ina }arawa na gode,

Yadda ka yi aiki lafiya Allah sa ka wanye lafiya,

Ko yau ka bar duniya Alhamdulillahi,

Mijin mai kitse da doki,

Jikan Umma Kaltume,

Na yi godiya na gode jikan Yaji,

Allah ja mana kwana mai yawa,

Godiya uwar Hadiza na gode uwar Yalwa cikin hairan…,

Ina godiya da arzikin Abdu jikan Abdu…,

Ina godiya ina }arawa na gode,

Godiya ta tabbata ina godiya na gode,

Amma Allah }ara sulalla mai yawa…,

Alhamdu lillahi kyautar Allah ta yi,

Allah kiyaye mana Sarkin Kano Ado Bayero,

Allah ja masa kwana mai yawa,

Ka kama sulalla toran giwa na Abdu,

Mu ko mu je su ba mu riguna da zannuwa,

Allah sa ka wanye lafiya,

Na yi godiya na gode ubangijin Keftin Rilwanu,

Mai tagwayen mata…,

Ko yau ka bar duniya Alhamdu lillahi,

Na ce na gode Allah,

Na kai shukura gun Annabi,

Ina godiya ina }arawa Abdu jikan Abdu,

Ina godiya Sarkin Kano Alhaji Ado,

Na gode da arzikinku…,

Na yi godiya na gode,

Sarki mai garin Birnin Kano,

Allah taimaki jikan mai suka da mashi,

Ina godiya da Aisha Fenda…,

Ina godiya da arzikinta na yi godiya na gode,

Ina godiya uwata Nana,

Godiya uwar Nafsi da A'i sun biya ni,

Na yi godiya uwar Fulani Balki,

Na yi godiya uwar Fulanin {araye,

Uwar Fulanin [anbatta,

Sun biya ni ba bashi ba,

Ina godiya da arzikinki Mai Babban [akin Kano,

Uwar gari tasa…

Ina godiya gare su ‘yan farare,

Sun biya ni ba bashi ba.

(Kirarin Sarkin Kano).

Idan aka nazarci kirarin Zabiyar Kano, za a ga cewa yabo da ya danganci kyauta, shi ya mamaye kirarin. Ta yi godiya ta }ara godewa, wanda ya sa har ta yi masa addu’a da fatan alheri gobe kiyama, kamar yadda take cewa:

Ina godiya ina }arawa na gode,

Yadda ka yi aiki lafiya Allah sa ka wanye lafiya.

Ko yau ka bar duniya Alhmadulillahi…

Allah kiyaye mana Sarkin Kano Ado Bayero,

Allah ja masa kwana mai yawa…

Riguna da riguma na gode,

Turmi da turame…

(Kirarin Sarkin Kano).

Ta kuma juya ta yi godiya ga Mai Babban [akin Kano (mahaifiyar Sarkin Kano Ado Bayero) inda kuma take cewa:

Ina godiya da arzikinta na yi godiya na gode…

Ina godiya da arzikinta mai Baban [akin Kano,

Uwar gari tasa…

(Kirarin Sarkin Kano).

Zabiyar ba ta yi }asa a gwiwa ba, ta kuma yaba wa Fulanin Kano (dukkan sarakin Kano), kamar yadda ake yi masu la}abi da ‘Fulani’ kasancewarsu zuri’ar Fulani a Sarautar Kano):

Ina godiya ina }arawa na gode,
Tsintsiya ma]aurinki ]aya…
Ina godiya ina }arawa ‘yan Fulani sun biya ni..
Ina godiya gare su ‘yan farare,
Sun biya ni ba bashi ba.

(Kirarin Sarkin Kano).

Ta }ara da godiya ga marigayi Sarkin {araye Ibrahim saboda irin kyautar mamakin da ya yi mata ranar sunan Hadiza ]iyarsa, sannan kuma ta yi juyayin rasuwarsa, kamar yadda take cewa:

Ina godiya ina }arawa na gode,
Kuma na yi bege mai tada rai,
Allah ji }an Sarkin {araye Ibrahim…
Ranar sunan Hadiza rannan riga da doki,
An biya ni ba bashi ba.

(Kirarin Sarkin Kano).

Su ma Hakiman Kano ba ta bar su a baya ba:

Sarki da Hakiman Kano na gode,
Autan Bawo mai Ila ka biya ni na gode…
(Kirarin Sarkin Kano).

Akwai kuma inda Zabiya Ajuji ke cewa:

Mai zubau kare –da kure…

Ina godiya da arzikinka mashashan Kano na Audu…

(Kirarin Sarkin Kano).

Wannan na nuni da kyautar Sarkin Kano wadda ba ta da iyaka, domin a kullum cikin bayarwa yake ba tare da gajiyawa ba. Irin wannan godiya da ta mamaye kirarin da Zabiyar Kano ta yi wa marigayi Sarkin Kano Ado Bayero, za a iya cewa yana da nasaba da kirarin Kano da ke cewa:

Kano ta Dabo cigari,
Jalla babbar Hausa,
Gari ba Kano ba dajin Allah,
Kamisilika alfun,
Yaro ko da me ka zo, an fi ka,
Kano, birni mai mata mai mota,
Tunjimin gari mai Dala da Gwauron Dutse.

Adabi a matsayinsa na hoto da ke nuna rayuwar al'umma, kirarin Kano ya tabbatar da albarkar dukiya a garin. Kano cibiyar ciniki ce ta {asashen Hausa, wadda kuma a sanadiyyar kasuwanci ta zama matattarar al'ummomi da dama na {asashen Hausa da ma Afirka. Wannan ya sa akwai wadatar arziki, saboda haka yabo da ya ji~anci kyauta ya mamaye kirarin da Zabiyar Kano ta yi. Ba abin mamaki ba ne domin, "Inda akwai nan ake bayarwa". Ya tabbata da irin wannan zungureriyar godiyar da Zabiya Ajuji Maitazargade ta

yi, kamar yadda aka ba ta, ba ta yi butulci ba, ta yi godiya ta }ara ta gode. Kodayake masu iya magana na cewa, “Fa]awa mai zuciya biki ba mai ku]i ba”.

Shi ma maka]a [an}wairo, haka ya yaba da kyautar Mai Martaba Sarkin Kano Ado Bayero, kamar yadda ya ce:

Jagora: Sarki mai kyautar doki,
: Sarki mai kyauta riguna,
: Sarki mai kyautar wanduna,
: Sarki mai kyautar kuftoci,
:Sarki mai kyautar alkyabba,
: Sarki mai kyautar rawunna,
: In dai yai maka kyan }awa,
: Ya mi}a ma ku]]i fan ]ari,
`Y/Amshi :Abin shagali ya samu.
([an}wairo, a wa}ar ‘Ba takura kaurin gaba, na yarda da Sarki Ado’)

Akwai kuma inda [an}wairo yake cewa:

Daura: kun ba ni ku]i da motoci,
`Y/Amshi: Kanawa na Dabo na gode,
: Ga ilimi ga kyauta.

Sunan kowane irin mawa}i ‘maro}i', idan kuwa maro}i bai yi ro}o ba mai zai ci? Su kansu maka]an sukan kira ki]a ro}o, wani lokaci su kira wa}a, ‘ro}o’. Idan za su fita fada, sukan kira wa}a ‘ro}o’ domin a duk lokacin za su fita fada su yi wa}a ba sa cewa, ‘za mu je mu yi wa}a’ ba, sai dai, ‘za mu je mu yi ki]a’, ko ‘za mu je mu yi ‘ro}o’. To, haka nan kuma, maka]i na da damar kai tsaye ya ce, ‘a ba ni kaza’ ko kuma ya yi nune a kan haka, a gane ‘ro}o’ yake yi. Wannan ya sa bayan Zabiyar Kano ta yi godiya ta ha]a da ‘ro}o’ da neman iri, kamar yadda take cewa:

Allah kiyaye mana Sarkin Kano Ado Bayero,
Allah ja masa kwana mai yawa,
Ka kama sullalla toron giwa na Abdu,
Mu ko mu je su ba mu riguna da zannuwa…
Allah sa ka ba ni yadi,
Da ma ka duba fanka ka ba ni,
In je in gyara gidan maigidandan…
(Kirarin Sarkin Kano)

Ro}o a wajen maro}in fada yana da dabaru hu]u, ro}o kai tsaye ko nune ga abin da ake so ko zugar ro}o ko kuma godiya gabanin kyauta. A nan, a ce Zabiyar Kano ro}o ne na nune ta yi ga abin take so, kamar yadda ta yi wa Sarki Kano fatan ya samu sulalla, su kuwa su lalla~a wurin matansa, a ba su zannuwa da riguna kasancewa samu ga maigida wadata ce ga iyalinsa. Ta kuma }ara ta yi ro}o kai tsaye, inda ta yi ro}o a ba ta yadi. [ankwairo a wa}ar Hassan Katsina, ya ro}i mota ta hanyar nune, kamar yadda yake cewa:

Jogora : [ankwairo ya yi mafarki,
Amshi : Yana jin }aran injin,

Jogora : Ko mota za a ba shi,

Amshi : Albarkacin Ciroma,

Jogora: An koma an ba ka mota.

([an}wairo, a wa}ar 'Baiban tsoro sadauki, Hassan [an Shehu Malam).

### 4.2.2 Habaici

A iya cewa baya ga jigon yabo, akwai }anana da suka }unshi 'habaici. Wasu daga cikin Zabiyoyin Fada da aka nazarci kirarin da suke yi wa saraki, musamman na Sarkin kansa, a }o}arin yaba masa sukan fake da yi da abokanan hamayya, wato su yi habaici. Maka]a, suna amfani da habaici domin su yi da abokanan hamayya a fakaice saboda farantawa iyayen gidansu. Habaici kamar yadda aka sani, magana ce ta hakima mai ~oyayyiyar manufa wadda ake yin ta a fakaice da nufin isar da sa}o. Ana la}aba habaici da wani abu da ya faru, kuma galibi habaici ya fi yawaita inda kishi yake ko }yashi. A kan sami habaici a wa}o}i da kirarin fada, musamman bayan da aka nemi sarauta, wani ya yi nasara, wasu daga cikin wa]anda suka yi takara suka }i dangana. A maimakon haka suka yi jayayya, suka zama `yan adawa, masu hassada. A ta}aice a ce lokuta da dama a adabin fada an fi yi wa abokan hamayya habaici.

Adamu (2008:133-135), ya kasa rabe–raben nau'o'in habaici wa]anda suka zuwa kashi biyar (5, ) da suka ha]a da 'hannunka mai sanda' da 'gugar zana' da 'zagi a kasuwa'da mai zuwa da 'nau'in karin magana' da kuma 'habaici a cikin wa}o}in baka'. Kamar yadda Adamu (2008:134), ya yi bayani, maka]an baka suna tsarma habaici a cikin wasu ]iyan

wa}o}insu wanda zai iya ]aukar sigogi daban–daban gwargwadon manufar da maka]i yake so ya isar ga jama'a. A nan, za a iya cewa Zabiyoyin Fada a matsayinsu na maro}an fada, su ma sukan sa habaici a cikin kirarin da suke yi wa saraki, wanda a wani lokaci yakan zama shagu~e, ko hannunka mai sanda. Ana kuma tsintar habaici mai sigar karin magana.

Zabiyar Kabbin Argungu a kirarin Sarki Sama tana cewa:

….marin ]aka mai ban haushi,
rugga na gani kana yadda ka so,
...gidan wani ya zama kwango,
.... rugga na gani kana wadda ka so,
…. Gidan Nabame mai wuyar shigga ga Fulani…
(Kirarin Sarki Sama)

Wannan nau'in kirarin shagu~e ne zabiyar ke yi wa Fulani, wa]anda Sarki Sama ya fafata da su a wasu ya}e-ya}en da suka yi. A iya cewa dukkan ~angarorin biyu sun ji jiki. Haka kuma, Zabiyar tana cewa:

…. gira ba ta maganin ]an Yakubu Nabame,
…. mai fushi da kai ya wahala,
.... gulbin teku mai wuyar iyo ]an Bawa,
.... katangar dutse daga gungura sai kallo...
(Kirarin Sarki Sama)

Idan aka yi nazarin wa]annan maganganu da idon basira, Zabiyar Kabin Argungu tana yi da abokanan hamayya ne, musamman wa]anda suka }i ba da kai bori ya hau. Watau wa]anda

bayan da aka yi takarar sarauta suka fa]i, suka }i amincewa da haka, a zahiri ko a ba]ini saboda haka, aka yi amfani da shagu~e aka yi da su a fakaice. Misali, tana cewa:

Gira  ba ta maganin ]an Yakubu Nabame,

… mai fushi da kai ya wahala…

(Kirarin Sarki Sama)

Zabiyar ta kuma yi amfani da nau'in habaici mai karin magana kamar yadda take cewa:

'…. Katangar dutse daga gungura sai kallo…'

(Kirarin Sarki Sama)

Wannan duk yana nuni ga buwayar Sarki ga abokanan hamayya. Da farko ga al'ada ana harara da gira, musamman ga yara domin hanya ce ta sadarwa da ke nuni ga hani, to, amma kirarin ya tabbatar da cewa harara ba ta tasiri ga Sarki Sama saboda matsayinsa  na gawutacce. Kirarin  yana kuma nuni ga cewa, duk mai fushi da Sarki ya yi a banza, a maimakon ya ci riba, }ara sa kansa wahala kawai yake watau, 'Banza a banza', in ji yara. Kirarin ya kuma abuntar da Sarki da 'Katangar dutse', a matsayinsa na wanda ya gagari kowa, musamman mahassada / abokan hamayya domin babu abin da za su iya yi masa da za su cuce shi. Ga al'ada ta sarauta, duk wanda ya gaji sarauta daga mahaifinsa ko kakansa, a kullum a cikin shiri yake na gadon wannan sarauta. Idan kuwa wannan sarauta ta ku~uce, wani yakan ]auki }addara, amma galibi da dama sukan zama `yan adawa ga wanda ya yi nasara ko da kuwa ciki ]aya suka.

Da Zabiyar Kabin Argungu ta koma ga Fulani, watau Toronkawa wa]anda suka sha wahalar juna amma a }arshe Kabawa suka tsira da masarautarsu. Musamman a zamanin mulkin Sarki Sama an kwaura da juna kafin a sami aminci da ya kawo sulhu. Zabiyar Kabi ta yi da Fulani a fakaice, kamar yadda take cewa:

….marin ]aka mai ban haushi,

rugga na gani kana wadda ka so,

… gidan wani ya zama kango,

…. Gulbin teku mai wuyar iyo ]an Bawa,

… gidan Nabame mai wuyar shiga ga Fulani…

(Kirarin Sarki Sama)

Tarihi ya nuna cewa Fulani da Torankawai sun sha kashin juna a fafatawar da suka yi , domin a kullim cikin ya}i da juna suke Wannan ya sa tun a farkon kirarin Sarki Kanta, bayan Zabiyar Kabin Argungu ta yi sallama ta dire da habaici ga Fulani, kamar yadda take cewa:

Bismillahi rahamani rahim,

Oooh sha]i!

(Kirarin Sarki Kanta)

Wato 'Kash Fulani / Wayyo! Duk inda kuwa aka ce 'kash' ko 'wayyo' lallai abu ne mara da]i, akasin yadda aka so. Zabiyar tana yi wa Fulan shagu~e a kan wani artabu da aka sami galaba a kansu.

Ita ma Zabiyar Ha]eja a kirarin Sarkin Ha]eja, tana cewa kamar haka:

… suri ba}in cikin mai gona,

Inuwa gagara bunna,

Yaya gara takan yi da dutse sai kallo.

Sama ta yi wa yaro nisa...

(Kirarin Sarkin Ha]eja)

Zabiyar ta kira Sarkin Ha]eja ‘suri’ da ‘inuwa’ da kuma ‘dutse’, wa]anda duk suke nuni da }arfin buwayarsa ga mahassada/abokan hamayya, wanda kuwa za a ce nau’in habaici ne na shagu~e. Da farko dai suri duk inda mai gona ya }i shi, babu abin da zai yi da shi sai kallo. To haka ma gara babu yadda za ta yi da dutse, sai fa idan gungura za ta yi, kuma har idan ta gungura sai dai idan ta gaji ta bar shi yadda ta iske shi, kamar yadda ake cewa, ‘Nan gani nan bari’. Sannan kuma, kamar yadda masu iya magana kan ce. ‘Idan rana ta fito tafin hannu ba ya kare ta’, to haka ma, Sarki a matsayinsa na gawurtacce, ya zarce duk wani da ke }ar}ashin masarautarsa, ko shi wane ne da masoya da masu hamayya, babba da yaro namiji da mace.

A kuma kirarin Ciroman Ha]eja Zabiyar ta yi amfani da nau’in karin magana na habaici ta yi da mahassada, kamar yadda take cewa:

‘[an Maciji wanda ya fi shuri da sawu…’

(Kirarin Ciroma Ha]eja)

Maciji, kamar yadda aka sani halitta ce wadda ta kasance ba abin tsokana ba, komai }an}antarsa. To, haka wannan kirari ke nuni ga Ciroma cewa ba abokin wasa ba ne ga kowa, musamman abokan hamayyarsa, domin wargi wuri yake samu. [an Maciji, komai }an}antarsa, ya wuce a shure shi da sawu, domin ba abin shuri ba ne a zauna lafiya.

Zabiyar Ha]eja ta kuma yi amfani da wannan nau'in na karin magana, wato habaici mai sigar karin magana ta yi da abokanan hamayya, kamar yadda take cewa:

> '[an na gada wanda ya fi ]an na koya'
>
> (Kirarin Sarakin Ha]eja).

A yawancin kirarin sarakin Ha]eja, Zabiyar tana ambaton wannan matani domin yi da abokan hamayya, masu neman sarauta rana tsaka. Musamman masu takarar neman sarauta da saraki saboda abun hannunsu.

Ita ma Zabiyar Kano a kirarin Mai Martaba Sarkin Kano, Ado Bayero akwai inda take yi da abokan hamayya a fakaice, inda take cewa:

> …. Wanda Allah Ya baiwa dole a bi shi
>
> Kan ba a bi shi ba ba zance….
>
> (Kirarin Sarkin Kano).

Wannan magana ce ake fa]awa abokanan takara da sauran `yan adawa cewa, sarautar nan Allah ke ba da ita. Saboda haka duk wanda Allah ya ba, dole a bi shi ko an }i ko an so, tilas a yi masa biyayya da bin umarninsa, duk kuwa yadda za a je a dawo. Wannan nau'in habaici ne mai gugar zana.

### 4.2.3 Zuga

Zuga shi ne amfani da kalmomin harzu}awa ko tunzurawa da kambamawa da kuma cicci~awa, musamman ga maro}an fada da na `yan tauri. Yabo da zuga a wa}o}i da kirarin fada a ce su ne wa}a su ne nama, domin basarake a kullum yakan so a yabe shi, da asalinsa, da iya mulki da ri}e addini da jaddada shi da kyauta da kuma jaruntaka. To haka kuma, saraki yakan so a zuga shi, domin a }ara masa }arfin guriwa da raunana zuciyar abokan hamayya.

A }o}arin yabon saraki, a kirarin da Zabiyoyin Fada kan aiwatar musamman a nau'in yabo na jaruntakar iyaye da kakanni da tarihin asalin saraki na gadon sarauta, Zaboyoyin suna zuga su ta amfani da kalmomin kambamawa matu}a. Kalmomi masu tunzurawa da cicci~awa da kuma kumbura saraki, wa]anda galibi sukan }ara masa }arfin gwiwar aiwatar da wani abu wanda haka nan, ba zai yi shi ba da sa shi tun}aho ko girman kai. Maro}an fada sukan zuga Sarakunansu su kai su inda Allah bai kai su ba. Har a wani lokaci ma sukan ce Sarkinsu ya fi kowane Sarki a {asashen Hausa ko kuma a duniya baki ]aya. Misali, Zabiyar Kabin Argungu, a kirarin Sarki Sama, ta yi amfani da nau'in zuga kumburau, wato nau'in zuga da maro}an fada ke amfani da shi domin kumbura saraki, wanda kan sa ya cika yana batsewa. Zabiyar tana cewa:

> … Rugga na gani kana yadda ka so….,
> [a mai zuciya ka ramkon gayya,
> Na Garba ka yi ramkon gayya,
> Kada in sake jin gari Kibiyare,
> Mai da waiwaye na Muhamman,

Rugga ta sauka zamaninka,

Na Garba ka yi ramkon gayya…,

Na Garba }ona wanda ya take ka,

Gidan wani ya zama kwango…,

Na Garba ba ka tsoron taro,

Adamawa ta iso,

Zinder ta iso,

Barno ta iso,

Kano ta  iso,

[an Garba ka fi }arfin rugga,

Gira ba ta maganin ]an Yakubu Nabame,

Amma a aika da shi a sami lafiya,

Domin birni tamanin da goma sha biyar

ya ta~e na Fulani,

Kabawa ku yi hankali Sama ba wargi,

Dangi ku dangana,

Kai aka tsoro na Garba,

Kai ka wa mutum ba shi yi wu wa,

Gulbin teku mai wuyar iyo ]an Bawa…,

ka yi }arko ka yi yawan rai,

ka sha don ma}iya su ji kunya,

Hadari sa gabanka inda ka sammawa,

Katangar dutse daga gungura sai kallo..,

Katsantsan ra}umin da ba shi akala,

Mai son mutuwa shi kama akalar,

Jigon Sarakuna ]an Muhammadu Uban Kabawa Kanta…,
Hana zazahe mai sa uban gari gudu shi bar birni nai,
Rugga na gan kana yadda ka so,
Gabanka takuban fama bayanka masun daga,
Yamma gare ka `yan kibau sun daza kawai,
Ko da masu son fansa…,
Yau kai agga Muhammadu Kanta na farko…,
Yau kai agga Muhammadu Mera,
Zaman yau duk ]aukaka da martaba na wajjenka,
Wadda duk gidan Sarauta ta girma,
Bai da salsala da martaba da muhibba irin gidan Muhammadu Kanta,
Yau rinjaya da ]aukaka da martabar na gidan Nabame,
Mai kai gaba rugga,
Sai ka yi shekara arba'in da arbamiyya
da arba'in da hu]u kana mulkin gidan Nabame…

(Kirarin Sarki Sama)

Wannan kirari na Sarki Sama cike yake da zuga matu}a, saboda nuna bajinta da jaruntakar basaraken da ya yi a zamaninsa. A wajen shekara ta 1721, aka ]auke babban birnin daular Kabi daga Surame zuwa Birnin Kabi, saboda wata galaba da aka samu kan Kabawa daga harin Gobirawa da Azbinawa da Zamfarawa. Bayan nan, Kabawa sun zauna a Birnin Kabi har lokacin da masu jihadi suka kore su zuwa Augi, a inda aka ci nasara kan Kabawa, Gusau (2008:35). Amma a lokacin mulkin Sarki Sama (]an Yakubu Nabame, 1874-1915), ya yi ramakon gayya ga duk wa]anda suka sami galaba a kan iyaye da kakanninsa.

Wannan ya sa Zabiyar ke cewa:

… Rugga na gani kana yadda ka so…,
[a mai zucciya ka ramkon gayya,
Na Garba ka yi ramkon gayya..,
Rugga ta sauka zamaninka…,
Na Garba ka fi }arfin rugga…,
Domin birni tamanin da goma sha biyar ka tu~e na Fulani,
Hana zazahe mai sa uban gari gudu shi bar birni nai…
(Kirarin Sarki Sama)

Da kuma ta juya ga abokan hamayya da suka nemi sarauta, amma Sarki Sama ya yi nasara, nan ma ta zuga shi inda take cewa:

Kabawa ku yi hankali Sama ba wargi,
Ba a yi masa wargi…,
Sama ya girmi gidan uba,
Dangi ku dangana,
Kai aka tsoro na Garba…
Ka yi }arko ka yi yawan rai,
Ka sha don ma}iya su ji kunya…
Jigon Sarakuna ]an Muhammadu Uban Kabawa Kanta…
(Kirarin Sarki Sama)

Duk da cewa Zabiyar Kabin Argungu tana yi ne da abokanan hamayya da suka nemi sarauta tare, amma Sarki Sama ya sami nasara a kansu, zuga ne take yi ga sarakin a kan nasarar da ya samu. Watau zuga kariyau, domin kare Sarki Sama daga hawan }awarar abokan hamayya da ma wa]anda yake wa shugabanci domin kada ko da wasa su yi jayayya da shi, saboda shi ba abokin warginsu ba ne.

A kirarin uban Kabawa Muhammadu Kanta Zabiyar Kabin Argungu na cewa:

… Kakan duniya Sarki..,
Masu duniya ]an Mamman,
Yau duniyar ga ba ta raggo ta ba Kanta,
Haka lahira ba ta raggo ta ba Kanta…,
Ragasa tunku watarma son ya}i..,
Ingarma anka ba ku Kanta domin ya}i
Kowag gane ka ya ga ya}i
Wanda bai ganka ba bai ga mutuwa ba,
Guguwa sha da gatari,
Zangon farin wata arewa Kanta.
(Kirarin Sarki Kanta).

Sarki Kanta uban Kabawa shi ne Sarki na farko a jerin Sarakunan Lekawa a Surame, wanda ya jagoranci Kabawa tsakanin 1516-1554, wato ya yi shekara talatin da takwas (38), yana mulki. An ce Sarki Kanta  asalinsa Bakatsinen Lekawa ne, amma ya yi hijira zuwa Kabi, ya kuma ta~a zama manya cikin maya}an Askiya, kafin ya yi wa Sarkin Askiya tawaye, ya kafa tasa rundunar, daga baya ya zama Sarkin Kabi na farko a jerin Sarakunan Kabi. A

lokacinsa ya yi ya}e-ya}e da dama wa]anda ya sami nasara. Kanta mutum ne mai bajinta, musamman wajen jajircewa da ya ji~anci jaruntaka, domin ya kasance gwarzon namiji mai taurin hali, mara tsoro ko firgita.Wannan ya sa Zabiyar Kabin Argungu ta kira shi, ‘ingarma’, wato ‘}arfaffan mutum.

Wannan kirarin na Sarki Kanta, yana nuni ga irin rawar da ya taka ta fuskar jaruntaka a zamaninsa, domin haka ta kira shi ‘kakan duniya’ da ‘zangon farin wata’. Ba ga Kabawa ka]ai ba, Zabiya ta kai shi }o lin sarauta baki ]aya, na Sarkin duniya, musamman a fagen fama. Ta }ara ta zuga shi, domin ta }ara tsuma shi, a kan cewa ‘duniya ba ta rago ba ce’, to, haka ma ‘lahira ba ta rago ce’. Ta kira shi ko siffanta shi da ‘ya}i', duk dai saboda namijin }o}arinsa, na sa kai ga abin da ya dosa, musamman abin da ya shafi jaruntaka a filin daga. Wannan jaruntaka ce ta sa har gobe Kabawa suke alfahari da Sarki Kanta domin jajircewarsa ta sa duk da cewa Fulani masu jihadi sun sami galaba a kan Kabawa, amma ba su sami damar }wace mulki daga hannunsu gaba ]aya ba. Bara (2015), zuri’arsa (Muhammadu Kanta) suka cika shekara ]ari biyar (500) a gadon mulki. Lallai, matanin Zabiyar Kabin Argungu ya tabbatar da abin da take cewa:

> Wadda duk gidan sarauta ya girma,
> Bai da salsala da muhibba irin gidan Muhammadu Kanta…
> (Kirarin Sarki Sama)

Zabiyar Ha]eja ma ba a bar ta a baya ba, wajen zuga sarakin Ha]eja a kirarin da take yi masu musamman amfani da nau’in zuga kumburau. Kamar yadda take zuga Sarkin Ha]eja:

> … Ban dawa bakka da nisa sai wuyar zuwa,
> Kai ne Buhari kai ne Sambo…

Rana ba ki mu}ama,
Jeji ba a yi masa }yaure,
Toron giwa sha zamani…
(Kirarin Sarkin Ha]eja)

Burin kowane ]an Sarki shi ma wata rana a ce masa ‘Sarki’, Zabiyar ta zuga Sarkin Ha]eja a kan sarauta gidansu, saboda ya gaji sarautar  gada kaka da kakanni. Zabiyar ta yi amfani da nau’in zuga kumburau, kamar yadda take cewa:

Kai ne Buhari kai ne Sambo,
Kai ne gagara gamo da Sarki Jatau,
Ya gaji gadon Hari da Haru,
Ya mayar da gadon Sarki Karamba…
(Kirarin Sarkin Ha]eja).

Ambaton sunayen wa]annan Sarakuna, wa]anda iyaye da kakanni ne ga Sarki, zuga ce matu}a, wanda kansa Sarki zuciyarsa ta yi annuri, ya }ara tun}aho domin an kambama shi, an kuma cicci~a shi }olin -}oluwa, a sanadiyyar jero magabatansa wa]anda ba mutanen banza ba ne, a’a shugabannin gari ne na }warai. Ta kuma siffanta Sarkin da ‘rana’ da kuma ‘jeji’, a inda take nuni da ma}urarsu ko buwaya. Masu iya magana na cewa:

‘Idan rana ta fito tafin hannu ba ya mayar da ta.’

To, haka ma Sarki yake ga abokanan hamayya.Tarihi ya nuna cewa Sarkin Ha]eja Buhari ya kasance tauraro cikin taurari a zamaninsa, domin shi ne Sarkin da ya zauna da `yancinsa, saboda ~alle wa da ya yi daga daular Barno, kuma ya }i mi}a wuya ga Sarkin Musulmi, saboda jaruntaka.

A kirarin Ciroman Ha]eja ma tana cewa:

…[an babban amale,
[an na gada wanda ya fi ]an na koya,
Farin iri abin shukawa,
[an Sarki jikan Sarki Ciroma…
(Kirarin Ciroman Ha]eja)

Wannan kirari na Ciroma na zuga Ciroman Ha]eja, ya cicci~a shi, ta hanyar }ara fito da asalinsa na ]an manya /babban gida (wanda a {asar Hausa kowa yake da salsala da shi yake tun}aho). Zabiyar ta ci gaba tana jaddada cewa, 'Ciroma ]an Sarki ne jikan Sarki, ]an na gada wanda ya fi ]an na koya, komai gwanintarsa. Baya ga cewa 'farin iri' ne, wanda ke fitar da ru~anya nagartatta, watau mai asali na  gari. Haka wannan Zabiyar Fada take zuga dukkan sarakin Ha]eja da kirairnta.

Idan kuma muka koma kirarin da Zabiyar Daura take yi wa sarakin Daura, a ce maganar ba ta canza zani ba. Ita ma tana amfani da nau'in  zuga kumburau ta zuga sarakin Daura a kirarinta, kamar yadda take cewa:

Zabiya : Mararrafar madangari,
:Madur}usar madangari,

Amshi:Mararrafar madangari,

: Madur}usa madangari,

Zabiya: Hawan `yan Bawo,

Amshi: Hawan ‘yan Bawo

Zabiya: Kakan Anna,

Amshi: Kakan anna…

(Kirarin Sarkin Daura)

Wannan kirari hanya ce ta sanar da zuwa ko bayyanar Sarkin Daura, domin shi yake sanar da fadawa da sauran jama’a ga Sarki nan tafe, saboda haka ake umartar su, su dur}usa su yi gaisuwa ga mai gari. Watau ‘mararrafar madangari ‘ga masu gari nan tafe’, ‘madur}usa madangari’, ‘a dur}usa a gaishe da masu gari’. A irin wannan hali, jama’a musamman fadawa duk inda suke sukan dur}usa su yi gaisuwa, har inda Sarki zai kai. Wannan yanayi, yana harzu}a saraki, ganin yadda kowa zai dur}usa har }asa ya yi gaisuwa, shi kuwa yana tsaye saboda }arfin ikonsa da ingarma da buwaya.

Kamar yadda aka sani, sarautar Daura ana danganta ta da Bawo ]an Bayajidda saboda haka, maro}a suke kambama da jingina salsalar sarakin Daura da ‘Bawo’ ko ‘Bayajidda’. Wannan ne ya sa Zabiyar Daura a kirarin Sarkin Daura take cewa:

‘Hawan ‘yan Bawo…’

(Kirarin Sarkin Daura)

Manufa a nan  shi ne tsatson Bawo. ‘Kakan anna’, kamar yadda aka yi bayani }ar}ashin jaruntaka, ‘arna’, a nan na nufin gwarzayen maza jarumai. Ke nan Zabiya na zuga Sarkin da ‘uban jarumai. Wannan ma, nau’i  ne na zuga kumbura. Wannan ba ba}on abu ba ne a kirari da wa}o}in fada da na maza, kamar na `yan tauri da manoma. Alalmisali, kirarin Sarkin Kabawa Kanta, Ibrahim Babari na cewa:

Sha da azna,

Kada azna,

Manzon azna,

… yau kada ba zagawa,

Yau kada ba zagawa,

Dare wandara maye sha da azna,

Maye ya mayata.

Akwai kuma inda Zabiyar Daura take zuga Sarkin Daura kamar yadda take cewa:

… Rana ta yi hwargaba rana taka,

In suke kimammaye…

Innuwal dare saraki abokin jiro.

(Kirarin Sarkin Daura)

A nan, Zabiyar ta zuga Sarkin Daura a matsayinsa na ubangijin rana, duk kuwa da kasancewar ita ma ubangijiya ce (domin lokacin da aka fara aiwatar da wannan kirari akwai sauran ~ir~ishin addinin gargajiya), amma wai  idan ranar ta ga Sarki tana fargaba, saboda buwayarsa. Su ma sauran sarakin Daura maza da mata, zabiyar tana zuga su domin a duk kirarin da take yi masu, tana anbaton haka:

In ]an/’yar sasarin mutu ko dai ri}o,

In ]an /'yar maran maza da yawa,

[an/'yar mu je mu da anna.

(Kirarin Sarakin Daura)

Zabiyar tana zuga su a matsayinsu na `ya`yan saraki kuma jarumai, wa]anda idan suka shiga fagen fama masu ra'ayin ri}au ne, na ko dai a mutu ko kuma a yi rai. Kamar yadda ita ma Magajiyar Daura, Zabiyar take zuga ta inda take cewa:

… Gida zaman gida ga giwa garara cinnaki,

Baje –bajen toranke karnan tada damisa…,

In sa abuyar tsohon zaki…

(Kirarin Magajiyar Daura).

A nan Zabiyar ta cicci~a Magajiya a matsayinta na giwa wadda ta gagari sauran namun daji, ballantana cinnaka abun banza. Ta kuma kira ta abokiyar tsohon zaki, wanda yake fitinanne matu}a. Sannan kuma aka kira ta 'karen farautar damisa', wanda ba kowane irin kare ba ne, sai gawurtacce. A ta}aice, kirarin na nuni da cewa Magajiya ta hannun damar Sarki ce, abokayir shawararsa, ga ta kuma gawurtacciyar jaruma da ta gagari abokan gaba. Galadiman Daura ma ta zuga shi, a matsayinsa na shugaban maya}a kuma uban ]aki ga sarakin Daura, kamar yadda take cewa:

…Ka fi dawan ya}i…

In sungumi burema na 'yan tuma,

Tagar burema.

(Kirarin Galadiman Daura).

Galadima a masarautar Daura ba shi da dangantaka ta jini da Sarki da sauran sarakin Daura, to amma shi ne uban ]aki ga duk ‘ya’yan Sarkin Daura, wanda ya sa da shawararsa ake na]a su sarauta, kuma shi ke yi masu wakilci mazansu da matansu (lokacin aure). Duk wata shawara da shi suke yi, sannan daga baya ya sanar da Sarki. Saboda haka, yana da matsayi matu}a (burema a Masarautar Daura na nufin saraki), A ta}aice, a iya cewa Zabiyar Daura ta yi amfani da zuga kumburau, ta zuga sarakin Daura

A kirarin Zabiyar Kazaure, idan ana maganar ‘zuga saraki’, to an ce an tsince dami ne a kala, domin ita ma ta zuga Sarkin Kazaure matu}a. A matsayinsa na ]an Sarki jikan Sarki, wanda yake da ilimin Arabi da na boko, kamar yadda take cewa:

Sarki magajin Sarki…,
Sarki magajin Sarki Ibrahim,
Sarki magajin Sarki Hussaini Adamu,
Ga ka Bature ga ka Malam…
Dare marufar asiri,
Goshin jirgi ba ka tarbuwa,
Jirgi ba ka tarbuwa,
Zaki ka saba ka]ar maza…
(Kirarin Sarkin Kazaure Najib Hussaini).

A na a ce ta zuga basaraken ta kai shi }ololuwa a matsayinsa na jarumi mai tayar da hankalin maza. Ta kira shi’ goshin jirgi’, wato gawurtacce wanda ya buwayi kowa, musamman abokan hamayya. Ta kuma siffanta shi da ‘zaki’, wanda saraki ne a dawa da ya

fi }arfin sauran namun daji buwaya. Zabiyar ba ta yi }asa a gwiwa ba, ta zuga basaraken kan iliminsa na boko da na addini, wa]anda suke yi masa jagoranci a sarautar da yake ri}e da ita.

### 4.3 Tasirin Addinin Musulunci A Kan Zabiyanci

Daga kirarin da Zabiyoyin Fada ke yi wa saraki a {asar Hausa, an sami tasirin addinin Musulunci ya haifar da su. An sami tasirin wannan addini a kirarin ta fuskar jigonsa da aiwatar da shi da kuma yanayin sigarsa.

#### 4.3.1 Tasirin Addinin Musulunci ta Fuskar Jigo

Cikin shikashikan cim ma yabo da maro}an fada suke amfani da shi akwai yabon Sarakuna a kan ri}e addinin al'umma  da jaddada shi. Kasancewa yanzu Sarakunan Hausa shugabanni ne na addini ya sa Zabiyoyin Fadasuke yabonsu a kan ri}o da shi da kare martabarsa da kuma zama abin koyi, musamman kan harkokin yau da kullum. Addinin Musulunci addini ne da Musulmi suke bauta wa Allah shi ka]ai, babu tarayya da shi kuma Annabi Muhammadu Manzonsa ne. Kare  martabar addinin Musulunci da jaddada shi, ta hanyar zama abin koyi da hana kafurci (misali tsafe –tsafe), ]aya ne daga ayyukan da ya rataya a wuyan Sarakuna. Wannan ya sa maro}an suke yabonsu da shi, domin }ara masu }arfin gwiwa. Alalmisali, tun a farkon kirarin Sarki Muhammadu Kanta aka fara jin  ]uriyar jigon da ke nuni da tafiyar da rayuwa irin ta addinin Musulunci da Zabiyar ta yabi Sarkin da shi.

Zabiyar Kabin Argungu ta yabe shi da ‘tausayi da tausasawa’ da ‘taimako’ da ‘ibada’, da kuma ‘godiya’ ga Allah Subhanahu Wata’ala. Wa]annan dukka ]abi’u ne da addinin Musulunci yake }arfafa su ga kowane Musulmi, musamman Sarakuna domin na baya su yi koyi da su. Daga wannan kirari, za a iya ganin yadda Zabiyar ta sarrafa kalmomi irin su ‘Allah’( sunan da Musulmi ke kiran mahaliccinsu kuma abin bautarsu) da ‘Alkur’ani’ (littafi mai tsarki da Allah Ya aiko manzonsa, Annabi Muhammad (S.A.W.) da shi zuwa ga bayinsa) da ‘alwalla’ (ibadar da Musulmi suke aiwatarwa kafin su yi salla, wadda take wajibi ko ‘farilla’) da ‘tasalimi’ (ambaton ubangiji) da ‘Muhammadu rasulillahi’ (sunan Manzon Allah na }arshe). Duka wa]annan sun samu ne sanadiyyar tasirin addinin Musulunci, kamar yadda take cewa:

> …zullufi –wullifi yawanyin alaihin,
> …Sidi mai taimako da na Allah,
> Yau a duniya kowa ya kwana lafiya.
> Ya tashi lafiya ya kan yi mi}a,
> Ya yi tasalima ya tambayi al}ur’ani,
> A kawo masa ya yi alwalla,
> Ya mayar da gabansa gabas,
> Na ce ni wane na gode Allah.
> Na godewa Muhammadu rasulillahi…
> (Kirarin Sarki Kanta).

Zabiyar Kabin Argungu a kirarin Sarki Kanta, kamar yadda ayoyin Al}ur’ani da hadisan Annabi Muhammad (saw), suka bayyana cewa Allah ne mahaliccin dukkan abin da ke doran }asa, Zabiyar ta }ara tabbatar da haka, kamar yadda take cewa:

Rana da wata fataken Allah.
(watau bayin Allah ).
(Kirarin Sarki Kanta).

A kirarin Sarki Sama, an sake samun wani jigon da ke da tasirin addinin Musulunci, da yake nuni da cewa, mulki Allah ke bayar da shi ba wani ba:

Mai fushi da kai ya wahala,
Sama Sarkin da Allah Ya yi.
(Kirarin Sarki Sama).

Tabbas! Wannan magana ce Zabiyar Kabi ta yi wa abokan hamayyar Sarki Sama, domin Allah ne ya ]ora shi gadon sarauta, saboda haka ta jawo hankalinsu a kan imani da }addara. Musulunci da ma a kodayaushe yana horar da Musulmi  su yi imani da }addara, mai kyau da mara kyau.

Idan kuma koma Fadar Ha]eja, a ce an tsinci dami ne a kala, domin addinin Musulunci ya yi tasiri a kirarin da Zabiyar Fadar Ha]eja ke yi wa saraki. Za a iya ganin haka, saboda Musulmi a duk fa]in duniya suna yi wa `yanuwansa addu'ar samun rahama daga Allah, musamman a lokacin da suka rasu. Zabiyar ta yawaita ta'aziyyar iyaye da kakannin sarakin Ha]eja a kirarin da ta yi masu kamar haka:

…Allah Ya ji }an Ciroma Ali
Allah Ya bar mana [an Iya tudu abun dafawa,
…Allah Ya ji }an Turaki Abubakar,
Allah Ya ji }an Sa'adatu,

Allah Ya ji }ansa,

Allah Ya sa mutuwa hutu ce.

(Kirarin Sarkin Ha]eja).

Allah Ya ji }an Galadima Yusufu,

Allah Ya ji }an Galadima Zakari,

Allah Ya ji }an Galadima Usman,

Allah Ya ji }an Galadima Habibu.

(Kirarin Galadiman Ha]eja).

Allah Ya ji }an Sarki Abubakar,

Allah Ya ji }an Sarki Haruna,

Allah Ya ji }an Sarki Abubakar,

(Kirarin Magajin Garin Ha]eja).

A kirarin Sarakin Daura ma an sami ~ir~ishin tasirin addinin Musulunci dangane da sunan fiyayyen halitta, Annabi Muhammad (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) duk kuwa da cewa an yi kirarin shekaru da dama da suka wuce. Alalmisali:

Zabiya: Hazo na Muhamman,

`Y/Amshi: Hazo na Muhamman,

Zabiya: Alhajin Saraki,

`Y/Amshi: Alhajin saraki,

Zabiya: Gaba gare ka Allah,

`Y/Amshi: Gaba gare ka Allah,

Zabiya: Dama gare ka Allah,

`Y/Amshi: Dama gare ka Allah,

Zabiya: Nasara dai,
`Y/Amshi: Nasara dai,
Zabiya: Allah Mai iyawa,
`Y/Amshi: Allah Mai iyawa.
(Kirarin Sarkin Daura).

Muhamman (Muhammad) suna ne na ma’aikin Allah, Annabi Muhammad, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, wanda zuwan Musulunci ya sa aka sami sunan. Ita ma Zabiyar Kano ta yi amfani da wannan suna ta kira Mai Martaba Sarkin Kano, Ado Bayero ‘Muhammadu’, inda take cewa:

Da ma ka ba ni fanka ‘Muhammadu’…

(Kirarin Sarkin Kano Ado Bayero).

Haka ma kalmar ‘Alhaji’, la}abi ne da ake kiran duk wanda ya yi aikin hajji, watau ya ziyarci ]akin Allah mai rahama da Musulunci ya kawo. Sannan kuma, tasirin addinin Musulunci ne ya sa Zabiyar Daura ta ce Sarkin Daura ya yi imani ga Allah kan nasararsa. Kamar yadda kuma take nuni ga imanin Sarkin na dogaro ga Allah a kowane hali, domin ya yarda a kodayaushe Allah Yana tare da shi:

Gaba gare ka Allah,
Dama gare ka Allah…
Allah mai iyawa …
(Kirarin Sarkin Daura).

A kirarin Sarkin Sudan da Sarkin Kudu da kuma na Al}alin Garka, Zabiyar ta yi nuni ga martabarsu a matsayinsu na na masana. Watau malamai wa]anda suke taimakawa Sarki gudanar da harkoki a fada, kamar yadda addinin Musulunci ya yi horo a yi. Alalmisali, shari'a ko sasantawa:

'Karan masana kogin malami.'
(Kirarin Sarkin Sudan/Sarkin Kudu)

'In Alfa matambayan sani karaf da masana kogin malamai.'
(Kirarin Al}alin Garka / Malaman Fada).

Zabiyar Kano Hajiya Ajuji Maitazargade, tun a farkon kirarin Mai Martaba Sarkin Kano, Ado Bayero ta fara da ta'aziya ga kakansa Adananu. Sannan kuma ta ci gaba ta yi ta'aziyya ga rasuwar Sarkin {araye, wanda ke nuni da tasirin addinin Musulunci, kamar yadda aka yi bayani a baya, a kirarin Sarakin Ha]eja:

Allah ji }an Mai Data da gafara,
Muhammadu Adananu ya riga mu,
Allah shi gafarta mai fa.
Allah Ya ji }an Sarkin {araye Ibrahim,
Allah Ya sa mutuwa hutawa.
(Kirarin Sarkin Kano).

Har ila yau, tasirin addinin Musulunci ne ya sa Zabiyar ta yi wa Sarkin Kano Ado Bayero fatan ya tashi tutar malamai, cikin tutar Manzon tsira, Annabi Muhammad (SAW), gobe

kiyama. Domin kuwa addinin Musulunci ne ya kwa]aitar da Musulmi su yi abin }warai nan duniya, saboda sakamakon alheri gobe kiyama, watau shiga aljanna.Tsammanin sakamako gobe kiyama da kalmar ‘kiyama’, duk  an same su ne bayan zuwan addinin Musulunci, kamar yadda Zabiya Ajuji Maitazargade ke cewa:

Abin da nake mana fata ranar tashin kiyama
Allah sa mu tashi tutar maluma,
Abin da nake mana fata ranar tashin kiyama,
Mu tashi a tutar Annabi…
(Kirarin Sarkin Kano).

An kuma tsinci kalmar ‘Alhamdulillahi’ da dama a kirarin. Wannan kalma tana nufin ‘godiya ga Allah’ (SWA), wadda tasirin addinin Musulunci ya haifar da ita. Masu iya magana na cewa:

‘Ka gode wa Allah ko kana bakin kura.’

Zabiya Ajuji na cewa:

Yadda ka yi aiki lafiya Allah sa ka wanye lafiya…,
Ko yau ka bar duniya Alhamdulillahi,
Na yi shukara wurin Annabi…,
Alhamdulillahi kyautar Allah ta yi.
(Kirarin Sarkin Kano).

Akwai kuma inda Zabitar ta yi nuni da 'tir' da addinin Musulunci ya yi ga 'bokaye' da ayyukansu na 'tsafi'. A maimakon haka ta bayyana cewa, Sarkin ba ya hul]a da su, sai da malamai wa]anda suke ba shi shawara. To, dama dai al}alai da malamai a fada, abokan shawara ne na Sarki, domin haka makusantansa ne na kusa.

…Don ka ce a je gida a huta boka,
Malamai su za su fa]an ma shawara.
(Kirarin Sarkin Kano)

Zabiyar ta kuma ambato sunayen garuruwa biyu wa]anda tasirin addinin Musulunci ya kwa]aitar da duk Musulmi su ziyarce su kafin su koma ga mahaliccinsu, wato 'Makka' da Madina. Makka, babban birni ne mai tsarki a {asar Saudiyya, wurin da ]akin Ka'aba yake. 'Madina' kuwa, garin da Annabi Muhammad (SAW), ya zauna ne bayan ya yi hijara daga Makka. Nan ne kuma masallacinsa yake, masallaci na biyu mai daraja a duniya baki ]aya, kamar yadda Zabiya Ajuji ke cewa:

Na kai shukura wurin Annabi,
Manzallazina Jalla mai Makkan da Madina…
(Kirarin Sarkin Kano).

Tasirin addinin Musulunci ya }ara fitowa a kirarin, inda Zabiyar ke cewa:

Babu mai yi ban da Allah,
Waye mai yi Allah bai yi ba?
Wanda ya zo gare ka Allah Ya kai shukura gun Annabi…

(Kirarin Sarkin Kano).

Wannan na nuni da buwayar da Allah (SWA), da godiyada kuma dogaro gare shi, shi ka]ai. A kirarin Zabiyar Zazzau ma, wannan tasiri (na addinin Musulunci) ya fito matu}a, domin Zabiyar ta jaddada cewa Sarki Zazzau Shehu Idris, mai kare martabar addininsa da na al'ummarsa ne. Shi ya sa ya zama 'duddugen addini' da 'toya matsaya' a }asarsa:

Barka da zuwa toya matsafa,
Barka da zuwa duddugen addini,
Shiga da }arfin Allah jikan Sambo…
(Kirarin Sarkin Zazzau).

A wurare da dama Zabiyar ta yi nuni da cewa Sarkin Zazzau basarake ne da yake danganta al'amuransa ga Allah, baya ga son manzon tsira da aka yi horo da shi:

Allah ya fidda na kullum,
Allah ya }ara maka son Annabi ]an Idirisa,
(Kirarin Sarkin Zazzau)

Allah Ya taimake ki,
Allah Ya }ara maki martaba.
(Kirarin Matan Sarkin Zazzau)

Zabiya ta biyu a Fadar Zazzau, Rabi Bazamfara ma a kirarin da ta yi wa Sarkin Zazzau, an sami tasirin addinin Musulunci a ciki, wanda ke nuni da imani ga Allah da }arfafa addinin basaraken:

Fito da }arfin Allah ni}atau,
Fito da }arfin Allah toya matsafa,
Taka da }arfin Allah zaki…
(Kirarin Sarkin Zazzau).

A kirarin sarakin Kazaure ma an tsinci dami a kala:

Lafiya mai }arfi da }arfin Allah,
Lafiya mai iko da ikon Allah,
Lafiya Sarkin Musulunci Sarkin adalci…
Allah Ya taimake ka…
(Kirarin Sarkin Kazaure Ibrahim)

Wannan na nuni da }arfin imanin basaraken da kuma kasancewarsa Sarkin Musulunci, mai addini (addinin Musulunci), ba Sarkin gargajiya ba.

An sami kusan irin wannan matani a kirarin da Zabiyar Kazaure, Hajiya Indo ‘Yarsukola ta yi wa Sarki Hussaini Adamu da Sarki Najib Hussaini Adamu. Kamar haka:

Ga ka Sarki ga ka malami,
Ga ka Bature ga ka Balarabe,
Allah Ya taya ga ri}on jama’a…

(Kirarin Sarkin Kazure Hussaini Adamu da ]ansa Sarki Najib).

Wannan matani na nuni da cewa wa]annan Sarakuna sun sami ilimin addini matu}a, kuma suna amfani da shi wajen jagorancin da Allah Ya ]ora masu. Kamar yadda a wasu lokuta, bayan ta yi ta'aziyyar iyaye da kakannin sarakin, takan }arasa da yi masu addu'ar fatan alheri:

Allah Ya ji }an Yarima Sulaiman,
Allah Ya ji }an Sarki Ado,
Allah Ya ji }an Hajiya Amu,
Yadda suka gama lafiya,
Allah Ya sa ku gama lafiya da imani…
(Kirarin Ciroman Kazaure).

Ita ma Zabiya {arangiya (Zabiyar Kazaure ta biyu), a kirarin da take yi wa sarakin Kazaure, an tsinci tasirin addinin Musulunci a ciki. Zabiyar ta yi amfani da kalmomi da dama wa]anda suke da tasirin addinin Musulunci:

Magajin Sarki alhamdulillahi,
Allah ja da ran Falakin Kazaure na farko,
Ubangji Ya saka da alheri,
Allah ja da ran Dallatu,
[an Ummaru Alhamdulillahi…
Sakallahu hairan Allah Ya saka da alheri.
Komai ya yi zafi Ubangiji Yana maganinsa komin dare.

(Kirarin Sarkin Kazaure, Najib Hussaini)

Kalmomi irin su ‘alhamdulillahi’ da sakallahu hairan’, watau ‘godiya ga Allah’, da ‘Allah Ya saka da alheri’, masu nuni da tasirin addinin Musulunci duk an ji a wannan kirarin. Kirarin ya kuma yi nuniga tawakali ga Allah a dukkan al’amura. Ta kuma yi amfani da kalmar ‘lahira’, wadda tasirin addinin Musulunci ya kawo a kirarin matar Sarki Najib:

‘Allah Ya sa ki iske lahirarki fari tas kamar nan.’

(Kirarin Matar Sarki Najib Hussaini, Hajiya Umma).

**4.3.2 Tasirin Wayewar Addinin Musulunci A Kan Zabiyanci**

Baya ga tasirin addinin Musulunci ta fuskar jigon kirarin, akwai kuma tasirin addinin Musulunci dangane da aiwatar da Zabiyancin Fada. A wannan fage tarna}i ne addinin Musulunci ya yi wa Zabiyanci. Daga hirar da aka yi da Zabiyoyin da aka nazarci kirarin da suke aiwatar, an gano cewa ]aya daga cikin matsalolin da Zabiyanci ke fuskanta shi ne na rashin Zabiyoyin Fada a yau. Ba kuma wani abu ya bayar da gudunmuwa ga wannan ba, illa a ce tasirin addinin Musulunci da kuma zamani.Zabiyanci harka ce da ta ji~anci cu]anya tsakanin maza da mata da kuma ]aga murya (ga Zabiyoyin lokacin da suke aiwatar da kirarin). Zuwan Musulunci ya yi hani da wa]annan batutuwa (cu]anya da ]aya murya ga mace), wannan ya yi sanadiyyar }arancin Zabiyoyin Fada a yau.

Tasiri na biyu da ya ji~anci addinin Musulunci ga gurgunta Zabiyanci shi ne ‘kulle’, da Musulunci ya yi umarni ga mazaje, su killace matansa sa~anin da kafin zuwan Musulunci

da mata suke fita kara zube, kamar  dabbobi wanda ya sa ko katanka ba a yi a gidaje da dama. Wannan ya yi tasiri matu}a, wanda ya sa ba kowane namiji zai yarda matarsa ta fita ta bar ]akinta da tarbiyyar `ya`yanta ba, saboda Zabiyanci.

Tasiri na uku kuwa shi ne hani ga ro}o. Addinin Musulunci ya yi hani ga ro}o matu}a, musamman tsakanin mace da namiji. Ma'ana, hadisai da ayoyin Al}ur'ani sun yi hani ga ro}o, domin hanya ce ta nuna }as}anci. Musulunci ya hori al'ummar Musulmi su tashi su nemi halal, kada su dogara ga kowa, sai Allah Subhanahu Wata'alah. Babban  }as}anci shi ne mace ta ro}i namiji, musamman wanda ba muharraminta ba, domin gudun abin da zai iya haifarwa. Doi (1984:), ya ruwaito wani hadisi da manzon tsira (saw), yake cewa,"Duk wanda ya dogara da ro}o zai tashi ranar kiyama fuskarsa ta zagwanye". Ma'ana naman fuskarsa ya kwaye.Saboda haka an hori Musulmi su tashi su nemi na kansu, su kuma dogara da Allah, kamar yadda wannan aya take cewa: Allah Ya sanya muku }asa horarriya, sai ku ci daga arzikinSa, kuma zuwa gare shi ne tashin yake (Suratul Mulk 67:15). Wannan na nuni da cewa Allah cikin rahamarSa Ya azurta }asa ga bayinSa, domin haka Ya umarce su su tashi su nema. Sannan kuma kada su dogara ga kowa face Shi.

Wa]annan dalilai sun sa masarautu da dama yanzu ba su da Zabiyar Fada.  Da yawa sun rasu, amma  an kasa samun masu gadonsu. `Ya`yansu da suka gada sun guji al'adar, ko sha'awar a ce sun gaje ta ba su so su ji. Da yawa daga cikin Zabiyoyin da ake da su a yanzu, suna Zabiyancin ne saboda albashin da ake ba su, musamman da ya kasance galibinsu ba su da aure, mazajensu sun rasu, kuma ba su da mai kula da su da har zai ]auki nauyinsu na ci da sha da kuma sutura.

## 4.4 Tasirin Zamani A Kan Zabiyanci

A iya cewa an sami tasirin wayewar kai dangane da yanayin da al'umma suke ciki yanzu, wanda babban mu}asudi shi ne wayewar kan da ilimin boko ya samar, da shirin game-duniya da ake ciki a wannan zamani.

Da farko, kamar yadda addinin Musulunci ya wayar da kan al'ummar Musulmi, haka ilimin boko ya wayar da kan wa]anda suka yi shi, ko da kuwa a matakin firamari ne, domin akwai bambanci tsakanin wanda ya je makaranta da wanda bai je ba, musamman ta fuskar mu'amula da jama'a. Kamar yadda saraki ke gadon sarautar gidansu, galibi haka `ya`yan Zabiyoyin Fada suke gadon iyayensu a da. Wasu daga cikin Zabiyoyin, tun asali iyayensu maza ma maro}a ne, to haka ma iyayensu mata. Wannan ya sa a sau}a}e a da, da Zabiya ta rasu, sai Sarki ya na]a babbar ]iyarta ko wata daga cikin `ya`yanta da aka lura tana da basirar Zabiyanci, ko tana so ko ba ta so. Galibi ma a da, abin farin ciki da biki ne idan za a na]a sabuwar Zabiyar Fada. Yanzu kuwa, daga hirar da aka yi da Zabiyoyin da aka nazarci kirarinsu da wasu daga cikin `ya`yansu, ba sa fatan su gaji Zabiyanci (iyayen ba sa fatan `ya`yansu su gaje su, haka ma `ya`yan ba sa fatan haka). Wannan kuwa ya faru ne a dalilin karatun boko da `ya`yan Zabiyoyin suka yi. Da yawa daga cikinsu yanzu suna ganin Zabiyanci }auyanci ne ko jahilci , domin haka suke gudunsa. Iyayen nasu ma sun nuna cewa Allah ne Ya }addara masu ba domin sun so ba.

Tasiri na biyu da ilimin boko ya haifar shi ne, yanzu kusan Sarakunan Hausa `yan boko ne, wannan ya sa sannu a hankali suke watsi da al'adun da suka iske ana aiwatarwa kaka da

kakanni a masarautunsu.  Haka ya sa idan Zabiyar Fada ta rasu, babu kuma ]aya daga cikin `ya`yanta ko danginta da aka samu zai maye gurbinta, Sarakunan ba sa mayar da hankali a samo wadda za ta yi. Al'adun fada  da dama  yanzu sun ~ace, sanadiyyar watsi da Sarakuna suka  yi, na 'kallon sakainar kashi', saboda ilimin boko. A iya cewa wannan ne dalili, domin da yawa dagacikin Sarakunan Hausa a yau, sun sami ilimin boko har zuwa matakin digiri na farko, wasu a mataki na tsakiya. Sannan kuma, sun  ri}e mu}aman gwamnati da hukomomi daban-daban, wanda ya sa suka kuma zauna a wurare daban-daban, musamman bariki kafin su hau gadon sarauta.Wannan ya sa ba su da sha'awar wasu al'adu, sai dai girman sarauta, domin haka suka yi watsi da su, cikinsu kuwa har da Zabiyancin Fada.

Wani tasiri da zamani ya haifar shi ne na shirin game –duniya, wanda burinsa ne ya la}ume al'adu, musamman na Afirka, ya kuma watsa na yamma. Wannan ya sa da dama daga Hausawa ba su san da zaman Zabiyar Fada ba, ballantana su san gudunmuwar da take bayarwa ga adabi da al'adun fada. Ko hawan salla  da a da yara suke rubibi su je, yanzu galibi ba su cika zuwa ba, musamman `ya`yan da suka yi ilimin boko, kuma ya kasance iyayensu ma `yan bokon ne. Kallon hawan salla kuwa na sa matasa su san al'adunmu, kasancewa kusan al'adun al'umma na fada.

A iya cewa tasirin zamani ya taka taka rawa wajen na}asa wannan muhimmiyar al'ada ta fada, watau Zabiyanci. Haka ya sa sannu a hankali za a wayi gari babu Zabiyoyin Fadojin {asar Hausa.

### 4.5 Kammlawa

A babi na hu]u an yi tarken Zabiyancin Fada, wato kirarin da Zabiyoyin Fada ke yi wa saraki, aka nazarci jigonsa. Daga nazarin, za a iya tabbatar da cewa jigon kirarin ya tabbata yabo. Sauran }ananan jigogin kirarin sun ha]a da habaici da kuma zuga. Zabiyoyin sun yi amfani da tarihin asali da iya mulki ko ri}on jama'a da kyauta da ri}o da jaddada addini da tabbatar da shi da kuma jaruntaka. Nazarin ya kuma duba yadda tasirin addinin Musulunci ya gina jigon kirarin da kuma na}asun da ya haifar ga aiwatar da shi. Binciken ya kuma gano cewa zamani ya yi tasiri matu}a ga aiwatar da Zabiyanci a yau.

# BABI NA BIYAR

# SALO DA ZUBI A ZABIYANCIN FADA

## 5.1 Gabatarwa

A babi na hu]u an fara taciyar kirarin da Zabiyoyin Fada ke yi wa saraki, a inda aka nazarci jigon kirarin. A wannan babi, wato babi na biya an ci gaba, aka mayar da al}iblar nazarin ga salo da zubin kirarin. A }ar}ashin salo, an mayar da hankali a kan adon harshe da kuma aiwatar da harshe. Har ila yau, an nazarci irin nau'in kirarin a wannan babi, wato irin zubinsa.

## 5.2 Salo a Zabiyancin Fada

Al'ummar Hausawa ta ginu bisa fasahar harshe. Ta haka ne adabin baka ya ]amfaru ainun a rayuwar Hausawa, tun ma ba na farko ba, a inda ayyukan adabin baka, kamar kirari da karin magana da salon magana da wa}e-wa}e da sauran hanyoyin sakayawa da gajarce zance cikin hikima da balaga suka zama ruwan dare. Irin wannan al'umma mai son gwanintar harshe, da karakainar amfani da kalmomi da jimloli masu ma'ana daban-daban, ta haifar da mutane masu kirarin baki da maka]a da mawa}a masu yawan gaske a zangunan rayuwa da lokuta mabambanta, Gusau (2012:20). Zabiyar Fada na ]aya daga cikin wa]anda Allah Ya horewa wannan fasaha, ta shirya kirari da gabatar ko aiwatar da shi ga saraki. Saboda haka, a wannan fage, an nazarci salo to fuskar adabi. Wannan nau'i na nazarin salo, kamar yadda Garba (2011:44), ya ruwaito Olusegun da Adebayo (2008), shi ne salon da ake amfani da shi wajen }alailaice wani matani, ta hanyar za}ulo ire-iren hikimomi da dabarun da fasihi

ya sarrafa don kyautatawa da }awata mataninsa, musamman salon warwarar jigo da hikimomin da suka shafi adon harshe.

Wannan ya bibiyi wata al'ada ce ta fada, ta yadda aka sarrafa adabin da ke cikinta, wato kirarin da Zabiyoyin Fada kan yi wa saraki. Sannan daga kirarin aka fito da tunanin Bahaushe game da saraki, musamman daga jigon kirarin. A fagen nazarin salo, an za~i a nazarci adon harshe na kirarin Zabiyoyin da aka nazarta. An kuma nazarci yadda Zabiyoyin suka sarrafa kalmomin aro da tsofaffin kalmomin Hausa. Ke nan, ba za a nazarci sauran fannoni da suka ji~anci salo ba, kamar gundarin ma'ana da tsarin nahawu da sauran fannoni da suka ji~anci nahawu ko kimiyyar harshe. Kirarin Zabiyoyin Fada cike yake da fasahar harshe mai nuna azanci da gwanintar harshe mai ban sha'awa da armashi.

### 5.2.1 Adon Harshe.

Adon harshe, kamar yadda masana suka bayyana, shi ne dabarar yi wa harshe kwalliya cikin hikima da balaga domin ya }awatar, ya kuma sami }ar~uwa. Za a iya fahimtar cewa ba harshen wa}a ka]ai ake yi wa kwalliya ba, ana samun kwalliya a fannonin adabi da dama wa]anda suka ha]a da 'kirari', musamman na fada. Wannan bincike ya gano cewa Zabiyoyin Fada galibi suna amfani da nau'o'in adon harshe irin su jinsirtarwa (abuntarwa da dabbantarwa da mutuntarwa) da alamci da kwalliya da tamka da hotoncin zuci a kirarin da suke yi wa saraki.

#### 5.2.1.1 Jinsintarwa

'Jinsi' kalma ce da ke nuna irin nau'in wani abu, musamman bambanci tsakanin mace da namiji. A adon harshe kuwa, 'jinsi' kalma ce da ke nuna bambanci tsakanin mutum da

dabba ko tsuntsu ko kuma wata halitta mai rai ko mara rai. Jinsintarwa dabara ce ta ]aukar daraja ko siffa ko hali ko yanayi ko aikin wani jinsi a ba wani jinsi na daban. Alalmisali, a ]auki wata halayya da aka san mutum ka]ai ke yin ta a ]ora wa wani jinsi daban, kamar dabba ko tsuntsu ko wata halitta. Jinsintarwa babban kaso cikin nau'o'in adon harshe domin yana da }ananan nau'o'i }ar}ashinsa. Nau'o'in jinsintarwa sun ha]a da dabbantarwa da mutuntarwa da kuma abuntarwa.

**Abuntarwa:** Abuntarwa salo ne na mayar da mutum ko dabba ko tsuntsu ko wani abu mai rai ya zama mara rai. Alalmisali, Zabiyar Kabin Argungu a kirarin Sarki Muhammadu Kanta tana cewa:

...<u>Zangon farin wata</u> Kanta…

(Kirarin Sarki Kanta).

Zabiyar ta abuntar da Sarki Muhammadu Kanta da 'Zangon farin wata'. Ranar sha hu]u ga wata wata ke kai zango, watau }ololiyar haske. Sannan daga nan haskensa ya fara dushewa. Abuntar da Sarkin da Zabiyar Kabin Argungu ta yi, na nuni da haske ko annurin wannan basarake. Ke nan, Sarki hasken zangon farin wata ne a garinsa da ma sauran lokutan da yake cikin Sarakuna `yanuwansa, musamman a fagen fama domin ]uriyarsa aka fi ji fiye da kowa saboda jaruntakarsa.

A wani wuri kuma ta kira shi 'gadaragan', gadon da mata ke kwalliya da shi a ]aki, wanda ba a hawan sa. Bisa al'ada wannan ana yi masa }awa ba domin a kwanta ba.Ke nan, jarumin ya gawurta ya kuma buwaya, ya zama abin kallo da sha'awa:

…Gadaragan ba gadon kwanci ba,

ba gadon }ai}ai ba…

(Kirarin Sarkin Kanta)

Ita ma Zabiyar Fadar Ha]eja, ta abuntar da Sarkin Ha]eja da ‘jeji’ da ‘suri’ da ‘inuwa’, kamar yadda take cewa:

…Jeji ba a yi masa }yaure…
Suri ba}in cikin mai gona…
Yaya gara takan yi da dutse sai kallo?

(Kirarin Sarkin Sarki)

“Jeji’ makeken fili ne wanda babu gidaje ko gonaki a cikinsa kewaye da shi, wanda kuma yake cike da bishiyoyi da namun daji. Saboda haka girmansa da fa]insa ya wuce a yi masa }ofa.To haka Sarkin Ha]eja yake, kamar yadda Zabiyar take fa]i a kirarinta. Sarki girmansa ya sa babu wanda ya isa ya takura masa, domin kuwa }arfinsa (a kan jama’ar da yake mulki), ba shi da adadi. Shi ka]ai ya buwayi kowa daga abokan hamayya zuwa mabiya. Ga al’ada ba a yi wa mutum }ofa sai dai abubuwa irin su ‘]aki’ da ‘gida’ ko ‘harabawa’, domin haka a iya cewa Zabiyar ta abuntar da Sarki.

‘Suri’ gini ne mai tudu da huje-huje wanda gara ko zago kan yi. Suri halitta ce da ke cinye wuri wadda kuma ba ta da amfani, sai dai ~ata wuri, musamman ga manomi. Ga shi kuwa ko sare shi aka yi kafin gari ya waye yana iya fitowa saboda buwaya. A nan Zabiyar Fadar Ha]eja ta abuntar da Sarki ta kira shi ‘suri’, kasancewa Sarki ya buwaye su babu yadda za

su yi da shi. Saboda haka tilas suna ji suna gani su ha}ura, ko sun }i ko sun so, dole su bi shi su yi masa biyayya. Kamar yadda manomi ke ha}uri da suri a gonarsa.

Zabiyar Ha]eja a kirarin Magajin Garin Ha]eja ta abuntar ta kira shi, 'mari'. Mari, bisa al'ada, wani }arfe ne da ake ]aure mahaukaci da shi a }afafu, ko yaro mai gudun makaranta. Ana kuma ]aure mai laifi ko bawa da mari. Kasancewa duk bawan da aka sawa mari babu yadda zai yi ya gudu, Magajin Gari, kamar yadda Zabiyar ta kira shi 'mari', marin ne, maganin abokanan hamayya. Tana dai cewa:

…'Mari maganin gudajjen bawa…'

(Kirarin Magajin Ha]eja).

A kirarin Turakin Ha]eja da Ciroman Ha]eja da na [an Buran Ha]eja da [an Darman Ha]eja da Tafidan Ha]eja da Jarman Ha]eja da Mabu]in Ha]eja da ma amaryar Sarkin Ha]eja, duk Zabiyar ta abuntar da su da 'farin iri'. Kamar yadda aka sani, duk manomi yana neman iri na }warai, domin idan aka shuka shi, za a samu 'ya'ya da yawa, a kuma lokacin sayarwa, irin wannan rubanya ba darajar shi ]aya da kowane iri da za a shuka ba. Wannan ya nuna kyakkyawan asali na wa]annan saraki, wanda kuma ya haifar da abu mai asali, watau 'ya'ya ne na }warai ba mutanen banza ba. Kamar yadda take cewa:

…Turaki farin iri abin shukawa…
[an Darman farin iri abin shuka…
(Kirarin Sarakin Ha]eja).

A kuma kirarin Tafidan Ha]eja da Jarman Ha]eja, Zabiyar ta abuntar da su ta kira su 'rumfa' da kuma 'kwano', kamar yadda take cewa:

…Rumfa sha shirgi,

Kwano ba ka karaya…

(Kirarin Tafida / Jarman Ha]eja).

'Rumfa' a al'adance wuri ne mai kama da ]aki da ake yi da ciyawa ko }asa don hutawa ko don kasuwanci. Kamar yadda aka sani rumfa ba ]akin kwana ba ce, saboda haka komai aka jajibo, a kan aza mata a sama. To haka wa]annan saraki suke, duk wata matsala da bu}ata su ake nufa. Su yi ha}uri su ]auki nauyin da duk aka ]ora masu. 'Kwano' kuwa, saboda yanayinsa ba ya kokawa komai zafi komai sanyi. Duk abin da aka zuba masa ba ya gajiya domin ba ya karaya sai dai a ce ya yi 'lamba'. To, haka ma wa]annan saraki suke, kamar yadda kwano yake.

[an Iyan Ha]eja da Mabu]in Ha]eja kuwa, Zabiyar ta abuntar da su da 'tudu', kamar yadda ta ce:

…Tudu abun dafawa…

(Kirarin [an Iyan Ha]eja/Mabu]i).

Tudu fuskar }asa ce wadda ta ]an ]aga sama fiye da wata fuska, wadda kuma takan kasance abun dafawa a lokacin tafiya, musamman ga mara }arfi. To, haka ma wa]annan saraki suke bayar da taimako ga mabu}atu da marasa }arfi kwatancin 'tudu' ga mai tafiya, musamman gajiyayye da ke neman tallafi.

Ita ma Zabiyar Daura ta abuntar da Magajiyar Gari da 'kogi', kamar yadda take cewa:

> …In sa mai kayan da]i tsirga - tsirga kogi…
>
> (Kirarin Magajiyar Daura).

Kogi rami ne mai fa]i da zurfi da tsawon gaske da ruwa ke kwarara a cikinsa, rani da damina. Wannan na nuni da girma da darajar Magajiyar Gari a Masarautar Daura, wadda a da ita ce Sarauniyar Gari kuma duk da cewa yanzu akwai Sarki girma da darajarta na nan. Haka ya sa a lokutan bukukuwan salla }arama da babba da sallar gani ana 'Hawan Magajiya a Daura', tun da can har yanzu. Haka kuma, a wannan rana takanas, Sarki yake kai mata gaisuwa har gida tare da hakimansa. A kuma wannan rana, Sarki da duk hakiman Daura, babu mai sa alkyabba saboda girmama Magajiyar Gari (to sai dai ita da sauran mata 'yan'uwanta masu ri}e da sarautu za su sa alkyabar).

Zabiyar Daura ta kuma abuntar da {auran Daura, ta kira shi 'gwauron mashi', kamar yadda take cewa:

> …In magajin Audu magajin tafi gwauron mashi…
>
> (Kirarin {auran Daura)

Wata ma'ana ta 'gwauro' ban da wadda aka sani yau da kullum (ta tuzuru) ita ce 'fitaccen abu'. {aura fitacce ne a matsayinsa na fitaccen jarumi. {auran Daura sarauta ce ta jarumin namiji (a da can da ake ya}i), shi ya sa har gobe a hawan salla yake ri}e mashi a lokacin da ya kawo cafka yakan ]aga mashin sama sannan ya caka a }asa a matsayin gaisuwa ga Sarki

Ita ma Mai Babban [akin Daura, Zabiyar ta abuntar da ita ta kira ta 'yar wutar ma}era' da 'fure':

'In `yar wutar ma}era fure babba…'

(Kirarin Mai Babban [akin Daura).

Wutar ma}era bisa al'ada ba wutar wasa ba ce. A nan 'yar wutar ma}era' da Zabiyar ta ambato na nufin ]iyar jarumai kuma manyan saraki. Fure kuma na nufin iri na wani abu, saboda haka 'fure babba' a nan shi ne ]aya daga cikin manyan 'ya'yan Sarki, domin a Daura sarautar Mai Babban [a}i, a sarautun mata daga ta Magajiyar Gari ita ce ta biyu. Ba kamar a Masarautar Ha]eja da Kano ba da ake na]a mahaifiyar Sarki wannan sarauta. Ke nan, a Daura' Mai Babban [aki' ]iya ce ba uwa ba.

Sarakin Daura ma Zabiyar ta abuntar da ita da 'riga', rigar ma ta dodo! Sarakin Daura, ]aya ce daga cikin 'ya 'yan Sarkin Daura, masu ri}e da sarauta, wadda }arfinta da huruminta ya sa tana iya yi wa Sarki tawaye, a cire shi daga mu}amin da yake ri}e da shi (a da), Maimuna (1987). Zabiyar tana cewa:

…In juyar kambu ta Mamman rigar dodo…

(Kirarin Sarakin Daura).

Rabi Bazamfara ta kira Sarkin Zazzau 'dodo'. Dodo halitta ce wadda ake suranta ta a hoton zuci, musamman a tatsuniya domin tsoratarwa. Kiran Sarki 'dodo' na nuni da }arfin ikonsa wanda ba a kai masa wargi ganin ya wuce wargin, ya wuce tsara. Zabiyar tana cewa:

…Shigo da }arfin Allah dodo…

(Kirarin Sarkin Zazzau)

Ita ma Zabiyar Kazaure ta abuntar da Sarkin Kazaure ta kira shi ‘hadarin }asa da ‘dare’ da kuma ‘ goshin jirgi’, kamar yadda take cewa:

> …[an hadarin }asa maganin mai kabido,
> Dare marufa asiri,
> Goshin jirgi ba ka tarbuwa..
> (Kirarin Sarkin Kazaure).

‘Kabido’ rigar ruwa ce ta gargajiya da ake yi da kaba, wadda ake sa wa domin kare jiki daga ruwan sama. To, idan kuwa hadarin na }asa ne ba na sama ba, kamar yadda aka saba yaya za a yi? Akwai babbar matsala ke nan.Wannan kwatanci ne tsakanin Sarki da abokan hamayya, wa]anda dole su dangana. Shi ma ‘dare’, kamar yadda aka sani, sirri ne mai rufa asirin jama’a. Kamar kuma yadda dare ke bayar da mafaka haka ma Sarki yake ga jama’arsa, watau shi ne rufin asirinsu. Shi ma kogi ba kamar }orama ba, yana da }arfin gaske, kamar yadda jirgi yake, dukkanninsu, idan suka doso, sai dai a ba su hanya, to haka matsayin Sarki yake. Ko da wasa babu wanda zai yi gaba da gaba da shi, saboda }arfin mulkinsa da buwayarsa.

Zabiyar Kazaure Hajiya ‘Yarsukola ta abuntar Sarki Adamu da ‘tushiya’, inda ta }arasa da ‘mafarar dawa’. Watau ‘asali’ ko ‘salsala’, domin shi ne salsalar Sarki Hussaini Adamu da kuma Sarki Najib Hussaini Adamu (]ansa da jikansa). Lallai wannan farin iri ne. Zabiyar tana cewa kamar haka:

…Sarki Adamu toshiya mafarar dawa…

(Kirarin Sarkin Kazaure, Najib Hussaini).

Zabiya Ajuji Maitazargade ma ta kira Sarkin Kano ‘}asa’ kamar yadda ta ce:

…{asa mai ha}uri Nadabo…

(Kirarin Sarkin Kano)

{asa kamar yadda aka sani ita ke ]aukan komai tare da rufa asirinsu a doronta da cikinta. A nan Zabiyar ta alamta Sarkin Kano ne a matsayinsa na shugaba mai ha}uri. Kamar yadda aka sani, albarkatu suna }ar}ashin }asa. Halittu da dama kuma na samanta. Wannan na nuni ga ha}uri da juriyar basaraken.

**Dabbantarwa:** Dabbantarwa dabara ce ta mayar da mutum ko wani abu dabba, wato a ]auki siffa ka halayyar dabba a ba mutum ko wani abu daban. Maka]a suna amfani da wannan nau’i na adon harshe su cicci~a wani ko su }as}antar da shi. A kirarin da Zabiyoyin Fada kan yi wa saraki, sukan danganta su da dabbobi masu ban tsoro da razana da kwarjini da bajinta ko kyan hali ko iko. Yawanci sukan yi amfani da dabbobi irin su’ zaki’ da’’ giwa da’ amale’ da makamantansu. Sai dai kuma ba sa dabbantar da abokan hamayya da dabbobi irin su ‘mujiya’ da ‘’jaki da ‘bunsuru’ da ‘mujiya’ da makamantan dabbobi masu }as}anci kamar yadda takwarorinsu maza ke yi. Zabiyar Daura ta kira Sarkin Daura ‘amale’ kamar yadda take cewa:

Zabiya : Inuwal dare,

Amshi : Inuwal dare,

Zabiya: Amale,

Amshi: Amale….

(Kirarin Sarkin Daura).

Amale ri}a}}en gawurtaccen ra}umi ne a garke. Baya ga haka, amale dabba ce mai ha}uri/juriya. Saboda haka ta kira Sarki ‘amale’, kasancewarsa shugaba a garinsa kamar yadda amale yake a garke. Shugaba a kullum a shirye yake ya agaza wa jama’arsa. Sannan kuma mai tausayi da ha}uri da su. Masu iya magana na cewa:

‘Wani kaya sai amale wace ayayi mai ]an doro!’

Zabiyar Daurata kuma dabbantar da Magajiyar Daura inda ta kira ta giwa, watau:

…Giwa shiyagi buwayi,

Gida zaman gida ga giwa gagara cinnaki…

(Kirarin Magajiyar Daura).

Ga al’ada, duk wanda aka danganta shi da ‘giwa’, ana nuna girmansa da ha}urinsa, domin giwa dabba ce mai ha}uri. To haka kuma, giwa saboda girmanta, komai girman bishiya idan ta kama sai ta kada ta, wanda ke nuni da girman }arfinta. Masu iya magana na cewa:

‘Alamar }arfi tana ga mai }iba’

Giwa dabbar dawa ce da ta fi kowace dabba girma, mai haure biyu dogaye da hanci mai kama da hannu da manya-manyan kunnuwa. Tana kuma da ha}uri, wanda ya sa. Saboda girma da darajar Magajiyar Daura, Zabiyar ta kira ta giwa. Ko ba komai da Magajiya ita ce Sarauniya a Daura, kuma har yau tana taka muhimmiyar rawa a harkokin iko na masarautar. Saboda haka, har yanzu ana girmama duk mai ri}e da wannan sarauta a Daura. Haka kuma Magajiyar Daura, duk da tana zaman gida ne a matsayinta na mace babu abin da ya gagare ta, kamar yadda kirarin ya nuna. Ta kuma dabbantar da abokan hamayyarta ta kira su cinnaki' (cinnaku). Cinnaka wani ]an }waro ne ba}i mai cizo mai zafi. Duk kuwa da }an}antarsa, amma yake da zafin cizo. To, sai dai ba za a kamanta shi da giwa ba musamman ta fuskar halitta da }arfi.

Zabiyar da ta ci gaba ta kira Magajiyar Gari 'abuyar tsohon zaki', kamar yadda take cewa:

…In sa abuyar tsohon zaki…

(Kirarin Magajiyar Daura).

Tsohon zaki, kamar yadda aka sani fitina ne. Watau fitinanne ne amma aka danganta shi da giwa saboda girmanta da }arfinta. Kamar yadda yake a Daura har yanzu duk da cewa Sarki ke mulki ba Magajiya ba, amma abokiyar shawara ce, musamman abin da ya shafi matan gari da sauran 'yanuwanta mata saraki. Haka ya sa ita ke sa su lalle, da ita kuma ake shawararta idan za a ba wata daga cikinsu sarauta. Har ma da sarautar 'Mai [aki', wadda sarauta ce da ake ba ]aya daga cikin matan Sarki. Akwai kuma inda Zabiyar ta kira Magajiyar Daura:

… Karnan tarda damisa…

(Kirarin Magajiyar Daura).

Bisa al'ada kamar yadda aka sani, damisa ya fi }arfin kowane karen farauta, saboda haka wannan na nuni da buwayar Magajiya da kuma }arfinta. Kalmar 'karnai' a karin harshen Sakkwatanci tana nufin 'fi}a'. Wato ha}orin da ke fara fito wa yaro ko dabba idan ya fara }wari

Zabiyar Ha]eja ma ta dabbantar da Magajin Garin Ha]eja da [an Ruwatau, ta kira su 'ya'yan babban amale', a matsayinsu na 'ya'yan Sarki, kamar yadda take cewa:

…Magajin Gari Ha]eja ]an babban amale…

da

Salamu alaikun Ruwatau ]an babban amale…

(Kirarin Sarakin Ha]eja).

A wani wurin kuma Zabiyar Ha]eja ta danganta Sarkin Arewan Ha]eja da '}arfin giwa'. Watau mai }arfi kamar giwa, wanda kuma ba ya neman mafaka a ko'ina saboda }arfinsa, kamar yadda take cewa:

Sallamu alaikum }arfin giwa,<br>
Ba ka shiga ba ka la~e ruwa,<br>
Ginsau }arfin giwa…<br>
(Kirarin Sarkin Arewa Ha]eja).

Zabiyar Ha]eja ba ta yi }asa a gwiwa ba wajen dabbantar da sarakin Ha]eja, kamar yadda ta dabbantar da [an Darman da 'linzami'. Linzami wani tan}wararren }arfe ne da ake sawa a

bakin doki, a ]aura masa kamazuru, a ri}e don a samu damar sarrafa doki yadda ake so. Wannan na nuni da buwayar basaraken a matsayinsa na jarumin gaske. Kamar yadda linzami ke sarrafa doki/dabba ba a hawansa sai da shi, to haka muhimmancin [an Darman yake a Majalisar Ha]eja. Shi ya sa ma Zabiyar ta }ara da '}arin…", watau shi }ari ne na linzami. [an Darman, hakimi ne kuma ]aya ne daga cikin manyan 'yan majilisar Masarautar Ha]eja. Kamar yadda take cewa:

> …{arin linzami [an Darman…
>
> (Kirarin [andarman Ha]eja)

Zabiyar Kazaure ta dabbantar da Sarkin Kazaure, ta danganta shi da buwayar 'zaki'. Kamar yadda take cewa:

> …Zaki ka saba da ka]ar maza…
>
> (Kirarin Sarkin Kazaure).

A nan ta danganta }arfin Sarki da zaki a matsayinsa na }arfaffa, wanda ba ya jin tsoron komai, kuma ba a samun galaba a kansa. Watau wanda ya bawayi kowa. Zaki kamar yadda aka sani, dabba ce da idan ta tunkari abu sai ta ga bayansa. Zaki dabba ce da ba ta jin tsoro ballantana jin tsoron fa]a, kuma ba ya gudu duk wahala. Sannan kuma, kasance zaki ba kasafai yake kisa ba sai domin abinci, a duk lokaci da zaki ya fito neman abinci rurinsa na razana sauran namun daji domin wanda duk suka yi artabu sai dai wani ba shi ba. Manufar wannan dabbantarwa ita ce, domin a tunatar da Sarki aikin da ke gabansa na juriya da }wazon ri}e jama'a. Haka kuma, duk wanda ya zama Sarki ana san ran ya zama mai hangen

nesa da sanin ya kamata ga jama'arsa. Za a iya ganin wannan manufa ta dabbantarwa a kirarin Sarkin Zazzau, musamman inda Zabiyar take cewa:

…Zaki gyara }asa,
Zaki uban talakawa…
(Kirarin Sarkin Zazzau).

Wannan na }ara tabbatar da matsayin Sarkin Zazzau na shugaba mai gyara ne na duk wata ~arna a }asarsa, kamar yadda yake uba ga dukkan jama'arsa babba da yaro mace da namiji attajiri da talaka.

Zabiyar Kabi ta dabbantar da Sarki Sama da 'hul]e', watau farin doki tas marar sofane a jikinsa. Wannan doki, doki ne na alfarma da ban sha'awa a ido. Wanda ke nuni da basaraken a matsayinsa na mai kwarjini a duk inda ya shiga. Kamar yadda ta ce:

…Hul]e mai idon ~ata na Muhamman…
(Kirarin Sarki Sama)

Fari ga al'ada launi ne mai hasken gaske kamar auduga, domin haka abin so da }auna ne saboda kwarjininsa. Launin 'fari', launi ne na daban (za~a~~e) cikin sauran launuka, kamar yadda Sarki ya kasance cikin jama'arsa. Wannan ya sa Zabiyar ta danganta Sarki da shi, ta la'akari da cewa tasirinsa wajen kyautatawa al'ummarsa da zatinsa da kwarjininsa ba ya misaltuwa.

**Mutuntarwa** : Mutntarwa dabara ce ta ]aukar halayya ko sifa ko daraja da mutum ka]ai aka sani da su, a la}aba wa wani abu mara rai ko dabba ko tsuntsu. Wato mutuntarwa ita ce a mayar da abin da ba mutum ba ya zama mutum. Ke nan, an mutunta shi. Zabiyar Zazzau (Hajiya A'i) ta mutuntar da '}ofa', kamar yadda take cewa:

…Ladab }ofa…

(Kirarin Sarkin Zazzau)

A nan ta mutuntar da }ofa a matsayinta na halittar da ba ta aikata wani abu misali, ladabi da aka ce ta yi wanda aka san mutum da shi. A zahiri an umarci }ofar ne ta yi ladabi amma ana nuni ne ga Sarki ya tafi a hankali domin zai shiga }ofa, saboda ya tafi a sannu. Ta kuma irin wannan dabara ta mutuntar da addini, kamar yadda take cewa:

…Barka da zuwa duddugen addini…

(Kirarin Sarkin Zazzau)

Kamar yadda aka sani mutum ne yake da 'dudduge' ba addini. A nan Zabiyar ta mutuntar da shi yayin da take yabon Sarki da ri}o da addini ko na}altarsa a harkokin iko.

### 5.2.1.2 Alamci

Alamci dabara ce ta bayyana wani abu ta hanyar ba shi wata alama da ta yi kama da shi. (ko ta wakilce shi), dangane da siffa ko yanayi ko ]abi'a. An sami wannan dabara ta alamci a kirarin Zabiyoyin Fada a wannan nazari. Zabiyar Kabin Argungu a kirarin Sarki Muhammadu Kanta ta alamtar da Fulani, ta kira su 'sha]i'. Sha]i kamar yadda aka sani

al’ada ce wadda aka san Fulani da ita, saboda haka Zabiyar ta kira su da shi domin ya zama alama gare su. Ga dai yadda take cewa:

> …‘O’ooh sha]i!
>
> (Kirarin Sarki Kanta).

A duk inda aka furta ‘o’ooh’, mai ma’anar ‘wayyo’ ko ‘kash’, ana nuna takaici ne ko juyayi ga wani lamari. A nan Zabiyar Kabin Argungu tana bayyana tsananin tausayinta (wanda za a iya cewa bai kai zuci ba), ga Fulani na irin halin da suka tsinci kansu a hannun Sarki Kanta. Kamar kuma yadda ta sake kiran Fulanin ‘ruga’, a kirarin Sarki Sama:

> …Rugga na gani kana yadda kas so,
> Rugga ta sauka zamaninka,
> Ga zamaninka ruga ta }are,
> Na Garba ka fi }arfin rugga…
> (Kirarin Sarki Sama).

Ruga wuri ne ko muhalli da Fulani ke zaune da dabbobinsu. A nan ‘ruga’ na nufin Fulani sun }as}anta. Watau ana yi wa Fulani ko Sakkwato habaici saboda gabar da ke tsakaninta da Kabi, domin a wannan lokaci Kabi ta so ta buwaye ta. Wannan ya sa Kabi ce }asar da ta tsira daga mulkin Fulani masu jihadi.

Akwai kuma inda ta yi amfani da kalmar 'fatake' a maimakon 'bayi' da 'masu duniya' a maimako masu mulki, domin mulki na ]aya daga cikin abin da ake alfahari da shi a diniya, musamman a da da Sarakuna ke da cikakken iko. Zabiyar na cewa kamar haka:

…Rana da wata fataken Allah,
Mu kuma fatakenku,
Masu duniya ]an Mamman…
(Kirarin Sarki Kanta).

Zabiyar Kabi ta kuma alamtar da 'harara' ta kira ta 'gira' kasancewa da ido ha]e da gira ake harara. Ga al'ada harara sadarwa ce ta ga~o~in jiki da ake kallon mutum da gefen ido saboda jin haushinsa ko ba shi tsoro (musamman a kan harari yaro idan ya aikata ba daidai ba). A nan Zabiyar na yi da abokan hamayyar sarakin, kamar yadda take cewa:

…Gira ba ta maganin ]an Yakubu Nabame…

(Kirarin Sarki Sama)

Ita ma Zabiyar Ha]eja, ta alamta Sarkin Ha]eja ta kira shi 'sama', saboda yanayin girman Sarki a garinsa, shi ke sama sauran jama'a na }asa da shi, musamman abokan hamayya. A nan, a ce Zabiyar Ha]eja tana yi da abokan hamayyar Sarki, ta hanyar }ara tabbatar masu matsayinsa. Sarki a cikin al'ummarsa ya zarce kowa, ya wuce tsara, domin shi ne gaba da su. Zabiyar tana cewa kamar haka:

…Sama ta yi wa yaro nisa…
(Kirarin Sarkin Ha]eja)

Kamar yadda Zabiyar Zazzau ta alamta ‘ya’yan Sarki da ‘takalmin }arfe’ saboda }arfin ikonsu a matayinsu na saraki:

…[an/’yar Sarki mai takalmin }arfe…
Kowa ka/kika taka ya taku…
(Kirarin `ya`yan Sarkin Zazzau).

Zabiyar Ha]eja ma a wani gefen ta alamtar da Jarman Ha]eja da Mai Babban [akin Ha]eja da ‘girman ba}o’, watau mai karrama ba}i hannu bibbiyu a kuma biya masu bu}atunsu, idon sun zo da wata bu}ata:

…Jarma girman ba}o…
(Kirarin jarman Ha]eja)

Salamu alaikum sallama girman ba}o…
(Kirarin mai Babban [a}in Ha]eja).

A kirarin [an Iyan Ha]eja kuwa, ta alamta shi ne da ‘bugun tama’ da kuma ‘tudu’, kamar yadda take cewa.

…Abdu bugun tama sha nishi,
Tudu abun dafawa…
(Kirarin [an Iyan Ha]eja).

‘Bugun tama’ alama ce ta abu mai  wuya ko wata wahala da kwarafniya. Za a iya cewa buwayar [an Iyan Ha]eja, musamman kasancewarsa jarumin namiji ya sa Zabiyar ta ambaci wannan matani. Tudu kuwa abin dogaro ne, wanda ke nuni da basaraken a matsayinsa na mai taimako.

Ita ma Uwargidan Sarkin Ha]eja, Zabiyar ta alamta ta da ‘tutar fari’, kasancewarta mata ta fari a gidan, kamar yadda take cewa:

…Yayale tutar fari…
(Kirarin Uwargidan Sarkin Ha]eja).

Zabiyar Kano, ta yi amfani da hikimar harshe ta alamtar da wanda  ya yi mata sanadiyyar zuwan ta Fadar Kano, ta kira shi ‘dalili’. Wato wanda ya yi mata sanadin zuwa Masarautar Kano har ta fara Zabiyanci a fadar.Ta kuma alamta ‘yin hanya’ ko’ sanadi’ da ‘dalili’. Sannan ta kira mai sukuni (mai wadata ko hali)’dalili’ kamar yadda take cewa:

…Ina zaune na ce mai dalili,
Da ma ka yi min dalili…
Ta kai ni na je na gaida uwar Nadabo,
Uwarsu mai dalili…
Yau dalili ya yi dalili, sai ga ni cikin Birni Kano,
Mai dalili ya yi kirki,
Sai ya duba gida mai kyau ya ba ni…
Ina godiya da arzikinsa mashashan Kano na Abdu…
(Kirarin Sarkin Kano).

Ita ma Zabiyar Kazaure ta alamta ‘tsawan lokaci’ ta kira shi ‘nisan kwana’, a kirarin ]an babban Sarkin Kazaure, Muhammadu, kamar yadda take cewa:

> …Allah Ka }ara mana martaba da nisan kwana…
>
> (Kirarin ]an Babban Sarkin Kazaure, Muhammadu)

A nan Zabiyar ta yi wa sarakin fatan tsawon rai domin ya gaji sarautar gidansu, kasancewa wannan ne fatan duk wani saraki.

**5.2.1.3 Hotoncin Zuci**

Hotoncin zuci ]aya ne daga cikin nau’o’in adon harshe da mawa}a kan yi amfani da shi ta hanyar bayar da labarin wani abu ko bayyana shi cikin wa}a. A kirari ma a kan sami haka. Hotoncin zuci dabara ce ta zayyana abu a tunanin mai sauraro ko makaranci ta hanyar kallon wani batu a idon zuciya. Alalmisali Zabiyar Fadar Kano, Hajiya Ajuji Maitazargade, ta bayar da labarin yadda ta zo Fadar Kano, har ta zama Zabiyar Mai Martaba Sarki Ado Bayero, kamar yadda take cewa:

> …Ina zaune na ce mai dalili,
> Da ma ka yi min dalili,
> Dirhami gidan Sarkin Kano,
> Da dalili ya yi,
> Na zo neman arziki Birnin Kano,
> Na yi wata uku ina nemansa ban gan shi ba,
> Sai na ce ba zan je gida ba sai na je gidan Kano,
> In gano Uwar –uwar Nadabo,

Uwar Marke Kabiru,

Ko tana gida ‘yar Ladi?

Da dalili ya kai ni gidan Sarkin Kano,

Yarinya mai mudun awo,

Zumuntar Yahaya Magajin Baba,

Ta kai ni na je na gai da uwar Nadabo,

Uwarsu mai dalili,

Sai na ce a kai ni na gai da Sarkin Kano,

Abdu jikan Abdu,

{asa mai ha}uri Nadabo,

Na je na gai da Sarkin Kano na Abdu,

Ya ce ina kuka samu Zabiya Maigari?

Suka ce da dalili saboda yawo,

Yau dalili ya yi dalili sai ga ni cikin Birnin Kano,

Mai dalili ya yi kirki,

Sai ya duba gida mai kyau ya ba ni,

Ga shi na yi zaman Kano…

(Kirarin Sarkin Kano).

Babu shakka, Zabiya Ajuji ta yi amfani da hikima ta bayar da labarin zuwanta Kano, musamman Fadar Kano a cikin kirari. Da farko ta sanar da mai sauraro yadda ta yi wata uku a Kano, kafin ta ha]u da wani da ba ta ambaci sunansa ba, sai dai ta alamta, ta kira shi ‘mai dalili’, wanda shi ya yi mata iso ( ta ambaci sunansa daga baya a kirarin). Ta ci gaba ta bayar da hoton yadda ya fara ha]a ta da wata wadda ta kai ta domin ta gaishe da ‘Mai Babban [aki’, daga nan kuma ya kai ta wurin Mai Martaba Sarkin Kano. Ta kuma }ara nuna

irin wannan basira, ta bayar da labarin auren Hajiya Saude ]iyar Sarkin Musulmi Abubakar III, ga Sarkin Kano Ado Bayero, kamar yadda take cewa:

> …A yi mana gudunmuwa da idanu,
> Ga ‘yar mai yanka mutane,
> Jikar mai yanka mutane,
> Za mu kai ta gidan mai magana da mulki,
> [an Maje Nassarawa jikan Maje Nassarawa,
> Jikan Mai suka da mashi,
> Jikan Alu Mai Kano,
> Ina godiya da arzikinsa mashashan Kano na Abdu,
> Rannan mun ga abin mamaki,
> Ba mota da mota ba, mota tana ta tashi,
> Mota sai ka ce gindin zama,
> Birnin Kano babu ragi nasa,
> Ga babur da mota wa yake yance da keke?
> Ranar zuwan Hajiya Saude,
> Rannan na ga abin da dama,
> Albarkar mazarga dodo sai raga,
> Muka ci karo da Mai Babban [akin Kano Uwar gari tasa,
> Sai ga sa}e da sa}e na Sakkwato,
> Ga riguna da riguna,
> Ga turmi da turame,
> Ba a batun buta…
> (Kirarin Sarkin Kano).

A nan kuma Zabiyar ta fara da bayar da labarin auren tun daga Sakkwato, daidai lokacin da aka fito da amarya, za a kai ta Kano, kamar yadda ta ce:

…Ga ‘yar mai yanka mutane…

Za mu kai ta gidan mai magana da mulki…

(Kirarin Sarkin Kano).

Zabiya Ajuji ta ci gaba ta gina labari a kan isowar amaryar birnin Kano ta hanyar nuni ga abubuwan al’ajabi da suka faru a wannan rana. Abubuwa da suka ha]a da yawan motoci da riguna daban-daban da turamen atamfofi da sa}e irin na Sakkwato. Wannan duk yana nuni da irin bikin da aka yi na manya, kamar yadda ta kira,”…’Yar mai yanka mutane…” Watau aure irin na tsakanin saraki:

…Rannan mun ga abin mamaki…

(Kirarin Sarkin Kano).

Ita ma Zabiyar Kabin Argungu ta yi }o}arin fito da wannan dabara ta hotoncin zuci, kamar yadda ta }ara wa Sarki Kanta }arfin gwiwa jaruntakar da aka san shi da ita. Ta yi amfani da wannan dabara ta gina labari ta kwatanta zaman duniya da zuwa kasuwa. Za a iya ganin haka a inda Zabiyar ta yi nuni da cewa kamar yadda ake cin kasuwa a bar ta, haka zaman duniya yake. Ta ci gaba ta }ara nuni da cewa zaman duniya ba na rago ba ne, domin haka gara a fita a fafata a yi suna. A wani ~angare kuma ta zuga Sarki Muhammadu Kanta:

…Yau duniyag ga ba ta raggo ta ba Kanta,

Haka lahira ba ta raggo ta ba Kanta,

Idan duniya gida ta matabbaci,

Ka duba daga kassuwa in safiya ta yi,

Kassuwa cika za ta yi,
Idan rana ta yi kassuwa cika za ta yi,
Idan maraican nan ya yi, wani ya sayar,
Wani bai sayar ba,
Da ita da jin da]in nan nata,
Kana gida za shi ko da jan masare,
Ko da zafi da garin damina Kanta gibiri-gibiri…

(Kirarin Sarkin Kanta).

Zabiyar ta gina labari ta hanyar nuni da cewa duniya da lahira duka ba na rago ba ne. Ta kwatanta jin da]in zaman duniya da cin kasuwa. Ga al'ada duk yadda kasuwa ta kai muddin maraice ya yi dole a watse, kowa ya kama gabansa. Kamar yadda komai da]in zaman duniya idan lokacin barinta ya yi, za a bar ta ko da ya}i ko babu ya}i. Zabiyar ta zuga Sarki Kanta ta hanyar nuni da cewa, idan lokacin barin duniya ya yi, ko da ya}i ko babu shi dole a mutu. Saboda haka gara a fito a fafata a fagen fama ta hanyar nuna bajinta, idan mutuwa za a yi a mutu. Ke nan da a mutu haka nan salin'alin, gara a yi suna:

…Idan duniya gida ta matabbaci,
Ka duba daga kassuwa idan safiya ta yi…
Wani ya sayar,
Wani bai sayar ba,
Da ita da jin da]inta,
Kana gida za shi ko da jan masare… (watau ko da kayan ya}i).
(Kirarin Sarki Kanta).

#### 5.2.1.4 Tamka

Tamka dabara ce ta kwatanta abubuwa biyu ko fiye da haka dangane da darajarsu. A }o}arin kwatanta abubuwa, ana la’akari da wasu darajoji da za su iya zama na daidaito ko na fifiko ko kuma na kashi. Ana kwatanta abubuwa ta hanyar amfani da wasu kalmomin kamantawa ko kalmomi na tsakanin ko mizani da za su kwatanta abubuwa mabambanta. Misali, a ‘tamka ta daidaito’, ana amfani da kalmomi irin su ‘ *kamar’* da’ *tamkar* ‘da ‘ *sai ka ce’* da ‘*dai dai da*’ *da ‘i kaza*’ da sauransu. A ‘tamka ta fifiko’ kuma, ana amfani da kalmomi irin su ‘*wuce* ‘da ‘*zarce’* da ‘*tsare’* da *‘]ara’* da ‘*babu kamar’* da ‘*ya fi’* da makamantansu. Sannan a ‘tamka ta kashi’ ko ‘gazawa’, ana amfani da kalmomi irin su ‘*bai kai ga’* da *’babu kamar’* da ‘*kasa’* da ‘*gaza’* da makamantan wa]annan kalmomi masu }as}antar da wani abu a kan waninsa. Masana irin su [angambo (1981) da Yahya (1997 da 2002) da kuma Gusau (2003) sun kira wannan nau’i na adon harshe ‘kamantawa’.

Zabiyar Ha]eja ta yi amfani da wannan nau’i na adon harshe, ta kamanta sarakin Ha]eja wa]anda suka gaji sarauta da wa]anda ba su gaje ta ba, da kamanci na fifiko. Wannan na }ara tabbatar da cewa wanda ya gaji sarauta ko da wasa ya ]ara wanda ya tsince ta rana tsaka. Kamar yadda take cewa:

> …[an na gada ya fi ]an na koya…
>
> (Kirarin Sarakin Ha]eja).

Zabiyar ta y irin wannan kamanci na fifiko tsakanin damina da Sarkin Ha]eja:

> …Gamo da Sarki ya fi gamo da damina…
>
> (Kirarin Sarkin Ha]eja).

Zabiyar Ha]eja ta kwatanta ni'ima da albarkar damina da Sarkin Ha]eja, ta hanyar nuni da cewa Sarkin ya fi ta nesa ba kusa ba. Duk kuwa da cewa albarkar damina ba ta misaltuwa, domin baya ga samun isasshen abinci akwai ni'ima na dausayi.

Rabi Bazamfara kuwa ta kamanta Sarkin Zazzau ne da kakansa Sarki Sambo, kamanci na daidaito a matsayinsu na Sarakunan Zazzau. Wannan na nuni da darajar Sarakunan wanda ya kasance ]aya, kamar yadda take cewa:

> …Idan babu Sambo kai ne Sambo…
> (Kirarin Sarkin Zazzau).

Matan Sarkin Zazzau ma ta yi masu wannan kwatanci na daidaito. Kodayake ta ce sai Sarki ba ya nan suke zama saraki, sa~anin Sarki da kakansa Sarki Sambo da suke da matsayi ]aya.

> …Idan babu Sarki tamkar ku Sarakuna ne…
> (Kirarin Matan Sarkin Zazzau).

### 5.2.1.5 Kwalliya

Kwalliya dabara ce ta ]aukar darajar wani abu a ]ora wa wani kai tsaye ba tare da amfani da wani abu tsakani ba. Kwalliya siffantawa ce kamar kamantawa/ kwatantawa, sai dai ita kwatance ne na kai tsaye da a kan ]auki darajar wani abu a ]ora wa wani kai tsaye, ko a ce 'kaza' shi ne 'kaza'. Maro}an fada sukan danganta Sarakuna da abubuwa masu kwarjini da }ima da tsoro. Sukan yi haka ne kuwa domin kambama ubangida ko }askantar da abokan hamayya domin su tsorata su. Yahya (1997) da Gusau (2003), sun kira wannan nau'i

‘siffantawa’. Gusau (2003:57), ya yi sharhi kan wannan kamar yadda yake cewa,”Manazarta wa}o}in Hausa sun yi tsokace-tsokace daban-daban dangane da kwatancen siffantawa. Alalmisali wasu manazarta suna kiran siffantawa da ‘Hoto Cikin Bayani’ wasu kuma ‘Kwalliya’. A ra’ayin masu cewa kwalliya, suna ganin kwalliya tana zayyana abu ne ta }awata shi ya fito rambatsai, ta yadda duk wanda ya kale shi sai ya sake mayar da kallo. Wasu manazartan sun karkasa siffantawa zuwa gajeriyar siffantawa da kuma doguwar siffantawa (dubi [angambo, (1981:14) da Yahya (1997:140-167 da 2001:58-94 da kuma 2002:220-237) ya bayyana siffantawa da cewa ‘salo ne da ke kawo hoton abu yadda mawa}i ke bu}atar mai karatu ko mai sauraren wa}arsa ya kalle shi da idon zuciyarsa ko tunaninsa, salon siffantawa hoto ne da kalmomi suka kawo da ma’anoninsu’, (1997:14). A ra’ayinsa, siffantawa ta }unshi kamance da jinsarwa da alamtarwa da kinaya da kuma zayyana (2002:223)”. Domin haka idan aka ]auki wannan ra’ayi nasu, kwalliya siffantawa ce. Akwai kuma masanan da ke da’awar cewa kwalliya ta }unshi dukkan nau’o’in adon harshe gaba ]ayansu. Su ma Zabiyoyin Fada ba a bar su a baya ba wajen amfani da wannan nau’i na kwalliya a kirarin da suke yi wa saraki. Misali, Zabiyar Kabin Argungu a kirarin Sarki Muhammadu Kanta tana cewa:

…Zakin Sarakuna,  
Magume uban duniya,  
Kakan duniya Sarki,  
Sidi mai taimako da na Allah…  
(Kirarin Sarki Kanta).

A nan Zabiyar ta kira Sarki Kanta zaki kai tsaye ( Zakin Sarakuna). Zaki kamar yadda aka sani shugaba ne na namun dawa. Ke nan Sarki Kanta shugaba ne a cikin Sarakuna

‘yanuwansa, watau Sarki ne na Sarakuna. Ta kuma kira shi ‘kakan duniya’, saboda buwayarsa da }arfin iko, musamman a fagen fama. Akwai kuma wurin da Zabiyar ta kira Sarki Kanta ‘guguwa’, kamar haka:

> … Guguwa sha da gatari…
> (Kirarin Sarki Kanta).

Guguwa ‘iska’ ce mai }arfin gaske wadda take mi}ewa sama tana juyawa. A ma’ana ta biyu kuma, guguwa ita ce ‘matsanancin gudu’. A nan, Zabiyar ta yi amfani da kwalliya ta kira Sarki Kanta kai tsaye ‘guguwa’, saboda }arfinsa na jaruntaka ta siffanta shi da ita. Guguwa dai idan ta taso ko an jefe ta da gatari an yi aikin banza. Duk kuwa da cewa gatari makami ne na }warai amma ba a iya sare guguwa da shi. A kirarin Sarki Sama Zabiyar ta kira sarakin da kalmomi irin su ‘farshin wuta’ da’gulbin teku’ da ‘hadari’ da kuma ‘katangar dutse’, kamar haka:

> ...Farshin wuta na Ya}uba…
> Gulbin teku mai wuyar iyo ]an Bawa…
> Hadari sa gabanka inda ka sammawa…
> Katangar dutse daga gungura sai kallo…
> (Kirarin Sarki Sama).

Farshin wuta, wuta ce mai ci ganga –ganga ko garwashi da ya ci ya ruru. Ke nan, kamar yadda wuta ke ci ganga-ganga, haka Sarki Sama yake a matsayinsa na jarumin namiji kuma gawurtacce wanda babu wargi ko kasala tare da shi, musamman a fagen fama.

Zabiyar ta kira shi ‘gulbin teku’, kamar yadda bisa al’ada ‘gulbi }aramin kogi ne amma mai wuyar iyo. To haka ma Sarki Sama ya gagari abokan hamayya. Ya gagari a yi masa takakka sai dai shi ya yi.

‘Hadari’ kuwa girgije ne wanda ke da alamar saukar da ruwa. Zabiyar Kabin Argungu ta kira Sarki Sama ‘hadari’ saboda ba shi da shamaki ko tsoro a al’amuransa. Duk inda ya sa gabansa, gaba – ga]i yake babu shakku ko fargaba, domin babu tsoro tare da shi. To haka kuma, a iya cewa Sarkin cike yake da ni’ima tamkar yadda hadari yake. Domin kuwa, ganin hadari alama ce ta samun wata ni’ima daga Allah. Ni’imar ruwan sama da dausayi.

‘Katanga’ ginin laka ko siminti ne da ake kewaye gida da shi saboda kariya. Katangar laka ko siminti ta zama garkuwa, ballantana ta dutse? Nan gani nan bari! To, haka Sarki Sama yake ga abokan hamayya, kamar yadda Zabiyar ta fa]i a wannan kirari. Ta ci gaba ta kira shi ‘du}usuman’ ingantaccen dutse, dutse na gari mai nagarta. Ke nan, kamar yadda Sarki Sama ya zama ]a na gari abin alfahari, ya yi ramakon gayya ga Fulani da suka ci zarafin iyaye da kakanninsa kafin a sami sulhu a tsakaninsu a zamaninsa. Zabiyar Kabin Argungu na cewa:

> …Du}usuman ingantaccen dutse…
>
> (Kirarin Sarki Sama).

Akwai kuma inda Zabiyar Kabi ta kira Sarki Kanta ciyawar nan ta ‘aya-aya’ saboda buwayarsa, musamman ga abokan hamayyarsa, kamar yadda take cewa:

> …Ai Kanta gandun aya-aya na…
>
> (Kirarin Sarki Kanta).

Ciyawar ‘aya’aya’, ciyawa ce da ta bambanta da wadda aka sani. Ciyawa ce wadda ba a iya kashe ta a gona, saboda haka kawar da ita wahala ne. Wannan na nuni da buwayar Sarki Kanta a matsayinsa na jarumi gawurtacce da ya gaggari sauran jarumai a fagen fama,wato Sarki ne mai wuyar kawarwa. .

Ita ma Zabiyar Kazaure (‘Yarsukola) ta kira Wamban Kazaure ‘gagara badan Sarakuna’:

…Wambai ]an gagara badan Sarakuna…
(Kirarin Wamban Kazaure).

Kalmar ‘gagara badau’ tana nuni ga buwayar wani abu, domin haka Wambai ba kanwar lasa ba ne. Ta kuma kira Sarakunan Kazaure ‘alfanda saboda buwaya da }arfin iko’:

…Lafiya alfanda…
Taka da lafiya ]an-ja-gaban Sarakuna ]an Alfanda…
Zaki ka saba ka]ar maza…
(Kirarin Sarakin Kazaure).

A Kirarin Yarima ma tana cewa:

…Yarima magajin Yarima,
Makana ruwan da]i…
(Kirarin Yariman Kazaure).

Zabiya ‘Yarsukola ta yi amfani da ‘gagara badau’ (‘gagarabadon’ Sarakuna), ta kira sarakin Kazaure. Gagara badau ‘sanda ce da ake kara wa }ofa domin hana mutane wucewa’, ko

kuma ‘mai tsawata wa a majalisa’. Wannan na nuni ga sarakin Kazaure a matsayinsu na jarumai wa]anda suke kariya ga jama’arsu, sannan kuma masu bayar da umarni a bi dole. ‘Alfanda’ kuwa, kalma ce da ake amfani da ita a kirarin saraki domin nuna }arfin ikonsu da buwaya. Zaki kamar yadda aka sani Sarki ne a dawa tamkar yadda Sarki yake mai cikakken iko da bajinta a }asarsa. Zaki dabba ce da ke ka]a ran sauran dabbobi a dawa, musamman lokacin da ya fito neman abinci. Ta kuwa kira Yariman Kazaure ‘makana’ (makani a daidaitacciyar Hausa), kalmar da ke da ma’a’noni biyu. Na farko shi ne‘nau’in abinci dangin mabun}usa }asa mai kama da gwaza. A ma’ana ta biyu kuwa ‘makani’ shi ne ‘jinka da ake yi a kan rumfa wanda ake shiga a kwanta don maganin sauro’. A nan a iya ]aukar ma’ana ta biyu wadda ke nuni da cewa sarakin kamar yadda ‘jinka’ take kare jama’a daga sauro, tamkar haka shi ma yake kare jama’arsa da }asarsa, a matsayinsa na jarumi kuma gawurtaccen namiji wanda jan gwarzo ne da ake fargaba.

Zabiyar Daura ta kira Sarkin Daura ‘amale’ da inuwar dare’. Ta kira Magajiyar Daura ‘giwa’ da ‘karnan tarda damisa’. Kamar yadda su ma matan fada (matan Sarki) ta kira su ‘giwa’, ta kuma kira Markan Daura ‘ sandar }arfe da zaki’. Duk kuwa ta yi haka ne domin tunzura su da cicci~a su da kambama sarakin da kuma razana abokan hamayya, domin su ja da baya. Abokan hamayya musamman Fulani da suka }wace mulkin masarautar na tsawon shekara ]ari, kafin mulki ya sake dawo wa hannunsu. Kamar yadda take cewa:

…Inuwal dare,
Amale…
(Kirarin Sarkin Daura)

…Giwa shigayi buwayi…,

Baje –bajen toranke karnan tarda damisa…

(Kirarin Magajiyar Daura).

…In zana tali giwa tali…,

Ta Mamman giwa sagwarmaye…

(Kirarin Matan Fada)

…In da zaman homa ]an }arfaffa,

Sandar }arfe da zaki Marka…

(Kirarin Markan Daura)

Zabiyar Daura ta yi amfani kwalliya ta kwatanta sarakin Daura kai tsaye da wasu manyan namomin daji irin su zaki da giwa da kuma amale saboda kwarjininsu da buwaya da girmaman iko. Kamar yadda ta kira Markan Daura'sandar }arfe' wacce sanda ce ta musamman da saraki ka]ai suke da hurumin mallakarta (sandar }arfe ga al'ada sanda ce ta girma da ake ba saraki lokacin na]in sarauta). Ta kira Sarkin Daura'inuwar dare' saboda buwayarsa, duk kuwa da cewa aljani ne kawai ke da inuwar dare. Kalmar 'inuwa' za ta iya ]aukar ma'ana uku: (i) surar abu da haske ya ]auka (ii) wurin da babu zafin rana da kuma (iii) yalwa ko wadata. Wa]annan ma'anoni na iya ]aukar surar sarakin. Da farko duk da cewa aljani ka]ai ke da inuwar dare shi ma basaraken saboda }arfinsa ko bajintarsa da girmansa ko buwayarsa, aka kira shi 'inuwar dare'. Na biyu kuwa shi ne basaraken ni'ima ne ga al'ummarsa. Sannan kuma mai yalwa da wadata ne, musamman ga jama'arsa.

Zabiyar Ha]eja ma ba a bar ta a baya ba wajen yin amfani da nau'in kwalliya. Ta kira Sarkin Ha]eja 'rana' da 'toron giwa'. Kamar yadda Galadiman Ha]eja shi ma ta kira shi

‘toron giwa’, sannan ta  kira wasu daga cikin sarakin Ha]eja ‘`ya`yan babban amale’. Ta kuma kira Ciroma ‘]an maciji’, ta kira uwargidan Mai Martaba ‘farin tuwo’. Ta ci gaba ta kira [an Iya ‘bugun tama’. Kamar haka:

…Rana ba ki mu}ama…
… Toron giwa sha zamani…
(Kirarin Sarkin Ha]eja).

Salamu alaikun toron giwa lumfasa fada,
Dubu a matsarar kowa….
(Kirarin Galadima Ha]eja)

Salamu alaikum ]an babban amale,
…Ku ne Buhari ku ne Sambo…
(Kirarin Magajin Ha]eja)

Salamu alaikum Baba Ciroma,
[an babban amale,
…[an maciji wanda ya fi shuri da sawu…
(Kirarin Ciroman Ha]eja)

…Uwargida Sarautar mata,
Kwari tankarin gida,
Fari da]in tuwo…
(Kirarin Uwargidan Sarkin Ha]eja)

Salamu alaikum `yar na gada,

….Allah ya ji }an [an Iya Abdu,

Abdu bugun tama sha nishi…

(Kirarin Amaryar Sarkin Ha]eja).

Kwatancen kai tsaye ko kuma kwalliya kamar yadda bayani ya gabata da Zabiyar Ha]eja ta yi na kiran wasu sarakin Ha]eja 'toron giwa', na nuni ga }ima da kwarjininsu. Toron giwa gawurtaccen namijin giwa ne. Kamar yadda 'bugun tama' da amale ke nuni ga }arfin sarakin da girmansu da kuma darajarsu, musamman a idanun talakawansu.

Zabiyar ta kuma kira Sarki inuwa 'Inuwa' gagara bunna', kamar yadda ita ma Zabiyar Daura ta kira Sarkin Daura 'inuwar dare'. A nan Zabiyar Ha]eja tana yi ne da abokan hamayyar Sarki domin inuwa kamar yadda aka sani ba rami ba ne bullantana a rufe. Saboda haka ana ganinta a zahiri dole a bar ta ko an so ko an }i. Wannan haka yake tsakanin Sarki da abokan hamayyarsa, ya zama }adangaren bakin tulu. Ke nan, "Dole a ce da mijin Iya Baba". Kamar yadda take cewa:

…Inuwa gagara bunna…

(Kirarin Sarkin Ha]eja)

Har ila yau Zabiyar ta kira Sarkin Ha]eja 'dutse'. Dutse kamar yadda aka sani, ya fi }arfin gara ta ci shi. Saboda haka Sarki ya gagari abokan hamayyarsa domin ya fi }arfinsu. Tsakaninsu sai dai kallo. Nan gani nan bari:

…Yaya gara takan yi da dutse sai kallo…

(Kirarin Sarkin Ha]eja)

A kuma kirarin Sarki Sama, Zabiyar Kabin Argungu ta kira shi' sadaukin Sarki' da 'jigon Sarakuna. Wannan na nuni da matsayin basaraken na' jarumin Sarki' kuma' shugaba ko jagoran Sarakuna', wanda ya kasance fitacce, musamman a fagen fama. Zabiyar tana cewa kamar haka:

…Jigon Sarakuna ]an Muhammadu Uban Kabawa Kanta…
Sadaukin Sarakuna na Zarmakwai mai danda…
(Kirarin Sarki Sama).

Zabiyar Zazzau ta kira Sarkin Zazzau 'sadaukin Sarki':

…Sadaukin Sarki,
Zaki gyara }asa gyara duniya,
Zaki uban talakawa…

(Kirarin Sarkin Zazzau).

'Sadauki', jarumi ke nan. La}abi ne kuma da ake kiran mai suna Abubakar. Zabiyar ta kira Sarkin Zazzau 'zaki', a matsayinsa na uba ga jama'arsa, musamman masu rauni ko marasa }arfi. Sarki a matsayinsa na shugaba yana amfani da }arfin ikonsa, ya gyara duk wani abu da ya ~aci ko ya lalace, ya kuma kawo abin alheri ga }asarsa. Kamar yadda ta kira uwargidan Sarki da 'kwarin gida', saboda kwarjinita a matsayinta na matar basaraken ta farko, shugabar dukkan matan gida da ta kafa turken da ba mai iya cire shi (kamar yadda ake yi wa kowace uwargida wannan kirari):

‘Uwargida kwarin gida tankarin gida…’

Ita ma Zabiyar Ha]eja haka ta kira uwargidan Sarkin Ha]eja. Baya ga kiranta ‘farin tuwo’, wanda haskensa ya sa yake da sha’awa da kwarjini, kamar haka:

Kwari tankarin gida,
Fari da]in tuwo,
Uwargida ta }afa gida,
Uwargida ta kafa gida ya zauna…
(Kirarin uwargidan Sarkin Ha]eja)

Zabiyar Kano Hajiya Ajuji Maitazargade ta kira Sarkin Kano Ado Bayero’Mashasha’, kalmar da ke nuni ga mashahurin mai arziki. Wannan na nuni da arziki da kyautar mamaki ta Sarkin Kano wadda ba ta da iyaka, domin a kullum cikin bayarwa yake ba tare da gajiyawa ba Zabiyar tana cewa kamar haka:

…Ina godiya da arzikinka mashashan Kano na Audu…
(Kirarin Sarkin Kano).

Zabiyoyin Fada sun yi amfani da kwalliya matu}a. Kodayake ba amfani da kalmomin ban tsoro kamar takwarorinsu maza. Alalmisali, ba a ji ]uriyar kalmomi kalmomi irin su:

‘katakore’ da ‘wandara’ da ‘tan}wafau’ da ‘aljani’ da ‘zarto’ da ‘]ibgau’’ da makamantansu ba.

### 5.2.1.6 Karin Magana

Karin magana fasaha ce ta mayar da zance mai tsawo zuwa gajere. [angambo (1984), ya bayyana karin magana da dabarar dun}ule magana ko zance a cikin ‘yan kalmomi }alilan, cikin hikima da fasaha. Mawa}a na amfani da karin magana a wa}o}insa, to haka ma Zabiyar Fada takan yi amfani da karin magana a kararin da take yi wa saraki domin nuna fasahar harshe ta hanyar dun}ule magana cikin jimla guda wadda take da cikakkar ma’ana. Misali, Zabiyar Kazaure (‘Yarsukola) a kirarin Sarkin Kazaure tana cewa:

> …[an alfanda,
> [an hadarin }asa maganin mai kibido…
> (Kirarin Sarkin Kazure)

Wannan na nuni da buwayar basaraken kamar yadda hadari ko ruwan }asa ya gagari kabido. Ita ma Zabiyar Ha]eja, ta yi amfani da karin magana a wurare da dama kamar haka:

> ..Rumfa sha shirgi…
> (Kirarin Tafidan Ha]eja)
>
> …Suri ba}in cikin mai gona…
> (Kirarin Sarkin Ha]eja)
>
> …Sama ta yi wa yaro nisa…
> (Kirarin Sarkin Ha]eja)

…[an na gada wanda ya fi ]an na koya..
(Kirarin sarakin Ha]eja)

…Farin iri abin shukawa…
(Kirarin sarakin Ha]eja)

…[an maciji wanda ya fi shuri da sawu…
(Kirarin Ciroman Ha]eja)

‘Rumfa sha shirgi’ na nuni ga ha}urin sarakin Ha]eja da rashin nuna gajiyawarsu ga taimakon talaka. Tamkar yadda rumfa ta kasance yadda ga al’ada duk abin aka jaji~o ake jefa mata. Kamar yadda ‘Farin iri’ ya kasance abin nema wajen za~in irin shukawa . Wannan na nuni da nagartar sarakin Ha]eja, a matsayinsu na mutanen arziki ba na banza ba. Farin iri a kullum ana kyautata zaton ya bayar da ru~anya ta gari. Amfani da karin maganganu irn su; ‘Suri ba}in cikin mai gona’ da’Sama ta yi wa yaro nisa’ da ‘[an na gada wanda ya fi ]an na koya’ da kuma ‘[an maciji ya fi shuri da sawu’, karin maganganu ne masu nau’in habaici. Kamar yadda aka yi bayani }ar}ashin habaici. Zabiyar Ha]eja tana yi da abokan hamayyar sarakin Ha]eja ne a fakaice. A kan fake a yi da abokan hamayya a fakaice domin fitowa fili na iya haddasa wata fitina, kamar yadda Zabiyar Kabin Argungu ita ma ta yi da abokan hamayyar sarakin Kabi, a inda take cewa:

...[a mai zuciya ka ramkon gayya…

(Kirarin Sarki Sama)

Zabiyar Kabi ta yi amfani da wannan karin magana domin jinjina ga Sarki Sama na biyan bashin da ya yi ga Fulani (Toronkawa) da sauran }asashen da ya ya}a a zamaninsa. Sarki Sama ya yi ramakon gayya ne na cin zarafi da aka yi wa iyayensa.Wannan na nuni da cewa Sarki Sama ya cika ]a.

Zabiyar Kano ta yi amfani da karin magana da ke nuni ga ha]in kan sarakin Kano. Masu iya magana na cewa "Hannu ]aya ba ya ]aukar jinka", kuma "Ha]in kai ba ha]in baki ba" Ke nan karin maganar na tabbatar da cewa babu hamayya tsakanin sarakin Kano, domin kansu ha]e yake. Kowa na son ]an'uwansa. Saboda haka babu hamayya a tsakaninsu kamar yadda aka san sauran saraki da hamayya da ta auku a sanadiyyar neman sarauta.

…Tsintsiya ma]aurinki ]aya…

(Kirarin Sarkin Kano)

**5.2.1.7 Amsa kama**

Amsa kama furuci ne da sautinsa ke da ma'anarsa. Maro}an baka na amfani da amsa-kama cikin wa}o}insu domin nuna balaga. Zabiyar Fada tana amfani da wannan salo a kirarinta. Zabiyar Kabin Argungu ta yi amfani da amsa-kama a wurare kamar haka:

…Ai Kanta gandun aya-aya na,
Na gaba birjim na baya birjim…
(Kirarin Sarki Sama).

da

…Ragasa tunku watarma son ya}i…,
Ko da zafi da garin damina gibiri – gibir…

(Kirarin Sarki Kanta).

da

…Da}ile-}ishali ]an Yakubu Nabame…

(Kirarin Sarki Sama).

da kuma

… Hur]e mai idon ~ata na Muhamman…
Gadan – gadan ]an Ya}uba…
(Kirarin Sarki Sama).

Zabiyar ta yi amfani da ‘Gadan-gadan’ mai nuni da fiye ko aiki da }arfi babu tsayawa. Watau kamar yadda Sarki Sama yake ke nan,ba shi da kasala wajen ya}i. Wannan na nuni da jaruntar Sarki Sama ya yi fice a zamaninsa. Sama Sarki ya kasance gawurtaccen jarumin namiji.

Zabiyar Daura, Dakamar Sarkin Daura ta yi amfani da kalmomin amsa-kama a kirarin Sarakin Daura:

…In suke kimammaye,

Innuwal dare saraki abokin jiro…
(Kirarin Sarkin Daura).

…In sa mai kayan da]i tsirga –tsirga kogi…
In sa ta mammaye…
(Kirarin Magajiyar Daura).

…Ta Mamman giwa sagwarmaye…
(Kirarin Matan Sarkin Daura).

…In sungumi mafarar da}in burema,
Tagam mafarar burema…
(Kirarin Galadiman Daura).

Zabiyar Kano ta yi amfani da' kure da kure' (watau yawa babu iyaka), domin nuni ga irin kyautar basaraken:

…Mai zubau kure da kure…
(Kirarin Sarkin Kano).

Rabi Bazamfara ta yi amfani da 'ni}atau' a kirarin Sarkin Zazzau:

Fito da }arfin Allah ni}atau,
Taka da }arfin Allah ni}atau…
(Kirarin Sarkin Zazzau).

Kalmar 'ni}atau' amsa kama ce wadda aka yi amfani da ita a kirarin Sarkin Zazzau. Kalmar tana nuni ga }arfin ikon Sarkin Zazzau Shehu Idris. Ga al'ada }arfin Sarki a masarautarsa,

musamman a da can da }arfin ikon Sarki ba ya misaltuwa, saboda mulki da iko sun ba shi dammar yin abin da ya so. Ko ya kashe ko ya rayar tamkar mahalicci ga ne al'ummarsa. Wannan ne ya sa ake yi wa Sarki la}abi da 'Sarkin yanka'. Kuma ake kiransa, "Ba}on dole" (wanda aka ce ko gidan mutum ya je ya fi shi).

### 5.2.1.8 Kambamawa

Kambamawa dabara ce ta ]aukaka abu fiye da yadda hankali zai iya ]auka/aminta. Maro}a musamman na fada suna amfani da wannan nau'i na adon harshe domin su ]aukaka iyayen gidansu, su kai su inda ba su kai ba. Zabiyar Kabin Argungu ta kambama nasarar da Sarki Sama ya samu a ya}e-ya}en da ya yi da Fulani, kamar yadda take cewa:

> …Gira ba ta maganin ]an Ya}uba Nabame,
> Amma a aika da shi a sami lafiya,
> Domin birni tamanin da goma sha biyar ya tu~e na Fulani,
> Kabawa ku yi hankali Sama ba shi wargi…
> (Kirarin Saraki Sama)

Wannan kambamwawar zula}e ce, domin Zabiyar Kabin Argungu ta ce Sarki Sama ya ci garuruwan Fulani har tasa'in da biyar (95)! Ba goma ba ko ashirin ko kuma talatin ba? Tarihi ya nuna cewaSarki Sama ya ya}i garuruwan Fulani da ke kewaye da Kabin Argungu, ya kuma sami galaba a kan wasu daga cikinsu, amma ba tasa'in ba kamar yadda Zabiyar ta ce. Wannan ya wuce ]aukar hankali. A wani wuri kuma tana cewa:

> …Wadda duk gidan sarauta ya girma,
> Bai da salsala da martaba da muhibba,

Irin gidan Muhammadu Kanta…

(Kirarin Sarki Sama)

A nan ma a ce Zabiyar Kabin Argungu ta kambama wannan masarauta a kan girma da salsala da martaba da muhibbarta. Kodayake masu jihadi ba su sami nasara kan masarautar Kabi ba, kamar yadda suka ri}a ]ora Fulani `yanuwansu su maye gurbin Sarakunan da suka sami nasara a kansu a sauran {asasshen Hausa. Saboda haka, dole a yaba masu domin sun jajirce wajen }watar kansu hannun Torankawa. Tun zamanin uban Kabawa, Sarki Muhammadu Kanta, ya zuwa yanzu zuri'arsa ke gadon mulki a masarautar Kabin Argungu, duk kuwa da cewa akwai lokacin da aka sami nasara a kansu. Amma ba a sami nasarar tu~e su daga gadon sarautar da suka gada kaka da kakanni ba. Sai dai a ce an sha gwagwarmaya da su. Masu iya magana na cewa, "Da }yar na sha gara da }yar aka kama ni".

Ita ma Zabiyar Daura ta kambama Sarkin Daura ta hanyar nuni da cewa hatta rana tana fargaba idan ta ga Sarkin, saboda jaruntakarsa da buwayarsa kuma da }arfin ikonsa.

....Rana ta yi hwargaba rana taka…

(Kirarin Sarkin Daura)

Dakamar Sarkin Daura (Zabiyar Daura), ta kambama Sarkin Daura yadda hankali ba ya aminta, domin ta ce rana idan ta ga Sarkin Daura tana fargaba. (tana jin tsoransa ko shakkarsa). Duk kuwa da cewa an yi wannan kirari lokacin da ake da sauran ~ir~ishin addinin gargajiya, lokacin da za a ce, shi kansa Sarki ranar Ubangijiyarsa ce. A wani wuri kuma ta ce shi ne 'makashin zaki' da kuma 'dodo', duk kuwa saboda buwaya da }arfin jaruntakarsa:

Zabiya : Makazaki,
Amshi : Makazaki,
Zabiya : Makadodo.
Amshi: Makadodo…
(Kirarin Sarkin Daura).

Bisa al’ada dodo abu ne da ake tsoransa mutu}a, domin an yi imani cewa dodo ya fi }arfin mutum, Sarki kuma ya fi }arfin dukkan al’ummarsa. Sai dai a ce ban da dodo domin a zamanin da aka aiwata da kirarin al’ummomi da dama sun dogara ga bautar dodo, da lokacin da ake ‘kan gida’ da shi. Zabiyar Daura a wannan kirari ta kambama Sarkin da cewa ya fi }arfin dodo saboda buwayarsa, har ta yi ikirarin shi ne ‘makashinsa’. Ke nan shi mai kashe dodon ne har ma da zaki. Zaki dabba ce mai }arfin gaske kuma mafa]aci wanda ya sa ake kiransa, ‘Sarkin dawa’ amma Zabiyar ta ce Sarki yakan sami nasara a kansa, har ma ya kashe shi. Ta yi haka ne domin ta kambama Sarkin, ta kuma tsoratar da abokan hamayyarsa domin su ja baya.

Zabiyar Kabin Argungu ta kambama Sarki Sama saboda buwayarsa. A kirarin, Zabiyar ta ce buwayar Sarki Sama ta sa wani maigari sanadiyyar barin garinsa da sasassafe ko kalaci yi ba saboda tsoron ha]uwa basaraken. Wannan kuwa ya faru ne artabu da Sarki Sama ba alheri ba ne. Zabiyar Kabin Argungu ta kambama Sarki Sama saboda }arfin jaruntakarsa da ya sa maigari gudu ya bar garinsa. A maimakon ya tsaya ya kare su daga hayin maya}a irin su Sarki Sama. Kamar yadda a tunanin Bahaushe ake tsammanin Sarki ya kare jama’arsa iya }arfinsa daga duk wani bala’i da ka auku:

…Hana zahahe mai sa uban gari gudu shi bar birni nai…
(Kirarin Sarki Sama).

### 5.2.2 Salon Aiwatar da Harshe a Zabiyancin Fada

Aiwatar da harshe shi ne irin dabarar da fasihi ya bi na za~ar kalmomi domin isar da sakonsa, musamman a adabi. Alalmisali, amfani da sababbin kalmomi ko kalmomin dauri ko kuma na aro da makamantan haka domin sarrafa su, musamman a adabi. A wannan nazari an za~i a nazarci fagen za~en kalmomi daga kirarin da Zabiyoyin Fada ke yi wa saraki a {asar Hausa. A za~en kalmomi an ta}aita ga amfani da kalmomin dauri (wato tsofaffin kalmomi) da na aro, domin an lura cewa su ne suka yawaita a kirarin. Ke nan, ba za a nazarci yadda Zabiyoyin ke amfani da }i}irarrun kalmomi ko sababbi ba.

#### 5.2.2.1 Tsofaffin Kalmomi

Tsofaffin kalmomi su ne aka yi wa la}abi da ‘kalmomin dauri. Tsofaffin kalmomi kalmomi ne wa]anda da can zamani mai nisa da ya shu]e aka yi amfani da su. Watau kalmomin da yanzu saboda tsawon lokaci mai nisa da tasirin wasu harsuna a kan wasu, suke nema su ~ace. Tsofaffin kalmomi, kalmomi ne wa]anda aka fi jin ]uriyarsu a adabin baka. Misali, wa}a da kirari. Da ma ]aya daga cikin muhimmancin kirari shi ne raya harshe, ta hanyar amfani da tsofaffin kalmomi. A wajen amfani da tsofaffin kalmomin Hausa, a ce Zabiyoyin Fada sun shahara matu}a, musamman Zabiyar Kabin Argungu da ta Daura. A iya cewa kasancewa an aiwatar da kirarin a wa]annan fada shekaru da dama da suka shu]e, ya haifar da haka. Tun a farkon kirarin Sarki Muhammadu Kanta, aka fara jin kalmomin dauri:

…Arnan Bagudu

Sidi  Manzon Sarakuna….,

Magume uban duniya Sarki…,

Kana gida za shi ko da jan masare…

Ragasa tunku watarma son ya}i,

Gadaragan ba gadon kwanci ba,

Ba gadon }ai}ai ba…,

Du}usuman  ingantaccen dutsai,

Mai uwa kan kasari,

Mai uba kasausawa ranar ya}i,

Ingarma an ka jinka…

An ka ba ku domin ya}i….

(Kirarin Sarki Kanta).

Kalmar 'arna' ko kuwa 'arne' a maganar yau da kullum tana nufin 'wanda ba shi da addinin' ko 'matsafi', watau wanda ke bin addinin gargajiya na kaka da kakanni. Ko kuwa 'duk wanda ba ya bautar ubangiji Allah, bayan bayyanar addinin Musulunci'. To amma, Hausawa a da can (a Maguzance), suna amfani da wannan kalma a matsayin 'abokin gaba', ko kuma 'abokin hamayya' ko kuwa 'jarumin gaske'. Domin haka, kalmar 'arnan…' da Zabiyar ta yi amfani da shi, tana nuni ga 'gawurtacce', 'jajirtaccen jarumi', Sarki Muhammadu Kanta.

Zabiyar Daura ta yi amfani da wannan kalma a kusan mafi yawan kirarin sarakin Daura, in ban da na Galadima da na Al}alin Garka/Malaman Fada da na Durbin Daura da kuma na Magajiyar Daura. Alalmisali:

Zabiya: Hawan `yan Bawo,

`Y/Amshi: Hawan `yan Bawo,

Zabiya: Kakan *anna*,

`Y/amshi: Kakan *anna…*

(Kirarin Sarkin Daura)

…Aminin makadodo,

In `yan maran maza da yawa,

[an mu je mu da anna…

(Kirarin Magajin Garin Daura)

…[an mu je mu da anna,

In ]an sasarin mutu ko dai ri}o..

(Kirarin |unturawan Daura)

Kirarin Sarkin Daura na nuni da cewa basaraken 'kaka' ne na jarumai', wanda ya rinjayi abokan hamayya. To, haka kuma sauran sarakin Daura, kirarin nasu na nuni da jaddada cewa sun gaji jaruntaka, domin 'ya'ya ne da jikoki na jarumai wa]anda idan suka shiga sararin fama suke da ra'ayin ri}au na ko dai a mutu ko kuma a yi rai tsakaninsu da abokan hamayya'.

Ita ma kalmar 'Bagudu' da Zabiyar Kabin Argungu ta yi amfani da ita, a iya cewa a yau, jama'a da dama sun ]auke ta a matsayin sunan maza**.** 'Bagugu', la}abi ne da ake yi wa 'jarumin namiji' wanda ba kowane namiji ba ne, sai wanda a fagen fama 'Ba ya gudu', 'ba

ya ja da baya’ komai tsanani. Domin haka, kalmar tsohuwar kalmar Hausa ce wadda aka tsince ta a wannan kirari, kamar yadda Zabiyar take cewa:

…Arnan Bagudu…
(Kirarin Sarki Kanta)

…Bagudu mun gode ma…
(Kirarin Sarki Sama).

Kalmar ‘Sidi’ ita ma tsohuwar kalmar Hausa ce da ke da ma’anar ‘Sharifin mutum’. Ko Sarki Kanta sharifi ne ko ba sharifi ba ne, Zabiyar Kabin Argungu ta kira shi ‘Sidi, kasancewa kamar yadda sharifi wuta ba ta }ona shi, domin haka ba ya fargabanta ko tsoronta, to haka ma basaraken yake ‘sharifi a fagen gama’. Ya}i ba ya tsoratar da shi, kasancewa shi kansa ya}in ne, kamar yadda Zabiyar ta fa]a a cikin kirarin sarakin:

…Kowwag gane ka ya ga ya}i,
Wanda bai ganka ba bai ga matuwa…
(Kirarin Sarki Kanta).

Tarihi ya nuna cewa a zamaninsa, Sarki Kanta ya sami nasara a mafi yawancin ya}e-ya}en da ya yi da daulolin Hausa. Wannan kalma (‘Sidi’) ta dace da shi matu}a. Kanta jarumin jarumi ne’ }i gudu sa gudu’. Bayan zuwan Musulunci an sami fa]a]a ma’ana ta wannan kalma, a inda ake yi wa duk mai suna ‘Abdu}adir la}abi da ‘Sidi’. Ma’ana ta biyu ke nan, wadda ta samo asali tasirin addinin Musulunci.

Zabiyar Kabi ta yi amfani da kalmar ‘magume’, wadda ita ma tsohuwar Hausa ce da ke da ma’anar ‘gajeran mutum’ kakkaura’ kuma ‘}arfaffa’, wanda ba rago ba ne. A ma’ana ta

biyu ‘magume’ shi ne ‘doki matsakaicin tsawo’. A nan, a iya cewa Zabiyar ta sarrafa kalmar da nufin ma’ana ta farko, kamar yadda ta ce:

…Magume uban duniya Sarki…
(Kirarin Sarki Kanta).

Wannan na nuni }arara cewa duk da gajartar basaraken, wannan bai hana shi zama fitacce cikin sauran ‘yanuwansa Sarakuna ba saboda jaruntakarsa. Ga al’ada gajeran mutum yakan so a san da zamansa a duk inda yake domin bai cika son raini ba.

Akwai kuma inda Zabiyar ta kira Sarki Kanta, ‘Gadaragan’. Wannan kalma ta dauri ce mai ma’anar ‘gadon da mata ke yi wa kwalliya ko }awa matu}a’, wanda kuma ba a kwanciya a kansa saboda wannan ado. {ila wannan ya sa Zabiyar ta ce:

…Gadagaran ba gadon kwanci ba,
Ba gadon }ai}ai ba,
Shi ke tarar da }wan}wani…
(Kirarin Sarki Kanta).

Kiran basaraken ‘gadagaran’ na nuni da cewa Sarki Kanta jarumin duniya ne wanda ya zama abin sha’awa a zamaninsa. Watau ya kasance jarumi ne na gani a fa]a. Domin kuwa a lokacin da daulolin Hausa suke ya}e - ya}en junansu, jarumin Sarki yakan kasance abin rububin sauran Sarakuna saboda dalilai biyu. Na farko shi ne, domin kada ya kawo masu hayi. Na biyu kuma domin ya agaza masu idan wata }asa ta kawo masu hari. Sarki Kanta ya zamanto }adangaren bakin tulu kafin Allah ya amshi ransa.

‘Du}usuman’ ma tsohuwar kalma ce ta wani nau’in dutse na musamman, wato dutse mai daraja, mai inganci. Zabiyar ta suranta Sarki Kanta da wannan dutse, a matsayinsa na

tauraron jarumai. Kamar yadda ta sarrafa kalmar ‘kasari’ a kirarin. Kasari tsohuwar kalmar Hausa ce da take da ma’anar ‘asabari’. Wato mai uwa ke da gata har yake samun asabarin da zai shimfi]a ya kwanta. Kamar yadda masu iya magana suke cewa, “Mai uwa a bakin murhu ba ya cin tuwonsa gaya”. Zabiyar tana cewa:

> …Mai uwa kan kasari…
> (Kirarin Sarki Kanta).

Akwai kuma inda Zabiyar Kabin Argungu ta yi amfani da kalmomin ‘kasausawa’ (kasassawa) da ‘jan masare’. Kasausawa a Hausar dauri wani mashi ne mai tsawon gaske. Kamar yadda ‘jan masare’ ma wani nau’in kayan ya}i ne wa]anda dukkansu ‘yanzu ba amfani da su saboda wayewar zamani. A ma’ana ta biyu ta ‘kasausawa’, kalmar na nufin ‘tun}aho’ ko ‘bugungaba’ ko kuma ‘fariya’. Wannan ya sa mai wannan mashi (kasausawa) a zamanin da aka yi ya}i yake tan}aho da fariya a fagen fama domin yana da kayan aiki ingantacce na gari. Zabiyar Kabin Argungu tana cewa:

> …Mai uba ka kasausawa ranar ya}i…
> (Kirarin Sarki Kanta).

Kasancewa Fadar / Masarautar Kabin Argungu ta yi suna kan jaruntaka, an kuma sami sunayen nau’o’in kayan ya}i biyu a kirarin Sarki Sama, wa]anda kamar ‘kasausawa’ da ‘jan masare’, yanzu sai a ]akunan tara kayan al’adu ake ganinsu. Watau ‘takuba’, da ‘kibiya’. ‘Takobi’ (takuba), makamin }arfe ne mai tsawo, mai siffar wu}a wanda ake amfani da shi wajen ya}i ko kare hari. ‘Kibiya’ kuwa, tsinke ko sililin kara ne da ake ]osa wa wani }arfe

mai kaifi da tsini don yin amfani da shi wajen harbi tare da taimakon baka. Kamar yadda Zabiyar ta kawo su:

> …Gabanka takuban fama bayanka masun daga,
> Yamma gare ka 'yan kibau sun daza kwai,
> Ko da masu son taya fansa…
> (Kirarin Sarki Sama).

Zabiya ta kuma yi amfani da 'ragasa' a Sarki Kanta:

> …Ragasa tunku watarma son ya}i…
> (Kirarin Sarki Kanta).

Kalmar 'ragasa' wadda asalinta shi ne 'ragas', kalmar amsa kama ce da ke nuna mutuwar kasko ko kayan aras. 'Tunku' kuwa, wata }aramar dabbar daji ce mai gashi kamar kyanwa, amma girmanta ya ]ara na kyanwa, kuma tana da mummunan wari. 'Watarma', kalma ce da ta sano asali daga 'wuta', wacce wata halitta ko iska ce mai zafi da ake amfani da ita a }ona ko a gasa ko a dafa wani abu. A ma'ana ta biyu , watarma na nufin 'ya}i ko rikici ko hargitsi'. Ke nan, kamar yadda ma'anonin wa]annan kalmomi ya nuna, Sarki Kanta jarumin jarumai ne wanda ganinsa a fagen fama ba alheri ba ne, musamman ga abokan hamayya. Kasancewa ganin nasa ko dai mutuwa ce ko kuma mummunan gamo, kamar yadda dabbar 'tunku' take. Ko kuwa hargitsi ko rikici domin babu abin da ya sa gaba sai ya}i. Wannan, ya sa Zabiyar ta siffanta basaraken da mai 'son ya}i', domin haka duk wanda ya gansa ya ga ya}i. Wanda kuma suka yi artabu a fagen fama, a ce ya gamu da ajalinsa.

A kirarin  Sarki Sama, an sami tsofaffin kalmomi irin su ‘tsumbure’ da ‘da}ili’ da ‘hul]e’ da ‘budunbuduma’ da ‘katsantsan’ da ‘takuba’ da ‘kibau’ da kuma ‘arbaminya’. Kalmar ‘tsumbure’ tana da ma’anonihar guda hu]u.

(i) Ya}une
(ii) Noma wani wuri a }i nome wani wurin a gona.
(iii) Binne ciyawa da }asa ba tare da an sare ta ba a gona.
(iv) Aske wani wuri a bar wani a kai.

A nan a iya cewa Zabiyar Kabin Argungu na nufin ma’anonin duka. Alalmisali, idan aka binne ciyawa da }asa ba tare da an sare ta ba a gona, shuka za ta ya}une saboda rashin wadatar isasshen wuri, domin ciyawar za ta sake tsirowa. Kamar yadda Zabiyar take cewa:

…Ruga na gani kana yadda ka so,
Yau ina laifin na Garba?
Gaba in ta yi tsumbure ka nome…
(Kirarin Sarki Sama).

Sarki Sama ya yi ramakon gayya ga Fulani, abokan hamayyar iyaye da kakanninsa. Wannan na nuni da cewa idan ya yi tsumbure, kamar yadda ciyawar da aka yi tsumbure kan tashi ta nemi kashe shuka a gona, Fulani  za su fin }arfinsa wata rana. Wannan ya sa ya gama da su gaba ]aya, kada a yi ‘da na sani’. Saboda haka Zabiyar take cewa kada a ga laifin gwaninta:

…Yau ina laifin na Garba?
(Kirarin Sarki Sama).

Kalmar ‘da}ili’( da}ile) ma tsohuwar kalmar Hausa ce, wadda ke da ma’anar ‘}in amsa kira’ ko’ }in magana’, saboda miskilanci. Ambaton wannan kalma a kirarin na nuni da cewa Sarki Sama, mutum ne mara son magana wanda haka ya sa ya kasance mai gaskiya. Kamar yadda bisa al’ada, an aminta da cewa; yawan magana na sa }arya. Zabiyar Kabin Argungu tana cewa:

…Da}ili kishali ]an Yakubu Nabame,
Yawan magana kan sa }arya,
Ai ko kurum magana ta…
(Kirarin Sarki Sama).

Wannan ya tabbatar da cewa Sarkin Sama mutum ne mai gaskiya da imani da ita. Tun a farkon kirarin domin tun a  Zabiyar ke cewa:

…Sama kowwwag }i  gaskiya ka }i shi…
(Kirarin Sarki Sama)

A kirarin na Sarki Sama an tsinci kalmar ‘hul]e’, wadda ke da ma’anar ‘farin duki tas marar sofane (dabbare-dabbare a jikinsa). Akwai kuma kalmar ‘budumbuduma’, kalmar da ke siffanta mutum mai son duniya. Sannan da kalmar ‘danda’, wadda ita ma wani irin nau’in doki ne mai ba}a}en }afafu da farin goshi. Kamar yadda Zabiyar ta sarrafa su a kirarin:

…Hul]e mai idon ~ata na Muhamman…
Sadaukin Sarakuna na Zarmakwai mai danda…
(Kirarin Sarki Sama).

Baya ga wannan, an kuma sami kalmar ‘arbaminya’, a kirarin Sarki Sama. ‘Arbaminya’, tsohuwar kalma ce da ke nufin ‘]ari hu]u (400). Arba’in (40) sau hu]u ke nan. Wannan nau’i ne na lissafi a Hausar dauri da Hausawa suka aro daga Larabci.

A kirarin Zabiyoyin Ha]eja da Kano an tsinci kalmar ‘ginsau’. Ginsau la}abi ne da ake yi wa mai suna ‘Haruna’. A masarautar Ha]eja, kasancewa sunan Sarkin Arewan Ha]eja ‘Haruna’, Zabiyar ta yi amfani da wannan la}abi:

…Ginsau }arfin giwa…
(Kirarin Sarkin Arewan Ha]eja)

…Sannan irin Ginsau wan Nuniya…
(Kirarin Sarkin Kano)

An kuma sami kalmar ‘haula’, a kirarin sarakin Ha]eja:

…Allah Ya ji }an Sarki Usman,
Haular mabu]in Hausa,
Halar mabu]i Sulaimanu,
Haular mabu]i Abubakar…
(Kirarin [anburan Ha]eja).

…[an na gada wanda ya fi ]an na koya,
Haular mabu]i Sulaiman,
Haular mabu]i Ibrahim,
Haular mabu]i Muhamman…
(Kirarin Mabu]in Ha]eja).

‘Haula’ na da ma’anonin ’reshen bishiya’ ko ’karan dawa’ ko kuma ’dangi’ ko ‘zuri’a.’ A nan Zabiyar Ha]eja ta yi amfani da ‘haula’, a matsayin ‘zuri’a’, watau [anburan Ha]eja da Mabu]in Ha]eja tsatso ne daga Mabu]i Sulaiman da Mabu]i Materi da Mabu]i Ibrahim da kuma Mabu]i Muhamman. To haka kuma, ana yi wa {asar Ha]eja kirari da:

‘Haular Mabu]in Hausa’.

{asar Ha]eja ce ta yi iyaka da daular Barebari. Kasancewa Ha]eja mabu]in shigowa {asar Hausa daga Barno, ya sa ake yi mata wannan kirari, domin ita ce {asar da ta raba {asar Hausa da wata daula. Kiran Ha]eja ‘Mabu]in Hausa’ ba kuskure ba ne, domin Ha]eja ta ta~a zama }ar}ashin Barnon kafin ta ~alle saboda jaruntaka. A wannan lokacin ne kuma daular Sakkwato ta so ta koma }ar}ashinta amma Ha]eja ta }i. Ke nan, Ha]eja ta ta~a zama kan gashin kanta, kafin yanzu da take }ar}ashin daular ‘Usmaniyya’ saboda Musulunci.

Sarautar ‘Galadima’ sarauta ce ta ‘hakimi’ a {asar Hausa. A Masarautun Kano da Ha]eja, Galadima na ]aya daga cikin masu jiran gado. A Daura da Katsina kuwa, Galadima yana ]aya daga cikin masu za~en sabon Sarki, domin sarauta ce wadda ba ta `ya`yan Sarki ko zuri’arsu ba. To amma Galadima shi ne kusan uba ga ‘ya’yan Sarki, domin shi ke yi masu sallama wurin Sarki da waliyanci idan za su yi aure. Haka ya sa ake yi wa Galadima kirari da ‘tomo lumfasa fada’. Wannan kalma ta ‘tomo’, la}abi ne na Galadima a Hausar dauri. An tsince ta a kirarin uwargidan Sarkin Ha]eja, kasancewarta ]iyar Galadima:

…Salamu alaikum `yar tomo lumfasa fada,
Uwargida sarautar mata…
(Kirarin Uwargida Sarki Ha]eja).

Har ila yau an tsinci kalmar' tama' a kirarin amaryar Sarkin Ha]eja, kamar yadda Zabiyar ke cewa:

…Allah Ya ji }an [an Iya Abdu,
Abdu bugun tama sha nishi,
An kwana lafiya an tashi lafiyar `yar Garba…
(Kirarin Amaryar Sarkin Ha]eja).

'Tama' ]anyen }arfe ne wanda yake gauraye da dutse da ake ha}owa daga }asa, a dafa kafin ya zama }arfe zalla. Narkar da }arfe domin sarrafa shi ne 'kira', ]aya daga cikin tsofaffin sana'o'in hannu a {asar Hausa. Wannan kirari na nuni da cewa, '[an Iya Abdu ([an Iyan Ha]eja), tamkar bugun tama ne saboda jaruntakarsa, kasancewa bugun tama ba sana'a ko aikin rago ba ce. Wannan kalma ta 'tama' kalma ce wadda zamani ya sa Hausawa da dama ba su san ta ba.

Ita ma Zabiyar Daura ta yi amfani da kalmomi masu ala}a da wannan kalma ta 'tama'

…In da zaman homa ]an }arfaffa,
Sandar }arfe da zaki Marka…
(Kirarin Markan Daura)

…[an }otar ma}era fure babba…

(Kirarin Dur~in Daura)

In fa]ega faskaran tama…

(Kirarin {auran Daura)

…In `yar wutar ma}era fure bbba…

(Kirain Mai Babban Da}in Daura)

.

‘Sanda’ bisa ga al’ada, wadda aka fi sani ita ce ta itace. Watau wadda aka sarrafa daga reshen bishiya. To, amma idan aka ce, ‘sandar }arfe’, ana nufin ‘sandar girma’ ke nan. Sandar }arfe sanda ce da ake ba Sarakuna domin nuna alamar mu}aminsu ko mulkinsu. Ana ba su sandar ne a lokacin da aka rantsar da su. ‘Faskaren 'tama’ ]aya yake da bugun tama’, kamar yadda aka yi bayani a baya. ‘Wutar ma}era’ kuwa ita ce gawurtacciyar wutar da a kan ha]a a ma}era domin nar}ar da tama ko }arfe, kafin a sarrafa shi zuwa nau’o’in abubuwa daban-daban.

A kirarin Sarakin Daura, an tsinci kalmar ‘toranke’:

…Baje-bajen toranke karnan tarda damisa…

(Kirarin Magajiyar Daura).

A kirarin Magajiyar Daura, Zabiyar ta kira ta ‘toranke’. Toranke shi ne gawurtaccen namijin giwa ko namijin ~auna ko na agwagwa. Zabiyar ta siffanta Magajiya da ‘toranke, karnan tarda (kama) damisa, kasancewa ba ko wane irin karen farauta ke iya kama damisa ba.

Damisa dabba ce mai zafin fa]a da mugunta, amma Zabiyar Daura ta ce Magajiya ta fi }arfinta a matsayinta na jarumar gaske.

To fuskar nau'in halitta, akwai wata dabba wadda ita ba doki ba, ba kuma jaki ba, watau 'alfadari'. Alfadari, dabba ce mai siffofin jaki irin na doki, wadda kuma girmanta ya fi na jaki amma ba ta kai doki ba. Afadari dabba ce mai kama da doki amma kuma jelarta irin ta jaki. Wannan dabba yanzu ana samun ]a]aikunta a gidajen saratu na {asar Hausa, domin dabba ce ta musamman wadda ake ji da ita. A kirarin da Zabiyar Daura ke yi wa Matan Sarkin Daura, ta yi amfani da 'alfadari' ta siffanta su, kasancewarsu mata masu }ima da daraja a idanun al'umma, saboda girman sarautar mijinsu. Wannan ne ya sa ga al'ada, da wuya ake ganin matan Sarki a waje kuma ko da Sarki ya rasu, babu wani namiji daga cikin al'ummarsa da zai fito ya ce zai auri wata daga cikin matansa, domin matsayinsu na iyayen al'umma. To haka ma, alfadari dabba ce ta musamman wadda ake lura da ita matu}a domin darajarta. Kamar yadda Zabiyar take cewa:

> …In funce giye karya wu}a}e alfadarin masu ]akuna…
> (Kirarin Matan Sarkin Daura)

Zabiyar Daura ta maimaita kalmar 'Korau' a wurare da dama a kirarin sarakin Daura. Alalmisali:

> …In Bunturawan makazaki da Korau,
> Bunturawan makadodo da Korau Zaki…
> (Kirarin |unturawan Daura)

> …In har Magajin Har]o aminin makazaki da Korau…

(Kirarin Sarkin Fulani Daura)

…In ko sunguni babban ]an Korau…

(Kirarin Dur~in Daura)

‘Korau’ la}abi ne da ake yi wa wanda aka haifa aka sa sunan maigida da bai da]e da rasuwa ba. To haka kuma, la}abi ne da ake yi wa ‘Shamaki’. Shamaki shugaba ne na masu ]aure dawaki, wato sarauta ce ta manyan amintattun bayin Sarki a fada. Zabiyar ta yi amfani da ma’ana ta biyu ta ‘Korau’, domin Shamaki a Daura da wasu fadoji na {asar Hausa, amini ne cikin na hannun daman Sarki. Misali a Daura bayan masu za~en Sarki sun cika aikinsu, a kan kai wanda aka za~a gidan Shamaki ya yi mako biyu, domin a nuna masa al’adun sarauta. Al’adu kama tun daga hul]a da jama’a da sauran tanade-tanaden da al’ada ta gindaya, kafin a yi wankan sarauta. Wannan ya sa duk Sarkin da aka za~a Shamaki yake zama babban amini cikin bayinsa, saboda wannan sha}uwa ta mako biyu. Baya ga wannan, ga al’ada ba kowane bawan Sarki ake ba wannan sarauta ta Shamaki ba, sai amintacce, kasancewa ana iya ha]a baki da shi a cuci Sarki. A ta}aice, ‘Korau’, Hausar dauri ce ta mai ri}e da sarautar ‘Shamaki’.

Zabiyar ta kuma yi amfani da kalmar ‘sagagi’ a kirarin matan Sarki. ‘Sagagi’ a Hausar dauri jeji ne kusa da birni ko alkarya. Ma’ana, idan aka ce }unar ruwa da zafi, a je jeji, wurin da ba za a sami ruwan ba. Kusan a ce wannan habaici ne. Ke nan, duk halin da ake ciki a yi godiya. Masu iya magana ma na cewa; “Idan ba a godewa Allah ba a godewa azabarsa”. Kamar yadda take cewa:

…In }unar ruwa da zafi ga sagagi…

(Kirarin Matan Sarkin Daura)

Zabiyar Daura ta kuma yi amfani da kalmar ‘homa’ ta siffanta Markan Daura. Kalmar ‘homa’, tsohuwar kalma ce ta Hausa da ke da ma’anoni har guda hu]u.

(i) {in cin abinci ga dabba alhalin tana so

(ii) Yanga ko fele}e

(iii) Nuna isa

(iv) Ragar da ake sawa zare domin kamun kifi.

A nan idan aka ]auki ma’ana ta uku, ‘nuna isa’, ba a kuskure ba. Wannan ma’ana ita ta fi dacewa, domin bisa al’ada, nuna isa, ]abi’a ce da aka san saraki da ita, musamman manyan ‘ya`ya masu jiran gado. Sarautar ‘Markan Daura’, sarauta ce ta ]aya daga cikin manyan `ya`yan Sarki, wanda kan kasance na biyu ko na uku. Saboda haka, amfani da wannan kalma ta ‘homa’, ta dace da basara}en matu}a, domin }arfin iko na sa saraki ya nuna isa a duk inda yake, musamman a gaban talakawansa. Kamar yadda Zabiyar take cewa:

…In da zaman homa ]an }arfaffa…
(Kirarin Markan Daura).

A kirarin Galadiman Daura, an tsinci kalmar ‘burema’ da `jajeri(-n) da ‘makoma’ a kirarin Sarkin Ban Daura. A yayin da aka sami kalmar ‘falke’ a kirarin {auran Daura. Sannan kuma, aka tsinci ‘mashigi’ da ‘kambu’ a kirarin ]aya daga cikin ‘ya’yan Sarki mata da ke ri}e da sarauta a Daura, wato Sarakin Daura’, kamar haka:

…Jajerin saraki…,

In sungumi mafarar ]akin burema na `yan tama,

Tangam burema…

(Kirarin Galadima Daura)

…Babban falke sai tabki wanda ya haifi ya}i…

(Kirarin {auran Daura)

…In juyar kambu ta Mamman rigardodo,

Ba da mashigi masgarin ya}i…

(Kirarin Sarakin Daura).

…In tausa giwa makomin talaka…

(Kirarin Sarkin Ban Daura).

‘Jaje’ kalma ce da ke nuni ga tausayi ga wanda ya ha]u da wani bala’i ko ha]ari. ‘Jajeri(-n), kuma na nuni ga mai tausayawa. Galadiman Daura shi ne uba ga `ya`yan Sarki, saboda haka, duk halin da suke ciki, shi suke fara sanarwa, shi kuma ya sanar da Sarki, domin haka shi ne abokin shawara tsakanin `ya`yan Sarki da Sarki. Wannan ya sa Zabiyar ta yabe shi a kirarin, a matsayinsa na mai tausayawa `ya`yan Sarki’ idan sun shiga }unci, na wani bala’i ko ha]ari. Kamar yadda Zabiyar ta sarrafa kalmar ‘burema’, ta siffanta Galadima da ‘mafarar ]a}in burema’ da ‘tangam burema’. Kalmar burema na da ma’anar ‘ya`yan Sarki, kamar yadda Galadiman Daura shi ne waliyinsu a lokacin da suka tashi aure. Wannan ya sa Zabiyar ta ce ‘shi ne mafarar ]akin burema’. Ma’ana, wakilcin da ya yi masu suka shiga nau’in al’umma ma’aurata.

‘Mashigi’ ma wata tsohuwar kalmar Hausa ce da ke bayyana ‘wani wuri marar zurfi a kogi da ake hayewa a wuce’, kamar yadda ‘mazgaya’ ke da ma’anar ‘juyawa ko kuma komawa baya’. Zabiyar Daura, ta kira Sarakin Daura da ‘mashigi mazgaya’, domin Saraki duk da cewa ]iya ce ga Sarki, a da al’ada ta ba ta iko cikin ruwan sanyi ta juyawa Sarki baya, idan ya aikata ba daidai ba. {arfin ikonta ya kai ta sa a sauke Sarki daga gadon sarauta. Zabiyar ta kuma kira ta ‘juya kambu’. Kambu, maganin sammu ne ko kariya da ake tufkawa a rufe da fata ko }yalle a ]aura a dantse. Sarakin Daura, kamar yadda aka yi bayani, tana da }arfin juyawa Sarki baya, kuma tana ]aya daga cikin masu aikata tsafe-tsafe da suka shafi al’adun sarauta a Masarautar Daura a da. Wannan ya sa Zabiyar ta kira ta ‘juyar kambu’, domin tana daga cikin masu sarrafa kambu, kamar yadda Zabiyar ta kira {auran Daura ‘baban falke’. ‘Falke’, wani nau’in kifi ne da ake samu a makeken wurin da ruwa kan taru ya da]e. Wanda ke nuni da {aura a matsayinsa na bajimi, gawurtaccen namiji a fagen fama. Watau kamar yadda Zabiyar ke cewa:

> …Baban falke sai tabki wanda ya haifi ya}i...
> (Kirarin {auran Daura).

Zabiyar ta kuma yi amfani da kalmar ‘makoma’, ta siffanta Sarkin Ban Daura, saboda tausayi da taimakon da basaraken ke yi wa talaka. ‘Makoma’, wuri ne da mutum zai sami taimako. Kamar Zabiyar Daura ke cewa:

> …In tausa giwa makomin talaka…
> (Kirarin Sarkin Ban Daura)

#### 5.2.2.2 Kalmomin Aro

Maro}a sukan yi aron kalmomi daga wasu harsuna domin nuna }warewa da burge jama'a, musamman wanda aka yi wa}a ko kirari dominsa. Kusancin harsunan Larabci da Turanci ga harshen Hausa ya sa maro}an suka fi yin aro daga wa]annan harsuna biyu. Ita ma Zabiyar Fada ba bar ta a baya ba, domin takan aro ba}in kalmomi ta sarrafa su a kirarin da take yi wa Saraki.

**Aro Daga Larabci:** Harshen Larabci harshe ne da ya zo {asar Hausa daga fatake Larabawan Arewacin Afirka. Daga baya kuma harshen ya }arfafa da Hausawa suka amshi addinin Musulunci. Harshen Larabci, harshe ne da kusan yanzu ya mamaye kalmomin Hausa da dama, wa]anda ko dai aka aro su kai tsaye ake amfani da su, ko kuma aka Hausantar da su. An tsinci kalmomin Larabci da dama a kirarin da Zabiyoyin Fada ke yi wa saraki a {asar Hausa.

Yawanci kalmomin da Zabiyoyin suka aro daga Larabci sun shafi addinin Musulunci ne. Wannan ba ya rasa nasaba da cewa su kansu Zabiyoyin Musulmai ne, kuma sarakin da suke yi wa kirarin, su ma Musulmai ne. Zabiyoyin Fada sun sarrafa kalmomin da ke dangantaka da Musulunci irin su:

Allah
Bismillahi
Al}ur'ani

Salamu alaikum

Makka

Madina

Rasudillahi

Annabi da saura da dama. Alalmisali:

…Sidi mai taimako da na Allah…

(Kirarin Sarki Kanta)

…Sama Sarkin da Allah Ya yi…

(Kirarin Sarki Sama)

Allah Ya bar mana [an Iya tudu abun dafawa…

(Kirarin Sarkin Ha]eja)

…Ko yau ka bar duniya Alhamdulillahi…

(Kirarin Sarkin Kano)

…Manzallazina Jalla mai Makkan da Madina…

(Kirarin Sarkin Kano)

…Magajin Sarki alhamdulillahi…

(Kirarin Sarkin Kazaure Najib Hussaini)

Assalamu alaikum }arfin giwa…

(Kirarin Sarkin Arewan Ha]eja)

An aro wa]annan kalmomi kai tsaye, tamkar yadda suke a harshen Larabci. Kamar yadda aka yi bayani }ar}ashin tasirin addinin Musulunci. A iya  cewa maro}a wani lokaci sukan aro kalmomin Larabci ne, ba wai don sun rasa kalmomin Hausa da suka dace su yi amfani da su ba, sai dai kawai don su burge mutane, a ce suna jin Larabci, yadda mutane za su ]auke su da wata daraja daban, ban da ki]an da suke yi.

**Fasalin Aro:** An kuma sami fasalin aro, wato canje-canjen da ke faruwa a jikin kalmomi yayin da suka yi }aura daga harshen kar~a. A yayin aro daga wani harshe zuwa wani, al'umma sukan ari kalmomi gwargwadon yadda kunnuwansu suka ba su. Wannan kan sa sautin kalmomi da tsarin nahawunsu, har ma da ma'anonimsu galibi, suke canzawa. An samu irin wannan yanayi, lokacin da Hausa ta aro kalmomi daga Larabci zuwa. Kamar yadda ba a raba jini da tsoka, to haka ba a raba Musulmi da kalmomin Larabci, musamman wa]anda suka shafi addinin Musulunci. An sami irin wa]annan kalmomi, kodayake ba a sami canjin ma'ana ba. Misali, Zabiyoyin Fada sun yi irin wannan aro kamar haka:

| **Larabci** | **Hausa** |
|---|---|
| Mu}am | mu}ama |
| addin | addini |
| dirham | dirhami |
| imam | imani |
| taslim | tasalima |
| arba'um'a | arbaminya |
| shukurun | shukura |
| al'iman | liman |
| al'akhair | alheri |

| | |
|---|---|
| `adlu | adalc i |
| al’akhira | lahira |
| `adlu | adalci |
| amanah | amana |
| mu’allim | malam |
| zuruyyah | zuri’a |
| Al’arab | Balarabe |
| Zuu ludifin ludifin | Zullifimullifi (yawanyin alaihim) |

Wa]annan kalmomi sun fito a kirarin Zabiyoyin ba tare da canjin ma’ana ba. Alalmisali kamar haka:

…Ya yi tasalima…,
Ya ce na gode Allah,
Na godewa Muhammadu rasulillahi…
(Kirarin Sarki Kanta).

Assalamu alaikum ban dawa…,
Rana ba ki mu}ama…
(Kirarin Sarkin Ha]eja).

…Ko yau ka bar duniya Alhamdulillahi,
Na kai shukura wurin Annabi…,
Bayan mutuwar Abdullahi Dabo kun ri}e amana…
Dirhamin  gidan Sarkin Kano..
(Kirarin Sarkin Kano).

…Allah Ya }ara wa Sarki lafiya da imani,
Allah Ya }ara wa Sarki lafiya da adalci…
(Kirarin Sarkin Kazaure, na Zabiya `Yar Sukola).

…Ubangiji ya saka da alheri…
(Kirarin Sarkin Kazaure, na Zabiya {arangiya)

**Aron Aro Daga Yarabanci:** A Daura, an tsinci kalmar 'Alfa'. 'Alfa' ararriyar kalma ce daga harsunan mutanen Mali da Dahomey da Yarabanci ya aro, wadda ke da ma'anar 'malami', wato an sami aron–aro:

In Alfa matambayan Sani karaf da masana kogin malamai…
(Kirarin Al}alin Garka/Malamai a Masarautar Daura).

**Aro Daga Turanci:** An kuma sami kalmomin Turanci biyu rak (kaftin da Bature) a kirarin da Zabiyoyin ke aiwatarwa:

…Na yi godiya na gode ubangijin kaftin Rilwanu…
(Kirarin Sarkin Kano).

…Ga ka Sarki ga ka malam,
Ga ka Bature ga ka Balarabe…
(Kirarin Sarkin Kazaure Hussaini Adamu da Najib H. Adamu).

### 5.3 Zubi a Zabiyancin Fada

A wannan sashe za a dubi irin nau'in zubin wannan kirari, watau kirarin da Zabiyoyin Fada suke yi wa saraki. Alalmisali, zubi ne irin na wa}a ko wasan kwaikwayo ko kuwa na zube? Saboda haka za a nazarci sigar kirarin da yanayinsa. Za a amsa tambayoyi kamar haka:

- yaya tsarin ga~o~insa suke, yana zuwa ne kamar baitoci?
- akwai amsa-amo?
- a baka yake ko a rubuce?
- akwai sigar tambaya da amsa?
- akwai amshi ko kar~i?
- ana yi ana hutawa?
- ana samun maimai?
- kirarin yana da farko da }arshe?

Za a amsa wa]annan tambayoyi domin gano abin da ake nema a sani (irin zubin kirarin). Kamar yadda aka yi bayani a babi na biyu, kirari nau'i ne na adabin baka. Nau'i ne na adabin bakan zube da ke }ar}ashin azancin magana. Kirari na zuwa a zubin wa}a - wa}a, magana- magana, domin shi ba wa}a ba ne kasancewa ba a rangwa]ar da murya kamar yadda ake yi a wa}a domin a sami rauji, shi kuma ba magana ba irin ta yau da kullum (magana kara zube), kasance ana iya jin wani kari a cikinsa. Kodayake ana samun kirari ya fito a wa}a da zummar kamanci ko kwatanci, to amma kirari ba wa}a ba ce. Kirari tsararrun kalmomi ne na washi da ake amfani da su domin ko]a kai ko kambama wani ko wani abu ko wani muhimmin lamari. Saboda haka wa]annan kalmomi sun }unshi siffantawa da

kamantawa, domin haka za a iya cewa sigar kirari siga ce ta kamantawa ko siffanta wani mutum ko wasu mashahuran al'amura.

Kodayake kirari nau'i ne na adabin bakan zube, sigarsa ta bambanta da nau'o'i takwarorinsa irin su karin magana da habaici da ba}ar magana da zaurance da makamantansu. Alalmisali, karin magana da habaici ba sa wuce jimla ]aya rak, kirari kuwa na iya samun fiye da jimloli goma. Haka kuma shi ba ba}ar magana ba, domin ita za a iya mayar da martani wanda shi ma yana iya kasancewa a jimla ]aya. Ba kuma za a kira shi rubutaccen zube irin na tsarin littafi ba domin ba ya zuwa a tsarin babi-babi irin na littattafan zube.

To haka kuma zubin kirari ba ]aya yake da na wasan kwaikwayo ba, domin tun farko ba shi da siga irin tasa. Alalmisali, idan aka ]auki rubutaccen wasan kwaikwayo, yana zuwa da tsari na shiga da fita dandamali da amfani da mai shela da makamantansu. Haka shi ma wasan kwaikwayo na gargayiya yana da sigarsa da ta ke~anta da shi. Shi kuwa kirari yana zuwa ne kara zube kuma ba kwaikwayo ake ba na kamance, a zahiri ake aiwatar da shi. Yana zuwa ne a jimla ba tare da fitowa-fitowa ba.

A iya cewa zubin kirari ya fi kusanci da na wa}a, wa}ar ma ta baka wadda ita ma take zuwa kara zube cikin 'yan jimloli. To sai dai kirari ba shi da ]ango ko baitoci (za a yi bayani nan gaba).

### 5.3.1 Tsarin Ga~o~i a Kirarin Zabiyoyin Fada

Sigar kirari ta bambanta daga abin da ake so a wasa ko a kambama. Wani kirarin cikin jimla ]aya ya wadatar, misali:

giwa bukkar daji.
maza gumbar dutse.
amarya ba kya laifi.
yaro da ku]i abokin tafiyar manya.
uwargida sarautar mata.
tantabara uwar al}awari.
tsatsa kashe }arfe.
sanwa adon mace.
sarki goma zamani goma.
rimi adon gari.

To amma, kirarin Zabiyar Fada ba ya cika cikin jimla ]aya, saboda manufarsa ta yabon saraki. Kamar yadda aka yi bayani a farkon wannan babi jigon kirarin shi ne yabo, kuma Zabiyoyin na }o}arin cim ma wannan yabo ta amfani da shikashikan yabo (asali gami da zuri'a da ri}on addini da kyauta da iya mulki ko ri}on jama'a da kuma jaruntaka). A iya cewa ko da biyu daga cikin shikashikan aka ]auka, domin a gina kirari a kansu, dole kirarin ya wuce jimla ]aya. To sai dai, kirarin ba shi da takamaiman yawan layuka. Haka nan kuma ana iya juya wa layukan gurbin zama ba tare da ma'anarsu ta gur~ace ba. Daga cikin kirarin da binciken ya nazarta mafi }aranci daga cikinsu shi ne mai layuka uku kacal. Misali:

In ]an maran maza da yawa Wamban Daura,
In ]an sasarin mutu ko dai ri}o,

[an mu je mu da anna.
(Kirarin wamban Darua)

Ranki ya da]e kwarin gida tankarin gida,
Ja yawa fara,
Kowa da ya zo fara ne.
(Kirarin Uwargidan Mai Martaba Sarkin Zazzau Shehu Idris)

Kirarin Zabiyar Kabin Argungu da na Zabiyar Kano su ne mafi tsawo a cikin kirarin Zabiyoyin da aka nazarta. Alalmisali a kirarin Sarki Muhammadu Kanta, an sami layuka arb'in da shiga (46) a na Sarki Sama ]ari da ashirin da ]aya (121) na Sarkin Kano, Mai Martaba Ado Bayero kuma, ]ari biyu da talatin da biyar (235). Saura kuwa wasu layuka hu]u ko biyar ko bakwai ko goma har zuwa yadda ya samu.

Ta fannin baitoci kirarin ba a tsarin baiti yake ba, yana zuwa ne kara zube. Ba a tsarin baiti yake ba, kamar a rubutacciyar wa}a da take zuwa cikin wannan tsari na baitoci, har inda za a sami wata wa}ar 'yar }war biyu (baitoci biyu–biyu), wata }war uku, wata }war hu]u, zuwa yadda mai ita ya tsara abinsa. Misali, kirarin Zabiyar Fada yakan zo da siga irin ta wa}ar baka, kamar haka:

Na Abdu gatarin Ya}uba,
Na Bawa hankalinka gare ka,
Sama kowwag }i gaskiya ka }i shi,
Marin ]aka mai ban haushi….
(Kirarin Sarki Sama)

Assalamu alaikum ban dawa bakka da nisa sai wuyar isa,

Kai ne Buhari kai ne Sambo,

Kai ne gagara gammo da Sarki Jatau,

Ubanmu uban Sarakuna,

Rana ba ki mu}ama….

(Kirarin Sarkin Ha]eja)

Zabiya: Mararrafar madangari,

:Madur}usar madangari,

‘Y/Amshi: Mararrafar madangari

:Madur}usar madangari,

Zabiya: Hawan ‘yan Bawo,

`Y/Amshi: Hawan ‘yan Bawo,

Zabiya: Kakan anna,

`Y/Amshi: Kakan anna,

Zabiya: Hazo na Muhamman,

`Y/Amshi: Hazo na Muhamman,

Zabiya: Makazaki,

`Y/Amshi: Makazaki,

Zabiya: Makadodo,

`Y/Amshi: Makadodo,

Zabiya: Kamunka nawa,

`Y/Amshi: Kamunka nawa,

Zabiya: Dosono…

`Y/Amshi: Dosono…

(Kirarin Sarkin Daura).

Allah ji }an mai Data da gafara,

Muhammadu Adananu ya riga mu,

Allah shi gafarta mai fa,

Sannan da Alhaji Muntari,

Mijin Fulani mai gadon Masar Balkisu,

Ka biya ni na gode ma,

Ina Bashar ]an masu gida?

Saboda mai Baban [akin Kano yake ba ni riga….

(Kirarin Sarkin Kano)

Salamu alaikum,

Ni ce Zabiyar Sarkin Kazaure Muhamman Najib Usaini,

[an gagara badon Sarakuna,

Lafiya alfanda,

Lafiya ]an gagara badon Sarakuna,

Lafiya alfanda ]an hadarin }asa maganin maikabido,

Lafiya alfanda,

Barka da kwana barka da tashi barka da yini,

Ka kwana lafiya ka tashi lafiya ka yini lafiya,

Godiyar Allah ta yi…

(Kirarin Sarkin Kazaure)

Fito da }arfin Allah ni}atau,

Fito da }arfin Allah toya matsafa

Sarki Uban Sarakana,

Taka da }arfin Allah zaki,

Taka da }arfin Allah ni}atau,

[an Idirisa autan Sambo,
[an Aminatu baban Aminatu…
(Kirarin Sarkin Zazzau).

Kirarin na zuwa a sigar ]ango kamar yadda yake a wa}ar baka. Wannan ya }ara tabbatar da cewa sigarsa tamkar ta wa}ar baka ce.

### 5.3.2. Amsa -Amo a Kirarin Zabiyoyin Fada

Amsa- amo shi ne sautin ga~ar }arshe na kowane ]ango ko baiti (a wa}a) wajen samun harafi iri ]aya. Amsa-amo ya kasu kashi biyu: amsa-amon waje da amsa-amon ciki (ko kuma babban amsa-amo da }aramin amsa-amo). Babban amsa- amo shi ne sautin }arshe na ga~ar kalmar }arshe na ]angon }arshe a kowane baiti, wanda a kodayaushe ga }a'ida bai cika canjawa ba. {aramin amsa-amo shi ne sautin ga~ar }arshe na kalmar }arshe na ]ango ko ]angwayen da suka zo kafin na }arshe.

Masana sun sake raba amsa-amo zuwa amsa-amon harafi da amsa-amon kari. Amsa- amon harafi shi ne samun harafi iri ]aya ya }are a }arshen baitoci a wa}a rubutacciya. Kodayake, a kan samun amsa-amon harafi a wa}o}in baka a wasu lokuta. Alalmisali, kamar yadda Muhammad (1978), ya kawo misali da wa}ar "Imfiraji" ta Aliyu Namangi. Amsa-amon kari kuwa, shi ne samun ga~o~in }arshe na kowane baiti su kasance ]aya wajen kari, ban da wajen harafi, duk kuwa da cewa kalmomin sun bambanta da juna. Wato, samun kari ]aya na uwar goyon amsa-amon harafin wa}a, a sami karin sauti mai sauka }asa ko hawa. Amsa-amon kari ne yake daidaita hawa da sauka da fa]uwar murya a layuka, su tafi a jere ba tare da sa~awa ba.

A iya cewa tun da kirarin ba a tsarin baiti yake ba, maganar ya sami amsa –amo ba ta taso ba. A ta}aice, kirarin Zabiyar Fada ba shi da amsa-amo, sai dai a kan yi katari, wani lokaci ga~ar kalmar wasu layuka kan kasance iri ]aya wanda ba wai an yi da niyyar haka ba. A'a sai dai a ce sa'a ce wadda ta fi rabo. Alalmisali:

…Magume uban duniya Sarki,

Kakan duniya Sarki…

Sidi mai taimako da na Allah,

Rana da wata fataken Allah…

Ka duba daga kassuwa idan safiya ta yi,

Kassuwa cika za ta yi,

Idan maraican nan ya yi…

Mai uba ka sausawa ga ranar ya}i,

Ingarma anka ji anka ba ku domin ya}i,

Kowwag gane ka ya ga ya}i,

(Kirarin Sarki Muhammadu Kanta).

A wannan kirari an sami amsa-amon harafi ]aya a wasu layuka, misali:

ki da lah da yi da kuma }i

To haka ma a kirarin Sarki Sama an yi wannan gamo da katar ]in:

…Sama kowwag }i gaskiya ka }i shi,

Marin ]aka mai ban haushi,

[a mai zuciya ka ramkon gayya,

Na Garba ka yi ramkon gayya…

Adamawa ta iso,

Zindar ta iso,

Barno ta iso,

Ai Sama Sarkin nasara na,

Ashe bugun mari wargina,

Kabawa ku yi hankali Sama ba shi wargi,

Ba a yi masa wargi…

Kai ka wa mutum ba shi yiwu wa,

Gulbin teku mai wuyar iyo ]an Bawa…

Katsantsan ra}umin da bai da akala,

Mai son mutuwa shi kama akala.

(Kirarin Sarki Sama)

A wannan kirari na Sarki Sama ma an sami amsa-amon harafi mabambanta, kamar haka:

shi da ya da iso da nas da wa, da kuma la.

Har ila yau, a kirarin Galadiman Daura da na Sarkin Kano ma ana iya ganin ~ullar amsa-amon harafi irin wa]annan: /ya/ da /wa/ da /wa/ da kuma /ra/, kamar haka:

…Shuka bugun wuya.

Ci da ma}iya,

Sha da ma}iya…

(Kirarin Galadiman Daura)

Allah ji }an Hauwa,

Allah sa mutuwa hutawa,

Allah ji }an Shekara,

Allah ji }an Hussaina da gafara…

(Kirarin Sarkin Kano).

### 5.3.3 Kirarin Zabiyoyin Fada a Matsayinsa na Adabin Baka

A rabe-raben da masana irin su Ibrahim (1988:1-7), suka yi na maka]an sarauta, ya kasu su zuwa kashi uku. Maka]a masu ka]a take da masu bushe –bushe da kuma ‘yan bamba]o/’yan mu’abba/’yan magana/kwando.Wannan kaso na uku su ne maka]a wa]anda ba su da abin ki]a ko bushe –bushe, sai dai suna kirarin baki. Zabiyar Fada ta kasance cikin wannan kaso, saboda haka kirarin da take yi na baka ne, ba a rubuce yake ba. Wato ba a tsara shi a rubuce kafin ba daga baya a aiwatar da shi, a ka yake kamar wa}ar baka. A iya cewa dukkan Zabiyoyin da aka yi amfani da su a wannan nazari babu wadda ta iya rubutun Arabi ballantana na boko, da za su tsara kirarin da suke yi, sannan kuma su rubuta shi. Domin haka kirarin a baka yake. Za a iya tabbatar da haka domin a tsakanin kirarin da Zabiya ‘Yarsukola (Zabiyar Fadar Kazaure) take yi wa Mai Martaba Sarkin Kazaure Najib Hussaini, akwai bambanci tsakanin wanda ta yi ‘yan watanni da suka gabata da wanda ta yi a lokacin da aka ziyarce ta na biyu. Sai dai a ce bambancin ba na a zo a gani ba ne. {ari ne ko ragi na wasu layuka a kirarin.

### 5.3.4 Sigar Tambaya a Kirarin Zabiyoyin Fada

A wasu daga cikin kirarin da Zabiyoyin Fada ke yi wa saraki, ana samun sigar tambaya. To, sai dai, ba a cika amsa tambayar ba. A maimakon haka a kan shiga wani batu na daban. Alalmisali:

…Rugga na gani kana yadda ka so,
Yau ina laifin na Garba?
Gaba in ta yi tsumbure ka nome…
(Kirarin Sarki Sama)

A nan an sami tambaya inkani, wato nau'in tambaya da ke musanta abu. Alalmisali, a zamanin Sarki Sama ya ci nasara a wasu daga cikin ya}e-ya}en da ya yi da garuruwan Fulani, saboda haka Zabiyar ke musanta masu ganin laifinsa.

To haka ma a kirarin Sarkin Daura, an sami nau'in tambaya taha}i}i. Tambaya mai tabbatar da wani abu. Zabiyar a kirarin Sarkin Daura ta ce shi mai kama dodo ne har ma ya mur}ushe ya kashe, sannan ta tambaye shi, guda nawa ya kama? Ba a amsar tambayar ba sai aka ci gaba da wani batu, kamar haka:

Zabiya: Hazo na Muhamman,
Amshi : Hazo na Muhamman,
Zabiya: Makazaki,
Amshi: Makazaki,
Zabiya: Makadodo,
Amshi: Makadodo,
Zabiya : Kamunka nawa?
Amshi: Kamunka nawa?
Zabiya : Dosono,
Amshi: Dosono,
Zabiya: Har ya fi kyau …
Amshi: Har ya fi kyau…
(Kirarin Sarkin Daura).

A wa]annan kirarin da ke }asa na Sarki Sama da kuma Sarkin Kano kuwa, an sami nau'in tambaya tabikh. Watau tambaya da ke }as}antar da wani abu. Alalmisali, an }as}antar da

wani Sarki (daga cikin Sarkunan Fulani) da Sarki Sama ya samu galaba a kansa. A kuma Kirarin Sarkin Kano a inda Zabiyar Kano ke bayyana auren Sarki ga ]iyar Sarkin Musulmi (Ha]eja Saude), an yi tambaya da ta }as}antar da keke a kan mota da babur. Kamar yadda take cewa:

…Ga babur da mota wa yake zance da keke?
(Kirarin Sarkin Kano)

…Ana fa]in Magajin [anmusa ina Sarki ya yi?
Hur]e mai idon ~ata na Muhamman,
Na Garba ba ka tsoron taro…
(Kirarin Sarki Sama).

…Rannan mun ga abin mamaki,
Ba mota ba da mota, mota tana ta tashi,
Mota sai ka ce gindin zama?,
Birnin Kano babu ragi nasa,
Ga babur da mota wa yake zance da keke?
Ranar zuwan Hajiya Saude,
Rannan na ga abin da dama…
(Kirarin Sarkin Kano).

A wani wuri ma an sami tambayar taha}i}i da ta tabbatar da Yarima Bashar, wanda Zabiyar ta ce yana ba ta riga albarkacin mahaifiyarsa, watau Mai Babban [akin Kano. Kamar yadda a na gaba ma tambayar take tabbatar da samun Zabiyar Kano Hajiya Ajuji Maitazargade, a lokacin Mai Martaba Sarkin Kano ya yi tambaya wace ce ita?

…Ina godiya da arzikinka mashashan Kano na Audu,

Na je na gaida Sarkin Kano na Audu,

Ya ce ina kuka samu Zabiya maigari?

Suka ce da dalili saboda yawo,

Yau dalili ya yi dalili ga ni cikin Birnin Kano,

Mai dalili ya yi kirki,

Sai ya duba gida da kyau ya ba ni,

Ga shi na yi zaman birnin Kano…

(Kirarin Sarki Kano).

…Mijin Fulani mai gadon Masar Balkisu,

Ka biya ni na gode ma,

Ina Bashar ]an masu gida?

Saboda mai Babban [akin Kano yake ba ni riga,

Sai da gwanda ake kabewa…

(Kirarin Sarkin Kano)

Daga wa]annan misalai, a ce a wuri ]aya ne aka yi tambaya aka amsa, wato:

…Ya ce ina kuka sami zabiya maigari?

Suka ce da dalili saboda yawo…

(Kirarin Sarkin Kano).

A nan, an amsa tambayar da Sarkin Kano ya yi a lokacin da aka zo da Zabiya Maitazargade ta gaishe shi a fada.

### 5.3.5 Amshi da Kar~i a Kirarin Zabiyoyin Fada

Amshi shi ne maimaita wata magana da jagora ya yi, a yayin da kar~i kuwa shi ne iyar da magana da ita ma jagora ya yi,`yan amshi su }arasa masa. Wa}o}in Maka]a [ankwairo sun shahara wajen samun kar~i daga maka]ansa. Alalmisali:

Jagora: Gungurun,
`Y/Amshi: {ashin giwa na Alu ba ka ha]uwa,
:Kowc ci ka sai ya cake ma}oshi,
Jagora: Gabas da yamma kudu da arewa,
:An san kai ne Sardauna mai kwana kyauta,
`Y/Amshi: Saboda baiwa, Amadu saboda hairi aka sakam ma…
([an}wairo, wa}ar `Ya wuce raini ba a yi mai shi, Amadu jikan Garba Saduaki).

[aukacin Zabiyoyin Fadojin da aka nazarci kirarinsu a wannan bincike, ]ai-]ai suke aiwatar da kirarin nasu. Sai dai a Fadar Daura a }ungiya suke, su biyar tare da shugabarsu, wadda ake kira 'Dakamar Sarkin Daura', sauran kuwa ana kiransu, 'Dakamawa'. Wannan ya sa sauran Zabiyoyin ba su da mai yi masu amshi ko kar~i. A Fadar Daura ma da suke da yawa ba a kar~i, to amma ana amshi. Amshin da ake yi na sashen farkon kirarin Sarkin Daura ne kawai. Ke nan, sauran kirarin sarakin Daura, ba a amshi amma Zabiyoyin suna aiwatarwa tare a lokaci guda. Ga sashen kirarin Sarkin Daura da Dakamar Sarkin Daura take fa]i, sauran 'yan'uwanta su maimaita abin da ta fa]a:

Zabiya : Mararrafar madangari,

:Madur}usar madangari,

Amshi: Mararrafar madangari,

:Madur}usar madangari,

Zabiya: Hawan ‘yan Bawo,

Amshi: Hawan ‘yan Bawo,

Zabiya: Kakan anna,

Amshi: Kakan anna,

Zabiya: Hazo na Muhamman,

Amshi: Hazo na Muhamman,

Zabiya: Makazaki,

Amshi: Makazaki,

Zabiya: Makadodo,

Amshi: Makadodo,

Zabiya: Kamunka nawa?,

Amshi: Kamunka nawa?,

Zabiya: Dosono,

Amshi: Dosono,

Zabiya: Har ya fi kyau,

Amshi: Har ya fi kyau,

Zabiya: Sannu ta fi kus,

Amshi: Sannu ta fi kus,

Zabiya: Inuwal dare,

Amshi: Inuwal dare,

Zabiya: Amale,

Amshi: Amale,

Zabiya: Ba gada jiya,

Amshi: Ba gada jiya,

Zabiya: Alhajin Saraki,

Amshi: Alhajin Saraki,

Zabiya: Mun ji yau,
Amshi: Mun ji yau,
Zabiya: Gaba gare ka Allah,
Amshi: Gaba gare ka Allah,
Zabiya: Nasara dai!,
Amshi: Nasara dai!,
Zabiya: Allah mai iyawa…
Amshi: Allah mai iyawa…
Zabiya: (hutawa/ numfasawa)
Amshi: (hutawa/ numfasawa)

Bayan Zabiyoyin sun numfasa na ]an da}i}a kadan, sai dukkansu a lokaci guda su ]auka daga nan:

…In suke kimammaye,
In sha da rago abokin Jiro,
Rana ta yi hwargaba rana taka,
In suke dai kimammaye…
(Kirarin Sarkin Daura)

### 5.3.6 Numfasawa a Kirarin Zabiyoyin Fada

Kodayake cikin kirarin da aka nazarta akwai mai layi uku kacal, akwai kuma mai layi fiye da ]ari biyu, duk da haka ko a mai layi ukun, bayan kowane layi, ana numfasawa na a}alla da}i}a ]aya, kafin a ci gaba. Wannan a ce al'adar wa}ar baka ce. Alalmisali:

In ]an maran maza da yawa Wamban Daura,
In ]an sasarin mutu ko dai ri}o,
[an mu je mu da anna,
(Kirarin Wamban Daura)

Ranki ya da]e kwarin gida tankarin gida,
Ja yawa fara,
Kowa da ya zo fara ne,

(Kirarin Uwargidan Sarkin Zazzau).

A rubuce (idan aka rubuta kirarin) za a iya ganin haka, bayan kowane layi an yi wa}afi. Haka yake a sauran kirarin da Zabiyoyin Fada ke yi wa saraki. To sai dai a kirarin Mai Martaba Sarkin Daura bayan an kammala sashe na farko, wanda Dakamar Sarkin Daura na fa]i, sauran Zabiyoyin na maimaita abin da ta fa]a, a kan sami hutu na kamar da}i}a biyu zuwa uku, wanda daga nan za su ci gaba su aiwatar da sashe na biyu tare (kamar yadda bayani ya gabata).

**5.3.7 Maimai a Kirarin Zabiyoyin Fada**

'Maimai' nanata wata kalma ce ko wasu kalmomi masu ala}a da juna a wani muhalli cikin matani. A kirarin da Zabiyoyin ke yi wa saraki, an samu mamai na wasu layuka. A iya cewa }ila saboda muhimmancin matanin ko batu, }ila kuma haka kawai aka so a tsara shi. Wannan al'adar wa}ar baka ce na maimaita wasu ]angwaye. Alalmisal:

Jagora: Uban }asa Usumanu na Shantali,
: Na Garba jikan Malam Sambo,
`Y/Amshi: Alhaji Sarkin Zazzau Shehu.
Jagora: Uban }asa Usumanu na Shantali,

: Na Garba jikan Malam Sambo,

`Y/Amshi: Alhaji Sarkin Zazzau Shehu.

Jagora: Jikan Mujaddadi a wajen matarshi,

`Y/Amshi: Alhaji Sarkin Zazzau Shehu.

Jagora: Shehu jikan Mujaddadi a wajen matarshi,

`Y/Amshi: Alhaji Sarkin Zazzau Shehu.

(Wa}ar 'Alhaji Sarkin Zazzau Shehu' ta Dr. Mamman Shata Katsina)

Zabiyar Ha]eja ta maimaita wasu matani a kirarin Tafidan Ha]eja:

Salamu alaikum ]an na gada wanda ya fi ]an na koya,
<u>Farin iri abin shukawa</u>,
Jikan Tafida Umaru…,
<u>Farin iri abin shukawa</u>**,**
Jikan Tafida Umaru…

(Kirarin Tafidan Ha]eja).

Haka kuma, Zabiyar Kano ta maimaita wasu layuka a lokuta da dama a kirarin Mai Martaba Sarkin Kano, musamman:

…Ina godiya ina }arawa na gode,

da

Kyauta ba biyan bashi ba,

da

Ka biya ni na gode ma,

da

Ko yau ka bar duniya alhamdulillahi,

(Kirarin Sarkin Kano, Ado Bayero).

A kirarin da Zabiyar Kazaure ta yi wa Mai Martaba Sarkin Kazaure ma, an samu maimai na ]aya daga cikin layukan kirarin, kamar haka:

…Lafiya alfanda….
Lafiya alfanda…
Lafiya alfanda… (watau har sau uku amma ba a lokaci ]aya ba).

(Kirarin Sarkin Kazaure Naijb H. Adamu)

### 5.3.8 Mabu]i da Marufi a Kirarin Zabiyoyin Fada

Mabu]i a nan shi ne yadda Zabiyoyin bisa ga al'ada suke fara bu]e / fara kirarin da suke yi wa saraki. Marufi kuwa shi ne yadda suke rufewa ko }arasa/kawo }arshensa. Alalmisali, a wasu daga cikin kirarin da Zabiyoyin Fada kan yi wa saraki, sukan fara da 'basmalla' ko 'sallama'. Kirarin Sarki Muhammadu Kanta ya fara da:

Bismilahi Rahmani Rahim,
O'ooh Sha]i!....
(Kirarin Sarki Kanta)

A nan Zabiyar Kazaure tana farawa da:

Assalamu alaikum ban dawa bakka da nisa sai wuyar zuwa,
Kai ne Buhari kai ne Sambo…
(Kirarin Mai Martaba Sarkin Ha]eja)

Assalamu alaikum ]an babban amale,
Kai ne Buhari kai ne Sambo…
(Kirarin Magajin Garin Ha]eja)

Assalamu alaikum Turaki Ammani,
[an na gada wanda ya fi ]an na koya…
(Kirarin Turakin Ha]eja)

Assalamu alaikum }arfin giwa,
Ba ka shiga ba ka la~e ruwa…
(Kirarin Sarkin Arewan Ha]eja)

Assalamu alaikum Baba Ciroma,
[an babban amale…
(Kirarin Ciroman Ha]eja)

To, haka dai Zabiyar Ha]eja take fara nata kirarin, wato takan yi sallama ga saraki. Kamar yadda ita ma Zabiyar Kabin Argungu ta fara da 'Basmallah'. Wannan a ce tasirin addinin Musulunci ya haifar da haka.

A Fadar Kazaure kuwa, kasancewa akwai Zabiyoyin Fada biyu, kowace idan za ta fara nata kirarin, musamman na Sarkin Kazaure, Mai Martaba Najib Hussaini. Wannan ya sa kowacce Zabiya tana fara ambaton sunanta domin a san ko wace ce ita. Misali:

Ni ce Zabiya 'Yar sukola,

Zabiyar Sarkin Kazaure Muhammad Najib Hussaini…
(Zabiya `Yarsukola)

Bismillahi Rahmani Rahim,
Ni ce Zabiya {arangiya,
Zabiyar Mai Martaba Najib ]an Hussaini…
(Zabiya {arangiya).

Kirarin Zabiyar Fada hanya ce ta sanarwar bayyanar saraki, musamman ga fadawan ciki da waje da sauran jama'a, domin su san isowar Sarki a wani wuri. Zabiyar Daura a kirarin Mai Martaba Sarkin Daura, tana farawa da sanar ko umarni ga fadawa da sauran jama'a cewa ga Sarki nan tafe, a dur}usa a yi gaisuwa, kamar yadda take cewa (kodayake ba kai tsaye take fa]in haka ba):

Mararrafar madangari,
Madur}usar madangari…
(Kirarin Sarkin Daura)

Wannan matani na nuni da cewa ga maigari nan tafe, a dur}usa a gaishe ida maigari. Sauran nauo'in kirarin suna zuwa ne kai tsaye ta yadda ko da za a juya guraben layukan kirarin, manufarsa ko ma'anarsa ba za ta canza ba. Ke nan, ba kasafai layukan kan dogara da junansu ba. Sa}on da ke cikiin kirarin kan zo gutsire-gutsire, nan ya yabi kyauta, can jaruntaka, a can kuma a ambato tarihin asali, can-can kuma a yabe shi da ri}on addini. Wannan ya sa a mafi lokuta, kirarin ba shi da farko ko }arshe, in ban da na Sarkin Daura da

ke bayyana isowa ko bayyanarsa a farkon kirarin. To, haka kuma sashen }arshensa da Zabiyoyin kan yi tare.

### 5.3.9 Tasirin Addinin Musulunci Dangane da Sigar Kirarin Zabiyoyin Fada

Kamar yadda aka sami tasirin addinin Musulunci ta fuskar jigon kirarin da Zabiyoyin Fada ke yi wa saraki, ta fuskar siga ma an sami haka. Siga a nan shi ne 'sura', watau zubin kirarin, musamman mabu]i. Alalmisali, a wasu lokuta Zabiyoyin sukan fara kirarin da addu'a ko kuma 'sallama'. Zabiyar Kabin Argungu a kirairn Sarki Kanta, ta fara da:

> Bismillahi Rahamani Rahim..
> (Kirarin Sarki Kanta)

A nan, za a iya ganin yadda Zabiyar ta fara da 'Da sunan Allah Mai Rahama Mai Jin {ai', wanda ya samo tasiri daga addinin Musulunci, kamar yadda aka umarci Musulmi ya fara duk abin da zai yi da 'basmallah'.

Takwarar wannan Zabiya a Kazaure (Zabiya {arangiya) ma an sami inda ita ma ta fara kirarin Sarkin Kazaure, Muhammadu Najib Hussaini da 'Bismillah':

> Bismillahi Rahmanir Rahim,
> Ni ce Zabiyar Mai Martaba Najib ]an Hussaini…
> (Zabiya {arangiya, kirarin Sarki Najib)

Kamar yadda Zabiyar Ha]eja kuma take fara nata kirarin da 'Sallama'. Misali:

Salamu alaikum ban dawa bakka da nisa sai wuyar zuwa…

(Kirarin Sarkin Ha]eja)

Salamu alaikum toron giwa sha zamani…

(Kirarin Sarkin Ha]eja na Dangin Uwa)

Salamu alaikum toron giwa lumfasa fada…

(Kirarin Galadiman Ha]eja)

Salamu alaikum ]an babban amale…

(Kirarin Magajin Garin Ha]eja)

Salamu alaikum Turaki Ammani…

(Kirarin Turakin Ha]eja)

Salamu alaikum Baba Ciroma…

(Kirarin Ciroman Ha]eja).

‘Salamu alaikum’, wanda ke da ma’anar ‘Amincin Allah Ya Tabbata a Gare Ka’, abu ne muhimmi a addinin Musulunci wanda aka hori Musulmi, ya yi wa ]anuwansa Musulmi a duk lokacin da suka ha]u. Shi ma wanda aka yi wa wannan ‘sallama’ aka umarce shi ya amsa da ‘Amin walalaikum Salam’ – har ma a }ara da ‘Warahamatullah Wabarakatuku’. Musulunci ya kwa]aitar da Musulmi cewa duk wanda ya yi wa ]an’uwansa Musulmi salama, yana da lada kamar yadda wanda kuma ya amsa, shi ma yana da tasa ladar. Kamar

yadda Zabiya ‘Yarsukola (Zabiyar Kazaure), a wasu lokuta take fara kirarin sarakin Kazaure da ‘Sallama’:

> Salamu Alaikum Sarkin Shanun Kazaure…
> (Kirarin Sarkin Shanun Kazaure).
>
> Salamu Alaikum,
> Ni ce Hajiya Indo ‘Yarsukola Kazaure…
> (Kirarin Mai Gamom Kazaure).
>
> Salamu Alaikum,
> [an gagarabadon Sarakuna,
> [an alfanda ]an hadarin }asa maganin mai kibido,
> Wambai magajin wambai Sanusi…
> (Kirarin Wamban Kazaure).

Ta fuskar sigar rufe kirarin kuwa, an sami }alilan daga cikin kirarin Zabiyoyin suna rufewa da addu’a, musamman  Zabiyar Ha]eja da ta Zazzau. Wannan ma tasirin addinin Musulunci ya haifar da shi; misali:

> ..Allah Ya bar mana [an Iya tudu abun dafawa.
> (Kirarin Sarkin Ha]eja  na Dangin Uba).
>
> …Allah Ya ji }an Galadima Habibu,
> Allah Ya bar mana na yanzu, shi ne Abdullahi.
> (Kirarin Galadima Ha]eja).

…Allah Ya ji }an Sarki Usman.

(Kirarin  Turakin Ha]eja)

…Allah Ya ji }an Iya mai itace.

(Kirarin Sarkin Arewa Ha]eja).

…Allah Ya bar mana Maina Ginsau.

(Kirarin Turakin Gida (Hajja).

…Allah Ya taimake ki/ka /ku Larabawan asali.

(Kirarin ‘ya’yan Sarkin Zazzau, Shehu Idris na Hajiya A’i Dogariyar Zazzau).

…Taka da }arfin Allah toya matsafa .

(Kirarin Sarkin Zazzau, na Rabi Bazamfara)

…Allah Ya taya ka ri}on jama’a,

Da abun da zai cuce ka da abin da zai cuci jama’arka,

Da abin da zai cuci }asarka,

Ubangiji Ya kiyaye shi da kiyayewarsa.

(Zabiya ‘Yarsukola, Kirarin Sarki Hussaini Adamu)

Allah Ya ji }an Yarima Audu,

Allah Ya ji }an Yarima Muhamman Sakimanu.

(Zabiya ‘Yarsukola, Kirarin Yariman Kazaure)

Yadda suka gama lafiya,

Allah Ya sa ku gama lafiya da imani

(Zabiya ‘Yarsukola, Kirarin Ciroman Kazaure)

…Allah Ya sa ki iske lahirarki fari tas kamar nan.

(Zabiya ‘Yarsukola, Kirarin Matar Sarki Najib Hussaini).

…Komai ya yi zafi ubangiji yana maganinsa komin dare,

Allah Ya saka da alheri.

(Zabiya {arangiya, Kirarin Sarki Najib Hussaini).

## 5.4 Kammalawa

A wannan babi an ci gaba da tarken Zabiyancin Fada a {asar Hausa, wato kirarin da Zabiyoyin Fada ke yi wa saraki, musamman Sarki. An nazarci kirarin ne ta sigogi biyu: salonsa ta fannin (adon harshe da aiwatar da harshe) da kuma zubinsa. Daga wannan nazari, za a iya cewa jigon kirarin na yabo ne kuma Zabiyoyin Fada, kamar sauran maro}an fada, suna amfani da adon harshe, musamman jinsirtarwa da kwalliya. Ta fuskar aiwatar da harshe kuwa, Zabiyoyin suna amfani da tsofaffin kalmomin Hausa. Suna kuma aron kalmomi musamman daga Larabci. Ta fannin zubin kirarin kuwa, za a iya cewa zubin kirarin zubi ne na adabin baka, }ar}ashin azancin magana. Kirari kamar yadda aka sani, nau’i ne daga cikin nau’o’in zantukan hikima na Hausa. To, sai dai kirarin da Zabiyoyin kan aiwatar wani lokaci yana da mabu]i amma ba shi da marufi.Yana iya farawa ko }arewa da komai. Kirarin na zuwa ne a tsarin layuka kuma galibi kowanne mai zaman kansa, a inda ko da za a sauyawa layukan gurabensu, ba za a samu sauyin ma’ana ba.

**BABI NA SHIDDA**

**NA[EWA**

## 6.1 Gabatarwa

Masu iya magana na cewa, “Wuyar aiki farawa”. Babi na shidda shi ne cikamakon wannan bincike mai taken,*‘Kirarin Saraki a Bakin Mata: Nazarin Zabiyanci a {asar Hausa*.’ A wannan babi ne aka daddale aikin, watau aka na]e ta hanyar ta}aitawa, sannan kuma aka bayyana sakamakon bincike tare da shawarwari ga masana da manazarta al’ada da adabi.

## 6.2 Ta}aitawa

Wannan bincike ya }unshi babi shidda. Babi na farko, watau ‘shimfi]a’, ya yi sharar fage ga aikin da aka aiwatarwa. Da farko dai an yi sharhi a kan abin da ya haifar da tunanin gudanar da binciken, watau kasancewar fada ita ce idon jama’a a {asar Hausa, masana da manazarta sun gabartar da ayyuka da dama da suka shafi fada, kama tun daga kafuwarta zuwa

al’adunta da adabinta, to amma abin mamaki shi ne babu wanda aka gudanar musamman a kan Zabiyoyin Fadojin {asar Hausa, duk kuwa da muhimmanci / babbar rawar da suke takawa. Sauran batutuwan da wannan babi ya }unsa sun ha]a da ‘manufar bincike’ da ‘hujjar ci gaba da bincike’ da ‘dalilan bincike’ da ‘muhimmancin bincike’ da ‘iyakacin bincike’ da kuma ‘hasashen wannan bincike’.

Babi na biyu ya yi bita da sharhi na ayyukan da suka gabata masu ala}a da wannan bincike. An yi bitar batutuwa kamar Hausa da {asar Hausa da Hausawa da adabi ‘kirari’ da nau’o’in adabi masu dangantaka ta }ut da }ut da kirari, kamar ‘take’ da ‘wa}a’ da manyan jigogin adabin fada, watau ‘yabo’ da zuga. Har ila yau an yi bitar ayyukan masana da manazarta da ya ji~anci fada kama daga tarihi zuwa adabi da al’adu. Sannan kuma, kasancewa aikin ya yi amfani da al’ada ce ya nazarci adabin da ke ciki aka kuma hango al’adar da ke cikinsa. An yi bita a kan ma’anar al’ada kamar yadda masana suka bayyana, tare da saraki da mata a {asar Hausa. Babu shakka, bitar wa]annan ayyuka ya taimakawa wannan bincike. Masu iya magana dai sun ce, “Da na gaba ake gane zurfin ruwa”.

Babi na uku ya }unshi hanyoyin gudanar da bincike, wanda ya ha]a da ‘farfajiyar bincike da dabarar za~en fada da kuma ‘hanyoyin tace bayanai’. An kuma kawo tarihin zabiyoyin da aka nazarci kirarin da suke yi wa saraki a Fadojin {asar Hausa tare da nau’in tambayoyin da aka yi wa zabiyoyin da sauran al’ummomin fada da aka gana da su. Farfajiyar wannan bincike kuwa ta ha]a da fadar Argungu da Daura da Ha]eja da Kano da Kazaure da kuma Zazzau (wato }asashen da suka yi fice bayan jihadi). An kuma za~i hanyoyi biyu }warara aka gudanar da binciken, akwai }wa}}warar hanya da ta }unshi ganawa da Zabiyoyin da aka nazarci kirarin da suke aiwatarwa da wasu jami’an fada da kuma wasu daga cikin saraki. Sauran hanyoyi sun ha]a da bibiyar ]akunan karatu domin ganawa da ayyukan

masana masu ala}a da wannan nazari da hukumomin adana tarihi na wasu jihohi da makamantansu. Har ila yau, an za~i ra'in tarihin al'umma 'ethnographic theory', aka dora wannan bincike a kansa. Ra'in tarihin al'umma wani ~angare ne daga ra'o'in al'ada wanda yake binciken }abila da ]abi'unta dangane da adabinta ko tarihinta ko kuma tsawon cu]anya da ita na a}alla shekara ]aya (1). Ra'in yana nazartar al'umma ta hanyoyi uku }warara" (i) ganawa da wa]anda da ake gudanar da bincike a kansu (ii) shiga cikin al'umma gadan-gadan da kuma (iii) sa ido ga abin da ake nazarinsa (gani da ido), wa]anda wannan bincike ya bi su ]aya bayan ]ayas domin cim ma burinsa.

Babi na hu]u ya yi taciyar bayanan da aka tattaro, ma'ana kirarin Zabiyoyin Fadoji shida na {asar Hausa. Wannan babi shi ne zakaran gwajin dafi domin shi ne ya }unshi gundarin wannan bincike. A nan ne aka }wan}wance jigon kirarin saraki a bakin mata, wato Zabiyoyin Fada. Sannan kuma an bibiyi tasirin addinin Musulunci da na zamani a kan Zabiyancin Fada. Wannan kuwa ya taso ne bayan daddale jigon kirarin, aka ga akwai bu}atar haka.

Babi na biyar ya ci gaba da taciyar kirarin, a inda aka nazarci salo ( ta fuskar adon harshe da aiwatar da harshe) da kuma irin nau'in zubin kirarin da Zabiyoyin Fada ke yi wa saraki.

### 6.3 Kammalawa

Sakamakon wannan bincike ya ci nasarar gano batutuwa kamar haka:

- sanannen abu ne a Hausa cewa kirari cike yake da yabo da zuga. Wannan bincike ya gano cewa babban jigon kirarin da Zabiyoyin Fada ke yi wa saraki ya tabbata yabo.

**Yabo**

- a }o}arin cim ma wannan yabo, Zabiyoyin Fada kamar sauran takwarorinsu maro}an fada suna amfani da shikashikan cim ma yabo da suka }unshi asali (salsala) da ambaton zuri'a da ri}e addini da jaddada shi da iya mulki (ri}on jama'a) da kyauta da kuma jaruntaka, su yabi saraki. {ananan jigogin kirarin su ne zuga da habaici.

**Zuga**

- ga al'ada babu abin da ya fi zuga kambama saraki kamar a yabe shi, a kuma zuga shi. To, su ma Zabiyoyin Fada a }o}arin yabo suna zuga saraki, ta hanyar kambama su da su cicci~a da kuma harzu}a su. Musamman ana zuga su ta fuskar jaruntaka ta iyaye da kakanni da dangantakarsu ko asalinsu na gadon sarauta.

**Habaici**

- basarake ba ya rasa `yan hamayya. Wannan ya sa a wasu lokuta Zabiyoyin Fada suna amfani da habaici domin su yi da abokan hamayyar saraki a fakaice. Musamman wa]anda aka yi takarar neman sarauta da su suka fa]i kuma suka }i dangana, a maimakon haka suka zama `yan adawa. Har ila yau, a wani lokaci a kan yi habaicin ne a fakaice tsakanin jinsin gidan sarauta biyu.

**Mizanin da Talaka ke Auna Saraki**

- aikin ya gano cewa wa]annan shikashikan cim ma yabo mizani ne da talaka yake auna saraki saboda wasu dalilai.

**Asali**

(i) kamar yadda aka sani a {asar Hausa sarauta yanzu gadonta ake yi. Wannan ya sa ba a amince wani wanda ba kowa ba ko bare ya sarauci al'umma kai tsaye, a'a sai ]an na gada, musamman sarauta ta Sarkin Yanka. Irin wannan sarauta sai wanda ya gada daga iyayensa da kakanni (ta hannun dama). Ko cikin wa]anda suka gada, ba a ba mutumin banza sarauta sai wanda ya cancanta. Wannan ya sa Zabiyoyin Fada ke jaddada salsalar saraki a kirarin da suke aiwatarwa.

**Iya Mulki/Ri}on Jama'a**

(ii) daga cikin sinadaran da ake bu}ata daga shugaba musamman saraki a {asar Hausa, akwai cancanta ta }warewa wajen hul]arsa da jama'arsa. Wato iya shugabantar al'ummar da suke }ar}ashinsa cikin adalci da tausayi da kulawa. Wannan ya sa Zabiyoyin Fada suke yabon saraki da iya mulki ko ri}on jama'a.

**Kyauta**

(iii) kamar yadda masu iya magana suke cewa, "Laifin babba rowa laifin yaro }yuya", a al'adance wannan ya sa ake kyautata zaton hannun babba a kullum ke sama, wato hannunsa a bu]e yake wajen kyauta. Haka ya sa Zabiyoyin suke yabon saraki da kyauta domin ana son shugaba ya kasance mai hannun baiwa.

**Jaruntaka**

(iv) duk kuwa da cewa yanzu daulolin da suka ha]u suka kafa {asar Hausa sun daina ya}ar junansu, har yau cikin shikashikan cancanta ga sarauta, jaruntaka na taka muhimmiyar rawa. Domin ana so shugaba ya zama jarumi ko wajen yanke hukunci ya kasance mai kaifi ]aya (tsayuwa kan magana ]aya). Wannan ya sa Zabiyoyin Fada ke danganta saraki da jaruntaka.

**Addini**

(v) wajibi ne shugaba ya kasance mai ri}o da jaddada addinin al'umma da kare martabarsa. A nan ma Zabiyoyin Fada suna yabon saraki da iya ri}e addinin al'ummarsa da jaddada shi.Wannan ya sa ake masa la}abi da'Duddugen addini' ko kuma '{ona matsafa'

Wa]annan dalilai ya sa wa}a da kirarin fada ba sa cika sai da yabon saraki da wa]annan abubuwa biyar (shikashikan cim ma yabo).

**Tasirin Tarihin Masarauta a Zabiyancin Fada**

- aikin ya gano cewa wasu daga cikin wa]annan shikashikan cim ma yabo sun fi tasiri ko mamaye kirarin da ake aiwatarwa a wata fada fiye da saura. Wannan a ce ba ya rasa nasaba da tarihin masarauta. Ke nan, tarihin masarauta yana tasiri ga kirarin da Zabiyoyin ke yi. Alalmisali:

**Nanata Muhimmancin Tarihin Asali ga Sarauta a Fadar Ha]eja**

(i) duk da cewa a kirarin kowace fada ana nanata da jaddada salsalar saraki saboda muhimmancin gadon sarauta a {asar Hausa, Zabiyar Ha]eja tana yawaita maimaita wannan matani, "[an na gada wanda ya fi ]an na koya". Wannan ba ya rasa nasaba da cewa sarautar Ha]eja ta jinsi biyu ce, Hausawa da Barebari da kuma Fulani.

**Yabo da ya Ji~anci Jaruntaka a Fadar Kabin Argungu.**

(ii) An fi ji amon jaruntaka a kirarin Zabiyar Kabin Argungu. Wannan ba ya rasa nasaba ko tasiri a kan dalilai biyu. Na farko dai masarautar Kabin Argungu ta yi suna a kan jaruntaka ta ya}i. Za a iya ganin haka daga tarihin masarautar musamman zamanin uban Kabawa, Sarki Muhammadu Kanta har zuwa lokacin Sarki Sama (]an Yakubu Nabame). Wannan ne ma ya sa har yau, duk Sarkin da ke Sarautar Kabin Argungu, galibi ba a }ir}iro kirari na musamman dominsa, a maimakon haka ana yi masa kirarin kakanninsa Kanta da Sama. Dalili na biyu shi ne an aiwatar da kirarin shekaru da dama

da suka wuce ( da ake ya}e-ya}e a daulolin {asar Hausa). Wannan ya sa idan aka koma ga zuga, za a iske cewa Zabiyar Fadar ta zuga saraki da jaruntar iyaye da kakanninsu.

**Kyauta a Fadar Kano**

(iii) Hausawa na cewa, "Yaba kyauta tukwici". Yabo da ya ji~anci kyauta ya mamaye kirarin da Zabiyar Kano ta yi wa marigayi Sarkin Kano Ado Bayero. Wannan a ce wata}ila saboda tasirin dukiya na harkokin kasuwanci, a matsayin Kano na cibiyar kasuwanci na {asashen Hausa ya haifar da haka. Masu iya magana na cewa" In da akwai nan ake bayarwa". Sannan kuma idan aka yi la'akari da wa}o}in da aka yi wa Sarkin Kano Ado Bayero, galibi kowane mawa}i ya yabe shi da kyauta. Wannan na nuni da cewa basaraken mai hannun baiwa ne matu}a.

**Iya mulki a Fadar Ha]eja**

(iv) Zabiyoyin Fada ba su cika mayar da hankali a kan yabon saraki ga iya ri}on jama'a ba, sai dai abin da ba a rasa ba.Kodayake Zabiyar Ha]eja ta }o}arta, musamman a kirarin Tafidan Ha]eja, Zabiyar tana cewa:

… Rumfa sha shirgi,

Kwano ba ka karaya…

Tana kuma yawan maimaita wani matani da ke nuni ga halin babba na ha}uri da ]aukan nauyi da taimako.

… Tudu abin dafawa…

Su ma sauran Zabiyoyin a ce sun yi }o}ari. Misali, Zabiyar Daura ta yabi Sarkin Daura da 'ha}uri', kamar yadda Zabiyar Kabi ta yabi Sarki Sama da 'gaskiya. Ita kuma Zabiyar Kazaure ta yabi sarakin Kazaure da 'adalci'.

**Ri}o ga addini**

(v) Dukkan Zabiyoyin da aka nazarta sun yabi saraki a kan ri}o ga addini da tabbatar da shi. To sai dai a ce ba kamar yadda Zabiyar Zazzau ta kira Sarkin Zazzau ‘duddugen addini’ da ‘toya matsafa’ ba. Ita ma Zabiyar Kazaure ta kira Sarkin Kazaure ‘Sarkin Musulunci’, kamar yadda ita ma Zabiyar Kano ta tabbatar da haka. Zabiyar Daura kuwa ta yabi Sarkin Daura ne da dogaro ga Allah. A yayin da Zabiyar Kabin Argungu ta yabi Sarki Kanta da yawaita ibada.

**Zuga a Kabin Argungu**

(vi) an fi samun ~ir~ishin zuga a kirarin da Zabiyar Kabin Argungu ta aiwatar.Wannan ba ya rasa nasaba da jaruntakar Sarakunan Kabi Argungu, kamar yadda aka yi bayani }ar}ashin jaruntaka.

**Habaici a Fadojin Kabin Argungu da Ha]eja**

(vii) an fi jin amon habaici a kirarin da Zabiyoyin Kabin Argungu da Ha]eja suka aiwatar.

**Adon harshe**

- aikin ya gano cewa cikin nau’o’in adon harshe, Zabiyoyin Fada sun fi amfani da nau’in kwalliya da jinsintarwa. Zabiyoyin suna amfani da abubuwa marasa rai irin su ‘guguwa’ da ‘zangon farin wata’ da ‘farshin wuta’ da ‘gulbin teku’ da ‘hadari’ da ‘katangar dutse’ da ‘rana’ da ‘jeji’ da ‘suri’ da ‘inuwa’ da makamantansu domin nuna }arfin iko da gawurtar saraki. Sauran nau’o’in adon harshe da Zabiyoyin suke amfani da su sun ha]a da alamtarwa da hotoncin zuci da tamka da karin magana da amsa kama da kuma kambamawa.

- Zabiyoyin Fada ba su cika amfani da kalmomin ban tsoro da ke tada hankalin abokan hamayya ba, kamar takwarorinsu maza. {ila a ce matsayin jinsi ne ya taka rawa a nan. Yabon saraki ta hanyar amfani da kalmomin ban tsoro }alubale ne ga abokan hamayya da sauran Sarakuna da dau}a}a sarakin da

aka yi wa. Kalmomi irin su: *katakore* da *wandara* da *tan}wafau* da *gajimare* da *aljan* da *zarto* da *]ibgau* da makamantansu.

**Aiwatar da Harshe**

- Zabiyoyin Fada suna amfani da sassau}an harshe wajen aiwatar da kirarin da suke yi wa saraki. Suna kuma sarrafa tsofaffin kalmomin Hausa, sannan sukan aro kalmomi daga wasu Harsuna, musamman Larabci.

**Tsofaffin Kalmomi**

- An Sani karakainar tsoffafin kalmomi a kirarin da Zabiyoyin Fada ke yi wa saraki, musamman kirarin Zabiyar Kabin Argungu. An tsinci kalmomi irin su: *Magume* gajeren mutum kuma }arfaffa) da *gadaragan* (gadon da mata ke yi wa }awa na }awatarwa, wanda kuma ba a kwanciya a kansa saboda adon da aka yi masa) da *kasari* (asabari) da *kasassawa* (wani irin mashi mai tsawan gaske) da *hulde* (farin doki tas marar sofane) da makamantansu.

**Aron Kalmomi**

- Zabiyoyin Fada kamar takwarorinsu maza, sun yin amfnai da dammar aron kalmomi daga wasu harsuna suka sarrafa su a kirarin da suke yi wa saraki, musamman harshen Larabci. An kuma tsinci kalma ]aya tilo da aka yi aron-aro daga Yarabanci, wato kalmar'Alfa'.

**Harshen Larabci**

- Kasancewa Zabiyoyin Musulmi ne kuma wa]anda suke yi wa kirarin su ma Musulmi, aron kalmomin Larabci ya yawaita a kirarin saraki a {asar Hausa.

Zabiyoyin sun ari kalmomin Larabci suka sarrafa su kai tsaye yadda suke a Larabci. Wasu kalmomin kuma sukan yi amfani da su kamar yadda aka Hausantar da su, watau fasahar nan ta 'fasalin aro'.

**Harshen Ingilishi**

- Harshen Ingilishi bai taka muhimmiyar rawa kamar yadda Larabci ya yi a kirarin Zabiyoyin Fada ba. A }alla in ban da kalmomin 'Bature' da 'Kaftin', ba a ji ]uriyar kalmomin Ingishi a kirarin ba.

**Zubi**

- ta fannin yanayin zubin kirarin Zabiyoyin Fada kuwa, binciken ya gano cewa:

i) sigarsa ta bambanta da kirarin da aka sani, wanda galibi yana iya kammaluwa a jimla ]aya rak. A iya cewa sigar kirarin da Zabiyoyin Fada kan aiwatar ya danganta ga abubuwan da ake so a yabi saraki da su. Kirarin ba zai iya kammaluwa a jimla ]aya ba, ko da kuwa za a yabi saraki da shikashikan cim ma yabo biyu kacal. Daga cikin kirarin da aka nazarta, mafi }aranci daga cikinsu shi ne mai jimla uku. Wani yakan zo cikin jimla hu]u ko biyar ko shida ko goma ko ma fiye da haka. Kirarin da Zabiyar Kabin Argungu ta yi wa Sarki Sama ya kai jimloli ]ari da ashirin da biyu (122), na Zabiyar Kano kuwa ya haura ]ari biyu. Ya kai ]ari biyu da talatin da biyar (235).

ii) kirarin ba a tsarin baiti yake ba, yana zuwa ne kara zube kamar yadda yake a sigar wa}ar baka.

iii) kirarin ba a rubuce yake ba.

iv) kirarin ba shi da amsa-amo.

v) wani lokaci kirarin yana zuwa da sigar tambaya amma ba kasafai ake samun amsar tambayar ba. An sami nau'in tambaya tabikh (domin }as}antar da abu). Misali a kirarin Sarki Sama, Zabiyar Kabin Argungu na cewa:

…Ana fa]in Magajin [anmusa ina Sarki ya yi?

Hur]e mai idon ~ata na Muhamman…

Wani misali shi ne na kirarin da Zabiyar Kano ta yi inda take cewa:

…Ga babur da mota wa yake zance da keke?

Ranar zuwan Hajiya Saude…

An kuma sami tambaya taha}i}i (tambaya mai tabbatar da abu). Misali, Zabiyar Kano a kirarin Sarkin Kano, tana cewa:

…Ina Bashar ]an masu gida?

Saboda mai Babban [aki yake ba ni riga.

Haka ma Zabiyar Daura, tana cewa:

Zabiya: Makazaki

`Yan Amshi: Makazaki

Zabiya: Makadodo

`Yan Amshi: Makadodo

Zabiya: Kamunka nawa?

`Yan Amshi: Kamunka nawa?

Zabiya: Dosono,

`Yan Amshi: Dosono.

Akwai kuma inda aka sami tambaya inkani (tambaya domin musanta abu) a kirarin Sarki Sama, kamar yadda Zabiyar Kabin Argungu ke cewa:

…Rugga na gani kana yadda ka so,

Yau ina laifin na Garba?

Gaba in ta yi tsambare ka nome…

(vi) kirarin ba ya zuwa da sigar kar~i, amma ana samun amshi a farkon kirarin da Zabiyar Daura take yi wa Sarkin Daura.

(vii) ana samun wasu jimloli su maimaita junansu a wani lokaci, musamman a kirarin Mai Martaba Sarkin Kano da wasu daga cikin kirarin sarakin Ha]eja

(viii) galibi kirarin ba shi da alamar da ke tabbatar da farkonsa ko }arshensa. Wannan ya sa ko da za a juya jimlolin kirarin, sa}onsa da ake so a isar ba zai canza ba.

(ix) Ta sigar kirarin, an sami tasirin addinin Musulunci. Alalmisali, Zabiyoyin wani lokaci sukan bu]e kirarin da sunan Allah, watau:

Bismillahi Rahmani Rahim…

Wooh Sha]i!

(Kirarin Sarki Kanta).

Suna kuma bu]ewa da Sallama:

Salamu alikum ban dawa bakka da nisa…

(Kirarin Sarkin Ha]eja)

An sami tasirin Musulunci da na zamani da ya yi wa Zabiyanci tarna}i.

- Tasirin Musulunci

Musulunci ya gurgunta zabiyanci ta hanyoyi uku:

(i) hani ga cu]anya tsakanin maza da mata da ]aya muryar mace. Zabiyar Fada kuwa mace ce da take Zabiyanci cikin maza. To haka kuma,

aiwatar da zabiyanci yana bu}atar ]aya muryr wanda Musulunci shi ma ya yi hani a kansa.

(ii) Kulle

Musulunci ya yi umarni ga ma zaje su killace matansu, su kuma daina barinsu kara zube kamar dabbobi. Wannan ya sa ba kowane namiji zai bar matarsa ta yi Zabiyanci ba. Ke nan, a ce Musulunci ya }as}antar da Zabiyanci saboda kyamatar cu]anyar maza da mata.

(iii) Hani ga ro}o

Addinin Musulunci ya yi hani ga ro}o. Ya bayyana ro}o hanyar da ke }as}antar da ]an Adam. Wannan ya sa Zabiyanci ya raunana.To sai dai a ce kirarin ya fito da tasirin Musulunci ta yadda ya bu}asa shi ta fuskar samar da sabon tunani da isassun kalmomi da suka bun}asa rumbun kalmomin Zabiyanci.

(iv) Tasirin Zamani

Baya ga addinin Musulunci, zamani ma ya taka babbar gudunmuwa wajen gurguata Zabiyancin Fada ta fuskoki da dama. Alalmisali:

- Ilimin Boko

Ilimin boko ya bayar da gundumuwa ta fannoni kamar haka.

i. `Ya'yan Zabiyoyin Fada da suka yi ilimin boko ba sa sha'awar gadon iyayensu saboda wayewar da suka samu daga ilimin boko.

ii. Sarakunan {asar Hausa ma sun bayar da tasu gudunmuwa wajen na}asa Zabiyancin Fada. Musamman yanzu da aka samu Sarakuna `yan boko bas u da sha'awar al'adunmu, sai dai sarautar. Wannan ya sa al'adun fada da dama sannu a hankali ana watsi da su. Cikinsu kuwa har da Zabiyancin Fad

iii. Shirin Game-Duniya ya sa matasa da dama ba su san al'adunmu. Alalmisali, a farkon wannan nazari, an fuskanci cewa da yawa daga al'ummar Hausa ba su san da zaman Zabiyancin Fada ba, ballantana su san rawar da yake takawa a al'adu da adbin fada ba.

**Muhimmancin Kirarin Zabiyoyin Fada**

A yayin gudanar da wannan bincike an gano cewa kirarin da Zabiyoyin Fada ke yi wa saraki a {asar Hausa, yana taka muhimmiyar rawa ta fuskoki da dama:

- Adana tarihi

  Ta hanyar ambato sunayen Sarakuna da sauran saraki a kirairn Zabiyoyin Fada, ana adana tarihin fada.

- Raya harshe

  Amfani da tsofaffin kalmomi a kirarin hanya ce ta raya harshe.

- {arfafa Zuciyar Saraki

  Jero sunayen iyaye da kakannin saraki da Zabiyar Fada kan yi, ta hanyar fa]in kyawawan halayensu da bajinta da kwarjini, yana }arfafa zuciyar saraki.

- Nuna bayyanar Sarki. Kirarin sanarwa ce ta bayyanar saraki a duk inda yake.

- Matsayin gaisuwa ne ga saraki

Kirarin yakan kasance matsayin gaisuwa ga saraki. Alalmisal, farkon kirarin Sarkin Daura yana umartar fadawa da sauran jama'a su dur}usa su yi gaisuwa. Ma'anar wannan sashe na kirari shi ne, " Ga masu gari nan tafe, a dar}usa a gaishe da masu garin."

Mararrafar madangari,

Madur}usar madangari.

- raha da nisha]i.

Kirarin yana samar da raha da nisha]a, musamman ga wanda ake yi hirarin dominsa. Alalmisali, a ziyarar da aka yi Kano an iske babu Zabiyar Fada, amma an sami faifan CD da ake sawa Mai Martaba Sarkin Kano Ado Bayero, duk lokacin da ya nemi haka (domin samun nisha]i).

- fito da rayuwar al'umma

kirarin yana fito da rayuwa al'umma. Alalmisali, kirarin da Zabiyoyin Fada ke aiwatarwa ya fito da yadda talaka ya dauki saraki a {asar Hausa:

(i) ]an na gada (mai asali ba bare ko mutumin banza ba).

(ii) jarumi da zai iya kare su .

(iii) mai jaddada addinin al'ummarsa da kare martabarsa.

(iv) mai hannun kyauta (musamman ga mabu}ata).

(v) }wararre wajen mulki (mai ha}uri da gaskiya da adalci da tausayi da makamantansa), wa]annan duk sun }ara tabbatar da cewa adabi hoto ne da ke bayyana rayuwar al'umma.

- nuna gwanintar harshe

Kirarin yana nuna gwanintar harshe ta hanyar amfani da nau'o'in adon harshe daban-daban da suka taimaka wajen gina sa}o.

Wannan bincike ya }ara tabbatar da kasancewar adabi madubin rayuwar al'umma ne. Misali: jarunta a Argungu, malamta a Kano da Kazaure.

A ta}aice, aikin ya yi amfani da wata al'adar fada, ya nazarci adabin da ke cikinsa. Sannan ya fito da rayuwar al'umma daga kirarin. Sanannan abu ne cewa al'ada a aikace ake aiwatar da ita, a yayin da adabi a magance yake. Adabi fasaha ce da take bayyana al'ada ( adabi ke bayyana al'adun al'umma a gansu }uru-}uru, baya ga kasancewarsa rumbun tanada al'ada).

## 6.4 Shawarwari

Wannan bincike yana shawartar masana da manazarta a kan:

- taskace al'adunmu a rubuce a fagen ilimi ( a littattafai da kundayen bincike irin wannan ) domin amfanin gobe. Ko ba komai na baya za su sami damar sanin wasu al'adun iyaye da kakanni magabata. Masana da manazarta kuma za su sami ayyukan nazari.
- kamar yadda Magaji (2002), ya taskace wasu al'adu uku na Masarautar Katsina masu nuni da kirarin da ake yi wa Katsina (na Dikko ]akin kara), ya kamata a taskace sauran al'adunmu, musamman masu nuni da irin kyawawan ]abi'unmu. Wannan aiki ya yi }o}ari daidai gwargwado ya fito da Zabiyoyin Fada a {asar Hausa, wa]anda aka so a manta da rawar da suke takawa.
- kamar yadda wannan nazari ya yi amfani da al'adar Zabiyanci a fadar {asar Hausa, ya nazarci adabin da ke cikinsa, sannan ya fito da rayuwar al'umma daga adabin. Akwai bu}atar manazarta su nazarci al'adar Zabiyanci a fagen nazari.

- zai zama alfanu gare mu idan aka sami manazarta suka taskato sauran al'adunmu na Fada kamar haka:

(i) Innar Gobir

(ii) Magajiyar Argungu

(iii) Jakadanci a Fada

(iv) Sauran sarautu da ayyukan mata a Masarautun {asar Hausa, kamar Magu]iya da Uwar Soro da makamantansu.

(v) Sauran al'adun fada.

- masana da manazarta su ]auki kyawawan al'adunmu a majigi a sa su a kafafen sadarwa na zamani domin duniya ta sansu.

## Manazarta


Abubakar, A.S. (2013) "Sarautar Sarkin Hatsi a Fadar Kano", Cikin *Harsunan Nijeriya XXIII,* Kano: Centre for the Study of Nigerian Languages, Bayero University.

Abubakar, M. (2009), The Gwandara and Hausa Cognates. A Lexico Statistical Analysis M.A. Dissertation, Zaria: Department of Nigeria and African Languages, Ahmadu Bello University, Zaria.

Abdul}adir, D. (2011)." Gyara Kayanka: Tasirin Al'adun Hausa Ga Ci Gaban {asa", Cikin Yalwa, Bichi da Sammani (ed), *Studies in Hausa Language, Literature and Culture*, Proceedings of the Sixth Hausa International Conference, Kano: Centre for the Study of Nigerian Languages, Bayero Univresity.

Abraham, R.C. (1967). *Dictionary of the Hausa Language*, Second Edition, London: University of London Press Limited.

Adamu, J.S. (2008). "Habaici a Zamantakewar Hausawa", in *Algaita Journal of Current Research in Hausa Studies,* No.5 Vol.1, Kano: Department of Nigerian Languages, Bayero University.

Adamu, M. (1977). "Towards the Definition of Hausa Culture in African Context" Seminar Paper Presented at the Centre for Nigerian Cultural Studies, Zaria: Ahmadu Bello University.

Adamu, M. (1978). *The Hausa Factor in West African History,* Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Adamu, M. (1980). “The Hausa and Other People of Northern Nigeria, 1200-1600AD” Paper Presented at a Departmental Seminar Series, Zaria: Department of History, Ahmadu Bello University.

Adamu, M. T. (1997). *Asalin Hausawa da Harshensu,* Kano: [an Sarkin Kura Publishers Limited.

Adamu, M.U. (2011).*Sabon Tarihin Asalin Hausawa,* Kaduna: Espee Printing and Advertising.

Ahmad, L. (2011). Sarauta a Wa}o}in Shata: Nazarin Yabau, Kundin Digiri na Farko, Zariya: Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello .

Ahmed, S. B. (1990). Tsarin Sarautar Gargajiya a Ha]eja, Kundin Digiri na Farko, Kano: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Ahmed, S. (1984). Take a Fadar Zazzau, Kundin Digiri na Farko, Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello.

Alhassan, H. da Wasu (1982). *Zaman Hausawa*, Zaria: Institute of Education Press, Ahmadu Bello University.

Almajir, T.S. (2010). “Zamantakewar Hausawa Matasa a {ar}ashin Shirin Game-Duniya, “Cikin *Mujallar Harshe 4,* Zariya:Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello.

Ako, S.A. (2002). Sarautar {aura: Tarihinta da Matsayinta a Masarautar Daura, Kundin Digiri na Farko, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Amfani, A. H. (2011). “Hausa da Hausawa: Jiya da Yau da Gobe” Cikin Champion of Hausa Cikin Hausa: A Festschrift in Honour of [alhatu Muhammad, Zariya: Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello.

Amin, M. (2010). Kirari a Talla, Kundin Digiri na Farko, Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello.

Amin, M.L. (2002). Hausa Metaphysical Worldview: A Premiological Expasition, Unpublished PhD Thesis, Zaria: Department of Nigeria and African Languages, Ahmadu Bello University.

Amin, M.L. (2012). “Globalization and Cultural Synchronization in Hausa: A Literary Reflection”, in *Harshe* 6, (Special Edition), Zaria: Department of African Languages and Cultures, Ahmadu Bello University.

Aminu, A. M. (2002). Sarautu a Masarautar Kano, Kundin Digiri na Farko, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Aminu, M. (1978). “Muhimmancin Maro}an Baka a {asar Hausa”, Cikin Yahaya, I.Y. da Rufa’i, A, *Studies in Hausa Language, Literature and Culture,* First Hausa

International Conference, Centre for The Studies of Nigerian Languages, Kano: Bayero University.

Augie, A. R. (1984). The Gobir Factor in the Social and Political History of the Rima Basin, Unpublished PhD Thesis, Zaria: Department of History, Ahmadu Bello University.

Argungu, I (2007). "Kirari da Wa}ar Kamun Kifi a Garin Argungu:, Kundin Digiri na Tsakiya, Sakkwato: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu [anfodiyo.

Bagudu, M.T. (1974). *History of the Land Zazzau*, Zariya: Gaskiya Corporation Limited.

Balbasatu, I (2009). Gudunmuwar Mata Ga Ha~aka Rubutaccen Adabi, Kundin Digirin {oli, Sakkwato: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usman [anfodiyo.

Bahago, A.A. (1998). *Kano Ta Dabo Tumbin Giwa,* Kano: Munawwar Books Foundation.

Bappah, S. M. (1984). Ro}o: Traditon and Change in a Hausa Theotrical Form, Unpublished M.A Dissertation, Zaria: Department of English, Ahmadu Bello University.

Baldic, C. (2004). *Concise Dictionary of Literary Terms*, New York: Oxford University Press Inc.

Bargery, G.P. (1993). *A Hausa English Dictionary and English Hausa Vocabulary (*2nd ed) Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited.

Barker, C. (2012). *Cultural Studies: Theory and Practice* (4th ed), London: Sage Publications Limited.

Bello, G. (1976). "Yabo, Zuga da Zambo a Wa}o}in Sarauta", Cikin *Harsunan Nijeriya* (iv) CSNL, Kano: Abdullahi Bayero College, Ahmadu Bello University.

Bello, I. (1985). Take da Kirari Fadar a Gombe, Kundin Digiri na [aya, Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Besmer, F.E. (1973). "Praise Epithets and Songs Text for Some Important Bori Spirits in Kano" in *Harsunan Nijeriya* III, Kano: CSNL, Abdullahi Bayero College, Ahmadu Bello University.

Bichi, A. Y. (2011). " Bayajidda Legend in the 21st Century: A Reassessment" in Yalwa, L.D. el al (ed), *Studies in Hausa Language, Literature and Culture, Zaria:* CSNL, Bayero University.

Bichi, A. Y. (2013). "Praise Songs, African Foklore and Globalisation", Paper, Presented at the International Conference on Folklore, National Intergration and Development in Honour of Prefessor [andatti Abdul}adir, Kano: Bayero Unversity.

Binta, W. (1998). Adabin Baka: Sigoginsu da Hikimominsu, Kandin Digiri na Tsakiya, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Bunza, A. M. (1990). Haya}i Fidda na Kogo, Kundin Digiri na Tsakiya, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya.

Bunza, A.M. (2006). *Gadon Fede Al'ada*, Lagos: Ibrash Islamic Publications.

Bunza, A.M. (2009). *Naramba]a*, Lagos: Ibrash Islamic Publications.

Bunza, A. M. (2011). "Sakkwato Ce Tushen Hausa, In ji Naramba]a", Mu}alar da aka Gabatar a Taron {ara wa Juna Sani, Katsina: Nazarin Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Umaru Musa `Yar'adua.

Butcher, S.H. (2000). *The Poetics of Aristotle,* Pennsylvania: A Penn State Electronic Publications.

Boyd, I. (1979). "Sarkin Gobir Bawa Jan Gwarzo", Cikin *Mazan Jiya*, Sakkwato: Ma'aikatar Ilimi ta Jihar Sakkwato.

Crystal, D. (2009). *A Dictionary of Linguistics and Phonetics,* (6th ed), USA: Blackwell Publishers.

CSNL, (1981). *Rayuwar Hausa*, Lagos: Thomas Nelson Nigeria Limited.

CSNL, (2006). *{amusun Hausa,* Zaria: ABU Press Limited.

Dalhatu, U. (2002). *Malam Jafaru [an Isyaku: The Great Emir of Zazzau*, Zaria: Woodpecker Communications Service.

Dalhatu, U. (2005). *Abdullahi Bayero: The Pre-Eminant Emir of Kano.* Zaria: Woodpecker Communications Service.

[angambo, A. (1984). *Rabe-Raben Adabin Hausa da Mahimmancinsa Ga Rayuwar Hausa,* Kano: Triumph Publishing Company.

[angambo, A. (2007). *[aurayar Gadon Fe]e Wa}ar, Zariya:* Amana Publishers Limited.

[angambo, A, (2011). "Wa}a da Rawar da Take Takawa a Rayuwar Hausawa", Ma}alar da aka Gabatar Domin Tunawa da Cikar Shekara Goma Sha Biyu da Rasuwar Dr. Mamman Shata, Katsina: Kwalejin Ilimin ta Tarayya.

[an'iya, D (1997). Adon Harshe Cikin Rubutaccen Adabin Hausa, Kundin [igiri na {oli, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

[anhausa, A. M. (2012). *Hausa Mai Dubun Hikima*. Kano: Century Research and Publishing Company.

[anlami, U.H. (1982). Kirarin Sarautu da Sana'o'in da Unguwannin Zariya, Kundin Digiri na Farko, Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

[antumbushi, M.A, (2007). “Matsayin Wa}a ga Al’umma: Tsokaci Kan Wasu Wa}o}in Hausa”, in *Degel Journal*, Vol. VIII, Sokoto: Faculty of Arts and Islamic Studies, Usmanu [anfodiyo University.

Daura, B. (2000). *Tuna Baya: Tarihin al’adun Mutanen Nijeriya*, Kaduna: Informat Publishers Limited.

Diso, A. H. (1997). Zambo da Yabo a Matsayin Dabarun Jawo Hankali a Rubutattun Wa}o}in Siyasa, Kundin Digiri na Tsakiya, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Dunfawa, A.A. (2004). “Zuga a Wa}o}in Fada”, in *Algaita Journal of Current Research in Hausa Studies*, No.3 Vol.1, Kano: Department of Nigerian Languages, Bayero University.

Dokaji, A. A. (1978). *Kano ta Dabo Ci Gari*, Zaria: Northern Nigeria Publishing Company Limited.

Edward, B.F. (1971). “Hausa Court Music in Kano:” Unpublished PhD, Thesis, London: University of Columbia.

Eagleton, T. (2008). *Literary Theory: An Introduction*, USA: Blackwell Publishing.

East, R.M. (1936). *Six Hausa Plays,* London: West African Publicity Limited.

Elizabeth, D. (2007). A Critical Study of Praise Singer Yesterday, Today And Tomorrow, Unpublished M.A, Dissertation, South Africa: Department of African Languages, University of South Africa.

Faruk, B (2010). Wasu Al’adun Gidan Sarautar Katsina da Yadda Ake Gudanar da Su, Kundin Digiri na Farko, Katsina: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami’ar Umaru Musa `Yar’adua.

Fatima U.A. (2012). Kwatanta Jigon Yabo a Wa}o}in Sarakuna na Baka da Rubutattu, Kundin Digiri na Tsakiya, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Field, S. (2007). *Oral History Methodology,* Philippines: University of Philippines Press.

Furniss, G. (1996). *Poetry, Prose and Popular Culture in Hausa*, London: Edinburgn University Press Limited.

Garba, D. (1997). Azancin Magana a Wa}o}in Baka, Kundin Digiri na Tsakiya, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Garba, S. (2011). Salon Sarrafa Harshe a Wa}o}in A}ilu Aliyu, Kundin Digiri na {oli, Zariya: Sashen Harsuna da al’adun Afirka, Zariya: Jami’ar Ahmadu Bello.

Garba, S. (2014). “Hotoncin Zuci a Wa}ar Sabo Wakilin Tauri ta Hamisu Sarkin Ki]i", Mu}alar da aka Gabatar a Taron {asa, Kan Nazarin Harsuna da Adabi da Al’adun Nijeriya,Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Gaya, A.M. (1998). Tsarin Mulkin Gargajiya Jiya da Yau: Musamman a Kano, Kundin Digiri na Farko, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Gaya, A.M. (2012). Tasirin Siyasa a Masarautun Gargajiya Musamman a Masarautun Sakkwato da Katsina da Kano da Daura, Daga 1960 -2000, Kundin Digiri na Tsakiya, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Gi]a]awa, A. B. (2004). *Baje Kolin Hajar Tunani, Kaduna*: Fisbas Media Services.

Groove, A.T. (1957). *The Land and Population of Katsina Province*, Kaduna: Govenrment Printer.

Gusau, S.M. (1988). Wa}o}in Fada, Sigoginsu da Yanaye – Yanayensu, Musamman a {asar Sakkwato, Kundin Digiri na {oli, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Gusau, S.M. (1991). "Tsokaci Kan Tushen Kalmar Adabi", Cikin *Mujallar Bagaruwa,* No.1, Vol.1, Kano: Kungiyar Hausa, Jami'ar Bayero.

Gusau, S.M. (1999). "Mahimman Garuruwan {asar Hausa: Waiwaye kan Tarihin Kafuwarsu," Cikin *Mujallar WAJLLC*, Vol 1, No.2, Kano: Jami'ar Bayero.

Gusau, S.M. (2000). "Kirari a Wa}o}in Maka]an Hausa", in *Hausa Studies, Vol. II, No 12,* a Journal of the Department of Nigerian Languages, Sokoto: Usmanu [anfodiyo University.

Gusau, S.M. (2002). *Sarkin Taushi Salihu Janki]i,* Kaduna: Baraka Publishers Limited.

Gusau, S.M. (2003). *Jagoran Nazarin Wa}ar Baka,* Kano: Benchmarch Publishers Limited.

Gusau, S.M. (2005).*Maka]a da Mawa}an Hausa, Kano:* Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S.M. (2008). *Wa}o}in Baka a {asar Hausa: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu,* Kano: Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S.M. (2009). *Diwanin Wa}o}in Baka,* Kano: Century Research and Publishing Limited.

Gusau, S.M. (2010). "Al'adun Hausa a Ta}aice" Cikin Funtua, A.I. da Gusau, S.M. (ed), *Al'adu da [abi'un Hausawa da Fulani,* Kaduna: El-Abbas Printers and Media Concepts.

Gusau, S.M. (2011). *Adabin Hausa a Sau}a}e,* Kano: Century Research And Publishing Limited.

Gusau, S.M. (2013). "Tsokaci a Kan Al'adun Hausawa", Cikin *Harsunan Nijeriya xxiii,* Kano: CSNL, Bayero University.

Halima, K.D. (2010). "Nazarin Wa}ar Rayuwa", Cikin *Mujallar Himma*, Vol. 2, Katsina: Sashen Nazrin Harusnan Nijeriya, Jami'ar Umaru Musa `Yar'adua.

Hamza, M. W. (1984). Tatsuniya As a Mirrow of Hausa Social Relationships, Unpublished M.A.Dissertation, Zaria: Department of Nigeria and African Languages,Ahmadu Bello University.

Hauwa, M. (2008). "Karin Harshe na Rukuni a Hausa: Nazari a {asar Zazzau", Kundin Digiri na Tsakiya, Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Hauwa, M.B. (2011). Wa'azi a Rubutattun Wa}o}in Mata na {arni Ashirin, Kundin Digiri na Tsakiya, Zariya: Sashen Nazirin Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Hiskett, M.(1975). *History of Hausa Islamic Verse,* London: School of Oriented and African Studies, University of London.

Hauwa, R.[. (2005). Sarautar Mai Babban [aki a Fadar Kano, Kundin Digiri na Tsakiya, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Hitti, P.K (1961). *History of the Arabs,* London: Macmillan Company Limited.

Ibrahim, M.S. (1982). Dangantakar Al'ada da Addini: Tasirin Musulunci Kan Rayuwar Bahaushe ta Gargajiya, Kundin Digiri na Tsakiya, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Ibrahim, M.S. (1985). "Gudunmuwar Adabin Baka Wajen Raya Al'adun Gargajiya na Hausa", Cikin Rufa'I, A da Wasu (ed), *Nazari a kan Harshe da Adabi da Al'adun Hausa,* Kano: Jami'ar Bayero.

Ibrahim, M.S. (1988) *Kowa Ya Sha Ki]a,* Lagos: Longman Publishing Company Limited.

Ibrahim, M.S. (2004). "Kano Tumbin Giwa Jalla Babbar Hausa, Gari ba Kano ba Dajin Allah, Yaro Ko da Me Ka Zo an Fi Ka" Cikin *Mujallar Algaita,* Vol.I No3, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Ibrahim, A. (1991). *Alhaji Muhammadu Bashar: A Biography,* Katsina: Himma Press Limited.

Idris, Y. (2009). "Raggo a Mahangar Wasu Maka]an Noma na Hausa", Cikin *Mujallar Himma* Vol.I, Katsina: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Umaru Musa `Yar'adua**.**

Ikara, B. (1981). *The Nigerian Languages and Cultural Development* (ed), Lagos: The National Language Centre.

Junaida, I da Yar'adua, T.M. (2007). *Harshe da Adabin Hausa a Kammale,* Lagos: Spectrum Books Limited.

Kaduna State Government. (1977/1978). *Daura: Survey and Development Plans,* Kaduna: Max Loch Group Nigeria Limited.

Kafin Hausa, A.U. (1985). Kirari a Hausa: Matsayinsa da Yanayinsa, Kundin Digiri na Tsakiya, Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Kafin Hausa, A.U. (1997). " Kirarin Sarakuna da na Garuruwa", Cikin *Harsunan Nigeriya*, xviii, Kano: CSNL, Jami'ar Bayero.

Khalil, N.W. (2007a). " Hausar Gidan Sarauta: Cikin Kiran Lafiya a Fadar Kano", Paper Presented at the National Conference on Hausa Studies, Centre for the Study of Nigerian Cultural Studies, Sokoto: Usmanu [anfodiyo University.

Khalil, N.W. (2007b). *Bayi a Gidan Dabo,* Kano: Gidan Dabino Publishers.

King, A. (1980). "Statement, Restatement and Extension: Stanzaic Structure in Hausa Court Songs", Seminar Paper, Zaria: Department of Nigerian and African Languages, Ahmadu Bello University.

Kano State Government (1969).*Kano State This Month*, Kano: Government Printer.

Koforowola, E. O. (1982). Hausa Performing Arts and The Emir's Court, Unpublished PhD Dissertation Zaria, Department of English, Ahmadu Bello University.

Lugga, S.A. (1993). *The Great Province,* Katsina: Lugga Press Limited.

Lavers, E. J. (1980). " A Note on the Terms 'Hausa and Afuno', Paper Presented at the International Conference on Kanuri Language and Literature, Kano: CSNL: Bayero University.

Mack, B.B. (1990). "Women and Slavery in Northern Nigeria", in *Journal of Comparative Studies, Vol. 1, No.1,* London: Elizabeth Savage.

Mack, B.B. (2004). *Muslim Women Sing: Hausa Popular Song*, Bloomington and Indianapolis: Indiana University Press.

Magaji, A. (1982). " Gudunmuwa a Kan {o}arin da ake Yi na Samar da Cikakken Tarihin Hausa da Harshensu", Ma}alar da aka Gabatar a Taron {ara wa Juna Sani, Sashen Harsunan Nijeriya, Kano: Jami'ar Bayero.

Magaji, A (2002). Wasu Al'adun Hausa, Yanaye-yanayensu a {asar Katsina, Kundin Digiri na {oli, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Mamman, M. (2010). *Tarihin Katsina ({arni na 15-20).* Zariya: Gaskiya Corporation Limited.

Mamman, M. (2011). Tarihin Unguwannin Katsina, Zaria: ABU Press Limited.

Maijidda, A.S. (2002). "Wa}o}in Amada a Fadar Kano", Kundin Digiri na Tsakiya, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Maimuna, L. D. (1987). Fadar Daura, Kundin Digiri na Farko, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Mani, A. (1970). *Zuwan Turawa Nijeriya ta Arewa*, Zariya: Northern Nigeiran Publishing Company Limited.

Maryam, A. I. (2012). Adon Harshe a Wa}o}in Binta Zabaya da Barmani Coge, Kundin Digiri na Biyu, Zariya: Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Maradun, M.S. (1992). Sarautar Gargajiya a {asar Hausa, Nazarin Mu}aman Sarautar Gargajiya a Sakkwato, Kundin Digiri na Tsakiya, Sakkwato: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu [anfodiyo.

Mazawaje, M. I. (1985), Zambo da Habaici a Wa}ar Fada, Kundin Digiri na Farko, Zariya: Sashen Nazarin Harsunan da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Muhammad, A. B. (1991). Tasirin Zuwan Turawa Kan Sarautun Gargajiya a {asar Hausa: Tsokaci kan Sarautar Kano, Kundin Digiri na Tsakiya, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Muhammad,A.S.(2012). Nazarin Rayuwa da Ayyukan Maka]a Sa'idu Maidaji Ramba]awa, Kundin Digiri na Tsakiya, Sashen Nazarin Harsuna da Al'adun Afirka, Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

Muhammad, A.Y. (2001). *Adabin Hausa,* Zariya: Ahmadu Bello Unviersity Press Limited.

Muhammad, [. (1977). Individual Talent in the Hausa Poetic Tradition: A Study of A}ilu Aliyu and His Art, Unpublished PhD Thesis London: University of London.

Muhammad, [. (1978). "Wa}a Bahaushiya", Takardar da aka Gabatar a Taron {ara wa Juna Sani, kan Harshe da Adabin Hausa, Kano: Jami'ar Bayero.

Muhammad, [. (1990).*Hausa Metalanguage* (ed) Vol. I, Ibadan: University Press Limited.

Muhammad, [. (2011). " Hausa A Duniyar Yau: Tasirin Shirin Game-Duniya Kan Harshen Hausa", Cikin Yalwa, Da da Wasu, *Studies in Hausa Language, Literature and Culture,* Proceedings of The Sixth Hausa International Conference, Kano: Centre for the Study of Nigerian Languages, Bayero University.

Mukhtar, I. (2004). *Jagoran Nazarin {agaggen Labarai,* Kano: Benchmark Publishers Limited.

Mode, M.A. (2004). A Stytistic Study of Hausa Towns Kirari (Epithets), Unpublished PhD Thesis, Sokoto: Department of Foreign Languages, Usmanu [anfodiyo University.

Montgomery, M. (1995). *An Introduction to Language and Society* ($2^{nd}$ ed), New York: Routledge.

Mu'azu, A. (2005). Tasirin Ba}in Al'adu a {agaggun Labarun Soyayya na Hausa, Kundin Digiri na {oli, Kano: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

NNPC, (1970,1971). *Hausawa da Makwabtansu* (1 &II), Zaria: Northern Nigerian Publishing Company Limited.

Nuruddeen, M. (1982). Sallar Gani a Daura, Kundin Digiri na Farko, Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Nwabara, S.N. (1981). "The Wealth of Igbo Language and Culture" in Ikara, B. (ed) *Nigerian Languages and Cultural Development,* Lagos: The National Language Centre.

Otile and Ogimno (1979). *An Introduction to Sociological Studies,* Ibadan: Heinemann Education Books.

Powe, E.L. (1981). "Kirarin Duniya: a Semiological Study of Selected Epithets",In *Harsunan Nijeriya* XI, CSNL, Kano: Bayero University.

Rabi, G. (1998), Nazarin Jinsi da Adabi: Tsokaci Kan Matsayin Mace a Rubutattun Wasannin Kwaikwayo na Hausa, Kundin Digiri na Tsakiya, Zariya: Sashen Harsunan Nigeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Rabi, M. (2011). [abi'un Mata a Bakin Mawa}an Baka na Hausa, Kundin Digiri na Tsakiya, Zariya: Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Ramatu, A. (2003), "Maka]an Sarauta da Muhimmancinsu a Fadar Zazzau, Kundin Digiri na Tsakiya, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Ramlatu, J. D. (2012). "Sarautun {asar Daura da Mahimmancinsu ga Al'umma" Cikin *Champion of Hausa Cikin Hausa,* Amfani, A.H. da wasu (ed), Zariya: Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Sadiyya, O. (2010), Malam Mu'azu Ha]eja: Fasihin Mazan Jiya, Kundin Digiri na Uku, Sakkwato: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu [anfodiyo.

Safiya, A. (2011). A Study of the Challenges Faced by Female Executive Producers of Home Video in Kanywood, M.A Dissertation, Kano: Department of Mass Communication, Bayero University.

Salahu, I. A (1981), Ta}aitaccen Nazari Kan Maguzawa da Al'adunsu, Kundin Digiri na Farko, Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Saleh, G. (2006) Shamaki da Danrimi a Masarautar Kano, Kundin Digiri na Tsakiya, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Sa'id , B. (1978) Gudunmuwar Masu Jihadi Kan Adabin Hausa, Kundin Digiri na Tsakiya, Kano: Sashen Nazrin Harsunan Nijeriya, Kwalejin Jami'ar Bayero (ABC/ABU.)

Saulawa, A. M. (2001). "Origin of the Hausa States Revisited", In *Degel Journal,* Faculty of Arts and Islamic Studies, Sokoto: Usmanu [anfodiyo University.

Schuh R. G. (1982). "The Hausa Language and Its Nearest Relatives; in *Harsunan Nijeriya,* 17, Kano: CSNL, Bayero University.

Shafa'atu, M.T. (2013). Kirarin Mata a {asar Sakkwato, Kundin Digiri na Tsakiya, Sakkwato,Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu [anfodiyo.

Sharifai, B.I. (1990). Take da Kirarin Sana'o'in Gargajiya, Nazarin Ma'anarsu da Mahimmancinsu Ga Rayuwar Hausa, Kundin Digiri na Tsakiya, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Shehu, A (2005). {aramin {amus na Sarauta a {asar Hausa, Kundin Digiri na Farko, Zariya: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Shehu, I. (2012). "The Evolution and Establishment of {asar Zazzau to 1804, In *Harshe Journal* (6), Zaria: Department of African Languages and Cultures, Ahmadu Bello University.

Shifley, J. T. (1970). *Dictionary of World Literary Terms*, U.S.A: The Writer Inc.

Suleiman, B. (1990). Take da Tasirin Sana'o'in Gargajiya, Kundin Digiri na Tsakiya, Sakkwato: Sashen Nazrin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu [anfodiyo.

Smith, A. (1970). "Some Notes on the History of Zazzau Under the Hausa", In Martimare, M.I. (ed) *Zaria and Its Region*, Zaria: Ahmadu Bello Unviersity Press Limited.

Smith, A. (1977). "Early States of Central Sudan" in Ajayi, A and Crowder, M. (eds) *History of Africa* (2nd ed), Vol. 1, London: Longman Group.

Smith, M.G. (1957). "The Special Function And Meaning of Hausa Praise Singers", In *African Journal, Vo. 27, No. 1 pp26-45* Cambridge: Cambrige University Press.

Smith, M.G. (1960). *Government in Zazzau*, London: University of California Press.

Smith, M.G. (1978). *The Affairs of Daura*, London: University of California Press.

Tijjani, L.I. (1990). *Katsina [akin Kara*, Katsina: Himma Press Limited.

Tsiga, I.A. (1978). "Sarauniya Daurama", Ma}alar da Aka Gabatar a Taron {ungiyar Hausa, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Tsoho, M.Y. (2001). "Tubalin Ginin Yabo: Tsokaci Kan Yabau a Wa}o}in Iko", *FAIS Journal of Humanities* Vol.1, No.4, Kano: Bayero University.

Tsoho, M. Y. (2002). Elogues, the Building Blocks of Hausa Praise Song: A Thematic and Structural Examination, Unpublished PhD Thesis, Zaria: Department of Nigerian and African Languages, Zaria: Ahmadu Bello University.

Tsoho, M.Y. (2010a). "San}ira: Gudunmuwarsa a Gina Wa}o}in Yabo", In *Harshe 4*, Journal of the Department of Nigerian and African Languages, Zaria: Ahmadu Bello University.

Tsoho, M.Y. (2010b). "Jarunta a Wa}o}in Baka : Nazarin Wa}ar Shago", Cikin *Mujallar Himma*, Vol.2, No2, Katsina: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Umaru Musa `Yar'adua.

Turai, U.M.Y. (1983). Binta Zabaya da Wa}o}inta, Kundun Digiri Na Farko, Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Uba, M.T. (2003). Nazari Kan Kirarin Wa]ansu Garuruwan Hakiman Masarautar Kano, Kundin Digiri na Tsakiya, Kano Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Umar, M.B. (1987). *Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya*, Kano: Triumph Publishers Company Limited.

Umma, A. A. (2008). Sassar}uwar Adabi Cikin Adabi, Nazarin Adon Harshe a Wa}o}in Fina-Finan Hausa, Kano: Kundin Digiri Na {oli, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Umaru, A.N. (2008). *Daular Fulani a Kano*, Kano: Benchmark Publishers Limited.

Usman, B.B. (1985). Fadanci a {asar Hausa, Kundin Digiri na Farko, Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

Usman, B.B. (2009), Zari: Ki]an Sana'ar {ira don Zuga Ma}era, Cikin *Harshe 3*, Zariya: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Usman, Y.B. (1981). *The Transformation of Katsina 1400-1883: The Emergence and Overthrown of Sarauta System and Establishment of the Emirate*, Zaria: Ahmadu Bello University, Press Limited.

Usman, Y.B. (1983). "A Reconsideration of the History and Relations Between Barno and Hausa Land Before 1804 AD", In Usman, Y. B. and Al}ali, N. (eds), *Studies in The History of Pre-colonial Barno*, Zaria: Northern Nigerian Publishing Company Limited.

Wakili, H. (2005). *Turawa a {asar Ha]eja, Kano:* Benchmark Publishing Limited.

Waziri, U.D. (2012). Tasirin Sarautun Hausawa a Kan {abilun Kare-Kare da Sayawa (Zar), Kundin Digiri na Tsakiya, Sakkwato: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Usmanu [anfodiyo.

Ya~o, B.A. (2000). Karuwanci a Mahangar Mawa}an Hausa: Nazari Kan Jigon Karuwanci a Cikin Wa}o}in Baka da Rubutattu, Kundin Digiri na Tsakiya, Sakkwato: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu [anfodiyo.

Yahya, A.B. (1997) . *Jigon Nazarin Wa}ar Baka*, Kaduna:Fisbas Media Services.

Yahya, A.B. (2002). *Salo Asirin Wa}a*, Kaduna: Fisbas Media Services.

Yakasai, S.A. (2002). *Jagoran Ilimin Walwalar Harshe*, Sakkwato: Garkuwa Media Services Limited.

Yield, R. (1990). "Research on Status in Hausa Society" in Cole and Mack, *Hausa Women in the Twentieth Century*, Wisconsin: University of Wisconsin Press.

‘Yar’aduwa,T. M.(2007). *Wasan Kwaikwayo Na Hausa: Nau’o’insa da Sigoginsa,* Kano: Benchmark Publishers Limited.

Zara’u, I.W. (2002). *Kano da Masarautarta Jiya da Yau,* Zariya: Gaskiya Corporation Limited.

Zara’u, I.W. (2008). “Ya]uwar Hausawa da Al’adunsu Dangane da Aikin Hajji,” Cikin *Mujallar Algaita*, Vol. No.5, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Zarru}, R.M da Alhassan, H. (1976). *Kirarin Duniya 222,* Zariya: Ganuwa Publishers Limted.

Zarru}, R.M da Wasu (1987). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa* (11), Ibadan: University Press Limited.

**Rataye na [aya**

**1. Kirarin Zabiyar Kabbin Argungu (Magu]iya Fati Manukwai)**

**i) Na Sarki (Kanta)**

Bismillahi Rahamani Rahim
Woooh Sha]i,
Arnan Bagudu,
Sidi manzon sarakuna,
Iya wanda ya iya wani,
Zakin Sarakuna,
Zullufi-wullufi yawanyin alaihin,
Magume uban duniya Sarki,
Kakan duniya Sarki,
Sidi mai taimako da na Allah,
Rana da wata fataken Allah,
Mu kuma fatakenku,
Masu duniya ]an Mamman,
Yau na sallame ka jikan Abubakari,
Ba ka yi lami shi da]e sallamarka,
Wata bawan Allah mu kuma bayinka,
Babu mai kamancinka,
Yau a duniya kowa ya kwana lafiya,
Ya tashi lafiya ya kan yi mi}a,
Ya yi tasalima ya tambayi al}urani.
A kawo masa ya yi alwalla,
Ya mayar da gabansa gabas,
Ya ce ni wane na gode Allah,

Na godewa Muhammadu rasulillahi,
Yau duniyar ga ba ta raggo ta ba Kanta,
Haka lahira ba ta raggo ta ba Kanta,
Idan da duniya gida ta matabbaci,
Ka duba daga kasuwa in safiya ta yi,
Kasuwa cika za ta yi,
Idan rana ta yi kassuwa cika za ta yi,
Idan maraican nan ya yi,
Wani ya sayar,
Wani bai sayar ba,
Da ita da jin da]in nan nata,
Kowa gida za shi ko da jan masare,
Ko da zafi da garin damina gibiri –gibiri,
Ragasa tunku watarma son ya}i,
Gadaragam ba gadon kwanci ba ba gadon }ai}ai ba,
Shi ke tarar da }wan}wami,
Du}usuman  ingantaccen dutse,
Mai uwa kan kasari,
Mai uba ka sausawa ga ranar ya}i,
Ingarma an ka jinka,
An ka ba ku Kanta domin jiran ya}i,
Kowwag gane ka ya ga ya}i,
Wanda bai ganka ba bai ga mutawa ba,
Guguwa sha da gatari,
Zangon farin wata arewa Kanta.

**ii) Sarki Sama**

Na Abdu gatarin Ya}uba,
Na Bawa hankalinka gare ka,
Sama kowwag }i gaskiya ka }i shi,
Marin ]aka mai ban haushi,
Rugga na gani kana yadda ka so,
Yau ina laifin na Garba?
Gaba in ta yi tsumbare ka nome,
[a mai zucciya ka ramkon gayya,
Na Garba ka yi ramkon gayya,
Kada in }ara jin gari Kibiyare,
Mai da waiwaye na Muhamman,
Rugga ta sauka zamaninka,
Na Garba ka yi ramkon gayya,

Da}ile }ishali ]an Yakubu Nabame,
Yawan magana kan sa }arya,
Ai ko kurum magana ta,
Farshin wuta na Ya}ubu,
Na Garba }ona wanda ya take ka,
Gidan wani ya zama ksango,
Ka sare kaya na Muhamman,
Muna Binji kai ka tarar da sansani ]an Yakubu Nabame,
Abdu ]anyan kasko ko ruwa bai sha ba wurdi ya taka,
Abdu Madu ka kai baka mai soba ]an Atiku,
Ga zamaninka rugga ta }are,
Yau ga  wuya in suna ]urawa,
To su ]ura mu gani,
Damamisau na Yakubu ana ganinka an ka ]ora bu]akka,
Ana fa]in magajin [anmusa ina Sarki ya yi?
Hurde  mai idon ~ata na Muhamman,
Na Garba ba ka tsoron taro,
Adamawa ta iso,
Zinder ta iso,
Barno ta iso,
Kano ta iso ka kare,
[an Mera ba a kai maka ya}i,
Ka san dun}ula dubu a taru a karsu,
[an Alu ma}erin doki,
Na Garba ka fi }arfin rugga,
Ai Sama Sarkin nasara na,
Ashe bugun mari wargina,
Ai ga zamaninka ]an Ya}ubu Nabame,
Akurki muka wa bayu muna godiya,
Da arzikinka ]an Ya}ubu Nabame,
Dukiya ta isa kaya sun isa,
Ba zama Sarki ad da wuya ba,
Mu gan ka baya ga Toronkawa,
Gira ba ta maganinka ]an Ya}ubu Nabame,
Amma a aika da shi a sami lafiya,
Domin birni tamanin da goma sha biyar ya tu~e na Fulani,
Kabawa ku yi hankali Sama ba shi wargi,
Ba a yi masa wargi,
Gadan-gadan na Ya}ubu,
Sama ka girme gidan uba,

Dangi ku dangana,
{arya mun ci fansa jikan Sani
Mai fushi da kai ya wahala,
Sama Sarkin da Allah ya yi,
Kai aka tsoro na Garba,
Kai ka wa mutum ba shi yiwu wa,
Gulbin teku mai wuyar iyo ]an Bawa,
Sama budunbuduma,
Bagudu mun gode ma,
Ka yi }arko ka yi yawan rai,
Ka sha don ma}iya su ji kunya,
Hadari sa gabanka inda ka sammawa,
Katangar dutse daga gungura su kallo,
Ai Kanta gandun ayayana,
Na gaba birjim na baya birjim,
Kanta bar mai tugo,
Haza tafiyar jamadu,
Katsantsan rakumin da bai da akala,
Mai son mutuwa shi kama a}ala,
Jigon sarakuna ]an Muhammadu,
Uban Kabawa Kanta,
{ara shirin duniya uban Galadima Umaru,
Hana zahahe mai sa uban gari gudu shi bar birni nai,
Marin ]aka mai ban haushi,
Rugga  na gani kana wadda ka so,
Gabanka takuban fama bayanka masun daga,
Yamma gare ka `yan kibau sun daza kwai,
Ko da masu son taya fansa,
Kanta mai gidan Bame abiyar tarihi,
Gidan Nabame mai wuyar shigar Fulani,
Sadaukin Sarakuna na Zarmakwai mai danda,
Mulkinka ya wuce `yar boda,
Yau kai agga Muhammadu Kanta na farko,
Yau kai agga Dauda,
Yau kai agga Ibrahim ]an Muhammadu,
Yau kai agga Sulaiman ]an Dauda,
Yau kai agga Muhammadu ]an Kanta,
Yau kai agga Maliki ]an Ibrahim,
Yau kai agga Umaru Giwa,
Yau kai agga Muhammadu na Saifawa,

Yau kai agga Ahmadu,
Yau kai agga Tomo,
Yau kai agga Muhammadu [angiwa,
Yau kai agga Ismaila Tangandu,
Yau kai agga Muhammadu [antagalo,
Yau kai agga Abdullahi Toga,
Yau kai agga Abubakar Ukar,
Yau kai agga Muhammadu Hodi,
Yau kai agga Sama'ila Karari,
Yau kai agga Ya}ubu Nabame,
Yau kai agga Yusufu Mainasara,
Yau kai agga Muhammadu Ba'are,
Yau kai agga Sama na Ya}ubu,
Yau kai agga Dobe,
Yau kai agga Muhammadu Sama,
Yau kai agga Sani,
Yau kai agga Shehu,
Yau kai agga Mera,
Zaman yau duk ]aukakarsu da martabarsu na wajjenka,
Wadda duk gidan sarauta ya girma,
Bai da salsala da martaba da muhibba irin gidan Muhammadu Kanta,
Yau rinjaya da ]aukaka da martaba tana gidan Nabame,
Mai kai gaba rugga,
Sai ka yi shekara arba'in da arbaminya kana mulkin gidan Nabame.

**2. Kirarin Zabiyar Ha]eja (Hajara Alhassan)**
**(I a.) Na Sarki (Amir)**

Assalamu alaikum ban dawa bakka da nisa sai wuyar zuwa,
Kai ne Buhari kai ne Sambo,
Kai ne gagara gamo da Sarki Jatau,
Ubanmu uban Sarakuna,
Rana ba ki mu}ama,
Jeji ba a yi masa }yaure,
Ya gaji gadon Hari da Haru,
Ya mayar da gadon Sarki {adir,
Ban so ba}in cikin mai suri,
Suri ba}in cikin mai gona,
Inuwa gagara bunna,
Yaya gara takan yi da dutse sai kallo,
Sama ta yi wa yaro nisa,

Gamo da Sarki ya fi gamo da damina.

**(ii b.) Na Dangin Uba**

Kai ne Buhari kai ne Sambo,
Kai ne gagara gamo da Sarki Jatau,
Ubanmu uban Sarakuna,
Rana ba ki mu}ama,
Jeji ba a yi masa }yaure,
Ya gaji gadon Hari da Haru,
Ya mayar da gadon Sarki {adir,
Ya mayar da gadon Sarki Karamba,
Assalamu alaikum toron giwa sha – zamani.
Allah ya ji }an [an Iya Abdu,
Abdu bugun tama sha nishi,
Allah ya ji }an Ciroma Ali,
Allah Ya bar mana [an Iya tudu abun dafawa.

**(i c.) Na Dangin Uwa**

Salamu alaikum toron giwa sha – zamani,
Allah Ya ji }an Turaki Abubakar,
Allah Ya ji }an Hauwa'u,
Allah Ya ji }an Sa'adatu,
Allah Ya sa mutuwa hutu ce,
Abban Halima jikan Halima.

**(ii) Na Galadiman Ha]eja**

Salamu alaikum toron giwa lumfasa –fada,
Dubu a matserar kowa,
Kai ne na tutar fari,
Allah Ya ji }an Galadima Yusuhu,
Allah Ya ji }an Galadima Zakari,
Allah Ya ji }an Galadima Usman,
Allah Ya ji }an Galadima Habibu,
Allah Ya bar mana na yanzu shi ne Abdullahi.

**(iii) Na Magajin Garin Ha]eja**

Salamu alaikum ]an babban amale,
Ku ne Buhari ku ne Sambo,
Ku ne gagara gamo da Sarki Jatau,
Allah Ya ji }an Sarki Abubakar,

Allah ya ji }an Sarki Haruna,
Allah ya ji }an Sarki Abubakar,
Salamu alaikum ]an babban amale,
Haular mari matsa bayi,
Mari maganin gudajjen bawa,
Allah ya ji }an Ladi da gafara,
Magagin Gari na Ha]eja.

**(iv) Na Turakin Ha]eja**

Salamu alaikum Turaki Ammani,
[an na-gada wanda ya fi ]an na-koya,
Farin iri abin shukawa,
Ku ne Buhari ku ne Sambo,
Ku ne gagara gamo da Sarki Jatau,
Allah Ya ji }an Sarki Abubakar,
Allah Ya ji }an Sarki Haruna,
Allah Ya ji }an Sarki Usman.

**(v) Na Sarkin Arewan Ha]eja.**

Salamu alaikum }arfin giwa,
Ba ka shiga ba ka la~e ruwa,
[an na gada wanda ya fi ]an na koya, Sarkin Arewa Aliyu,
Allah Ya ji }an Abubakar Garba,
Allah Ya ji }an Sarkin Arewa Abubakar,
Allah Ya ji }an Sarkin Arewa Sulaiman,
Allah Ya ji }an Sarkin Arewa Idirisu,
Allah Ya ji }an Sarkin Arewa Usman da Kaka Gana,
[an na gada wanda ya fi ]an na koya,
Ginsau }arfin giwa,
Ba ka shiga ba ka la~e ruwa,
Irin magarya,
Allah Ya ji }an Baba Delu,
Allah Ya ji }an Iya mai itace.

**(vi) Na Ciroman Ha]eja**

Salamu alaikum Baba Ciroma,
[an babban amale,
Ku  ne Buhari ku ne Sambo,
Ku ne gagara gamo da Sarki Jatau,
Allah Ya ji }an Sarki Abubakar,

Allah Ya ji }an Sarki Haruna,
Allah Ya ji }an Sarki Usman,
Allah Ya ji }an Maina Babba da gafara,
[an na gada wanda ya fi ]an na koya,
Farin iri abin shukawa,
[an maciji wanda ya fi shuri da sawu,
[an ruwa daudun Ha]eja,
[an Sarki jikan Sarki Ciroma.

**(vii) Na [anburan Ha]eja**

Salamu alaikum [anburan Ha]eja,
[an na gada wanda ya fi ]an na koya,
Farin iri abin shukawa,
[anburan she}a ]an Abdullahi,
Ku ne Buhari ku ne Sambo,
Ku ne gagara gamo da Sarki Jatau,
Allah Ya ji }an Sarki Abubakar,
Allah Ya ji }an Sarki Usman,
Haular mabu]in Hausa,
Haular mabu]i Sulaimanu,
Haular mabu]i Materi,
Haular mabu]i Abubakar.

**(viii) Na [adarman Ha]eja.**

[an na gada wanda ya fi ]an na koya,
Farin iri abin shukawa,
{arin linzamin duniya [andarma,
Allah Ya ji }an Baba Ali da gafara,
Allah Ya bar mana Iya Amintudu abin dafawa.

**(ix) Na Tafidan Ha]eja.**

Salamu alaikum ]an na gada wanda ya fi ]an na koya,
Farin iri abin shukawa,
Ji }an Tafida Umaru,
Rumfa sha shirgi,
Kwano ba ba karaya,
[an na gada wanda na fi ]an na koya,
Farin iri abin shukawa,
Ji }an Tafida Umaru,
Ku ne Buhari ku ne Sambo,

Ku ne gagara gamo da Sarki Jatau,
Allah Ya ji }an Sarki Abubakar,
Allah Ya ji }an Sarki Haruna,
Allah Ya ji }an Sarki Usman.

**(x) Na Jarman Ha]eja.**

Salamu alaikum Jarma girman ba}o,
Ba}o babu sallama mugu ne,
Daga bayan gida yake,
Jarma magajin Jarma,
[an na gada wanda ya fi ]an na koya,
Farin iri abin shukawa,
Allah Ya bar mana Jarma na yanzu,
Kwano ba ka karaya.

**(xi) Na [an Ruwatau Ha]eja.**

Salamu alaikum ]an babban amale,
Ku ne Buhari ku ne Sambo,
Allah Ya ji }an Sarki Abubakar,
Allah Ya ji }an Sarki Haruna,
Allah Ya ji }an Sarki Usman,
Allah Ya ji }an Sarki Maina da gafara,
[an na gada wanda ya fi ]an na koya,
Farin iri abin shukawa [an Ruwatau Ha]eja.

**(xii) Na [an Iyan Ha]eja.**

Salamu alaikum [an Iyan Ha]eja,
Allah Ya ji }an [an Iya Abdu,
Abdu bugun tama sha nishi,
Allah Ya bar mana [an Iya-
tudu abun dafawa,
Allah Ya ji }an Iya Ashararudu.

**(xiii) Na Mubu]in Ha]eja.**

Salamu alaikum ]an na gada-
wanda ya fi ]an na koya,
Haular Mabu]i Sulaiman,
Haular Mabu]i Ibrahim,
Haular Mabu]i Muhamman,
[an na gada wanda ya fi ]an na koya,

Farin iri abin shukawa.

**(xiv) Na Mai Babban [aki (mahaifiyar Sarki)**

Salamu alaikum sallama girman ba}o,
Ba}o babu sallamu mugu ne,
Daga bayan gida yake,
Salamu alaikum Uwa `yar Abdu,
Allah Ya ji }an Ciroma Ali da gafara,
Allah Ya ji }an Iya Salma,
Allah Ya ji }an bar mana [an Iya-
na yanzu tudu abin dafawa.

**(xv) Na Uwargidan Sarki (Hajja Sa'adatu Yayale)**

Salamu alaikum `yar tomo lumfasa fada,
Uwargida sarautar mata,
Kwari tankarin gida,
Fari da]in tuwo,
Uwargida ta kafa gida,
Uwargida ta kafa gida ya zauna,
Dubu a matsarar kowa,
Yayale tutar fari,
Allah Ya ji }an Baba Malam Sambo da gafara,
Allah Ya sa mutuwa hutu ce.

**(xvi) Na Turakin Gida (Hajja)**

Salamu alaikum `yar babban amale,
Ku ne Buhari ku ne Sambo,
Irin Sarkin Arewa Sulaimanu,
Allah Ya ji }an Idirisu,
Allah Ya ji }an Sulaimanu,
Allah Ya ji }an Abubakar,
Allah Ya bar mana Maina Ginsau.

**(xvii) Na Amarya (Hajja Aisha)**

Salamu alaikum `yar na gada –
wanda ya fi ]an na koya,
Farin iri abin shukawa,
Allah Ya ji }an Ciroma Sambo da gafara,
Allah Ya ji }an [an Iya Abdu,

Abdu bugun tama sha nishi,
An kwana lafiya an tashi lafiya `yar Garba.

**(3) Fadar Daura**

**Kirarin Dakamar Sarkin Daura (Zabiyar Daura)**

**(i) Na Mai Martaba Sarkin Daura**

Jagora: Mararrafar madangari,
Madur}usar madangari,
‘Y/Amshi: Mararrafar madangari,
Madur}usar madangari,
Jagora: Hawan `yan Bawo,
`Y/Amshi: Hawan `yan Bawo,
Jagora: Kakan Anna,
‘Y/Amshi: Kakan Anna,
Jagora: Hazo na Muhamman,
‘Y/Amshi: Hazo na Muhamman,
Jagora: Makazaki,
‘Y/Amshi: Makazaki,
Jagora: Makadodo,
‘Y/Amshi: Makadodo,
Jagora: Kamunka nawa?
‘Y/Amshi: Kamunka nawa?
Jagora: Dosono,
‘Y/Amshi: Dosono,
Jagora: Har ya fi kyau,
‘Y/Amshi: Har ya fi kyau,
Jagora: Sannu ta fi kus,
‘Y/Amshi: Sannu ta fi kus,
Jagora: Inuwal dare,

| | |
|---|---|
| ‘Y/Amshi: | Inuwal dare, |
| Jagora: | Amale, |
| `Y/Amshi: | Amale, |
| Jagora: | Bagada jiya, |
| `Y/Amshi: | Bagada jiya, |
| Jagora: | Alhajin saraki, |
| `Y/Amshi: | Alhajin saraki, |
| Jagora: | Mun ji yau, |
| `Y/Amshi: | Mun ji yau, |
| Jagora: | Gaba gare ka Allah, |
| `Y/Amshi: | Gaba gare ka Allah, |
| Jagora: | Dama gare ka Allah, |
| `Y/Amshi: | Dama gare ka Allah, |
| Jagora: | Nasara dai, |
| `Y/Amshi: | Nasara dai, |
| Jagora: | Allah mai iyawa, |
| `Y/Amshi: | Allah mai yawa, |
| (hutawa) | |

**In suke kimammaye.**
In sha rago abokin jiro,
Rana ta yi hawargaba rana taka,
In suke kimammaye,
Innuwal dare saraki abokin jiro.

**(i) Na Magajin Garin Daura**
In gado rashin magada gado girman Allah,
Aminin makazaki da Korau,
Aminin makadodo da Korau,
In `yan maran maza da yawa,
[an mu je mu da anna,
In ]an sararin mutu ko dai ri}o.

**(ii) Na Magajiyar Garin Daura**
In `yar sararin mutu ko dai ri}o
Giwa shigayi buwayi
Maharba tu}an ta Mamman,
Sa ta Mamman,
In sa mai kayan da]i tsirga-tsirga kogi,
Saka rarrafa mararrafa Magajiyar hawa Korau ra}asa,

Gida zaman gida ga giwa garaya cinnaki,
Baje-baje toranke karnan tarda damisa,
Takan ta mammaye,
In sa ta mammaye,
In sa abuyar tsohon zaki.

**(iii) Na `ya`yan Sarki (mainawa/burema)**
In `yan maran maza da yawa,
`Yan mu je mu da anna,
In `yan sasarin mutu ko dai ri}o (idon biyu ne ko suna da yawa)

In ]an/ `yar maran maza da yawa,

[an /`yar mu je mu da anna,
In ]an/ `yar sasarin mutu ko dai ri}o.
**(idan saraki guda ne)**

**(iv) Matan Sarki (Matan fada)**
In zana tali giwa tali,
Zana abala koli,
In funce giye karya wu}a}e alfadarin masu ]akuna,
Yanka matar mai farar wu}a,
In }unar ruwa da zafi ga sugagi,
Ta Mamman giwa sagwarmaye,
In `yar maran maza da yawa,
`Yar mu je mu da anna,
In `yar sasarin mutu ko dai ri}o.

**(v) Na Bunturawan Daura (Hakimin Sandamu)**
In Bunturawan makazaki da Korau,
Bunturawan makadodo da Korau zaki,
In ]an maran maza da yawa,
[an mu je mu da anna,
In ]an sasarin mutu ko dai ri}o.

**(vi) Na Sarkin Fulanin Daura (Hakimin Rijiyar Tsamiya)**
In har Magajin Har]o aminin makazaki da Korau,
Aminin makadodo da Korau,
In ]an maran maza da yawa,

[an mu je mu da anna,
In ]an sasarin mutu ko dai ri}o.

**(vii) Na Markan Daura (Hakimin Zango)**

In bawa Magajin tale mammaye,
In da zaman homa ]an }arfaffa,
Sandar }arfe da zaki Marka,
In ]an maran maza da yawa,
[an mu je mu da anna,
In ]an sasarin mutu ko dai ri}o.

**(viii) Na Dur~in Daura**

[an }otar ma}era fure babba,
In ko sungumi babban ]an Korau,
In wanda mara kunya ke kunya,
Wanda mara tsoro ke tsoro.

**(ix) Na Galadiman Daura (Hakimin Mai'aduwa)**

Sungumi lada goma,
Shuka bugen wuya,
Ci da ma}iya,
Sha da ma}iya,
Kaf cizo,
Ka fi dawan ya}i,
Jereren saraki,
Tuba-tuba ra}umi dab da nishi,
In kana ji~a shassha~a tare da giwa,
In sungumi famarar ]akin burema na `yan tuna
Tangam burema.

**(x) [an Buran Daura (Hakimin Baure)**

In gado rashin magada gado girman Allah,
Aminin makazaki da Korau,
Aminin makadodo da Korau,
In ]an maran maza da yawa,
[an mu je mu da anna,
In ]an sasarin mutu ko dai ri}o.

**(xi) Na Barden Daura (Hakimin `Yardaje)**

In `yan maran maza da yawa Barden [aura,

In ]an maran maza da yawa,
[an mu je mu da anna,
In ]an sasarin mutu ko dai ri}o.

**(xii) Sarkin Ban Daura (Hakimin `Yanduna)**

In tausa giwa makomar talaka,
Korau na baba ashen a ba.
In ]an maran maza da yawa
In ]an sasarin mutu ko dai ri}o.

**(xiii) Na {auran Daura (Haminin Baure a da yanzu hakimin karaga)**

In fa]ega faskaran tama,
In sa kararrafi ]oran bazanciki,
Kaura mabu]in }ofar nasara,
In mabu]in Korau }aujen bawa,
In don kau da mai kyau da }ura,
In Magajin Audu Magajin tafi gwauron mashi,
In wa ka je sai ko ka zo,
Babban falke sai tabki,
{aura wanda ya haifi ya}i.

**(xiv) Na Sarkin Sudan/Sarkin Kudu**

[an ]akin Kangiwa mai tsotsai ka le}a,
Aminin makazaki da Korau,
Aminin makadodo da Korau,
In ]an maran maza da yawa,
Karan masana kogin malamai,
In ba }in gaskiya ma}aryata sa haye biri matsayin kishi,
Aminin makazaki da Korau,
Aminin makadodo da Korau,
In ]an maran maza da yawa,
[an mu je mu da anna,
In ]an sasarin mutu ko dai ri}o.

**(xv) Al}alin Garka / Malamai**

In Alfa matambayan sani karaf da masana kogin malamai,
In ba }in gaskiya ma}aryata sa haye kogin malamai,
Aminin makazaki da Korau,
Aminin makadodo da Korau.

**(xvi) Na Wamban Daura**

In ]an maran maza da yawa Wamban [aura,
In ]an sasarin mutu ko dai ri}o,
[an mu je mu da anna.

**(xvii) Na Mai Babban [aki (Mace)**

In `yar wutar ma}era fure babba,
In `yar maran maza da yawa,
`Yar mu je mu da anna,
In `yar sasarin mutu ko dai ri}o.

**(xviii) Na Sarakin Daura (mace)**

In juyar kambu ta Mamman rigar dodo,
Bada mashigi masgaya ya}i,
Masgaya nasara,
Magajiyar Fatimatin ta wabai,
Hazo ta kimammaye ]iyan `yan Mamman,
`Yar mu je mu da anna,
In `yar sasarin mutu ko dai ri}o.

**(xix) Na [angawan [aura**

In [angawar gari,
In `yar maran maza da yawa,
`Yar mu je mu da anna,
In `yar sasarin mutu ko dai ri}o.

**4. Kirarin Zabiyar Kano**

**Hajiya Ajuji Maitazargade**

Allah jiƙan mai Data da gafara,
Muhammadu Adananu ya riga mu,
Allah Shi gafarta mai fa,
Sannan da Alhaji Muntari,
Mijin Fulani mai gadon Masar Balkisu,
Ka biya ni na gode ma,

Ina Bashir ɗan masu gida?

Saboda Mai Babban Ɗaki yake ba ni riga,
Sai da gwanda ake kabewa,
Allah ya girmama shi a duniya,

Ina godiya ina ƙarawa na gode,
Goyon Fulaini Duduwa,
Na yi godiya na gode goyon Fulani Nafi,

Ya biya ni na gode mai fa,

Ina godiya ɗan Lamiɗo ka biya ni,
Kyauta ba biyan bashi ba,
Allah mai da ku birnin Kano gari,
Mun zo mun yi ziyara wacce ka taya ba naci,
Gaisuwa kuwa ba a yin muguwa,
Abin da nake mana fata ranar tashin kiyama,
Allah sa mu tashi a tutar maluma,
Abin da nake mana fata ranar tashin kiyama,
Mu tashi a tutar Annabi,

Ina godiya ina ƙarawa na gode,

Tsintsiya maɗaurinki ɗaya,
Kun biya ni na gode,

Ina godiya ina ƙarawa na gode,
Kuma na yi bege mai tada rayi,

Allah jiƙan Sarkin Ƙaraye Ibrahim,
Allah sa mutuwa hutawa,

Allah jiƙansa baban Hajiya Hadiza,
Na yi godiya na gode umh'
Allah sa mutuwa hutawa,
Ranar sunan Hadiza rannan riga da doki,
An biya ni ba bashi ba,

Allah jiƙan Alhaji Ibrahim na Amadu da Nura da Garba,

Sarki mai garin Ƙaraye,
Amanar Sarki autan Bawo,
Magajin Ila magajin Garba,

Ko yana gidan yallaɓai?
Mai zubau kure da kure,

Mijin Fulani mijin ʻYar Sidi,
Ko yana gida madalla?

Ina godiya ubangijin 'yar Joɗa,
Ubangijin Zainabu Abu ya biya ni,
Ubangijin su Lami da Dada ka biya ni,
Ubangijin A'i Gswadabo,
Ka biya ni na gode ma,
Sarki da Hakiman Kano na gode,
Autan Bawo mai Ila,
Ka biya ni na gode ma,

Ina godiya ina ƙarawa 'yan Fulani sun biya ni,
Kyauta ba biyan bashi ba,
Riguna da riguna na gode,

Turmi da turame,
Ba na dakan gumba ba.

Yadda muka zo lafiya babu ƙishin ruwa babu yunwa,

A gidan Alhaji Jakada na yi godiya babu ƙishirwa babu yunwa,
Har mu koma gida dai lafiya.
Allah sa ka ba ni yadi,
Da ma ka duba fanka ka ba ni,
In je in gyara gidan mai gidandan,
Da ma ka ba ni fanka Muhammadu,

Muhammadu ɗan Turuka jikan Turuka,
Sannan irin Ginsau wan Nuniya,
Irin Yusufa Nadabo ka biya ni,
Ka biya ni na gode ma,

Ina godiya ina ƙarawa na gode,
Yadda ka yi aiki lafiya Allah sa ka wanye lafiya,
Ko yau ka bar duniya Alhamdulillahi,
Mijin mai kitse taura da doki,
Jikan Umma Kaltume,
Na yi godiya na gode jikan Yaji,
Allah ja mana kwana mai yawa,
Godiya uwar Hadiza na gode uwar Yalwa cikin hairi,
Na yi godiya na gode,
Allah ja mana kwana mai yawa,
Ko yau ka bar duniya Alhamdulillahi,
Na kai shukura wurin Annabi.
Ina godiya da arzikin Abdu jikan Abdu,

Tun da na zo garin nan kun riƙe kayan amana,

Bayan mutuwar Abdullahi Dabo kun riƙe kayan amana,
Ta'ala Shi gafarta masa,

Ya matsa ya bar mu kun riƙe kayan amana,

Ba na ƙishin ruwa ba ni yunwa a cikin albarkacinsa,
Ta'ala Shi gafarta masa,

Ina godiya ina ƙarawa na gode,
Godiya ta tabbata ina godiya na gode,

Amma Allah ƙara sulalla mai yawa.

Ina godiya ina ƙarawa, na yi godiya 'yan Fulani kun biya ni,
Kun biya ni ba bashi ba,
Alhamdulillahi kyautar Allah ta yi,
Allah kiyaye mana Sarkin Kano Ado Bayero,
Allah ja masa kwana mai yawa,
Ka kama sulalla toron giwa na Abdu,
Mu ko mu je su ba mu riguna da zannuwa,

Allah sa ka wanye lafiya,
Allah kiyaye Sarkin Kano Alhaji Ado,
Kada a tsokane ka sai inda aka fafato,
Idan ba a ba mu saboda kai ba,
Don ka ce a je gida a huta boka,

Malamai su za su faɗan ma shawara,
Na yi godiya na gode ubangijin Kaftin Rilwanu,
Mai tawayen mata,
Balaraben A'ishatu Nafi'u,
Mijin Hajiya Yalwa mijin Hajiya 'Yar Aba,
Mijin Rakiya ka biya ni,
Ka biya ni ba bashi ba.
Allah raya man Abdu jikan Abdu,

Allah jiƙan mai Kanon Galadima.
Allah sa mutuwa hutawa,
Ni ce naican gida gida ni ko nawa gidan ba na zuwa?

Ina godiya ina ƙarawa ina ƙarawa na gode,

Alherin da kai musu ko suna gida yallaɓai?
Ko yau ka bar duniya Alhamdulillahi,
Na ce na gode Allah,
Na kai shukura wurin Annabi,
Manzallazina Jalla mai Makkan mai Madina,
Babu mai yi ban da Allah,
Waye mai yi Allah bai yi ba?
Wanda ya zo gare ka Allah Ya kai shukura gun Annabi,
Za mu wanye lafiya dai baba,

Ina godiya ina ƙarawa Abdu jikan Abdu,
Ina godiya Sarkin Kano Alhaji Ado,
Na gode da arzikinku,
Allah sa a wanye lafiya,
Na yi godiya na gode,
Sarki mai garin Birnin Kano.
Allah taimaki jikan Mai Suka da Mashi,
Jikan Alu Mai Kano.
Allah zaunar da Sarakuna dai Hajiya Saude,
Na ce mijinsu `yar'uwarki,
Allah ba da zaman lafiya.
Allah ji }an Abdu jikan Abdu,

Ƙasa mai ha}uri na Dabo,
Allah sa mutuwa hutawa,
A yi mana gudunmawa da idanu,

Ga 'yar mai yanka mutane,
Za mu kai ta gidan mai magana da mulki,

Ɗan Maje Nasarawa jikan Maje Nasarawa,
Jikan Mai Suka da Mashi,
Jikan Alu Mai Kano,
Ina godiya da arzikinsa mashashan Kano na Audu,
Rannan mun ga abin mamaki,
Ba mota ba da mota, mota tana ta tashi,
Mota sai ka ce gindin zama,
Birnin Kano babu ragi nasa,
Ga babur da mota wa yake zance da keke?
Ranar zuwan Hajiya Saude,
Rannan na ga abin da dama,
Albarkar mazarga dodo sai raga,

Muka ci karo da mai Babban Ɗakin Kano uwar gari tasa,
Sai ga sa}e da sa}e na Sakkwato,
Ga riguna da riguna,
Ga turmi da turme,
Ba a batun buta ba,
Allah ji }an Umma-Kaltume da gafara,
Allah ji }an Ungulu da gafara,
Allah ji }an Ibrahim da gafara,
Allah ji }an Alhajiya Tagudu,
Allah ji }an Shehu,
Allah sa mutuwa hutawa,
Ina godiya da A'isha Fenda,

Allah ne Ya ba ki mai Babban Ɗakin Kano,
Dole sai kin wuce kowa ya zo ya bi ki,

Ko sun ƙi bare sun yarda,
Ina godiya da arzikinta na yi godiya na gode,
Wanda Allah Ya bai wa dole ne a bi shi,
Kan ba a bi shi ba, ba a zance,
Ina godiya uwata Nana,
Godiya uwar Nafi da A'i sun biya ni,
Na yi godiya uwar Fulani Balki,

Na yi godiya uwar Fulani Karaye,

Uwar Fulani Ɗambatta,
Sun biya ni ba bashi,

Ina godiya da arzi}inki Mai Babban Ɗakin Kano,
Uwar gari tasa,
Ta zage Mariya,

Ta zage Mai Babban Ɗaki Hauwa,
Ta zage mai }aton Dakin Kano Hadiza,
Allah ja miki kwana mai yawa,
Ina nan zaune sai na ce mai dalili,
Da ma ka yi min dalili,
Dirhamin gidan Sarkin Kano,
Da dalili ya yi,
Na zo neman arziki Birnin Kano,
Na yi wata uku ina nemansa ban gan shi ba,
Sai na ce ba zan je gida ba sai na je gidan Kano,
In gano uwar Nadabo,
Uwar Marke Kabiru,
Ko tana gida 'yar Ladi?
Dalili ya kai ni gidan Sarkin Kano,
Yarinya mai mudun awo,
Zumuntar Magajiya Babba,
Ta kai ni na je na gai da uwar Nadabo,
Uwarsu mai dalili,
Sai na ce a kai ni na gaida Sarkin Kano,
Abdu jikan Abdu,

Ƙasa mai haƙuri na Dabo,
Ta'ala Shi gafarta masa,
Na je na gaida Sarkin Kano na Abdu,
Ya ce ina kuka samu zabiya Maigari?
Suka ce da dalili saboda yawo,
Yau dalili ya yi dalili sai ga ni cikin Birnin Kano,
Mai garin Kano ya yi kirki,
Sai ya duba gida da kyau ya ba ni,
Ga shi na yi zaman Birnin Kano,

Wannan shaƙuwar da ka yi,
Ba daga tsokana ba,
Sai na haye gidan Sarkin Kano,

Allah ji ƙan Abdu jikan Abdu,

Ƙasa mai haƙuri na Dabo,
Ina godiya da arzikinka Abdu jikan Abdu,

Ɗan'Maje Nasarawa,
Jikan Maje Nasarawa,

Ɗan Alu mai Kano.

Allah ji ƙan Mariya,

Allah ji ƙan Hauwa,
Allah sa mutuwa hutawa.

Allah ji ƙan Shekara,

Allah ji ƙan Hussaina da gafara,
Allah sa mutuwa hutawa.

Allah ji ƙan Muhamman,
Adam Maje Nasarawa,
Ta'ala Shi gafarta masa,

Ina godiya ina ƙarawa na gode,
Duka Birnin Kano gari,
Zuwa kasuwa ba riba ba ne,
Da ungulu ta more Sarkin Fawa,
Ina godiya gare su 'yan Farare,
Sun biya ni ba bashi ba.

**5. Fadar Zazzau**

**(A) Hajiya A'i Usman (Dogariyar Zazzau)**

i(a) **Na Sarki (Alhaji Shehu Idris zuwa majalisa)**
Barka da fita /fitowa jikan Sambo
Yadda ka fito lafiya, Allah Ya maishe ka lafiya,
Ladab }ofa,
Shiga da }arfin Allah,
[an Idirisa autan Sambo.

(b) **(Rakiya idan zai yi tafiya)**
Barka da fita fitowa jikan Sambo,
Yadda ka fito lafiya Allah Ya maishe ka lafiya,
Ladab }ofa,
Shiga da }arfin Allah,
Ka dawo lafiya ]an Idirisa autan Sambo.

(c) **(Maraba idan ya dawo daga majalisa ko tafiya)**

Barka da zuwa sadaukin Sarki,
Barka da zuwa adalin Sarki,
Barka da zuwa toya matsafa,
Barka da zuwa duddugen addini,
Shiga da }arfin Allah jikan Sambo,
Allah Ya fidda na kullum,
Allah Ya }ara maka lafiya,
Allah Ya }ara maka son Annabi ]an Idirisa.

ii. **Na Uwargida (Baba/ Hajiya Habiba)**
Ranki ya da]e kwarin gida tankarin gida,
Ja yawa fara,
Kowa da ya zo fara ne.

**iii. Ta Biyu (Dada Hajiya Fatsuma)**
Ranki ya da]e matar Sarki,
Allah Ya taimake ki,
Allah Ya }ara miki martaba.

vi. **Ta Uku (Yaya, Hajiya Binta**)
Ranki ya da]e Gimbiya,
Allah Ya }ara ]aukaka,
Allah Ya }ara maki martaba,
[iyar Sarki matar Sarki.

v**. Ta Hu]u (Goggo, Hajiya Mariya)**
Ranki ya da]e,
Allah Ya taimake ki,
[iyar Sarki matar Sarki,
Allah Ya taimake ki Goggo,
Allah Ya ba ki lafiya.

vi. **Na 'Ya'yan Sarki (Mata)**
Ranki ya da]e Gimbiya,
Allah Ya taimake ki Gimbiya,
Takawarki lafiya Gimbiya,
'Yar Sarki mai takalmin }arfe,
Kowa kika taka ya taku,
Allah Ya taimake ki Larabawan asali.

vii. **Na 'Ya'yan Sarki (Maza)**

Ranka ya da]e Yarima,
Allah Ya taimake ka,
[an Sarki mai takalmin }arfe,
Kowa ka taka ya taku,
Allah Ya taimake ka Larabawan asali.

viii. **Na 'Ya'yan Sarki (Maza da mata)**

Ranku ya da]e,
Allah ya taimake ku,
'Ya'yan Sarki masu takalmin }arfe,
Kowa kuka taka ya taku,
Allah Ya taimake ku Larabawan asali.

**(B) Rabi Bazamfara**

**Na Mai Martaba Sarki (zuwa majalisa)**

Fito da }arfin Allah ni}atau,
Fito da }arfin Allah toya matsafa,
Sarki uban Sarakuna,
Taka da }arfin Allah zaki,
Taka da }arfin Allah ni}atau,
[an Idirisa autan Sambo,
Zaki uban Sarakuna,
Sarki uban Sarakuna,
[an Aminatu baban Aminatu,
Zaki gyara }asa gyara duniya,
Zaki uban talakawa,
Baban Kabiru baban Sambo,
Baban Ali baban Umar.

**ii. Dawowa Gida Bayan Zaman Majalisa**

Shiga da }arfin Allah ni}atau,
Shigo da lafiya ]an Idrisa,
Shigo da lafiya ]an Idrisa jikan Sambo,
Idan babu Sambo kai ne Sambo,
Shigo da }arfin Allah taka lafiya ]an Idirisa ]an Abdul}adir ]an Zainaba,
Taka da }arfin Allah toya matsafa.

iii. **Na Matan Sarki (Gaba ]ayansu lokacin da suke zuwa gaishe da Sarki kafin ya fita majalisa)**

A shiga lafiya,
A taka cikin }arfin Allah,
A shiga da ikon Allah,
Idan babu Sarki tamkar ku Sarakuna ne.

**6. Fadar Kazaure**

**A. Zabiya Indo `Yar Sukola**

**(i) Kirarin Sarki Ibrahim (Wan Sarki Hussaini Adamu)**

Lafiya Alfanda,
Lafiya mai }arfi da }arfin Allah,
Mai iko da ikon Allah,
Lafiya Sarkin Musulunci, Sarkin adalci,
Sarkin Gari, Sarkin Noma,
]an Sarki Adamu,
Na Audu mai takalmin }arfe, kowa ka taka ya taku,
Suci ka baibayi kowa,
Ramar shuka ba ka mugunta,
Ka raba ka ba birni ka ba }auye,
Allah Ya taimaki Sarki,
Sarki ya taimaki jama'ar da ke bayansa,
Allah Ya }ara wa Sarki lafiya da imani,
Allah Ya }ara wa Sarki lafiya da adalci,
Sarki magajin Sarki,
Sarki magajin Sarki Ado.

**(ii) Kirarin Sarki Hussaini Adamu**

Lafiya Alfanda,
Lafiya mai }arfi da }arfin Allah,
Mai iko da ikon Allah,
Lafiya Sarkin Musulunci, Sarkin adalci,
Sarkin Gari, Sarkin Noma,
Ga ka Sarki ga ka malami,
Ga ka Bature ga ka Balarabe,
Allah Ya taya ka ri}on jama'a,
Allah ya taya ka ri}on jama'a
Da abun da zai cuce ka da abun da zai cuci jama'arka,
Da abun da zai cuci }asarka,
Ubangiji ya kiyaye shi da kiyayewarSa.

### (iii) Kirarin Sarki Muhammadu Najib Hussaini Adamu

Lafiya Alfanda,
Lafiya mai }arfi da }arfin Allah,
Mai iko da ikon Allah,
Lafiya Sarkin Musulunci, Sarkin adalci,
Sarkin Gari, Sarkin Noma,
Na Audu jikan Muhamman Jibir,
Na Audu mai takalmin }arfe, kowa ka taka ya taku,
Shuci ka baibayi kowa,
Ramar shuka ba ka mugunta,
Ka raba ka ba birni ka ba }auye,
Allah Ya taimaki Sarki,
Sarki ya taimaki jama'ar da ke bayansa,
Allah Ya }ara wa Sarki lafiya da imani,
Allah Ya }ara wa Sarki lafiya da adalci,
Sarki magajin Sarki,
Sarki magajin Sarki Ado,
Sarki magajin Sarki Ibrahim,
Sarki magajin Sarki Usaini Adamu,
Ga ka Sarki ga ka malama,
Ga ka Bature ga ka Balarabe,
Allah Ya taya ka ri}on jama'a,
Allah ya taya ka ri}on jama'a.
Da abun da zai cuce ka da abun da zai cuci jama'arka,
Da abun da zai cuci }asarka,
Ubangiji ya kiyaye shi da kiyayewarSa,
Dare marufa asiri,
Goshin jirgi ba ya tarbuwa,
Zaki ka saba da ka]an maza,
Lafiya alfanda, lafiya alfanda,

### (iv) Kirarin Wamban Kazaure (Hakiman Cikin Gari)

Taka lafiya ]an ja-gaban Sarakuna [an Alfanda,
[an hadarin }asa maganin mai kabido,
Wambai magajin Wambai Audu,
Allah ji }an Sarki Audu,
Allah ji }an Sarki Ibrahim,
Allah ji }an Sarki Usaini Adamu,
Allah sa ka gama lafiya,

Allah ji }an Hajiya Ade.

**(v) Kirarin Yarima**

Yarima magajin Yarima,
Yarima Muhamman makana ruwan da]i,
Makana ruwan da]i,
Kowa na Allah ne amma Muhamman ya fi shi,
Mamman magajin Mamman,
Yarima magajin Yarima,
Makana ruwan da]i,
Kowa na Allah ne amma Muhamman ya fi shi,
Allah ji }an Yarima Tsahiro,
Allah ji }an Yarima Shehu,
Allah ji }an Yarima Audu,
Allah ji }an Yarima Muhamman Sulaimanu.

**(**vi) **Kirarin Marafa (Hakimin Rorai)**

Takawa lafiya Marafan Kazaure,
Ba da kaya jibga kaya,
Kowa ya je gidanka godiya ya je,
Allah ji }an Dambo da Maya}i,
Allah ji }an Muhamman Tura,
Allah ji }an Ummarun Dambo,
Allah ji }an Shehu da Shehu,
Allah ji }an Madawakin Kazaure,
Allah ji }an Mamuda da Mudi,
Allah ji }an Zakari ba da kaya,
Allah ji }an Fatsima,
Allah ji }an Hajiya Fatsima.

(vii) **Ciroma Kazaure**

Allah Ya ji }an rai Ummaru Ciroman Kazaure,
[an Yarima Tsahiro,
[an Yarima Shehu,
[an Yarima Audu,
[an Yarima Muhamman,
[an Yarima Sulaimanu,
Allah ji }an Sarki Ado,
Allah ji }an Hajiya Amu,

Yadda suka gama lafiya,
Allah Ya sa mu gama lafiya da imani,
Amin don son Annabi.

**viii. Sarkin Shanun Kazaure**

Salamu Alaikum Sarkin Shanun Kazaure,
Alhaji Abdulkarim Adamu,
Allah sa ka gama lafiya da imani,
Mu ma mu gama lafiya da imani,

Allah Ya taya ka aikin Sarki da ka amsa,

Allah ji }an Sarkin Tasha Ado

Allah ji }an Habubakar,

Allah ji }an Alhaji Amadu,

Allah ji }an Isuhu Hauni,
Allah ji }an Safiya Delu,
Allah ji }an Je-Kara]e Mu'azu,
Allah ji }an Je-Kara]e Muhamman Bello,
Allah ji]an Je-Kara]e Audul'azizu,
Allah ji }an Je-Kara]e Muhamman na yanzu,
Allah Ya sa ka gama lafiya,
Don mun gada, mun gode Allah,
Allah Ya sa ka gama lafiya.

**(ix) Turakin Kazaure**

Ni ce Hajiya Indo 'Yar Sukola Kazaure,
Zabiyar Sarkin Kazaure Adamu,
Zabiyar Sarkin Kazaure Ibrahim Adamu,
Zabiyar Sarkin Kazaure Usman Adamu,
Zabiyar Sarkin Kazaure Husaini Adamu,
Zabiyar Sarkin Kazaure Muhammadu Najib,
Salamu alaikum Turaki,
[an gagarabadan Sarakuna,
[an alfanda,
[an hadarin }asa maganin mai kabido,
Allah ji }an Sarki Ado,
Allah ji }an Hajiya Fatsuma,
Allah ji }an Al}ali Habubakar,
Allah ji }an Hajiya Jisu,

Allah ji }an Waziri Har]o,
Allah ji }an Hajiya Habi 'Yar Burji,
Allah ji }an Hajiya ta-bara,
Allah ji }an Hajiya ta-bana,
Allah ji }an Hajiya Habbi.

**(x) Mai Gamon Kazaure**

Salamu alaikum,
Ni ce Hajiya Indo 'Yar Sukola Kazaure,
Ni ce Zabiyar Sarkin Kazaure Adamu,
Ni ce Zabiyar Sarkin Kazaure Ibrahim Adamu,
Ni ce Zabiyar Sarkin Kazaure Husaini Adamu,
Ni ce Zabiyar Sarkin Kazaure Muhamman Najib,
Barka da yini, barka da hutawa Alhaji Audu Mai gamo,
Allah ji }an Muhamman,
Allah ji }an Hadiza,
Allah ji }an Mai Unguwa Aliko Muhamman,
[an Sarki Muhammad Najib,
Allah sa kana nan lafiya lau,
Allah sa ka gaji Sarki Muhamman Najib,
Allah sa ka gaji Sarki Usaini,
Allah sa ka gaji Sarki Ibrahim,
Allah sa ka gaji Sarki Adamu
Allah sa kana nan lafiya lau [an Sulaimanu ]an Sarki Muhamman Najib,
Goyon Muhamman Bashar,
Goyon Hajiya Rabi,
Goyon Hajiya Fatsuma,
Goyon Hajiya Amina,
Goyon Hajiya Hasana,
Allah sa kana nan }alau,
Allah sa ka gaji gadon sarauta yadda aka iske a gidanku,
Allah sa kai ma ka yi.

**(xi) Baraden Kazaure**

Ni ce Hajiya Indo 'Yar Sukola,
Zabiyar Sarki Adamu,
Zabiyar Sarki Usaini Adamu,
Zabiyar Sarki Muhammad Najib Sarkin Kazaure,
Barka da zama Baraden Kazaure,
Barka da hutawa Baraden Kazaure,

Allah ji }an Galadima Audu,
Allah ji }an Assatu,
Allah ji }an Hasana,
Allah ji }an Usaina,
Allah ji }an Hajiya Sahu,
Allah ji }an Sarki Ibrahim,
Allah ji }an Sarki Usaini Adamu,
Allah ji }an Ciroma Ummaru,
Allah ji }an Wambai Audu,
Allah ja da ran Wambai Sunusi,
Allah ji }an Assatu,
Allah ji }an Halima,
Allah ji }an Jarmai Ummaru [ankura,
Allah ji }an Jarmai }arami,
Allah ji }an Amina Dakumi,
Aallah ji }an Yalwa.

**(xii) Wamban Kazaure**
Assalamu alaikum,
[an gagara badan Sarakuna,
[an alfanda ]an hadarin }asa maganin mai kabido,
Wambai magajin Wambai Sunusi,
Allah Ya sa ka gama lafiya da imani da son Annabi a zucci,
Allah Ya ji }an Wambai Audu,
Allah Ya ji }an [an Iyan Kazaure x2
Allah Ya ji }an Sarki Ibrahim x 2
Allah Ya ji }an Alhaji Audu Kazaure,
Allah Ya ji }an [an Isa babba,
Allah Ya ji }an [an Isa {arami,
Allah Ya ji }an Hajiya Ade,
Allah Ya ji }an Audul}adiri,
Allah ja da ran Audurrahman,
Allah ja da ran Hajiya Atti Matar Magatakarda Wakilin Gona Amadu,
[an gidan Al}ali Bakatsine.

**(xiii) Na Sarkin Kazaure (Najib Hussaini wanda aka ]auka zuwa na biyu)**

Salammu alaikum
Ni ce Zabiyar Sarkin Kazaure Muhamman Najib Usaini,
[an gagarabadan Sarakuna,
Lafiya alfanda,

Lafiya ]an gagarabadan Sarakuna,
Lafiya alfanda ]an hadarin }asa maganin mai kabido,
Lafiya alfanda,
Barka da kwana barka da tashi,
Barka da yini barka da tashi,
Ka kwana lafiya ka tashi lafiya ka yini lafiya,
Godiyar Allah ta yi,
Sarki magajin Sarki,
Sarki magajin Sarki Ado,
Sarki magajin Sarki Ibrahim,
Sarki magajin Sarki Usaini Adamu,
Ga ka Sarki ga ka malam,
Ga ka Bature ga ka Balarabe,
Allah Ya taya ka ri}on jama'a x2
Da abin da zai cuce ka da abin da zai cuci }asarka,
Da abin da zai cuci jama'arka,
Ubangiji Ya kiyaye shi da kiyayewarSa,
Dare marufar asiri,
Goshin jirgi ba ka tarbuwa,
Zaki ka saba da ka]ar maza,
Allah Ya taimaki Sarki,
Allah ji }an Sarki Ado,
Allah ji }an Sarki Ibrahim,
Allah ji }an Sarki Usaini Adamu x2
Allah ji }an Assatu,
Allah ja da ran Hajiya Hadiza,
Allah ji }an Hajiya A'isha,
Allah ji }an Hajiya Gambo,
Allah ji }an Hajiya Kilishi,
Allah ja da ran Hajiya Hauwa,
Allah ja da ran Alhaji Hassan,
Allah ja da ran Hajiya Hadiza,
Allah ji }an Hajiya A'isha,
Allah Ya taimaki Sarki,
Sarki ya taimaki jama'ar da ke bayansa,
Lafiya alfanda,
Lafiya mai }arfi da }arfin Allah,
Mai iko da ikon Allah,
Lafiya Sarkin Musulunci Sarkin adalci,
Sarkin Noma na Audu jikan Muhammadu,

Lafiya angon Hajiya Umma.

**(xiv) Matar Sarki Najib Hussaini (Hajiya Umma)**

Barka da yini barka da hutawa Hajiya Umma,
Barka da yini matar gagarabadan Sarakuna matar alfanda,
Allah ji }an Hajiya Asama'u,
Allah ji }an Alhaji Mukhtar,
Allah ji }an Limamin Kano x 2
Allah amfana zuri'a,
Abin da kike mana Ubangiji Ya saka miki,
Allah sa ki iske lahirarki fari tas kamar nan.

**7. Fadar Kazaure**

**B. Zabiya {arangiya**

**(i) Kirarin Sarkin Kazaure (Najib Hussaini)**
**Bismillahir Rahamanir Rahim**

Ni ce Zabayar Mai Martaba Najib ]an Husaini,
Ma so zama da shi ya bi doka a Kazaure,
Allah Ya ji }an Sarki Husaini,
Allah Ya ji }an Sarki Ibrahim,
Ubangiji Ya ji }an Sarki Adamu toshiya mafarar dawa,
Ubangijinmu Allahu Ya ja da ran Sarki,
Magajin Sarki Alhamdulillahi,
Allah ja da ran Falakin Kazaure na farko,
Ubangiji Ya saka da alheri,
Allah ja da ran Dallatu,
[an Ummaru Alhamdulillahi,
Allah ji }an Sarki Ibrahim da Husaini,
Ubangiji Ya ji }an Maitama uban Falaki,
Sakallahu hairan Allah Ya saka da alheri,
Ubangiji Ya ji }an Falakin Kazaure na yanzu,
Allah Ya ja da ran shi,
Allah ja da ran ]an Armu na Sulaimanu,
Alhamdulilahi Allah saka da alheri,
Mai Martaba Sarki Najib ]an Hussaini,
Ma so zama da shi ya bi doka,
Sarki magajin Sarki alhamdulillahi,
Rabon rago da madalla tun ran da tararin ta yaye shi,

Kazaure namijin gari,
Garin Najib ]an Hussani,
Alhamdulillahi Allah saka da alheri,
Ubangiji ya }ara }auna da rufin asirin Allah,
Sakallahu hairan ta fi }arfin rago,
Ubangiji Allah ya saka da Alheri,
Allah sa kai ma ka ci gaba,
Ka nemi Zabiyar Sarki Najib,
Ni {arangiya nike, maganin abu Allah,
Komai ya yi zafi Ubangiji Yana maganinsa komin dare,
Allah saka da alheri.

**(ii) Kirarin Umma (Matar Sarki Najib Hussaini)**

Ya yi daidai Umma,
Zabiyarki tana gaida ki,
Matar Sarki Najib ]an Hussaini ikon Allah,
Allah ya ji }an Adamu,
Allah saka da alheri matar Sarki,
{arangiya na gaida ki,
Sannunki da dawowa da hanya,
Sannunki da sabka,
Ba don kina ciwo ba,
Don darajar Mai Martaba [an Usaini,
Ma so zama da shi ya bi doka,
’Yar Sarki jikar Sarki ’yar malamai alhamdulillahi,
Ni ce {arangiya ina gaishe ki da sassafen nan safiyar Talata.

**(iii) Dan Babban Sarki Najib Hussaini (Muhammadu)**

Ke nan alhamdulillahi,
Allah sa ka zamo Sarkin gobe Muhammadu,
Madallah na Umma ikon Allah,
Allah Ka }ara mana martaba da nisan kwana,
Da imani da sanin Allah a zucci,
Ka taimaki talakawanka,
Talakawanka na gaida kai,
Alhamdulillahi Allah saka da alheri,
Komai ya yi na Abti-Ibti alhamdulillahi,
{arangiya na gaida kai da sassafe,
Ka gaida min Sarki {arami,

Najib ke nan Magajin Najib.

Rataye na Biyu (mutanen da aka gana da su).

**Katsina**

i. Malam Aliyu Ahmad {ofar Soro, ]an shekara 40, a {ofar Soro Katsina, ranar 21/08/2013.
ii. [anmorin Katsina, Alhaji Abubakar Ibrahim, ]an shekara 54, a {ofar Soro Katsina, ranar 21/08/2013.
iii. Maka]an Katsina, Alhaji Darda'u Lawal, ]an shekara 44, a {ofar Soro Katsina, ranar 21/08/2013.
iv. Farfesa Aliyu Muhammad Bunza, ]an shekara 52, a ofishinsa da ke Jami'ar Umaru Musa 'Yar'adua, Katsina.

**Ha]eja**

i. Wazirin Ha]eja, Alhaji Kashim Amar, ]an shekara 71, a gidansa da ke {ofar Fadar Ha]eja, ranar 18-19/01/2014.
ii. Baba Jummai,'yar shekara 48, a gidan Wazirn Ha]eja, ranar 19/01/2014.
iii. Sakataren Masarautar Ha]eja, Alhaji Maina Kawu, ]an shekara 50, a Fadar Ha]eja, ranar 18-19/01/2014.
iv. Zabiyar Ha]eja, Malama Hajara Alhassan,'yar kimanin shekara 61, a Fadar Ha]eja, ranar 18-19/01/2014.
v. Mai Babban [akin Ha]eja, 'yar kimanin shekara 70, a ]akinta da ke Fadar Ha]eja, ranar 19/01/2014.
vi. {oramar Sarkin Ha]eja, Hajiya Maryam Abubakar, 'yar shekara 50, a Fadar Ha]eja, ranar 19/01/2014.
vii. Malam Ibrahim Muhammad, a {ofar Fadar Ha]eja, ]an shekara 30, ranar 19/01/2014.

**Kano**

**i.** Farfesa Aliyu Muhammad Gusau, ]an shekara 60 a gidansa da ke Rimin Gata, Kano, ranar 30/10/2012.

**ii.** Malam Nasir Khalid Wada, ]an shekara 40, a Gidan Dabino, Sabon Titi, Kano, ranakun 13-14/01/2014 da 03/02/2014.

**iii.** Sallaman Kano, Alhaji aminu Dako, ]an shekara 50, a ofishinsa da ke Fadar Kano, ranar 03/02/2014.

**iv.** Jakadiyya Adama, ‘yar kimanin shekara 54, a ]akinta da ke Fadar Kano, ranar 03/02/2014.

**v.** Malama Fa’i’za Nasir Khalid Wada, ‘yar shekara 30, a gidanta da ke Sabon Titi, Kano, ranar 14/01/2014.

**vi.** Nanin [an]ago, Hajiya Khadija Abdullahi Bayero, kimanin’yar shekara 70, a ]akinta da ke Masarautar Kano.

**vii.** Nanin Daura, Hajiya Zara’u Abdullahi Bayero,’yar kimanin shekara 68, a Masarautar Kano, ranar 14/01/2014.

**viii.** Ya Hajja (sa]akar Sarki Ado Bayero), ‘yar kimanin shekara 50, a Masarautar Kano.

**ix.** Jakadiyyar Kano A’isha,’yar kimanin shekara 52, a Masarautar Kno, ranar 14/01/2014.

**x.** Hajiya Zara’u Ibrahim Waya, ‘yar shekara 40, a gidanta da ke Rijiyar Zaki, ranar 13/01/2014.

**Daura**

i. Marigayi Wakilin Tarihi, Alhaji Mamman Siya Abubakar, ]an kimanin shekara 68, a ofishinsa da ke Masarautar Daura, ranakun 09-10/09/2012.

ii. Dakamar Sarkin Daura, Hajiya Zulai, ‘yar kimanin shekara 80, a Masarautar Daura ranakun 09-10/09/2012, a Masarautar Daura, da

kuma ranakun 10-11/08/2013, a gidanta da ke Unguwar Mangwaron Kamaye,Shagon Kamasho, Daura.

iii. Dakama Laure,'yar shekara 60, a Masarautar Daura, ranar10/09/2012.

iv. Dakama Amina ‘yar shekara 55, a Masarautar Daura, ranar 10/09/2012.

v. Dakama Nafisa, ‘yar shekara 35, a Masarautar Daura, ranar 10/09/2012.

vi. Dakama Hasiya, ‘yar shekara 40, a Masarautar Daura, ranar 10/09/2012.

vii. Magajiya {arama, Hajiya Zariya Sarki Abdulrahaman Musa, ‘yar shekara 65, a gidanta da ke Kangiwa, ranar 22 -23/07/2013.

viii. Sarkin Labarai, Alhaji Ibrahim Yaro, ]an shekara 62, a gidansa da ke Fegi, ranar 22/07/2013.

ix. Sarkin Zagi, Alhaji Nalado, ]an kimanin shekara 76, a Masarautar Daura, ranar 22/07/2013.

x. [an Daushe, ]an kimanin shekara 60, a Masarautar Daura, ranar 22/07/2013.

xi. Sarkin Ba}i, Alhaji Hamza {ane, ]an shekara 65, a Masarautar Daura, ranar 22/07/2013.

xii. Magajiya Babba, Hajiya Halima Sarki Muhammadu Bashar,'yar shekara 58, a gidan Magajin Gari Sa'idu, ranar 23/07/2013.

xiii. Sarkin Sudan, Alhaji Nalado Yusuf, ]an shekara 65, a gidansa da ke Sabon Fegi Daura, ranar 23/07/2013.

xiv. Wakilin Tarihi, Alhaji Lawal Sa'idu, ]an shekara 54, a Fadar Daura, ranar 15/12/2014.

**Mai'aduwa**

**i.** Baba, Hajiya Rabi'atu Muhammad, ‘yar kimanin shekara 70, a gidanta da ke {ofar Fada, Mai'aduwa, ranar 16/08/2013.

**ii.** Alhaji Abdullahi Fathi Muhammad, ]an shekara 48, a gidan Hajiya Rabi'atu, ranar 16/08/2013.

**Kazaure**

**i.** Malam Rabi’u Bashir, ]an shekara 30, a gidansa da ke Lokon Rijiya, ranar 25/08/2013.

**ii.** Zabiya ‘Yarsukola, ‘yar kimanin shekara 63, a Unguwar Galadanchi, ranar 25/08/2013.

**iii.** Zabiya {arangiya, ‘yar shekara 58, a Unguwar Mahauta, ranar 25/08/2013.

**Kabin Argungu**

i. Wakila Kanta, Alhaji Yakubu Bagaye, ]an shekara 52, a Fadar Kabin Argungu, ranar 18-19/12/2014.

ii. Magajin [anmusa, ]an shekara 50, a Fadar Kabin Argungu, ranar 19/12/2014.

iii. Malam Yusuf Bello, ]an shekara 25, a Fadar Kabin Argungu, ranar 19/12/2014.

iv. Hajiya Zulaihatu Aliyu Mera, ‘yar shekara 60, a Fadar Kabin Argungu, ranar 19/12/2014.

v. Hajiya ‘Yar So (matar marigayi Sarki Muhammadu Mera), ‘yar shekara 70, a Fadar Kabin Argungu, ranar 19/12/2014.

vi. Hajiya ‘Yar Tudu (matar marigayi Sarki Muhammadu Mera), a Fadar Kabin Argungu, ranar 19/12/2014.

**Zariya/ Zazzau**

**i.** Hajiya Hashiya Ibrahim, ‘yar shekara 30, a Fadar Zazzau, ranar 29/01/2014.

**ii.** Hajiya Hajjaju, ‘yar shekara 48, a Fadar Zazzau, anar 29/12/2012.

**iii.** Jakadiyyar Zazzau, Hajiya Hauwa, ‘yar shekara 58, a Fadar Zazzau, ranar 29/12/2014.

**iv.** Dogariyar Zazzau, Hajiya A’i, ‘yar shekara 66, a Fadar Zazzau, ranar 29/12/2014.

**v.** Hajiya Rabi Bazamfara, ‘yar shekara 68, a Fadar Zazzau, ranar 29/12/2014.

**Jumhuriyar Nijar**

A Jumhuriyar Nijar an gana da Dr Garba Ibrahim a ofishinsa da ke Jami’ar Abdulmumini, a Niamey, ranar 08/05/2011. An kuma gana da Malam Muhammadu Ado a kusa da babbar kasuwar Maradi, ranar 30/09/2014.